🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: Fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:-Gureenjo6763

*Hey readers am here again with another story, hope yhu will like it. Banyi muku alkawarin samu kullum ba sbd yanayin lectures d'ina but zanyi iya kokari don ganin na faranta muku, and I will be considering votes and comments ko da na gaji In har naga comments d'inku ze iya kara min karfin gwiwan yin muku wani page d'in ku biyoni*

'Yar mutan Adamawa

Page➡️1️⃣▶️2️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Tsugune take a gefen babban kogin da ake kira kogin sarki wanki takeyi a natse tana 'yar wakanta da fillanci kyakyawa ce sossai irin sossai d'innan duk da yadda talauci da babu ya nuna sossai a jikinta hakan be hana kyaunta fitowa ba, sanye take da doguwar rigan material me flowers kanana kanana yellow da baki rigan daga gani zaka san ya dade sbd kodewar da yayi har ya fara fari ta d'aura brown silky hijab d'an daidai da baze wuce gwiwarta ba duk da wanki takeyi hakan be sa ta cire hijabin ba sbd maza dake kai kawo da wasu dake wanka daga bakin gabar kogin gefe da gefenta mata ne manya da kanana wasu na wanki wasu na wanke wanke kaman daga sama taji ance "Adda khairi, Adda khairi" d'aga dara daran fararen sol din idonta tayi ta zubawa yaron dake ihun sunanta wadda baze wuce 5years ba, da gudu ya gangaro bakin ga'bar daga kan tudu yace "Adda khairi Dada d'o nyaune(dada na kira)" a hankali ta bud'e pink well carved and attractive lips d'inta tace "Nabeel ko wad'i an kam a nanata hala?(me yasa kai kam baka jin magana) mi had'ai ma nyaunugo inde am dayinga na?(ban hana ka kiran sunana daga nesa ba?)" tura cute lips dinshi yayi gaba fuskanshi futu futu da kura da alamu wasa yakeyi aka kirashi aka aikeshi kayan jikinshi kod'add'iyar shadda ce blue color irin yadi marasa tsadan nan a cikin masu saukin kud'inma na karshe duk zarenshi ya fiffito a yanayi shagwa'ba yace "wad'u munyal Adda manga(yi hakuri Adda babba)" murmushi tayi hakoranta da suke da d'an girma farare tas suka bayyana tace "daad'i na da kai kenan oya

jod'u renu kare d'o ha mi yaha mi wara bo mi viyai a lota(zauna ka kula da kayan nan bari inje In zo kuma bance ka wanke ba) kai ya gyad'a mata ita kuma ta mike, ban san lokacin da na furta 'fa tabarakallahu ahsanul khalikeen' duk da yarinyar da naji an kira khairin ba zata wuce shekaru 17 ba amma Allah ya mata halitta manyan ido gareta farare tas, hancinta me tsawo d'an daidai ba har chan ba bakinta d'an karami ne sossai amma tana da manyan fararen hakora ba irin manya masu munin nan ba a jere suke a kuma had'e gashin giranta a kwance kaman anyi carving Fara ce tas kamanninsu d'aya da Indian actress nan "Drashti dhami, wacce tayi madhubala ta kuma yi geet series" zaka iya cewa 'yan biyu ne abunda zata nunawa khairi to hutu ne yayinda khairi zata nuna mata hips don Allah ya bata bajajjen hips sossai,
a natse ta fara takawa tana haurawa tudu har ta haura ta d'auki hanyar gidansu da tafiya kad'an ne daga bakin kogin sarki, tana cikin tafiya kanta a kasa taji an bangajeta da sauri ta d'ago a kuma zafafe don bata barin ko ta kwana had'a ido sukayi da Hauwa yarinyar da tunda suka taso bata san me ta tare mata ba ita da mahaifiyarta suka d'auki karan tsana suka d'auramusu da family d'inta dukda makwafta ne na sossai har hauwan ta wuce khairi tasa hannu ta fisgo hannunta tare da dawo da ita baya tace "ke hauwa baki ji kin buge ni bane?" Da yake hauwan ba fulani bace wasu kabila ne daga cikin kabilun taraba state, seda hauwan ta dankara mata harara tukun tace "an buge d'in kiyi abunda zakiyi" har khairi ta bud'i baki zatayi magana taji ance "ummul sweetheart wani me kararren kwanan ne ya ta'ba min ke In yi kasa kasa dashi yanzu nan" yana magana ne cikin gadara da murya da ya nuna tsananin dabancinshi baki ne dogo sossai kakkarfa daga shi se shorts da bakar vest jikinshi ko ta Ina yanka ne ga wani tsar'be'biyar tsirarar Adda a hannunshi, shi a dole son unnulkhairi yakeyi tunda ta taso yake kula da ita ba wani shegen da ze ta'bata be rama mata ba se su dada da Abbanta duk da haka ummulkhairi bata ta'ba kula shi ba sbd nasihar Dada da Abba a gareta akan wannan rikakken d'an daban Idi shed'an da ya gagari kowa ciki harda iyayenshi gabad'aya unguwan tsoronshi suke, harara ta zabga mishi dashi da hauwan tukun tayi karamin tsaki tare da ci gaba da tafiya gida d'aya, biyu, uku na hud'un ta shige wadda shine nasu runfar su idi shaid'an da 'yan kungiyanshi na 'yan shila na kafe daga gaban gidansu suna facing juna tsiririyar hanya ne irin na cikin unguwa ya raba tsakaninsu wai yayi hakan ne duk don ya ringa bawa gimbiyartashi kula, madaidaicin gida ne zagaye yake da zana cikinshi shimfid'e da yashi me kyau daga gefe kusa da langalangar kofarsu d'akin bukka ne guda d'aya O kenan, se ginin block me d'akuna biyu daga Chan d'ayan bangaren ba plaster balle penti a jiki zallan blocks dinne se kofa da window na katako d'aya na dada da Abba d'ayan na Ummulkhairi da Nabeelah twin sister din yaron da aka aika kiranta yayinda O d'in ya kasance na Nabeel da twin brother d'in ummulkhairi wato Abulkhairi daga gefen d'akunan block d'in madaidaicin kitchen d'insu da akayi gininshi da jar kasa yake gaba da kitchen din sossai bayi ne da akayishi da langa langa wato zing amma daga gani tsoffi ne don duk jikinsu tsatsa ne duk da gidan talakawa ne amma seda tsabtar su yabani mamaki gidan kal kal dashi ko leda baza ka gani a kasa ba da sallama ummulkhairi ta shigo daga Chan d'akin Abba dada ta amsa tana fitowa da 'yar sandan ta tana cewa "se jotta dadaa am?(se yanzu mama na?)" Khairi tace "Eh dada mi dari be hauwa un ha lawol(na tsaya da hauwa ne a hanya)" dada tace "yau kuma khairiyya ban hanaki biye mata ba? Sam ba halin musulunci bane kiyi kokari ki ringa danne fushinki In ta tsokane ki Dan Allah" da lallami Dada tayiwa khairi magana sbd abu d'aya da ita shine ba'a mata fad'a don Allah ya jarabceta da iska wato aljannu a duk sadda ka d'aga mata murya In basu tashi ba toh tabbas zata kwana biyu a

kwance tsabar ciwon kai gwara ka daketa toh baza su tashi ba, baki ta zunburo dukda dadan tasu bata gani tace "ni shikenan In ta tsokane ni bazan amsa ta ba? Allah Dada kin cika sanyi da hakuri" murmushi dadan tayi tana seta inda take jin muryan khairi ta fitowa tayi mata dakuwa tana cewa "ungo naki, Abbanku ya kira akan cefene yace almajirin da ya saba turowa be zo ba ko za'a tura Abul, Abul kuma tunda ya fita da safe be dawo ba shine nace ko zaki ki kar'bo mana?" Cikin ladabi khairi tace "toh Dada bari In chanza kayan nan inzo inje" murmushi dadan tayi tana nufar inda suke ajiye taburma kaman ba makauniya ba da yake ta san kan komai na gidan shekara 18 a cikin gida d'aya ba wasa ba dole ta gane duk wani corner na gidan bayan ta shimfid'a taburma ta zauna daga wurin windownsu khairi bata jima da zama ba khairi ta fito sanye da black hijab kayan de sune bata chanza ba se takalmi da ta d'auko na roba ta saka tana cewa "hato nabeelah bo(Ina nabeela kuma)" Dada tace "o d'ani ha sudu am(tayi bacci a d'akina)" khairi ta dafe kai tana cewa "ooh jotta mo doftatam? Wlh mi yid'a dillugo min tan(ooh yanzu wa ze rakani? Wlh ban son tafiya ni kad'ai)" Dada tace "toh tefu sulaimi le to o wala wad'a ko d'ume se o dofta ma(toh ki nemi sulaimi mana in bata komai se ta raka ki) tana d'an bubbuga kafa ta fice seda taje bakin kofa tukun tace "seto mi warti(se na dawo)" bata jira amsan dada ba ta fice gidan dake gefensu daga hannun damanta ta shige gidansu khairi yafi gidan rufin asiri sossai akan gidan da ta shiga don daga yanayin gidan ma kad'ai zaka tantance "salamu alaikum" wata yarinya da take tsaran khairince ta amsa da "wa'alaikissalam Aminiya sannu da shigowa" murmushi khairi tayi tana duban ummusulaimi tace "yauwa Aminiya Ina ummi" sulaimi tace "ummi taje barka Chan unguwan baraya nima yanzu nake shirin shiga gidanku ki rakani kasuwa" "laaa ai nima shigowa nayi ki rakani kasuwan fad'uwa yazo daidai da zama kenan" inji fad'an khairii "to taso muje yamma nayi amma inason gangarawa bakin kogi na had'awa nabeel kayan wankin da na fara ya dawo da su se mu wuce" sulaimi na sa hijabi ta amsa suka fice ba lefi sulaimin ma kyakyawar bafulatana ce dukda ko kwatan kyaun khairi batayi ba kawaye ne tare suka tashi dukda su khairi sun riga zuwa anguwan amma su sulaimi na zuwa kyakyawar alaka ta shiga tsakaninsu iyayensu suka zama aminai haka yaran ma sulaimi ita kad'ai suka haifa sa'ar khairi da Abul ce, bayan sunje bakin kogi khairi ta had'awa nabeel kayan ya wuce su kuma suka d'auki hanyar da ze kaisu har kasuwa ta lunguna lunguna seda sukayi nisa da tafiya suna 'yar hiransu duk da khairi bata fiya surutu ba sulaimi ce tace "wai nikam me kikama hauwa ne? D'azu naji tana ta zage zage tana kiran sunanki dasu dada" dafe kirji khairi tayi tana cewa "ni 'yar umaru? Ban mata komai ba nikam, hasali ma itace ta neme ni fad'a d'azu na tafi na barsu da idi shed'an" sulaimi tace "hmm to idi shed'an kam ya mata dukan mutuwa" dayake gidansu sulaimi da hauwa a manne yake duk abunda akeyi a cikin na d'aya zakaji inhar aka d'aga murya zaro ido khairi tayi tace "innalillahi wainna ilaihi rajiun na shiga uku"................

#vote
#share

#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️3️⃣▶️4️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

"Thulaimi(sulaimi) ba dukan hauwan da akayi nake tsoro ba thasoba (sbd) ko nima kusa nake da Chatha(chasa) ta thulaimi fad'an Abba ne ban shirya mishi ba Wlh kin than(san) ba son tashin hankali yake ba na tabbatar kuma se Maman hauwa ta kawo kara" khairi tayiwa sulaimi maganan cikin sanyin murya ganin yadda sulaimin ke dariyar rud'ewantan daga farko shiru kawai sulaimin tayi don bata san me zata ce ba hakan yasa khairi ma tayi shiru da bakinta har suka isa kasuwa ta gate d'in baya suka shiga hakan yasa sukayi saurin isa layin 'yan kayan miya daga nesa take hangan malam umaru wato mahaifinsu da suke kira Abba zaune a gaban kayan miyanshi da ba wani yawan kirki ne da su ba, har suka karasa kusa be lura dasu ba seda khairi tace "Salamu alaikum Abba" juyowa yayi yana sakar mata murmushi yace "wa'alaikissalam na'am 'yar Abba kun karasu kenan?" Har kasa suka duka suka gaisheshi tare da mishi sannu da kasuwa d'an ledan dake ganganshi ya d'auka ya mikawa khairi hannu biyu ta

sa ta kar'ba tana mishi godiya sallama suka mishi shi kuma yayi musu Allah tsare suka wuce seda suka sayi sakon sulaimi tukun suka juya gida..

Suna isa khairi ta hura murhu ta d'aura musu abincin daren tanayi suna hira da Dada har Abul ya dawo kusan lokaci d'aya suka shigo da Abba khairi ta kawo musu ruwa suna had'a baki da Dada wajen musu sannu da dawowa, abinda na fahimta shine akwai tsantsar kauna da shakuwa a cikin wannan gida suna tattali da kula da juna ba kad'an ba, dab magrib khairi ta gama girki ta fito daga kitchen din tana sharce gumi don duk tayi zufa sbd hayaki sannu sukayi mata Abul da take kira d'an uwa har da mata dariya bata kula shi ba ta d'ibi ruwa ta shige bayi tare da watsawa sauri sauri tana fitowa ana kiran magrib, ta samu ma Abul ya nemo nabeel duk sunyi alwala zasu fice massallaci itama alwalar ta d'aura tare da shigewa d'akinsu ta tada sallah tana idarwa ta fito ta d'auko katuwar taburmansu da ta ji jiki ta shimfid'a a tsakar gidan tare da shiga d'akin Dada ta tada nabeela tana fitowa ta kunna wani fitila me haske da ake makalawa a sama yana anfani da manyan batir a kan taburman ta ajiye tare da kara komawa d'akin Dada ta kwaso qur'anai dasu hadith, zadulmuslim, riyadussaliheen, Arrijalu wannisa'u fil jannah da dai sauransu ta ajiye akan taburman a daidai lokacin su Abba suka shigo akan taburman suka yada zango har nabeela da yanzu ta idar da sallah irin tasu ta yara karatu suka fara Abba ke koya musu dukkansu Dada ya fara yiwa tukun ummulkhairi da Abulkhairi su kuma suka karawa nabeel da nabeela suna gama hadith da sauran littatafan suka bud'e qur'ani me tsarki kowa ya fara inda yake so Dada na zaune tanayi da kai basu suka rufe alqur'anin ba se da sukaji ana kwala kiran sallahn isha adu'a Abul ya musu suka shafa mazan suka nufi massalaci yayin da matan suka yi a kan taburman suna idarwa Khairi ta shiga kitchen ta fiffito musu da abinci da plates, ruwan sha har dana wanke hannu ta Ajiye, su Abba na shigowa suka nufi taburman a natse suka zazzauna tare da wanke hannu suka fara cin abinci wadda ya kasance tuwon masara da aka d'aure da garin alabo se miyan kuka da akayishi da kifi banda, mazan su uku kwanonsu daban haka matan su uku nasu daban gidan Shiru kaman ba mutane har suka gama suka wanke hannu nabeela ta taya khairi tattare kwanukan zuwa kitchen, wai kafin su fito gidan ya kaure da hira nabeel se zubawa Abba surutu yakeyi yayinda Abul ke magana da Dada su khairi ma jona su sukayi yayinda Abul ke tsokanan khairi tana ta shagwa'ba Abba na kar'ba mata (kai readers gaskiya rayuwan gidannan ya burgeni) tsintar muryan Abul nayi yana cewa "In ba tsoro ba er uwa kice Asiya" Da karfi tace "Athiya" dariya suka face dashi kasancewar bata da "sa" duk yadda tayi sede ya fita a "tha" (ba lallaine duk maganan da khairi tayi in rubutashi da 'th' ba, sbd ba kowa ne ze fahimta ba kuma bazan iya dinga rubutawa sau biyu ba)..

Tura baki gaba khairi tayi tana bubbuga kafa tace "Abbana ba ka ganshi ba" wani dariyan suka sa Abba kam murmushi yayi yana cewa "Zo nan 'yar Abba kyaleshi zan rama miki ne" gwalo ta mishi tare da komawa kusa da Abba tana d'aura kanta kan kafanshi, Baammm suka ji an buga kofan gidan a tare suka maida hankali kan kofan lokaci d'aya khairi ta lumshe ido zuciyarta na bugawa alamun mutanenta suna kusa, hauwa ce da mamanta suka shigo a masifance har kan tsakiyar taburman da suke Maman na zuba masifa kaman zata ari baki "matsiyata en iska, en gudun hijira ko kuma ince korarru wai ku har kun isa? Nace kun isa? Kusa d'an isakan saurayin d'anku yima 'yata duka?" Shiru Abba yayi yana kallon khairiyya har ga Allah shi ba mutum ne

me son tashin hankali ba haka matarshi be san inda ummul ta d'auko zafin zuciya ba a sanyaye yace "ummulkhairi bata hakuri, Dan Allah Maman hauwa kiyi hakuri hakan baze sake faruwa ba" Abba ya furta Kan ya rufe baki Maman hauwa ta kar'be "baza'ayi ba, baza ayi hakurin ba Wlh se na rama mata ko akan wannan makauniyar nakasashiyar matan nan taka ko kuma kan gantalalliyar 'yarkan....." Abul yayi saurin cewa "dakata Malama ya za'ayi kizo har cikin gidanmu kina zagar mana iyaye toh ya isheki shiru shiru fah ba tsoro bane, wall......." Dada ce tace "Abulkhairi" Da kausasshen murya shiru yayi yana cije le'be duk da ya kasance marar fad'a ga hakuri amma In an kaishi makura shima ba baya ba wurin masifa, wani irin gud'a Maman hauwa ta sauke tana girgiza jiki tace "Ayyyirrriirii yaro man kaza kai baka kai inyi da kai ba haka uwarka sede inyi da uban ka" Abba yayi saurin cewa "dakata dakata talatu shiru shiru fah ba tsoro bane Wlh gudun magana ne ki kiyayi randa zaki kaini bango" be karasa ba ta sa hannu ta bankad'a shi zuwa jikin gini tace "an kaika umaru nace an kaika me zakayi" shiru gidan yayi na mintuna kan naji wani bala'e'en kara da ya sa hanjin cikina motsawa kaman kiftawar ido naga khairi dake kwance a taburma ta lumshe ido da farko kaman bata san abunda ke faruwa ba, ta isa gaban maman hauwa hannun da ta sa ta hankad'e Abba hannun khairi ta rike tare da kafe Maman hauwan da idanunta da suka koma ja tana mata wani irin deadly look wani irin ihu Maman hauwa tayi na azaba tana kiran hannunta hannunta, khairi ta kara murd'awa tana danne hakwaranta da gudu Abul da Abba sukayi kan khairi suna kokarin cire hannun khairi amma ko motsa hannun sun kasa hauwa ma ta karaso da d'ingishi tana ture khairi wani wawan mari me kurmantarwa khairi ta sakewa hauwa da hannun hagunta inda ta ci gaba da murd'a hannun uwar da na damanta, zuwa lokacin duk makwabta na kusa sun shigo mazan suka taru suna kokarin cire hannun Maman hauwa a cikin na khairi amma abun ya ci tura da sauri Abba ya nufi kitchen ya d'auki cup tare da kanfatan ruwa a randar kasarsu wasu adu'o'i yayi da sauri da sauri ya tofa tare da zuwa ya watsawa khairi a fuska wani irin ihu ta sake tare da sulalewa kasa ta sume nan kukan Maman hauwa ya cika gidan ita da 'yarta tana ta fad'in "ta karyani shikenan ta nakastani kaman uwarta" nace(Lallai matan nan wato bakin nan be mutu ba) wasu daga cikin waenda suka shigo ne suka fice da ita, yayinda gidan ya saura daga su Abba se sulaimi da iyayenta, wasu adu'o'in Abba ya karatofawa a same ruwa tare da watsawa khairi a hankali ta motsa tana dafe kanta da take jin kaman ze rabe sheshekar kukan mahaifiyanta da kannenta yasa ta fashe da kuka itama dukda bata san me y faru ba amma tasan abun beyi kyauba, sulaimi ce ta kamata zuwa kan taburma inda Abul ya kama hannun Dada ya zaunar da ita yana share mata hawaye Abba kuma na lallashin su nabeel, seda iyayen sulaimi suka ga gidan ya d'an natsu tukun suka saka 'yarsu a gaba suka fice suna adu'ar Allah ya kiyaye gaba, sossai khairi tayi kuka inda take ta maganganu tana neman yafiyar iyayenta musamman dada da ta sa kuka anan ne take fad'an "wlh Abba ban mata komai ba haka ban saka idi shed'an bugunta ba Wlh banda masaniyar hakan ze faru da data bangajeni ban tanka mata ba da shiru nayi kaichona...." Abba ne ya katse ta "kul uwar alkhairi yi shiru abinki ba laifinki tun kafin a haifeku take nuna mana wannan hali, ta musgunawa mahaifiyarku ba kad'an ba" Abul yace "Abbanmu me kuka mata?" Shiru Abba yayi kaman baze yi magana ba kuma se yace "talatu tazo ta same mu a unguwan nan da farko a mutunce muka kar'beta duk da bamu san inda ta fito ba hakan be hana mu bata kulawa ba ganin babban ciki a jikinta kuma tana halin neman taimako ni nayiwa Bala dillali magana ya bata gidan da taken nan haya da yake da d'an kud'inta ta zo shawarana ta tambaya na sana'an da zatayi inda na bata shawaran yin abincin sayarwa a bakin kasuwa

wadda har yanzu shine sana'anta bayan kwana biyu da ta d'an natsu se ta tareni da wani magana wai In ta haihu na yarda na aureta tunda matata makauniya ce, sam na nuna mata bana sonta ta nemi wani namijin tun Ina mata yadda zata fahimta taki har taja na fara wulakantata ana haka ta haifi 'yarta mace har nan ta zo ta roki mamanku wai inje In ma 'yarta hud'uba da sunan da yamin mamanku bata damu ba kasancewar bata san abunda ya faru tsakanina da ita ba, ta tursasani naje nama hauwa hud'uba da suna hauwa, bayan haihuwan hauwa ta ci gaba da bina ni kuma naci gaba da wulakantata har ya kai na kai karanta fadan sarki inda ya ce ta fita harkana don ta matsamin har kasuwa take bina daga lokacinfa ta d'auki tsana ta daura mana da mahaifiyarku ko motsin kirki bamu da daman yi shine har ya gangaro kanku, kun ji fah"..........

#vote
#comment
#share

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Written & story by: fateemah Muhammad Gurin

'Yar mutan Adamawa

Page➡️5️⃣▶️6️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Tsaye yake gaban balcony d'inshi idonshi na kan rana da yake shirin fad'uwa a lokaci d'aya hannunshi rike da karan sigari (taba) yana busawa kare mishi kallo na tsaya yi kai gaskiya gayen had'add'e ne sossai akallah zeyi 34 sanye yake da dark blue jeans da wani yellow riga me kaman sweater da gashi gashi a jikinshi long sleeve me had'e da hula igiyan hulan sun sauko gefe da gefe har kan faffad'an kirjinshi, kyakyawar kafanshi fari tas  me d'aukan hankali sanye da yellow normal flat shoe na maza na companin Gucci, a natse na kai idona kan fuskanshi Ina kare mishi kallo, yana da round face me d'an fad'i tare da kananan ido da ya had'u da tsiriryar hancinshi zuwa kan lips dinshi masu fad'i kad'an red ko kuma ince maroon kasancewar shi me shan taba lips dinshi yayi baki kad'an se ya had'u da red lips dinshi ya bada wani color me d'aukan hankali, abinda yafi d'auke hankalin mata kai harda wasu mazan a fuskanshi shine kwantaccen bakin sajenshi da ya mugun kawata fuskanshi gashin kanshi kaman wadda akayi coiling tsaban yauki da murdewa wadda ya zo har kan goshinshi kai masha Allah, duk da idonshi fad'uwar rana yake kallo amma tunaninshi ba nan yake ba yayi zurfi cikin tunanin bakar rayuwanshi na baya me cike da duhu da tsananin kalubale tabbas his father is the villain  of his story a take madaidaitan idanunshi da ake referring as kanana sbd kankancesu da yake yi suka koma red a fili ya furta "A bad egg" meaning worthless person, kara zukan taban da ya rike da hannun hagu yayi cikin kwarewa har seda karan ya kare jefarwa yayi a kasa yana shirin kunna wani kenan wayanshi dake cikin pocket dinshi ya fara ringing, kaman baze fiddo ba yana yatsuna fuska ya fiddo yana kallon fuskan screen din wayan nashi da ya kasance Samsung galaxy latest one d'in, 'My little' ya gani karamin murmushi da bai gama maye fuskanshi ba yayi tare da d'auka ya kara a kunnenshi cikin murya irinta yara yaji tana cewa "Afternoon paaapi" yace "Afternoon sweetheart how are yhu?" Daga d'ayan bangaren tace "I'm Fyn paapi, paapi I mistakenly broke my laptop" yace "Ohk baby uncle murtala will fix it for yhu, where is my momma?" He guess tana juya manyan idonta masu kama da balls da ta d'auko daga mahaifiyarta, sunan kawai da ya kira na 'mahaifiyarta' da yayi guessing a zuciyarshi yasa yaji ranshi yayi matukar 'baci d'an fara'an da yake kan fuskanshi duk ya 'bace a sama sama yaji tana cewa "she's at her sitting room lemme take the phone to her" a kasalance yace "no baby I will call her later, bye take care" ya kashe wayan yana sauke nannauyar ajiyar zuciya juyawa yayi zuwa cikin bedroom dinshi anan ya cire kaya daga shi se boxers, cikin tafiya ta cikakkun maza da suka sha gwagwarmayan rayuwa ya nufi bayi tare da tara ruwa a jacuzzi ya shige ciki tare da lumshe ido yana tuna bakin azabar da ya sha a rayuwanshi......

**

Safa da marwa kawai take tana tunanin hukuncin da zata d'auka akan malam umar sanda da familynshi idonta ta maida kan hannunta da yau kwana biyu kenan da aka gyara gurdewan wrist din amma maimakon ya sa'be se kara kumbura yake yi, kaman yadda suka sa ta wahala se ta d'an d'ana musu bakar azaba rayuwa tabbas akanta zasu san kaidin mace da ake cewa ko

shed'an tsoronshi yake  murmushin mugunta tayi da ta tuna abunda ya rabo ta da garinsu wani d'an banzan munafurci ta had'a har yakai aka yi rashe rashen rai Allah ya taimake ta tana da ciki da an Kone ta manyan sukace a barta albarkacin cikin jikinta taje amma kar ta sake shigowa cikin garin ko da bakin wasa shinefa ta shigo cikin garin jalingo, wani murmushin tayi tace a fili "zaka San ka sa mahaukaciyar 'yarka gurd'ani, bazan bari na warke ba a yau zan aikata abunda na kudurta akanka, se kayi zaman gidan kaso na shekaru kan ka fito kuma iyalanka sun tagayyara" wayanta ta fidda ta kira wasu 'yan iskan 'yan tasha tace su sameta da dare akwai haaja..

Tsaye take a jikin ginin kitchen d'insu ta jingina kanta da jikin gini gabad'aya jikinta a sanyaye da fad'uwar gaba da take fama dashi tunda garin Allah ya waye, Abba dake zaune kan taburma kusa da Dada ne ya kalleta, da yake yau ya dawo da wuri tun 4 ya shigo gidan suna ta shan hira abinsu Abul na zaune gefensu kan turmi yayinda nabeel da nabeela ke wasa a tsakar gidan duk rabin wasan fad'a ne, Abba na shirin magana kenan nabeel ya kwasa da gudu zuwa kanta yana Jan hannunta yace "Adda khairi Ina ni kika ce In na iya karatu zaki ba biyar In saya sweet?" Nabeela ma tazo da gudu ta taho ta rike d'ayan hannun tana cewa "A'a Adda khairi Ina ni kikace zaki bawa? Ai kince nafishi iya karatu koh" da Lafiya klau ne zatayi murmushi tace 'eh duk wadda ya iya karatu shi zan siyama sweet banda me kan kifi' Ai kuwa se su hau musu da bitar karatunsu duk da take musu, Amma yau se ta daga musu tsawa "dallah ku kyaleni haba!!!" A tsorace suka matsa suna kallonta Abul yace "er uwa??" Da tsantsan mamaki a muryanshi don ko mutanenta suna kusa ne tana fama da ciwon kai da bugun zuciya lalla'basu takeyi su kyaleta ba tsawa haka ba yayinda mutanentan karan kansu suke tsananin son kannen nasu, kuka ta fashe dashi harda shesheka se duk sukayi shiru suka zuba mata ido Abba da kanshi ya tashi yaje ya kamo hannunta ya karaso da ita kan taburman seda ta zauna tukun ya zauna yana zama ta fad'a jikinshi ta kuma fashewa da wani kukan da yafi na da, Dada tace "Eyyah bongel am me ke damunki ne haka? Tunda garin Allah ya waye na lura bakya cikin natsuwa da farin ciki sam me aka miki?" Cikin kuka tace "Dada nima ba za'bina bane d'aga muku hankali Wlh ban san me ke damuna ba ga gabana dake ta fad'uwa" Abba yace "In shaa Allahu alkhairi ne ki dinga maimaita la ilaha illalahu wahdahu la sharika lahu lahulmulku wa lahul hamdu yuhyi wa yumitu wa huwa ala kulli shai'in qadeer, zaki ji sauki In shaa Allah" Kai ta ringa gyad'awa tana ci gaba da shesheka Abul yayi shiru ya zuba mata ido, suna zaune shiru shiru duk jikinsu a mace har aka kira magrib suka mike kowa yayi alwala ya gabatar da sallah sukayi duk activities d'insu da suka saba bayan sunci abinci Abba ya mike yace "bari inje In zo" duk suka had'a baki wurin cewa "A dawo lafiya Abbanmu" yana fita Maman hauwa dake tsaye ta daka tsalle har da fame ciwonta amma bata damu ba dama da suka fito sallahn magrib ta aiki wani yaro ya kai mishi papper da ya kunshi rubutun sarki na son ganinshi bayan isha don shine limamin babban massallacin sarki dake cikin unguwan sarki unguwansu kenan na nan cikin jalingo, tana ta Allah Allah kar ya lura ba stamp na sarki Ai kuwa be luran ba ya fito don zuwa, ta had'a baki da wani dogari da yake cikin masu gadin gate akan idan yazo yace sarki ya ce ya zauna ya jirashi zuwa In ta kirashi se ya kuma cewa, sarki ya ce yayi hakuri ze sake nemanshi. Maman hauwa na shiga gida ta samu kujera ta zauna tana kallon samarin nan su biyu tace "kuje kuyi aikinku, ki tabbatar yayi kaman fyad'e aka mata" Kai suka gyad'a suka shige d'akinta suka hau kan 'yarta na cikinta tsabar bakar zuciya da hassada ne ko me zan kira wannan tana ji tana gani wasu

suka hau kan 'yarta duk don bakantawa wasu bayin Allahn da ko mummunan zato basa d'aurawa a kanta, dama chan 'yarta bata da budurci sbd business takeyi da ita sossai amma yau ta ce wa samarin nan su mata kaca kaca se tayi kaman fyad'e aka mata...

Malam Umar sanda ganin ya dad'e sarki be aiko ayi kiranshi ba yasa ya mike ya sake samun wannan dogarin ya tambayeshi hakuri dogarin ya bashi akan sarki abubuwa sun had'u mishi ze neme shi, godiya mal umar yayi tare da ficewa shapp ya manta hanky d'inshi da ya shimfid'a ya zauna akan dakalin kofan sarkin yayi gaba abunshi, nan dogarin da suka had'a baki ya kirata ya fad'a mata Ai kuwa tayi murna tace ya kawo mata dama ta samu takalminshi sawu d'aya zata had'a.. yana shiga gida ya samu har yara sunyi bacci seda suka ga shiganshi tukun ummulkhairi ta d'auki nabeela yayinda Abulkhairi ya d'auki nabeel sukayiwa juna se da safe suka shige d'akunansu don dare yayi.....

Washegari - wadda sukayiwa lakabi da bakar rana.

Bayan sun dawo sallahn asuba Abba ya shiga wanka yayinda Abul ya d'auki tsintsiya ya fara share musu tsakar gidan inda Khairi na kitchen tana shirin abun breakfast d'insu, bayan Abba ya fito ya shige d'aki don shiryawa zuwa kasuwa wani irin banko kofa akayi da yasa khairi fitowa da gudu Abul ma da yanzu shiganshi bayi don yin wanka ya fito da sauri Abba ma da sauri yasa riga ya fito dogarawa ne da polisawa a tare inda suna ganin Abba suka kamashi police d'aya ya rige kugunshi d'aya kuma ya kama hannunshi ya sa mishi handcuff cikin rawan murya khairi tace "bayin Allah lafiya me yayi muku?" Ta karasa tana kallon Abba da yayi mutuwan tsaye hawaye na zuba a idonta kaman panpo wani daga cikin dogarayen ne yace "kana nan kaman mutumin Allah limamin massallaci dakai da aikata aika aika irin haka, munafukin Allah ai Allah ba Azzalumin bawanshi bane kaima Kana da 'ya buduruwa" Abul yace "me yayi na wannan cin fuska haka?" Abba dake ta kallon Dada da tafito tana dogara sanda har bugewa take tsaban rud'ewa, a matukar firgice ya juyo jin wani dogari yace "fyad'e yayiwa 'yar mutane" a tare sukace "me??????"😳

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story & Written by: fateemah Muhammad Gurin

'Yar mutan Adamawa

Page➡️7️⃣▶️8️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

A kullum mahaifiya itace jigo a kan ko wani hali d'a ze shiga tana tsayama d'a akan ko wani kaddara ze fuskanceshi tabbas ya yarda da kalman nan na 'behind every successful man their must be a woman' in ba don mahaifiyarshi ba be ta'ba tunani ko zato ze zo inda yake yanzu ba, ta tsaya tsayin daka akanshi da rayuwanshi, ya ginu ne bisa kalaman nan guda uku "hakuri, kaddara, jarabawa" ya ga jarabawa iya jarabawa amma da ya kasance me hakuri da yarda da kaddara se hakan ya zame mishi nasara a rayuwa..

Maganan momma ne ya dake shi da kalaman da ba sabo bane a gareshi ya saba jinsu kullum In har yana tare da ita ko ze yi waya da ita "babu hutu da kwanciyar hankali ga bawa a wannan rayuwa ta duniya sai yayi imani da kaddarar Allah, wato ya sakankance cewa duk abinda Allah ya qaddara mai aukuwa ne kuma abinda be so faruwansa ba to haqiqa ba zai faru ba, Allah ya rantse cewa hakuri Alheri ne ga masu yinsa a inda yake cewa 'kuma Lallai idan kukayi hakuri toh babu shakkah shine mafi alheri ga masu hakuri' Musharraf ka sani masu haquri ne kawai ake cikawa ladar su ba da lissafi ba, toh kai me yasa bazakayi haquri ka rungumi kaddaranka da jarabawar da Allah ya saukar maka a rayuwa ba? Shekaru Akallah 4 ba wasa bane sam kaki bari komai ya wuce a rayuwanka? Ya ci ace yanzu ka manta da duk wani rayuwan mu na baya, ka samu mace ta gari ka aura itace zata zama fitila me haske rayuwanka da ta jima cikin duhu, Ina maka adu'a a kullum randa na gaji kuwa sede kaji an d'aura maka aure na gaji da wannan

halin naka" karyewa muryanta yayi alamun kuka na shirin kubce mata, idonshi dake runtse ya bud'e sunyi ja kaman an zuba mishi yaji yana jin tsananin ciwo da zafi a zuciyarshi cikin sanyin murya yace "kiyi hakuri momma" karamin murmushi tayi daga 'bangarenta tace "nayi Musharraf" ajiyar zuciya ya sauke shi de bayan mahaifiyarshi da 'yan uwanshi da suke ciki d'aya se 'yarshi ba macen ko namijin da ze kara yarda dashi a duniyannan kuma har yanzu ta'bon zuciyarshi d'anye ne sam be shirya wani aure yanzu ba ko nan gaba sbd ya gama sarewa da al'amarin mata, "Allah ya maka albarka ya za'ba maka mata ta gari" a sanyaye yace "Ameen Ina su Miemie?" Tace "sun shiga school Amrah nada lectures so ta raka ta" "uhm" kawai yace sun d'an ta'ba hira tukun sukayi sallama yana jinshi wasai..........

***

"Innalillahi wainna ilaihi rajiun" Da Abul ke ta nanatawa ne ya dawo da ummulkhairi daga suman tsayen da tayi, idonta ta kai inda dogarayen suke tare da polisawan da suka sama Abbanta ankwa, wayam taga wurin ba kowa alamun sun tafi dashi tana daskare a wurin wani irin kuka ta fashe dashi tana d'aura hannu akai a rud'e tayi hanyar kofa da gudu riketa Abul yayi hawaye na gangaro mishi fisfisgewa ta fara tana cewa "Abba! Abba!! Abbaaaaa!!!! D'an uwa sakeni sakeni kana ga zasu tafi da Abbanmu Wlh karya ce karya sukeyi Abba baze ta'ba aikata zina ba a rayuwanshi balle yayi wa wata 'ya mace fin karfi wacce irin shafin kaddara ce ta bud'e mana waiii hande 'yan boni(yau mun shiga uku)" ta karasa da wani irin kuka tana d'aura kanta kan kafad'an d'an uwanta shima hawaye kawai yakeyi yana tuna hukuncin fyad'e tabbas ya san Abbansu bazai aikata mummunan aikin nan ba amma ya san duniya da sharrin mutane ze sa a d'aureshi a matsayin mai laifi toh ma wacece yarinyar? Me shedansu? duk be sani ba, idonshi ne ya sauka akan Dada dake shirin fad'uwa da sauri ya saki khairi a guje yaje ya tare mahaifiyar tasu tare da d'aura kanta kan kafanshi yasa hannunshi kasan hancinta a firgice yace "er uwa dada.... dadaa bata numfashi" a guje khairi tayi wurin randa tare da d'ibo ruwa tazo ta zuba mata a fuska numfashi taja me karfi tare da sauke ajiyar zuciya se kuka tana maimaita "Allahuma Ajjirna fi musibatin, innalillahi wainna ilaihi rajiun" suma yaran kar'ba sukayi don su d'an samu natsuwa Ai kuwa maganan Allah se ga d'an natsuwa ya saukar musu khairi ta taya Abul suka d'aga Dada zuwa kan taburma suna ajiyeta Baban sulaimi na sallama a rude ya shigo yake tambayarsu wani labari ne yake ji a wajen nan khairi kam ta kasa magana se sabon kuka da ta 'barke dashi Abul ne ya samu ya mishi bayani, nan yace "Toh ai zama be kama mu ba, tashi maza Abulkhairi muje gidan sarkin muji wani chargi office aka kaishi" mikewa Abul yayi yana cewa "er uwa ki bar kukan nan haka ki kula da Dada" Kai ta gyad'a mishi suka fice inda Dada ke adu'ar Allah ya sa a samu nasara, bangaren Abba kuwa shock ya hana shi fahimtar me akeyi sam be san ya akayi tafiyar ba har suka iso Jalingo devision aka jefa shi cikin cell cikin hantara da bakar magana had'e da zagi, sam hankalinshi yaki dawowa jikinshi balle har yayi analyzing abunda yaji sunce, shi 'umar sanda' yayiwa wata fyad'e? Da sauri ya furta Auzubillahi minnashaid'anir rajeem wani irin dariya polisawa da masu laifi da suke cikin cell d'in suka fashe dashi na tsantsar shakiyanci wani yace "Da kake jin daadi a kan 'yar mutane baka San shed'an ba se da akayi ram dakai toh waye shed'an din anan In ba kai ba?" Suka kara shekewa da dariya hawaye ne ya silalowa malam Umar yana karanta duk adu'ar da tazo bakinshi don

samun sauki daga mahaliccinshi.

Gidan sarki su Abul suka fara zuwa inda suka ga tsantasr wulakanci kafin aka fad'a musu police station din da aka kaishi ba 'bata lokaci suka fara tafiya tunda Nisan dake tsakani ba har chan bane, sun isa inda suka nemi ganawa da wadda case d'in ke hannunshi inda aka had'a su da police d'in bayan dogon wulakanci kai tsaye yace ya riga yayi filling case d'in za'a shiga court dashi on Monday su nemi lawyer kawai shine, sun nemi ganinshi ma an hana haka suka taho damuwa fal fuskan Abul tunani yakeyi ta inda ze fara tunda shine namiji babba a gidan shi ze d'auki duk wani nauyi yanzu a shekaranshi ta 17 ta Ina ze fara? Ya san 'yan uwan iyayenshi ba taimakonsu zasuyi ba sema dariya da karin wulakanci da tunanin nan suka isa gida a inda suka bar su khairi anan suka dawo suka samesu zaman akallah awa biyu zama suma sukayi inda khairi ke tambayar "ya akayi D'an uwa? Ba shi bane ko?" Hannu Abul yasa ya share hawayen fuskanshi yace "se adu'a kawai za'a shiga court ran Monday sunce mu nemi lawyer kawai" kuka Dada ta sa dama khairi kam hawayenta tun tuni basu tsaya ba, d'an nasiha baban sulaimi ya musu akan jarabawarshi kenan su ta mishi adu'a ze fito ne in shaa Allahu se da yaga sun d'an natsu tukun yace "yanzu ya kukega za'ayi da batun lauyan ni ba karfi gareni ba balle ince zan taimaka da wani abin" khairi tace "ba komai baba yanzu ma kayi mana abunda baza mu ta'ba mantawa da kai ba, ka riqe mu kaman en uwanka wadda 'yan uwanmun na jini suka kasa" hawaye ta share ta ci gaba da yake khairi nada zurfin tunani se ta kawo wani shawara "me ze hana mu sayar da gonan Abba muyi hayan lawyer?" Abul yace "baze yiwu ba er uwa gonan fa kenan da muke da se gidan nan muka sayar Ina zamu samu kudin abubuwan bukata?" Dada tace "sayarwan shine kawai mafita Allah ze dube mu, kai kana nan kana tunanin abubuwan bukata ina muka samu kwanciyar hankalin anfani da abubuwan bukatan bayan mahaifinka na tsare" Baban sulaimi yace "tabbas shawaran khairi shine abun anfani da, bari zanje In nemo mai saya Allah yasa kar su mana sayen wulakanci don sunga muna kan kafa" Ameen suka amsa gabad'ayansu ya mike har ya kai kofa ya juyo yace "Abulkhairi zo muje ayi komai a gabanka" mikewa Abul yayi ya bi shi daidai lokacin nabeel ya fito yana hamma da kaikaya ido yazo ya fad'i kan kafan khairi yana cewa "Adda khairi velo mi nanata(yunwa nakeji)" se lokacin ta tuna bata d'aura abun karyawa ba mikewa tayi tana cewa "wad'u munyal ha mi defa jotta d'o(yi hakuri bari inyi girki yanzun nan)" kitchen ta shige tana jin fitowan nabeela tana tambayar Dada me yasa yau ba'a tashe su sunje makaranta ba Dada ta ce mata, Abba ne baida lafiya karsu damu zasuje gobe, suka ci gaba da ma Dada tambayoyin 'yan jarida tun tana amsa musu har ta gaji ta kyale su. Farin shinkafa kawai khairi ta dafa ta soya musu mai ta had'awa nabeel da nabeelah se ta sawa Dada tare da d'aukawa ta fito musu dashi nabeelah ce ta kar'bi nasu suka zauna suka fara ci inda Khairi tayiwa Dada bismillah hannu Dada ta sa ta fara ci duk jiki a sanyaye jin bata ji khairi naci ba yasa tace "ummulkhairi me yasa bakya cin abinci?" Khairi da ta buga tagumi damuwa ya nuna sossai a fuskanta bata ma san dada nayi ba, seda Dada ta kara cewa "khairi! Khairi!!" A firgice tace "na'am dada kina bukatar wani abu ne?" Dada tace "ki sa hannu muci abinci, zamanki da yunwa bashine ze sa a sake mahaifinku ba adu'a shine kawai magani" Kai khairi ta gyad'a tare da sa hannu asanyaye ta fara ci bata wani ci sossai ba ta mike tare da d'age kwanon don dada ta dad'e da cire hannu ita dinma karfin hali ne kawai sbd kar yaranta su karasa karaya amma ita kad'ai ta san abunda takeji, su nabeel tayiwa wanka suna ta mata surutu ta kasa amsa musu har ta shirya su, nabeel ya fice wasa yayinda nabeelah ta

zauna tana taya khairin lallice kwanonin da suka 'bata, suna gamawa khairi takai kitchen daga kitchen d'in ta fara jiyo kukan nabeel da sauri ta fita tana tambayrshi me ke faruwa yace "Adda ba kinga su Aisha ba naje muyi wasa wai uhm uhm mamanta ta hanata wasa damu wai Abbanmu yayiwa hauwa fyad'e kar wtkl nima halinshi nayi, Adda khairi me fyad'e?" Dafe gini khairi tayi jin wani irin hajijiya da ya d'auke ta juya ido ta fara don hana hawayen idonta zuba amma inaa kaman an bud'e fanfo maimaita innalillahi kawai takeyi don maganganun yaron sun girgizata yanzu har 'yan unguwan nan sun yarda Abbansu zai aikata fyad'e kuma da hauwa? Wait hauwa fah? Zamewa tayi ta zauna dirshan tare da sake kuka mai sauti........

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad gurin

'Yar mutan Adamawa

Page➡️9️⃣▶️🔟
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Wata kyakyawar yarinyace da baza ta wuce shekara hud'u ba an mata d'inkin atampha doguwar riga me kyau kaman ba yarinya ba, gashinta ya zubo har kumatunta ta gaba kasancewar kitson chuku da na gaba da aka mata an kawata shi da beets masu kyau, se tsalle take tana cewa "yes yes Anty Amrah, Anty Amrah" Kallon inda take kallo nayi se naga kyawawan 'yan mata na kokuwa a tsakiyar parlorn akan wani pink t-shirt dake hannun marar tsawon kuma tsiririyar wadda bazata wuce 17yrs ba wacce naji yarinyar tana kira da Anty Amrah se kokarin boyewa take yi a bayanta inda d'ayar da ta kasance doguwa kuma tafi Amrahn ki'ba bazata wuce 18 and half ba, ta samu nasarar fisgewa ihu yarinyar ta saka "yeeeeeeeeaaahhh Anty miemie!!! Anty Miemie!!" Ci gaba sukayi da kokawarsu akan rigan yayinda yarinyar take ta tsalle tana kiran duk wadda rigan yazo hannunshi, kaman daga sama sukaji ance "Amrah, miemie wai wani irin banzan hali ne wannan? Wai se yaushe zaku girma ne?" Kanta na maida idanuna wow wata kyakyawar mata na gani da baza ta wuce shekaru 49 ba daga kallo d'aya na gane fulanin gombe ce sbd farinsu da ya nuna sossai a jikinta sanye take da atamphar holland riga da zani ta yafa gyale akan d'ankwalin dake kanta kafanta sanye da flat shoe, shagwa'be fuska yarinyar chan tayi tace "ohh no granny you spoiled the fun" zaro ido momma tayi tace "kaniyarki ne zarah, ku kuma sakarkaru daku a gaban 'yarku kuke wannan iskancin dama?" Shagwa'be fuska Amrah tayi wadda itace karama tace "momma ai Miemie ce da neman fad'a sabuwar rigar da Adda nuri ta sayo jiya na d'auka zan saka yau shine fah wai ta rigani se na bata" miemie tayi saurin cewa "karya takeyi momma na fa riga ta d'auka kuma anjima kad'an nake son sawa sbd Ina da lectures don taga na d'auka shine wai se na bata" momma tace "rufemin baki miemie ba kece babba ba? To maza bar mata rigan ita kuma nuriyyahn zata zo ta sameni zata saya muku abu guda d'aya baza ta ce na waye ba kuma baza ta ce ga wadda taba kyauta ba ta barni da raba fad'a" turo baki Miemie tayi tana kallon Amrah inda Amrah tayi mata gwalo a harzuke tace "momma ba kin ganta ba!!!" Momma tace "Auta kika sake mata gwalo se na kwace rigan na bata" sum sum sum Amrah ta haura stairs inda miemie tabi bayanta don zuwa shiryawa ten take da lectures, kasancewarta d'alibar jami'a na gombe state university inda Amrah ke gombe high school sss3, nurriyah kuma tana service d'inta a nan cikin gomben, zarah kuma tana nursery two itama Gombe high school take, kallon zarah momma tayi tace "Hey little zo kiji" ganin yadda zarahn ke tura baki yasa ta kirata, tana bubbuga kafa ta karaso ta kwanta akan cinyar momman, momma tayi murmushi kan tace "I have some good news" zarah tace "what is it?" Momma tace "your paapi is coming 2morrow" wani irin tsalle zarah ta daka tana ihun murna da gudu ta haura stairs don sanar da Aunties d'inta murmushi kawai momma tayi tare da maida hankalinta kan katon plasman dake aiki a

parlorn ganin Bollywood ke aiki yasa ta d'auki remote don mayarwa sunnah tv..

parlor ne madaidaici a saman anyi furnishing dinshi da royals cushion masu tsananin kyau da tsada komai milk da gold ne a parlorn gefe karamin kitchen ne da basu anfani dashi amma akwai komai na bukata Chan gefen kitchen d'in kuma toilet ne babba me kyau, se wani corridor da a ciki d'akunan baccinsu yake, seda zarah ta isa kofar d'akinsu Amrah taja birki don tunowa da yadda suke nuna rashin jin daad'insu In aka ce Paapi d'inta ze zo, fasa shiga tayi ta juya zuwa room d'inta dake facing na su miemie yayinda na momma ke gefenta na nuriyyah kuma na gangan nasu miemie karshen corridor din kuma console ne had'add'e purple an jera wasu turarukan wuta masu kyau daga kasanshi socket ne wadda burner ke jone a jikinshi a kuma kunne yana fitar da hayaki me kamshi kad'an kad'an kasancewar a low aka saka ta, tana shiga ta fad'a kan gadonta tare da jawo wayanta iphone 6plus ta fara game (baki na rike tare da cewa shagali 'ya'yan masu akwai) ........

***

Ta bangarensu Abul kuwa da kyar suka samu mai sayan gonan inda ya tura wani ya gane mishi gonan kaman yadda suka ce ne? Sunje yaga gonan ya kira maigidanshi ya fad'a mishi sallamansu saurayin yayi su kuma suka damka mishi takardun dama sun riga sun gama ciniki akan naira dubu d'ari uku, Ajiyar zuciya Abul ya sauke saura neman lawyer nan suka bazama da kyar suka samu ganin wani lawyer 'Barr Aliyu karofi' inda yace kud'in aikinshi dubu d'ari bayan ya gama sauraronsu da kyar suka samu ya bar musu a 70thousand inda yace suje abinsu ze je ya gana da Malam Umar d'in kan ya shigo unguwar nasu exchanging contact sukayi da Abul godiya sossai suka mishi kan suka fice lokacin karfe 1 na rana dukkansu ba wadda ya karya a galabaice Abul ya shigo gidan tare da samun kan taburma ya zube da sauri khairi taje randa ta d'ibo mishi ruwa ta kawo mishi ba musu ya kar'ba yasha tana ajiye abinci a gabanshi take mishi sannu Dada ma sannu tayi mishi, da kai ya amsa yana kallon nabeel da nabeelah da suke kwance gefen dada suna barci, maida hankalinshi kan khairi yayi wacce ke tambayarshi "An kuwa dace?" Murmushi ya mata tukun yace "eh twiny mun samu mun sayar da gonan akan kud'i dubu d'ari uku, kuma mun samu lawyer wadda ya nemi a bashi 70thousand matsayin kud'in aikinshi" a take fara'a kad'an ya bayyanah a fuskan khairi da Dada sun d'an ji dama dama se faatan Allah ya basu nasara a shari'ahn, bayan Abul ya gama cin abinci ne yake tambayar khairi "er uwa ya akayi waennan sarakan wasan suke bacci yanzu? Ko basu da lafiya ne?" Runtse ido khairi tayi tana Jin zafin abinda zata furta a zuciyanta, a sanyaye tace "mutanen unguwa sun hana yaransu wasa dasu suna tsoron kar su lalata su" zaro ido Abul yayi a hankali yace "what??" Bayanin abunda ya faru d'azu da nabeel ya fita ta bashi inda ta d'aura da "yanzu d'an uwa abinda mutanen unguwan nan zasu saka mana dashi kenan? Koma da gaske hakan ya faru ya kamata su nuna mana kyama da kyara? Har su nabeel yara kanana da basu san me duniya take ciki ba?" Mikewa Abul yayi ba tare da yace komai ba ya wuce d'akinshi jin hawaye na shirin zubo mishi kenan mutane basu yarda da kaddara ba? Ko ma da gaske Abbansu ya aikata abunda ake zarginshi dashi be ci su tausaya mishi ba? Zaman shekaru 19 wasa ne? Katifanshi ya fad'a yana ji komai na duniyan ya fice mishi a rai.........

***

Tsaye yake gaban wardrobe d'inshi yana ta Jan tsaki kaman wani tsaka idonshi na yawo kan kayayyakin gaskiya shi baxe iya saka wani manyan kaya ba ya san kuma In yaje gombe a haka yau juma'a ba tare da manyan kaya ba se momma tayi fad'a maida idonshi yayi kan suits d'inshi kasancewarshi ma'aikacin banki suit sun ninka kowani irin kaya yawa a wardrobe d'inshi se kuma kananan kaya jumpopinshi kam tsab zaka iya kirge su da yatsun hannu janyo wani black suit yayi dake had'e da red long sleeve shirt tare da red neck tie, seda ya saka vest da boxers tukun ya d'auko well ironed trouser na suit d'in ya saka yabi da red long sleeve shirt d'in kan ya d'aura necktie dinshi wurin takalmanshi ya nufa ya za'bo wata cover black se sheki takeyi ya saka ya koma gaban dressing mirror ya feshe jikinshi da mahaukatan turarukanshi dake kashe en mata, brief case dinshi da ya zuba mahimman abubuwanshi ya d'auka tare da komawa bakin gadonshi ya d'auki bakin rigan suit d'inshi ya makala a hannunshi d'ayan hannun riqe da wayanshi ya fice a parlor ya samu me kula mishi da gida me mishi share share da goge goge daniel a tsaye yana jiran fitowanshi ba tare da ya kalli inda yake ba yace "ka kula" yayi ficewarshi Daniel na mishi Allah ya kiyaye a waje ya samu driver d'inshi isa na jiranshi shiga kawai yayi bakinshi d'auke da adu'ar matafiya, ba 'bata lokaci sukayi sallama da garin Abuja zuwa Gombe...

**

Tsaye tayi akan momma dake kitchen tana aikin yiwa d'anta namiji kwaya d'aya tal girki se tura baki take momma tace "Auta wai nikam lafiyanki bance ki gyara min kifin Chan tun d'azu ba?" Amrah tace "momma dan Allah mana laraba tayi wallahi ban son aikin kifin nan ga wancan boss d'in ya wani ce be cin abincin masu aiki ni wlh....." tsawan da momma ta daka mata ne yasata rufe bakin ta da hannu tare da saurin cewa "Afwan momma" kifin ta nufa ta fara aikinshi tabbas basa son ace hamma Musharraf ze zo amma suna sonshi har cikin ransu shine gatansu da ba don shi ba da basu kasance a wannan gida dasuke ciki ba da basu zama cikin d'alibai 'ya'yan masu kudi ba, da basa cikin farin ciki kaman yadda suke yanzu, dukda bata da wayo sossai abubuwa sukayi ta faruwa dasu hakan be sa ta manta waye Musharraf a rayuwansu ba shine katangarsu hagu da dama in ya zube toh suma sun zube yana iya kokarinshi wurin yi musu abunda suke so amma sam basa jin daadin zama dashi Inuwa d'aya kasancewarshi mafad'aci ko motsi me kyau kayi kan iya 'bata mishi rai ya maka tatas fad'ansu na sako da sakon nan ma da sukeyi da miemie duk sbd ba ya nan ne amma In yana nan ko tarin d'ayansu baza kaji da sunan fad'a ba, Allah ya sa ma be yin fiye da kwana biyu, dukan da miemie ta sake mata a baya ne ya dawo da ita daga tunanin da ta lula a masifance tace "kut Lallai Miemie wallahi kinci bashi" miemie na dariya tace "oho de, yau su Anty Amratu ne a kitchen? Me ake dafa mana?" Hararanta Amrah tayi jin ta kirata da sunan da bata so wai Amratu, ganin yadda Amrah ke hararanta ne yasa tace cikin dariya "yi hakuri Autanmu" Da gudu Miemie ta fice ganin Amrah tayi kanta da shirin duka momma bata tanka su ba se murmushi da take tana mamakin irin fad'an sako da sako da sukeyi da junansu wadda baza ka ta'ba gani Musharraf yayi da nuri ba ko don shekaru dayawa ya bata ba kaman waennan ba? Bata sani ba, A parlor Miemie taga zarah se jin daadi take tana ta aikin waya daga jin yadda take wayan ta gane da Ya Musharraf take waya bata jira gama wayansu ba ta nufi sama jin zarah na cewa "kun kusa paapi?" Ya sata tsayawa da tafiyar da takeyi bata san me aka fad'a a d'ayan bangaren ba taga zarah ta kashe waya tana murna, Miemie tace "little!!" Zarah ta juyo ba tare da ta jira taji me miemie zatace ba

tace "Anty Miemie paapi nah ya kusa isowa" ras gaban miemie ya fad'i murmushi kawai tayiwa zarah ta nufi sama tana cewa "dole musha nitsogin"

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story & written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

‘Yar mutan Adamawa

Page➡️1️⃣1️⃣▶️1️⃣2️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Sun shigo gombe after 5 dukda a kishingid’e yake idonshi a lumshe amma chanjin iska da nishad’in da yake ji a cikin ranshi ya tabbatar mishi da sun shigo mahaifanshi tabbas a ko yaushe gida daban ne, a hankali ya bud’e idonshi tare da mikewa ya zauna da kyau yana kallon window sassanyan murmushi ne ya bayyana a fuskanshi har dimple d’inshi na gefen dama ya bayyana wadda ya sani kusa yar da biro na ashe yana dariya!! Murmushin ba karamin kyau yayi mishi ba sede kash ba kasafai yakeyi ba, yana ta kallon cikin garinsu har suka isa GRA layin shiru ba kaman cikin gari da suka baro ba, horn da driver d’inshi ya danna ne yasa shi maido da idanunshi kan ash ion get d’insu da sauri mai gadinsu ya fito yana ganin motan maigidansu ne yayi saurin komawa ya tura get din zuwa karshe inda motarsu ta kutsa zuwa katuwar haraban gidan dake d’auke da flowers masu kyau daga jikin gini inda sukayi har baya wurin boysquaters inda nan ne masu aikinsu suke wasu harda iyalai kuma shi ke ciyar dasu, Chan karshe garden ne mai kyau wadda ruwa ke bulbula yana kuma gudana, qasan haraban shimfid’e yake da interlocks masu kyau daga gefe madaidaicin part ne me parlor da d’aki d’aya se kitchen da store wadda ya kasance nashi yayinda parking lot ke facing part d’inshi cikinshi motoci ne guda uku na different companies, main house d’in kuma duplex ne da ya gaji da had’uwa steps uku daga kasa kan ka haura kan varender din dake shimfid’e da white tiles zuwa babban parlor dake a kasa wadda komanshi ke In Ash and milk se kitchen, store da toilets guda biyu se d’aki guda d’aya. Motansu na tsayuwa tsakar gidan Zarah ta fito da gudu tayi kanshi be gama fita ba ta rungume shi karamin murmushi yayi kan ya duka yasa hannu ya d’aga ta yana juyata se dariya takeyi ajiyeta yayi yasa hannu a sit din bayan ya d’auko brief case dinshi d’ayan hannun kuma ya riqe hannun ‘yar shi cikin tsiririyar muryanta tace “I missed you paapi” yace “missed yhu too my little” nan ta fara zuba mishi surutu kananan murmushi kawai yake sakewa ba tare da ya amsa mata ba har suka shiga cikin parlorn ya so ya fara zuwa part dinshi yayi wanka amma baze iya ba se yaga momma d’inshi da ta kasance farin cikin rayuwanshi da sallama ya shiga parlorn inda momma dake zaune cikin shiga na alfarma ta mike fuskanta d’auke da murmushi tana welcoming nashi ajiye briefcase dinshi yayi tare da karasawa ya rungume ta tana murmushi ta ture shi tana cewa “kayya Musharraf se kace a india?” Murmushi yayi sossai tukun ya langwa’bar da kanshi gefe cikin shagwa’ba da yayi mugun kar’banshi yace “eww momma nayi missing naku ne fah” tace “muma munyi missing dinka sossai son” seda ta zauna tukun shima ya zauna a kasa tare da d’aura kanshi akan kafanta rigimar zarah ne ya ankarar dasu wanzuwar ta awurin duk ido suka maida kanta ta turo baki gaba tana bubbuga kafa a kasa cikin shagwa’ba tace “Paapi don kaga granny shine ka manta dani koo??” Yace “ohh sorry sweetheart zo abunki” karasawa tayi ta zauna daga kasa tare da kwanciya akan kafanshi, da yake ya riga ya d’aga kanshi daga kafan momma hakan yasa shi kallonta fuskanta fal murmushi a hankali yace “mun same ku lafiya momma?” Tace “lafiya klau Musharraf ya wurin aikin naku?” Yace “Alhamdulillah momma, Ina yaran nan?” Momma tace “nuri bata dawo daga wajen aiki ba yayinda Amrah ta raka miemie school tana da 4-6” d’an ‘bata fuska yayi tukun yace “but duka motocin gidan nan suna waje why?” Momma tace “hmmm sun je sun

karasar da man duka rankatakab yadda ba yadda za'ayi a fita dashi filling station Ina ta son in kira azo a sa tun safe se in sha'afa" 'bata fuska yayi sossai tukun yace "haba momma ya za'ayi a bar motocin gida duka ba mai fisabilillahi in wani urgent abu ya taso fa?" Murmushi tayi kawai sanin d'an nata yanzu wannan abu ya jawa duk 'yan matatan ta fad'a sam ta manta ne sbd hidiman dawowanshi amma da ko ita bazata so yazo ya same su haka ba, d'an shiru yayi don da gaske ranshi ya 'baci, kallon fuskan zarah yayi se yaga tayi bacci d'aga ta yayi ya sata a kafad'anshi tare da mikewa momma tace "kawota kaje dining abincinka na jiranka" yace "no momma lemme freshen up, zan tafi da ita In zan fito masjid se in tasota ta shigo" Kai momma ta gyad'a ya d'auki briefcase d'inshi ya fice, a tsakiyar gidan ya gamu da nuri murmushi shimfid'e a fuskanta tace "ya Musharraf san da zuwa, ya hanya?" Ba tare da ya saki fuska ba yace "yauwa Alhamdulillah" ya wuce ta yayi gaba abunshi da kallo ta bishi har ya shige part d'inshi baki ta ta'be, ta san yafi sake mata akan su Miemie amma bata san wa ya ta'bo shi ba daga dawowarshi ya fara cin ran nan nashi har ga Allah tausayi yake bata har ranta sbd ta san duk wani obstacles da ya shiga a rayuwanshi duk da wayonta ba har chan ba lokacin, da tunanin ta fad'a parlor bakinta d'auke da sallama. nayi mamakin ganinta me duhun fata a cikinsu, chocolate color ce ba kaman su da suke farare tas tas ba...

**

Abul be jima da kwanciya ba bacci ya kwashe shi a lokacin baban sulaimi ya shigo inda yace "Ina Abulkhairi yazo ya kaiwa babanku abinci a chargi office don na tambaya aka ce kaiwa ake yi" ajiyar zuciya khairi ta sauke kenan tun safe be ci komai ba? Tana jin Dada na amsawa baban sulaimin da "ya shige d'aki ba da jimawa ba, ummulkhairi tashi ki dubo shi" a sanyaye ummulkhairi ta tashi ta nufi d'akin nashi da sallama ta shiga ganin yana bacci yasa ta fitowa ta dubi baba tace "baba bacci yakeyi, mi andi o somi Un, ha mi wara mi yarana mo (na san duk a gajiye yake bari na zo na kai mishi)" kai Baban sulaimi ya gyad'a ya san dole ya gaji shi da be saba da irin wahalan nan ba duk da su ba masu hali bane amma babansu be bari suyi aikin wahala sam ko yayane gwara d'an d'inkin da yakeyi ma shima don Sana'a ne, duban khairi yayi ya san tana son zuwa taga mahaifinta ne baze hana ta ba se yace "toh bari na turo Ummu sulaimi ta raka ki" Kai khairi ta gyad'a shi kuma ya fice yana tausaya musu ya san In case ya fara daga wurin sarki toh se inda karfinshi ya kare ganin an kwatowa me hakki hakkinshi yana adu'ar gaskiya tayi halinta kar bayin Allahn nan su wahala akan abunda yake da tabbacin ba malam Umar bane ya aikata tuna abunda umman sulaimi ta fad'a mishi yayi shigowanshi Wai an hana su nabeel wasa a waje yau da maganganu se abin ya bashi mamaki ya kuma tokare mishi kirji a yadda malam Umar yake me kyautatawa mutane da makwabta shine don Allah ya jarabceshi 'yan unguwa zasu takurawa iyalanshi? Lallai ka guji duniya da mutanen cikinta da tunanin nan ya karasa cikin gidanshi inda ya samu sulaimi zaune ta zabga tagumi yanzu dawowanta makaranta ko uniform bata cire ba take jin abunda ke faruwa dama tana so In ta cire uniform se ta shiga taji me ya hana su Abul zuwa makaranta yau dayake makarantansu d'aya kuma yau bata jira su ba dama tare suke tafiya amma yau babanta yace ta wuce kawai sbd be da kud'in napep da ze bata kuma be so ya d'aurawa malam Umar d'awainiya bayan ga na yaranshi shiyasa tun da sassafe ta fice, seda babanta ya mata magana sau biyu kan ta dawo daga duniyan tunanin da ta fad'a yace "tashi sulaimi je ki raka khairi chargi office ta kaiwa Abbanku abinci" Da Toh ta amsa tana mikewa a sad'ad'e ta karasa d'aki ta shirya cikin doguwar

rigan atampha tana cikin sa hijab taji sallaman khairi wani hawaye ne ya cika idonta tana jin tausayin kawartata da sauri ta share ta fito ta samesu da ummanta tana kara mata nasiha da kyar take iya kakalo murmushi tana ganin sulaimi ta mike tace “baba, umma se mun dawo” jerawa sukayi da sulaimi suka fice, da kyar sulaimi ta kakaro magana inda tayi mata jaje murmushi kawai khairi tayi ta san in tace zatayi maganan ba abunda ze hanata sake kuka akan hanya, tafiya suka dinga yi kurma kurma har suka iso jalingo devision da kyar aka barsu suka shiga inda suka tsaya daga baki bakin kofa wani d’an sanda ya tambayesu “wa kuka zo gani?” Tace “Malam Umar sanda” “au kice me babban laifi kukazo gani akwai ershi a nan?” Kai khairi ta gyad’a kanta na tsananin sarawa mutumin ze kara magana sulaimi tace “kayi hakuri Dan Allah abinci muka kawo mishi muna bashi kuma zamu wuce bata jin daadi ne” Kallon khairi yayi tukun ya ta’be baki ya nufi cikin cell yana cewa “toh a de kiyaye don ance kama tudinu tudan abinda kayi shi za’ayi maka ehe” basu tanka shi ba se chan ya fito da Abban ganin fuskanshi kawai yasa khairi fashewa da kuka sulaimi kuwa hawaye ya silalo mata, fuskanshi a kumbure tsaban dukan da akayi mishi duk don ya amsa laifin da ba shi ya aikata ba, da kyar ya samu courage d’in yi mata murmushi yace “yi shiru mamana karki damu jarabawata ce tazo a haka in shaa Allahu kuma zan cinyeta tare da karfafawanku gareni In ku kun kasa d’auka ni da nake ciki tsundum kuma ya zanyi? Uhm” da kyar ya samu khairi tayi shiru tare da mika mishi abincin ze d’auka kenan d’ayan police d’in da tunda suka shigo be yi magana ba yace “dakata!! Bud’e ki ci tukun ki bashi” bud’ewa tayi ta d’iba a spoon tare da kaiwa bakinta da kyar ta ci ta had’iye sbd kuna da ranta keyi Wai yau Abbanta ne anan wurin cikin wannan hali, bayan tayi spoon biyu se ta rufe ta mika mishi kar’ba yyi har sun juya yace “ummul” se ta juyo yace “ki sha maganin da na kar’bo miki daga kauyen Abbare n nan” Kai ta gyad’a mishi kan suka juya suka fice har suka iso gida ummulkhairi na hawaye kukanta ya Karu ne sadda suka shigo layin unguwansu tun daga bakin hanya ake zund’ensu har suka iso depon su idi shaid’an nan kam zaginsu sukayi tayi ba tare da wani shayi ba dukda ummulkhairi bata ga idi shed’an a wurin ba amma tayi mamakin wai yau ‘yaranshi ne ke zaginta su da suke girmamata kaman itace ogan nasu ba idi ba, “khaih Allah ya isa mna hauwa Allah kayi mana sakayya” a fili ta furta hakan suna shiga cikin gidansu basu karasa shigewa ba ma khairi kam ta zube a wurin da sauri Abul da ke zaune ya taso yana ambaton “subhanallah kamata sulaimi mu karasa da ita”.............

#vote
#share
#comment

‘Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR  RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️1️⃣3️⃣▶️1️⃣4️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Cikin yanayin shi na Izza da kuzari ya shimfid'e zarah a gadonshi ya nufi wardrobe d'inshi yana cire kayan jikinshi seda ya saura daga shi se boxers tukun ya janyo light green towel ya yafa a kafad'arshi ya shige bayinshi dake manne da d'akin a gurguje yayi wanka ya fito sbd magrib daya gabato cikin light brown jallabiya a hankali ya haura gadon yana Dan bubbuga fuskan zarah kaman me tada wata babba, bud'e lumsassun idanunta tayi ta zubawa mahaifin nata murmushi ta sakar mishi tana mika, yana kallonta ya furta "Alhamdulillahillazi ahyana ba'ada ma amatana......" seda tayi murmushi tukun ta amsa da "wa ilaihin nushur"..................

"Oya wakeup magrib yayi" mikewa tayi yana rike da hannunta suka fito seda ya ga shiganta main house tukun ya fice masallaci da ba wani nisa ne dashi ba.......

Duk da yunwan da yake ji haka ya zauna se da akayi isha tukun ya fito dayake hakan ya kasance al'adarshi, ya d'an tsaya wurin mai gadi da driver d'insu ya tabbatar ba wani abinda ya

faru kuma ba'a musu wani cin fuska duk da ya san momma baza ta ta'ba bari ba amma yana da kyau ya tabbatar d'in.......

Da sallama ya tura kofan parlorn, Amrah da Miemie na tsaye hannunsu cikin na juna da alamu fad'a sukeyi suna d'aura ido a kanshi se suka washe baki suka maida hannun kaman irin rike juna kawai sukayi tare da zamewa kasa suka zauna suka natsu idonshi dake kansu ya kawar ya maida kan nuri dake kunshe dariya harara ya sakar mata se ta gimtse baki Momma kam se dariyanta takeyi karasowa yayi ya zauna gefenta yana shafa cikinshi ta gane Sarai yunwa yake ji amma miskilancinshi baxe barshi ya fad'a ba...........

Kallonsu Amrah tayi tace "Auta ku tashi muje muyi dinner ya Musharraf na jin yunwa" d'an baki ya turo jin Momma tace mishi yaya, ba tare da ta kalleshi ba ta nufi dining tana murmushi suma mikewa sukayi suka isa Amrah tayi serving d'insu tana hararan miemie "Ina Little?" Kallon sama Mimie tayi tare da kwala kiran "Zaaarahhh" bata ajiye numfashi ba taji an daka mata tsawa "kee wani irin iskanci ne wannan?? Ko mu sa'anninki ne zaki zauna kina ma mutane ihu a kai come on kije d'akinta ki kirata".............

Sumui sumui ta tashi ta nufi stairs Amrah se dariya take a ranta don itama In ta sake dariyan ya fita fili za ta samu rabonta, tsab ta gama serving d'insu a lokacin zarah da Miemie sun fito zuwa dining d'in kowa yayi bismillah ya fara ci.........

Seda ya tabbatar kowa ya gama ci tukun ya fara aikawa su Miemie mugun kallo suna ganin haka suka san sunyi laifi duk suka dukar da kai yana nuna su ya fara magana "duk kanku Kun sanni kun kuma san abinda zan iya da wadda bazan iya ba, Wlh Wlh yarinya ta kara fita da mota ta karar da mai bata biya filling station ta sha mai ba tazo ta ajiye mota Wlh ranta in yayi dubu ze baci"...........

Be jira yaji amsan su ba ya mike yana cewa "good night Momma am exhausted" momma tace "Allah tashe mu lafiya" Zarah ta shagwa'be fuska tace "am sleeping with yhu paapi" girgiza kai yayi "no In kin bini baza ki barni na huta ba I know yhu" a sanyaye Tace "sleep tight paapi" yace "night sweetheart" su Amrah suka had'a baki wurin cewa "good night ya Musharraf" hannu kawai ya d'aga musu yana ficewa duk suka sauke ajiyar zuciya suka kalli juna tare da fashewa da dariya lokaci d'aya..........

*************

Da kyar Abul ya samu jikin 'yar uwannashi ya lafa abun tausayi don seda ya zubda hawaye, Sulaimi ce ta share hawayen idonta tana duban Abul tace "Abba yace a fara mata anfani da maganin da ya kar'bo a Abbare last week" Dada tace "Ina yace magungunan karfi garesu? Baza su matsa mata ba In ta fara anfani da?" ..............

Abul yace "Ina ga gwara muyi anfani da shine kawai yadda Abba ya fad'a su d'an yi nisa da ita kar wani abin ya faru wadda ba za'a ji daadinshi ba tunda duk kwanakinnan ranta a 'bace yake"

ba musu Dada ta dogara sanda ta shige d'aki...........

Mintuna kad'an ta fito da wasu bakaken leda a hannunta tayi kiran Abul akan yazo ya kar'ba, kar'ba yayi ya bud'e dama Abba ya mishi bayanin magungunan tun da ya dawo, akwai na hayaki, na sha, na shafawa se wani kaman turare a lokacin duk suka mata banda na sha d'in se sauke ajiyar zuciya take tsabar ciwon kan da ke damunta.............

Two days later

A daddafe waennan family sukayi two days cikin zullumi da tsananin kewan jigonsu me tsananin kaunarsu kaman yadda suke kaunarshi, Kullum khairi da Abul ke kai mishi abinci safe, rana dare kuma kullum In sunje se sunyi kukan lalacewar da yayi, jikin Khairi be kara tashi ba don kullum tana kokarin anfani da magungunanta........

A yau za'a shiga court tunda abun ya faru basu ta'ba had'uwa da hauwa ko mahaifiyarta ba, ko son ganin sarki don su wanke mahaifinsu basayi, dukda sun san shi ya tsayawa su hauwa dukda akan mulkinshi irin na adalci yake amma kuma gaskiya ta shige mishi duhu suna de adu'ar Allah yasa ya fahimta ko ba jima ko ba dad'e................

Kaman yadda suka saba tashi a ranan makaranta haka suka tashi Abul yayi shara yayinda khairi tayi musu breakfast tayiwa su nabeel wanka Abul ya shiryasu suma sukayi wanka amma se suka shirya cikin kayan gida sabanin uniform sunyi akan Dada zata tsaya gida sbd yanayinta ba saba fita tayi ba In sun ajiye su nabeel se su wuce federal high court...............

Suna gama breakfast suka ji sallaman Baban sulaimi da sulaimi bayanshi ta shirya cikin kayan gida itama don baza ta iya barin kawarta ita kad'ai ba, fitowa sukayi inda Baba yace "ummanku baza ta zo ta zauna da dadanku ba? Naga ita kad'ai".............

Abul yayi murmushi yace "ba wani abu baba ai tana zama ita kad'ai" ba tare da baba ya tanka ba suka tsare napep suka shige seda suka tsaya muhammad nya suka sauke su nabeel kan suka wuce.............

****

Cike da kewar gida ya tashi don isowar dare yayi a jiya dukda a gajiye yake sbd tafiyar mota a haka ya shirya cikin 3peaces suit brown color ya zura brown cover tare da d'aura yazole wrist watch brown yayi kyau sossai gashinshi ya sha gyara..........

A gurguje ya feshe jikinshi da mix perfumes d'inshi masu tsananin kamshi, creed, mission ya d'aura da eternity a take d'akin ya bule da fitinannen kamshinshi, bud'e drowern jikin mirror d'inshi yayi kwalayen sigari ne dayawa da Liters har ya sa hannu zai d'auka se ya tuna da nasihohin momma akan cigarettes numfashi me karfi ya sauke yana kokarin fad'a da tunanin nasihohin cikin karfi ya yakice tunanin tare da d'eban kwalaye biyu da liter d'aya ya sa a brief

case d'nshi.............

Da sauri ya fice zuwa kasa ya bud'e motanshi kiran Corolla LS ya shige ba wani 'bata lokaci drivern ya ja motan bayan ya kwashi gaisuwa wurin ogan nashi se da ya d'an tsaya wurin gateman suka gaisa tukun suka fice mintuna kalilan ya kaisu CBN kasancewar gidanshi be da wani Nisan  kirki da nan............

Rike da briefcase d'inshi ya shige lift zuwa floor da office d'inshi yake yana tafiya yana amsa gaisuwan wasu daga cikin kananan workers a bankin jikin office d'inshi ya tsaya inda akayi rubutu da gold a jikin wani brown katako mai kyau, tsayawa karanta matsayinshi nayi cike da mamaki "Mr. Abubakar Mahmoud Adam" daga kasa kad'an aka rubuta "Accountant general of the federation" sossai nayi mamakin ganin yana cikin board members na CBN.................

******
Federal high court

Bayan kowa ya gama shigowa da mintuna kalilan Alkali ya sa kai ya shigo a take kowa ya mike don nuna girmamawa a gareshi seda ya zauna tukun kowa ya koma mazaninshi ya zauna harda lawyers da suke sanye cikin irin kayansu na lawyoyi...........

Su Khairi suna jere daga gaba gaba duk hankalinta na kan Abbanta tana kallon irin lalacewar da yayi duk ya dishe, ganin idonshi na kallon wani gefe daban yasa ta kai idanunta wurin Hauwa da mamanta ta gani zaune hankalinsu kwance da sauri ta kauda kanta tana ji akayiwa alkali bayanin case d'in da ya tara su anan inda ya nemi Barristers suyi introducing kansu...........

Wani tsamurarren bakin Barr ne ya mike "ya mai girma mai shari'ah sunana Barr mudassir qasim nine lawyern me kara" gyad'a kai Judge din yayi inda barr da su Abul sukayi hiring ya mike "sunana barr Aliyu karofi nine lawyer me kare wadda ake tuhuma"............

Barr mudassir ne ya mike ya fara kwararo bayanai da hujjojinsu inda a take ya bayyana yadda abun ya faru a yadda hauwa ta fad'a a nan bakin kogi yayi mata inda ya nuna shedarsu ta takalminshi da kuma hanky d'inshi. Zufa ne ke ketowa Barr Aliyu, khairi, Abul da Abba har baba da sulaimi, amma basu karaya ba sun mika lamuransu ga Allah................

Barr Aliyu yayi kokari sossai wurin ganin ya kare Abba inda yayi anfani da labarin da Abba ya bashi gabad'aya inda yaje da abubuwan da yayi, an nemi ganin hauwa da ta tashi ta bada labarin abunda ya faru, inda ta mike  ta bada labarinsu na karya cikin kuka inda kowa ya tausaya mata ban da waenda suka san karya take, an kira dogarin sarki da Abba ya furta a cikin labarin shi inda yace shi karya Abba ke mishi kwata kwata basu had'u da ko mai kama da shi ba a ranan............

Barr mudassir ya nemi ganin Abul inda ya tabbatar da fitan Abba a daidai lokacin da hauwa tace amma Abbanshi cewa yayi bari ya je yazo inda ya tabbatarwa da court ko sama zata had'e

da kasa baze ta'ba yadda Abbanshi ya aikata irin abu haka ba.............

an tambayeshi yinin ranan gabad'aya yana tare da mahaifinshi inda ya gyad'a kai, Barr mudassir ya sake tambayarshi ya ga wani d'an aike daga gidan sarki girigiza kai yayi, cikin murmushi Barr mudassir ya karasa cike wa court bayani inda yace "ya mai girma mai shari'ah wannan shariah a saukake take kuma a bayyane, mai laifi da lawyern shi basu da wani hujja da ze tabbatar da ba shi ya aikata ba inda muke da manyan shedu akanshi.............

Ya tozarta mace ya wulakantata ya kuma 'bata mata rayuwa na har abada Ina rokon wannan court me albarka tayi gaggawar yanke mishi hukunci bisa laifin da ya aikata cikin gaggawa don ya zama izina ga en baya"...............

Cikin gamsuwa Alkalin ya gyad'a kai tare da rubuce rubuce inda ya tambayi lawyer me kare wadda ake kara ko yana da abun fad'a inda ya nemi alkalin ya d'aga shari'ahn sam alkali ya ki, anan take ya yankewa Abba hukuncin shekara Ashirin da hud'u a gidan yari tare da azaba mai tsanani, be gama rufe baki ba Abba ya yanke jiki ya fad'i a take zuciyarshi ta buga ya bar musu duniyan da abinda ke cikinta, dama be cika lafiyan zuciya ba tun haihuwanshi..............

Da sauri wani ya tashi ya nufi inda Abba ya ke da alamu doctor ne, hannunshi ya kama yana jin pulse d'inshi a d'an tsorace ya sa kanshi kan kirjinshi cikin tsananin mutuwar jiki ya d'ago ya kalli alkalin tare da girgiza mishi kai alamun Abba babu.........

Kaman kiftawar ido khairi ta iso wurin tare da kama hannun mutumin a firgice tace "fad'a min dan girman Allah da darajar iyayenka me ya samu mahaifina? Me ya samu Abbana?" ta karashe da ihu "I'm sorry to say se hakuri ya riga ya kar'bi kiran mahaliccinshi sede fatan Allah ya yafe mishi" a take court din ya d'auki kabbara inda khairi ta sulale ta zauna dabas kan mazaunanta...................

😭😭😭

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story & Written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️1️⃣5️⃣▶️1️⃣6️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

"Abba aaa'aa Abba kar kayi mana haka, Abba ka tausayamana innalillahi wainna ilaihi rajiun wayyyooo, wai Allah am ku taimaka ku taimakemu kuce karya kuke ko ze tashi na san be mutu ba, Wlh be mutu ba" cikin matsanancin kuka khairi ke fidda duk abinda yazo bakinta tana jijjiga mahaifinta amma inaa ba alamun tashi a tare da shi...............

Dayawa daga cikin yan court d'in sun tausaya musu ba kad'an ba don Abul ma da yake namiji kuka yake kaman ranshi ze fita, hauwa da mamanta kuwa tuni zufa ya keto musu a lokaci d'aya cikinsu ya d'uri ruwa basu kawo haka ba sam a ransu, a take hauwa ta fashe da kuka tana jin har cikin kashinta itace ta kasheshi itace ajalinshi, Maman na ganin hauwa ta fara sarewa ta kama hannunta suka fice daga court d'in............

Da kyar alkalin ya samu ya nitsar da kanshi don mutum ya mutu farat d'aya a gabanka ba

karamin abu bane, mikewa yayi ya cire riganshi na alkali da hulan ya mikawa guard d'inshi a hankali ya tako zuwa kan gawan bayan yayi wayan da baifi da mintuna 3 ba, ya duka yana mishi adu'a...........

"Ku yi hakuri ku rungumi kaddara, haba baiwar Allah sai kace ba musulma ba? Kin kuwa san kukan da kikeyin nan kara mishi azaba ze yi? Haramun ne yiwa mamaci irin kukan da kikeyin nan ba'a hana hawaye ba amma banda kururuwa ki ta maimaita innalillahi wainna ilaihi rajiun zakiji sauki, Allah yaji kanshi ya gafarta mishi".........

Hawaye na zuba take girgizawa alkalin kai alamun bazai gane ba, sam baze gane ba, a daidai lokacin chairman na makabarta da mutanenshi suka iso don su alkalin ya kira kan ya zauna bawa su khairi baki, baba ne ya shige gaba akayi duk wani cike cike court ta mika gawan Abba ga family d'inshi aka d'aukeshi a motar gawa don zuwa gida a mishi wanka............

Cikin tausayawa Alkalin da wasu manya da suke nan suka shiga motocinsu wasu ma napep suka bi yayin da wasu suka hau machine me kafa biyu suka bi bayansu inda khairi da sulaimi suke motar alkalin Abul da Abba suna motar gawa............

A kofar gidansu motocin sukayi parking sede cikin tsananin mamaki suka tsaya kallon kofar gidansu garkame da katon sarka inda aka makala padlock daga karshe, da sauri Baba ya ce "mu karasa gidana a mishi wankan a chan" d'aukan Abba akayi zuwa cikin gida anan su khairi suka ga kullin kayayyakin sawansu gabad'ayansu Dada na zaune geje tana share kwallah...............

Jin mutane na shigowa gidan yasa ta mike tana dafa sandanta take cewa "Maman sulaimi Hamma buba ne ya dawo koh?" Maman sulaimi da ta daskare ganin an shigo da gawa bama ta san dada na magana ba tabbas gawa take gani ga khairi, sulaimi da Abul na ta kuka, ga mijinta nan tsaye Toh waye ya rasu? Ko de malam umaru??........

Ras gabanta ya fad'i inda ta furta "innalillahi wainna ilaihi rajiun" Dada se ta kara rud'ewa dama gashi tana ta fama da fad'uwar gaba, bata kai ga magana ba taji an fad'a jikinta bata karasa rud'ewa ba seda taji muryan 'yarta cikin kuka tana cewa "Dada am shikenan, shikenan mu kam, Dada.... daada....." kukan da takeyi ya hana maganan fitowa na kirki................

A rud'e Dada tace "menene? Menene ummulkhairi?" "Abba... Abba ya tafi dada sun kashe mana shi sun yi mana ajalinshi.... daa..." had'iye maganar tayi ganin Dada ta yanke jiki ta fad'i ihu ta kurma, Baba da ya d'ibi butoci ya kai wa mutanen waje da taburmai don suyi alwala kan a yiwa Abba wanka ya karaso da sauri yana kallon Maman sulaimi da take a tsorace daidai nan wasu mata suka shigo............

Duk en unguwan ne, ja baya yayi suka kama Dada bayan Abul ya sa mata ruwa ta de sauke ajiyar zuciya amma bata bud'e ido ba suka shigar da ita d'akin sulaimi, Gawan Abba kuma suka shigar d'akin baban sulaimin dama d'akuna biyu ne kachal a gidan se toilet da kitchen..............

A nan take akayiwa Abba wanka aka shirya shi cikin rigan kowa wato likkafani aka kira iyalanshi suyi mishi adu'a da kallon karshe, Dada, Abul da khairi suka shigo a tare suka rike mamansu a tsakiya, duk sun samu suna kuka yayinda Dada kukan yaki zuwa mata sam..............

A gabanshi suka durkusa duka inda Dada ta fara zuba mishi adu'o'i bayan ta gama ne kuka mai karfi ya kwace mata inda take cewa "Allah yaji kanka umaru Allah ya gafarta maka, yasa aljannah ce makomarka ya biyaka da gidan aljannah yadda ka taimakeni Allah ya taimakeka, tabbas ni nayi rashi na rasa miji na gari, uba na gari, uwa na gari, aboki na gari............

A lokacin da bani da duka waenchan kai ka maye min gurbinsu ka bani wani rayuwa na daban me cike da soyayya, ina Sonka amma Allah da ya hallice mu yafini sonka, daga yau na maka alkawari zan ci gaba da yi maka adu'a har karshen numfashi na......."

Kuka ne sossai ya sarke ta ja baya tayi tana hawaye, Abul ma ya matso ya yiwa Abban Adu'o'i, khairi ma haka sossai ta zuba mishi tanayi tana kuka, seda aka zo fitar da gawan Abba tukun ta rikirkice musu tana kankame makaran tana wani irin ihu da ya tsorata jama'ar gidan seda kowa yayi hawaye, da kyar aka samu aka 'ban'bareta wasu maza majiya karfi su biyar suka riketa aka samu aka wuce da Abba............

A take aka mika shi gidanshi na gaskiya ba karamin jama'a yayi ba se aka ajiye batun maganan fyad'e aka ringa maimaita ayyukan alherinshi, bayan an dawo ne Abul ya samu baba yace "baba dada tace, Abba ya sha fad'a mata cewa In ya mutu be so ayi zaman makoki daga an kaishi an dawo a watse shikenan".................

Baba ya samu alkali ya fad'a mishi don ya zama kaman shugaba a wurin da kud'i da karfinshi ake komai, sossai jikinshi yayi sanyi jin yadda ake yabon halin alheri irin na malam umaru sanda se yake ga kaman shima yayi contributing wurin kashe shi duk da ya san cewa ajali In tayi kira toh se an amsa, amma kuma da ya d'aga shari'ahn da Abba be ji abinda ze buga mai zuciya ba, tabbas idan da gaske ne malam Umar be aikata abinda ake zargin shi dashi ba, guiltiness ze ci gaba da binshi har karshen rayuwanshi..............

Yana cikin tunanin ne yaji maganan baba bayan ya fad'a mishi ne ya koma wurin zaman shi ya zauna suka ci gaba da amsan gaisuwa, ba jimawa wata mota tayi parking aka fara fidda abinci da ruwa na gora da spoons a takeaway abincin yake so se aka ringa ajiyewa d'aya d'aya a gaban kowa, da mamaki Baba ke kallonsu waen nan kuma daga Ina? Ya kasa ba kanshi amsa har suka gama suka shiga da dayawa cikin gida..............

Ashe alkalin ne ganin yanayinsu na babu yasa ya kira ya bada order akan ayi sharp sharp a kawo tun kawo gawa yaga kokarinsu ma na gamawa cikin kankanin lokaci dukda ya san aikinsu na da sauri, seda Baba Yaga Alkali ya mike ya nufe su bayan sun fito ya gane daga inda abincin ya fito adu'a sossai ya mishi a ranshi dama duk tunanin yadda za'ayi yakeyi.............

Bayan kowa yaci ya sha alkali ya mike ya musu bayani akan mamacin yace be bukatar kowa ya mishi zama, so se akayi mishi adu'a a take aka watse sede duk wadda zeyi gaisuwa ya shiga ciki ya ma iyalanshi ta'aziyya..........

bayan an samu da kyar khairi ta natsu ta dawo kanta ta jima zaune wuri d'aya hannunta dafe da kanta dake tsananin ciwo kaman ze rabe sam bata cikin duniyar mutane tayi nisa sossai cikin tunaninta gabad'aya bata jin daadin komai a cikin jikinta hawaye kuma yaki tsayawa ko ta samu tayi shiru In har ta tuna irin sharrin da ya kashe mata abbanta se ta 'barke da sabon kuka...............

Da kyar sulaimi da wasu mata suka lalla'bata tayi alwala tayi azahar a kan sallayan ta zauna ta bud'e wani sabon babin kuka, bata san iya lokacin da ta d'auka ba ta de ji ana raba abinci ita ma an ajiye mata amma ko kallon takeaway d'in batayi ba, se maimaita, "Ya Allah! ka gafarta mishi. Ya! Allah ka bashi tabbata" takeyi..............

Chan se ta mike da sauri tana cewa "ya subhanallah Nabeel da Nabeela" Dada ma tace "subhanallah na manta kwata kwata dasu" wata aka kira aka ce ta kira Abul a waje Ai kuwa taje ta kirashi yana shigowa, Dada ta fad'a mishi ba'a d'auko su nabeel ba gashi past 3...............

A gurguje ya fice ya tsare napep ya hau se muhammed nya a wajen get ya samesu a raku'be gefe sunyi futu da kura da alamu sunyi wasa sun gaji yunwa duk ya cinye su, suna ganinshi suka mike suka je suka rungume shi nabeelah tace "Hamma Abul me yasa baka zo ka d'auke mu ba?? Tun d'azu muka tashi mun gaji ga yunwa"..............

Hawayen da ya cika mishi ido ne ya gangaro da sauri ya share, nabeel kam ya kalla kuma yafi nabeela wayau se yace "Hamma kuka kakeyi? Fuskan ka duk ya kumbura me ya sameka?" Nabeela bata jira amsan Abul ba tace "Hamma kace zaku je ku taho da Abba shiyasa baku zo makaranta ba, kun dawo dashi?"...............

Da sauri ya tsuguna yana fashewa da kuka tare da rungume su cikin rawan murya yace "Abba ya rasu ya tafi inda ba'a dawowa, ku ringa mishi adu'a kullum kunji?" Be jira amsan su ba ya mike yana share hawayen fuskanshi ya tsare musu napep suka hau se gida duk jikinsu a sanyaye don sun san mutuwa a karatunsu na addini.................

Duk da ba wai sossai suka sani ba amma seda sukayi kuka ganin mutane a kofar gidan baba basu san me yasa aka shiga dasu gidan baba ba amma suna ganin Khairi da dada sukaje suka rungume su suna kuka................

*****

Yana jingine da jikin glass d'in dake mamaye da office d'inshi hannunshi rike da taba yana zuka yayinda idonshi ke kallon kasa, ko yaushe ya shiga cikin irin wannan yanayin rayuwa da abinda ke cikinta yake tunawa lumshe ido yayi a cikin kwakwalwanshi yake jin ihun kukan momman shi

da ya kasa d'aukewa a kunnuwanshi tsawon shekaru................

"Baba kayi hakuri ka dena dukanta haka me tayi maka?" A ko yaushe tambayar da yakeyi yiwa mahaifinsh kenan In ya sa mahaifiyarshi a gaba yana jibga tun be san kanshi ba har ya kai yayi girman da baze iya jurewa ba............

"Wallahi ka kara d'aga mata hannu se na rama mata" yana tuna irin kallon mamakin da babanshi ke mishi a sadda ya furta mishi wannan kalaman, a yayinda mahaifinshi be daddara ba a yammacin ranan ya hau dukan mommanshi duk basu ankara ba suka ji saukan abu akan baban nashi inda a take suka kaure da fad'a babanshi na dukanshi yana ramawa................

"Innalillahi wainna ilaihi rajiun Abubakar me zan gani haka? Me kake yi?" Inda tayi maganan cikin kuka da d'aukewar hankali..............

Wai waye Musharraf ne? Wani irin kalubale ya fuskanta a rayuwanshi??

Duk ku biyo 'yar mutan Adamawa ku sha labari☺☺

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad Gureen

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

*my first dedication in this book will goes to kindhearted woman, with a unique name and a very kind full habit- Sawdah-edress, Allah yasa ki fi haka, ya rabaki da sharrin makiya, ya kuma bar zumunci🥰🥰*

Page➡️1️⃣7️⃣▶️1️⃣8️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Bayan kwana uku

Yau Abba ya cika kwana uku cir da rasuwa yayinda family d'inshi suke cikin tsanani da matsin rayuwa, da ba don Allah ya basu makwabci me halin sahabbai ba da basu san inda zasu jefa kansu da rayuwansu ba............

Tunda aka watse a bayan an kai Abba an dawo, baba da kanshi ya dinga d'iban akwatunansu yana kaiwa d'akin sulaimi na Abul ne kawai ya shigar d'akinshi inda ya fitar wa Maman sulaimi da akwatin da ta had'a na kayanta zuwa d'akin sulaimi...........

Duk da shi talaka ne futuk amma yana da wadatar zuciya bade a rasa abinda za'a sa a baki a gidan na kwana ukun nan kam safe,rana, dare. Abunda ke d'aga mishi hankali shine In aka

wuce haka be san ta inda ze ciyar dasu ba, Ya nemi jin me ya faru gidan Malam umar ya kasance a kulle Maman sulaimi tace bata sani ba Wlh taji de kukan dada se ta fita ta samu yayan babansu khairi na ta watsar da kayakinsu shine na nemi yara suka tattaro zuwa nan, muna shigowa kenan kuma kuka shigo..............

Sauke ajiyar zuciya yayi inda ya kudurta a ranshi ana sadakar uku ze zaunar da Dada ta fad'a me ya faru me kuma yasa hamma habu ze koresu a gidan da yake na mijinta?............

Yauma Alkali ne ya kawo masa/waina da kunu ba'a wani 'bata lokaci ba akayi ma mamaci adu'o'i aka ci aka sha kowa ya watse yana me bin Abba da adua, har cikin gida baba yayiwa alkali iso inda ya kara yiwa su dada ta'aziyya su kuma suka mishi godiya sossai akan hidiman da yayi dasu..............

Bayan tafiyanshi ne baba ya kira Maman sulaimi, Abul, se khairi suka zauna daga tsakiyar gida, inda baba ya kalli dada dake sanye da khimar dogo har kasa, a natse yace "Maman nabeel ya kamata mu san me ya faru bayan tafiyar mu koto, me yasa hamma habu ya watso muku da kaya waje bayan gidan ya kasance mallakinku?"...........

Runtse ido dada tayi, idon da In ka gani zaka rantse ba makauniya bace In har ba fad'a maka akayi ba, a sanyaye tace "hmmm ban san me kaddara ta tanadar mana a gaba ba amma Ina matukar tsoro da shakkar abinda ze biyo baya muddin burin Hamma habu ya tabbata, mawiyacin hali da suka sa mu, da kuma tagayyar da rayuwanmu da sukayi be ishe su ba har se sunzo neman wani abin kuma a garemu a daidai lokacin da d'an uwansu ke halin mutuwa ko rayuwa....."........

Hawayen idonta ne suka zubo a kan kuncinta, khairi ce ta sa hannu ta goge mata, da dishashiyar muryarta da sam baya fita sossai tsaban kara da takeyi idan aljanunta sun tashi da kuma kukan da take sha bayan sun tafi, a kwanakin nan baza ta iya lissafa sau nawa sukazo ba duk ta rame se ido da tsiririn hancinta ake gani............

Tace "Dada ba tun yau ba muke rokon ku ku fad'a mana tarihin rayuwanku da abinda yasa 'yan uwanku gabad'aya basa sonku, sau d'aya kachal muka je 'baba gaasa' amma mun fuskanci wulakancin da bamu kara marmarin zuwa koda ta arean ba, me kukayi musu da zafi haka da har d'an uwansu na jini ze fad'i ya rasu ba wadda yazo ta'aziyya ko zaman makoki? Dan Allah ki daure ki fad'a mana su wanene ku"...........

Ajiyar zuciya Dada ta sauke seda ta nisa tukun ta fara magana "Kamar yadda kuka sani sunana safiyya Ali gamji Ni haifeffiyar cikin kauyen 'baba gaasa' ne dake chan bayan 'Abbare' karkashin karamar hukumar 'Lau' na nan cikin Taraba state......

Mu fulanin Chan ne dagani har mahaifinku sede iyayenmu mata ba daga Chan suke ba, ni mahaifiyata er wani kauye ne dake chan cikin gombe wadda ban san suna ko d'aya daga cikin 'yan uwanta ba, ban ma san karan kanta mahaifiyar tawa ba, kasancewar ta mutu a lokacin da

take haihuwana.................

Na taso gaban kishiyarta Ummi itace mace ta farko a wurin mahaifina kan mahaifiyata kamar yadda mahaifiyata taci wahala da azaba haka nima naci fiye da nata, duk wani aiki da wahalan aikin gida ni nake yinshi tun ban mallaki hankalin kaina ba, ba tare da sanin mahaifina ba, Yana tsananin so na kasancewata 'ya mace d'aya tilo a gareshi, Ummi 'ya'yanta hud'u maza da hamma bawuro, Hamma sharif, Hamma hamid se kanina Amadu...........

Duk wani wahalan da nake ci a wurin Ummi sam mahaifina be sani ba don shi ba mazauni bane ko yaushe yana yawo daji daji da shanukanshi, idan ya dawo kuwa na san ko na fad'a mishi ba yadda ze yi ba sbd fuska biyu Ummi ke da shi tana nunamin tsantsar kulawa idan yana nan amma daga ya tafi duk wani abinda na saba yi da tayi yana nan se ta fanshe shi a jikina.................

Baffa se ya kwashe wata kan yake zuwa wani lokacin ma fin haka..........

Kamar yadda nake er uba a cikin en uwa na haka mahaifinku ma yake d'an uba a cikin gidansu, mahaifinshi shine jauron kauyen mu, jauro umaru, sunanshi mahaifinku ya ci mutum me mutunci, da tsan tsan karamci kowa ya shedi kyawawan halayenshi, tsab halayenshi mahaifinku ya kwaso ga kuma an haife shi da ciwon zuciya, shi yasa mahaifinshi ke tsananin son shi magaji ake kiranshi, mahaifinshi ya ke kiranshi da hakan har gabad'aya kowa ya kama..............

Yana da sanyin hali da hakuri amma In ranshi ya 'baci to fah ba zaman lafiya haka yake, ko kwatan wahalan da nake sha a wurin Ummi ba ya sha a wurin Mama goggo sbd kasancewar shi namiji me tsananin zafin zuciya da taurin rai har shakkanshi yayyunshi sukeyi, shine d'a na uku a wurin jauro umaru, iya ballo, hamma habu se mahifinku, Babangida, bamanga da autansu Isma'il..............

Duk cikinsu ba wadda yayi karatun boko se mahaifinku sbd a lokacin da makarantan boko ya shigo cikin lau mama Goggo tace sam 'ya'yanta baza suyi karatu yahudawa ba duk yadda jauro umaru ya juya ta taki sam hakan yasa ya kyaleta ya tura umaru kad'ai se ya kasance umaru ya kuma finsu natsuwa da hankali gashi ya san wurare da dama a cikin gari don har cikin jalingo yana shigowa.............

Hakan ya kara mishi tsana a cikin en uwanshi, Sam be damu ba kuma be da alamun damuwa abunda ya sani de shine ba wadda ze dake shi ya bari ko kuwa ya zage shi, tun bai yi wayau ba mamanshi ta rasu itama er wani kauye ne dake chan cikin Adamawa................

Mafari.....

"Ke! Ke!! Safiya tashi ki je ki d'ibo min ruwa kan In tattaka ki" a natse na mike bakina d'auke da adu'ar tashi daga bacci kiran farko naji akeyi a massallacin dake kusa damu, ban damu ba sbd na saba tashi a irin wannan lokutan sede Ummi bata ta'ba aikata rafi war haka ba se gari yayi

haske................

A tsorace na fito na d'auki tulun da na saba d'iban ruwa na fita sam garin ba haske ba alaman sa a sad'ad'e nake tafiya motsi kad'an se in firgita In juya, a haka har na karasa bakin rafi da bismillah na d'ibi ruwana na kuma d'aura a kaina ina juyowa naga mutane tsatsaye a kaina a firgice na sake tulun ya fad'i ya fashe duk da duhu ne hakan be hana ni sheda d'an uwana dake cikin matasan dake tsayen ba da kuma d'an jauro, habu ba ..................

Baki na rawa nace "Hamma bawuro" wani irin dariya suka saka seda sukayi me isansu tukun Hamma bawuro ya dubi habu yace "dama na maka alkawarin cikawar burinka gashi na cika saura ka kashe kishirwanka" kwalalo ido nayi waje Ina kallonshi tare da son fahimtan me yake nufi ban gama tunani ba naga habu yayo kaina.............

Baya baya na farayi har na isa bakin gaa'bar rafin ban hankara ba naji hannun habu a kugu na, a lokacin ban wuce shekaru 15 ba ihu na sandara ko Allah ze sa wani ya jini amma kaman a banza don na tabbatar ba wadda ze zo ta wuraren a irin lokacin da karfi na buge hannun habun Ina hararanshi wani murmushi ya sake a lokaci d'aya ya sa hannu ya janyoni jikinshi tare da matse ni................

Da iya kacin karfina na sa hannu Ina kokarin raba jikina da nashi inaa karfi ba d'aya ba ganin yana kokarin raba ni da kayana yasa na gantsara mishi cizo me shiga jiki a tamanin ya sake ni yana ihu da mugun gudu na bar wurin inda su Hamma bawuro da sauran abokanshi suka rufa min baya..................

Gudu nake da iyakacin karfina Ina a taimake ni amma ko tsuntsu be bayyana ba, maimakon nayi cikin gari se kuma na nausa daji nayi gudu sossai har numfashi na na shirin d'aukewa naji an janyoni da karfi cikin wasu ciyayi masu tsai na bud'e baki da niyyan ihu se ji nayi an danne min baki tare da jin wani sautin shiiii alamun inyi shiru.................

Shirun kuwa nayi ba wani jimawa naji su hamma bawuro sun iso suna ta dube dube sun jima suna dubani ganin basu ganni ba yasa suka juya suka tafi suna cizon yatsa, se da ya tabbatar sun tafi tukun ya mike ya fito nima fitowa nayi a lokacin gari ya fara haske hakan yasa muke kallon fuskokin juna da kyau..............

"Me ya fito dake gida da asubahin farkon nan?" Shiru nayi tabbas na ganeshi umaru ne d'an gidan jauro wadda en matan kauyen ke rububinshi amma ni kam bamu ta'ba magana ba kallo ma sede In hange shi daga nesa, ganin bani da niyyan amsa mishi yasa ya soma tafiya ai da gudu nabi bayanshi muna tafiya a tare har muka shigo cikin kauyen namu...............

"Ke er wani gida ne?" A sanyaye nace "Aliyu gamji" gyad'a kai yayi don ya kasance ba mai yawan magana ba 'kamar yadda ummulkhairi kike' har kofan gida ya rakoni na shige Ina waiwayonshi, Ina shiga Ummi ta fara surfamin bala'i Ina ruwan da ta aikeni me kuma ya zaunar dani har yanzu, a sanyaye na sanar da ita abinda ya faru maimakon ta ji tausayina se ta rufe ni

da duka wai zanma d'an ta sharri............

Seda ta tabbatar na daku tukun ta bani wani tulun na je na debo ruwa a lokacin en mata dayawa sun fito d'iban ruwa hakan yasa ban damu ba, Ina dawowa na yi mana abin kari na share gida, nayi mata wanke wanke da wankinta tukun ta d'auramin tallahn nono zuwa cikin abbare ta kuma tabbatar mum da kar In sake in dawo ban sayar ba don wallahi In na dawo da ko guda ne se ta yanka ni............

Haka na d'auka na fice jiki a sanyaye da kafa na dinga bi har na isa cikin Abbare zuwa kasuwansu, bani da kawa ko d'aya haka nake rayuwa na ni kad'ai.......

Ashe lokacin da naga umarun nan mahaifinsu ne ba lafiya da dare ya shigo garin shine mahaifinshi ya aikeshi tsinko mishi ganyayyakin magani da shi kad'ai ya sansu cikin yaranshi kasancewa da jauron suke fita dajin.............

A bakin en matan kauyenmu naji ban ma san jauro Umaru ba lafiya ba se a lokacin, haka na zauna jugum Ina tunanin taimako na da umaru yayi ba ni na sayar da nonon nan ba se bayan magriba lokacin ba er kauyenmu ko d'aya a wurin a tsorace na d'auki kwaryata na d'aura a kai tare da nausa dajin da zai kaini baba gaasa cikin sauki..........

Nayi nisa sossai da tafiya dukda a tsorace nake haka na dinga ambaton adu'ar da ya zo bakina, kaman daga sama naga mutane biyu a gabana 'Hamma bawuro da habu' a tsorace nake kallonsu Ina ja baya su kuma se dariya suke, cikin zafin nama habu yasa hannu ya parke rigan sakin da ke jikina ihu na sandara Ina me kakkare jikina da tafukan hannuna...........

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️1️⃣9️⃣▶️2️⃣0️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Ihun da na sandara shi ya janyo hankalin umaru da ya idar da sallahn magrib kenan yana shirin kora shanukanshi da na mahaifinshi zuwa gida, da sauri yayo inda muke yana isowa ba tare da wata wata ba ya saukewa bawuro sandan goran hannunshi a kai a take ya sheme, duk da sarai ya gane wanshi ne a kaina ba tare da wani tunani ba shima ya sauke mishi a take ya baje shima.................

Da sauri ya kama hannuna ya d'aga ni tsaye tare da d'aukan kwaryan nono na fito me daad'i yayi wa shanukanshi a take suka iso inda muke, duka muka nufi cikin gari, tunda muka fara tafiya nake kuka kaman raina ze fita, yanzu su habu baza su tausayawa maraici na ba? Sannan hamma bawuro kaman ba d'an uwa na ba!! Shine wai ze rako a lalatamin rayuwa..............

Tsoro sossai ya kamani tunda na san ko na fad'awa ummi ba yarda zatayi ba, kuma baze hana gobe ta kara d'auramin tallah ba, gashi ba.... "Ke!! Da Allah ki rufewa mutane baki, akwai wadda ya aike ki ne? In ba rashin hankali ba kina mace me ze kawo ki cikin dajin nan da irin wannan lokaci?".................

Kafin na bashi amsa naji wani abu me tsananin zafi ya ciji kafana ihu na sandara tare da zamewa na zauna a kasan da sauri ya haska torchin da ke hannunshi se yaga katuwar kunama ce da sauri ya take ta, tare da dukawa a lokaci d'aya ya zame d'ankwalin kaina tulin gashin kaina ya bayyana, yaga d'ankwalin biyu yayi inda ya kama kafan ya d'aure da karfi................

Cikin azama ya fara dube dube yana haske hasken torchi har ya samu ganyen da yake nema, ni kam se kuka nake da duwatsu biyu ya samu ya markad'e ganyen tare da sawa a daidai inda kunaman ya sareni, kara na sake Ina me rike hannayenshi a hankali yace "sannu" kai kawai na gyad'a ruwan hannunshi ya mika min na kafa bakin goran a bakina ban sauke ba seda na shanye wasu hawayen na gangaromin.................

"Lallaba ki tashi mu shiga cikin gari dare na yi kar hankalin iyayenki ya tsahi" a sanyaye nace "ko da zan kwna a dajin nan banda wadda hankalinshi ze tashi saboda ni.." da mamaki yake kallo na a hankali yace "sbd me??" Haka kawai naji na fara bashi labarin rayuwana daga farko har kawo yau, na kara da "har yanzu kana ganin laifina don na shigo cikin daji da dare??" Na karasa Ina me kallon cikin kwayar idonshi da suka chanza kala sbd tausayi.............

Da sauri ya kauda kanshi yana me runtse ido ba tare da yace komai ba ya kama hannuna muka mike ba wani nisa ne tsakaninmu da cikin gari ba don haka nan da nan muka isa, har kofan gida ya rakani tare da mikamin kwarya na se da ya ga shiga na tukun ya juya ya fice.............

Ba wani fargaba na shiga don na san ko damuwa da abinda yasa nayi dare ummi bazatayi ba, ai ko hakan ta kasance Ina mika mata kwarya da kud'inta ta soke a zaninta ba sannu bare na gode ba me yasa kikayi dare haka? A sanyaye na wuce d'akina Ina kallon wuyan rigana dake a yage................

Tabbas da mamana na nan na san cikin tashin hankali zata rikeni tace me ya samu rigana ya yage haka? Me yasa nayi dare a waje? In ban sayar ba bazan dawo tun ido na ganin ido ba? Wani matsanancin kuka ne ya kwace min, kwanciya nayi akan er taburman kaba na Ina rerawa a haka bacci ya d'auke ni dukda tsananin yunwan da nake ji.............

Kaman jiya yau ma da asubar fari ta tasheni tare da bani tulu na tafi d'iban ruwa, Ina fitowa bakin kofan gidanmu na ganshi tsaye hard'e da hannu kasancewar akwai farin wata sossai yasa na kalli murmushin da yake aika min, nima murmushin na sakar mishi tare da karasawa wurinshi nace "en ummi jam?"(mun tashi lafiya?) yace "jam noi kusd'e ma mai?(lafiya ya kafan kin)...........

Murmushi kawai nayi muka kama hanyar rafi jefi jefi muna hira har muka isa na d'ibo ruwa da sauri ya kar'ba min muka kamo hanyar dawowa seda ya ga shiga na gida tukun ya juya ya tafi, haka lokacin tallah na nayi ya zo Ina fita muka gamu har Abbare ya rakani ya juyo da misalin biyar na yamma ya koma seda ya jira na sayar gabad'aya ya sani a gaba muka nufo hanyar kauyenmu..................

Wasa wasa shakuwa me karfi ta shiga tsakaninmu kusan satinmu uku kenan da muke tare In har zan fito daga gida Toh shi ze rakani duk inda zani abunku da karamin kauye nan da nan gulamanmu ta bazo masu zagi nayi masu jin haushina 'en mata' na ji, da maganan yazo kunnen ummi dukan mutuwa tayi min tace in rabu da magaji ko ta d'aura min sharrin da har na mutu

bazan manta ba.................

Ban ji magananta ba sbd ni ya ke taimaka ba ni ke taimakarshi ba, da kariyan Allah da kuma shi kad'ai na dogara, na de fad'amishi be ce min komai ba akai se in yi hakuri wata rana se labari, a na haka kwatsam mahaifinshi ya fad'i ya rasu bayan jinyar da ya sha, sossai na tausayawa umaru don kaman ze yi hauka sbd mutuwar ba karamin shiganshi tayi ba...................

Har gidansu naje nayi mishi ta'aziyya a sace na d'auki abinci na na fita da shi tare da tilasta mishi yaci ya kuwa ci dukda ba mai yawa bane, seda safe na mishi Ina shirin fita mama goggo na shigowa da tsantsar mamaki take kallonmu da alamun zargi, wani murmushi tayi kan ta juya ta fice da sauri nima na fice............

A washegarin na fita d'ibo ruwa har nayi nisa da tafiya naji ance "yau kuma ba jira ne?" Da sauri na juyo murmushi na kwace min ashe ze zo dukda a jiya mahaifinshi ya rasu saurin gimtse fuska na nayi nace "me ya fito da kai yanzu kai da kake fama da rashi?" A sanyaye yace "safiyya kenan se kace ba musulmi ba? Baffa ya riga ya rasu baze ta'ba dawowa ba adu'a kawai zamu ci gaba da yi mai shine gatan da zamu mishi yanzu"...................

Kai na gyad'a muka ci gaba da tafiya muna hira, a hanyar mu ta dawowa lokacin gari yayi shaa, kaman ance ya waiga se yaga hannuna da gefen fuska na duk sunyi rad'a rad'a kaman wadda cinnaku suka kwana cizo, a firgice ya rikemin hannu yana cewa "safiyya d'ume un d'o"(safiyya me wannan?) karamin murmushi nayi ina sauke ajiyar zuciya nace.............

"Nima ban sani ba wasu abu ne kaman qwari kaman cinnaku suke fitowa a d'akina ko na binne wurin se sun tono sun fito har garwashi nake sawa a wurin amma hakan be hana su fita ba" a d'an fad'ace yace "shine baki gayamin ba?" Shiru nayi, har muka isa kofan gidanmu be sake min magana ba ya juya ya fice na lura kaman ranshi a 'bace yake..........

Ashe yana barin wurin gari ya tafi ya sayo wani maganin kwari me karfi ya taho dashi, Ina shiga gida na samu babana na ya dawo da gudu na karasa na rungume shi bayan na ajiye tulun kaina, shima rungume ni yayi cikin farin ciki ya na tambaya na ya nake cikin murna na amsa, Ina satan kallon ummi dake sake mana harara a fakaice................

Tsaraban da ya yo min ya bani na wuce d'akina cikin murna, har rana ya d'aga ban fita ba na San ba aikin da zanyi ba kuma zuwa tallah sbd baba ya dawo, sallaman yaro ne yasa na fita Ina kallonshi d'an makwabtanmu ne cikin wasa yace "Safiya 'be d'o nyaune ha yasi"(ana kiranki a waje) na san baze wuce umaru ba hakan yasa na bishi Ina kallon ummi dake ta kallona da tsana karara a fuskanta...............

Ina fita na tare shi da hiran baba na ya dawo, murmushi yayi yace "ko zaki min iso?" Nace "ai In ya dawo baya ganin kowa a ranan baccin huce gajiya yake sha" yace "toh gashi Ina so muje In saka miki magani a d'akinki sbd abun kar su kara cizar min ke"...........

A kunyace nace "zaka iya shiga ai ummi ce kawai ke aiki a tsakar gida" gyad'a kai yayi tare da bin bayana muka shiga da sallama duk da naga kallon mamakin da ummi ke mana hakan be sa naji ko d'ar ba don babana na gida, har d'aki na na kaishi ya bud'e maganin da niyyan zubawa kenan mukaji an fisge................

D'ago idon da zanyi don kallon wadda ya fisgen kawai naji an zuba min wani ruwa me shegen rad'ad'i da azaba a cikin idon kara me tsanani na sake inda anan take Umaru yayi kaina ganin Ina shirin fad'uwa ya d'aura ni kan jikinshi, a sama sama naji ihun ummi tana cewa "mun shiga uku malam!! malam!! Innalillahi wainna ilaihi rajiun yau naga ta kaina ni zahara'u"..................

Da gudu baba ya shigo jin ihu da salatin yayi yawa a tsorace yake kallona lafe a jikin umaru salati ya saki, ummi tace "malam kwarto har cikin gid'a safiya ta kawo mana shikenan mun shiga bakin jama'a" idona da yayi dishi dishi tare da yin jaaa na fitan hankalin se ruwa yake zubarwa nake kallon baba, da alaman yarda ze yi....................

"Baba ba....." rufe min baki baba ya katse umaru dake shirin magana ze yi magana kenan mukaji sallama da karfi ba kakkautawa da sauri baba ya fita ummi ta rufa mishi baya, Umaru ma kama ni yayi ya tsayar tare da rike hannuna muka fito da mamaki yake kallon mama goggo zuwa lokacin duhu kawai nake gani................

"Na zo ne In jaa kunnen karuwan 'yarka, wato karuwancin da sukeyi da umaru a waje be wadatar ba se ta Bishi har cikin gidana ran rasuwar mijina suka aikata masha'arsu, don tsabar rashin tarbiya ko kunyan gidan rasuwa bata jiba, Toh wallahi ku kiyayeni baza ku zo a rana tsaka ku 'bata min tarbiyar yarana da ke tasowa ba".................

Da sauri baba ya dafe gini jin jiri na shirin kada shi se gumi yake had'awa take idanunshi sukayi ja, cikin lalau'be na isa inda yake tare da zamewa na rike kafanshi cikin rawan muryan nace "baba ka saurareni don Allah, ka kuma yarda dani wlh Wlh ban ta'ba aikata zina baa....." hankad'e ni da baba yayi ne yasa na dafe bakina Ina kecewa da kuka me tsanani shikenan shikenan baba ya yarda..............

Cikin fusata baba yace "tarbiyan da na miki kenan safiyya? Abinda zaki saka min dashi kenan a rayuwa? Tirr da haihuwanki daga rana irin ta yau na cire ki daga cikin 'y'yana wallahi ko kofan gidana kika tako Allah ya isa ban yafe ba kuma se na dawwama Ina tsine miki albarka idan har kika bayyana wannan munafukar fuskar taki akan nawa"...............

Cikin tsananin kuka naso In fahimtar dashi amma inaa yaki saurarena kaman daga sama muka ji muryan umaru yana cewa "ka yi hakuri ka aura min ita a haka, Ina neman alfarma don darajar annabi ka d'aura mata aure da kanka gareni ni kuma nayi maka alkawarin muddin Ina numfashi bazan ta'ba kawota ko da hanyar kauyen nan bane balle cikin garinnan ko gidanka".................

Tsit wurin yayi na mintuna tukun baba yace "muje a d'aura, wannan yarinya na tabbatar da mahaifiyarki na da rai da tayi Allah wadaran ranar da ta samu cikinki" ficewa sukayi, suka barni

Ina aikin matsanancin kuka gashi bana gani............

Ina a inda suka barni har suka je suka dawo, umaru ne ya kama hannuna muka mike Ina ta kiran sunan mahaifina amma ko...... ko(kuka ne ya sarke Dada sossai tana ganin kaman yanzu duk komai ya faru.. da kyar ta samu kukan ya tsaya tukun ta ci gaba)............

Ko kallon inda nake be yi ba har muka fice daga gidan, gidansu umaru muka nufa Ina aikin kuka sam be lura binshi kawai nake Ina d'aura kafana a duk inda ya sauke ba sbd bana kallo kwata kwata duk da kuwa idanuna bud'e suke, gidansu muka shiga ya had'a kan shanukanshi duk hannunshi cikin nawa muka fice...................

*ku yi hakuri Wlh ban jin daad'i ne kwata kwata, shiyasa kukajini shiru kwnaa biyu, ku lalla'ba da wannan*

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️2️⃣1️⃣➡️2️⃣2️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Ko 'lau' bamu tsaya ba muka wuto jalingo, a take ya sayar da duk shanukanshi a lokacin dare ya fara yi gashi bamu san kowa ba sam be lura da idona ba yace "je ga wani dutse Chan ki zauna ki jirani kinji?".........

Girgiza kai kawai nayi ganin Ina ganin wani gefen yasa yace "me ya faru? Kar ki damu komai ze wuce ne Allah yana tare damu" a hankali nace "bana gani" zaro ido yayi yana cewa "me???" Maimaita mishi na kumayi dafe kai kawai yayi yana ambaton sunan Allah...........

Wani tsohon Abokin babanshi ya tuna dake nan jalingo yana da gida a barde way, d'anshi babba ma dillalin filaye ne, ajiyar zuciya ya sauke kan ya tsare mana machine muka hau se unguwan, da mutunci tsohon ya kar'be mu, kwanan mu biyu d'anshi ya sama ma umaru gidan nan da kuma gona inda ya biya da kud'in shanukanshi da ya sayar...............

Bamu kara ko kwana d'aya ba muka komo unguwan nan, shekarata d'aya na haifeku inda na sha wahala sossai sbd kankantar shekaruna, ban haifi su nabeel ba seda kuka shekara 12, batun ido kam mun jarraba magunguna yaki budewa se kawai muka hkr, Allah sarki umaru Allah ya rahamce ka, ya gafarta maka...........

Cigaban labari🕸🕸

Duk seda suka zubda hawaye sossai labarin ya girgizasu musamman Abul da khairi kusan mintuna biyar tukun baba yace "toh yanzu wai me ya kawo habun?"........

Dada tace "yace In Ina son zama a gidan cikin kwanciyar hankali In bashi 'yata tunda ni be same ni ba, da na ki shine ya fara zage zage anan na san yana bibiyar kab labarinmu sossai yaci mana mutunci daga ni har d'an uwan nashi" "innalillahi wainna ilaihi rajiun" suka fad'a a tare ummulkhairi tace "what??? Ni??? Yana yayan babanan??"............

Murmushi mai ciwo dada tayi tace "hmmm khairi abinda duniyar yanzu ta koma kenan uba ya nemi 'ya, wa ya nemi kanwa se adu'a kawai" baba yace "toh yanzu menene shwaranki" Kai tsaye tace "mu bar garin nan".............

Abul yace "haba Dada sbd shi kawai se mu tafi mubar gidanmu, makarantanmu, Sana'an mu da kuma rayuwar da muka saba da shi?" "Dole kuwa ku tafi Abulkhairi a yadda naji labarinshi tabbas be barku ba nan ma ba tsira kukayi ba kuje ku sake Gina wani sabuwar rayuwan kawai tun ba'a zo ana da na sani ba"............

"Baba toh yanzu Ina zamu je?" Cewar Abul, Haka kawai khairi ta tsinci kanta da cewa "Gombe" gyad'a kai dada tayi cike da gamsuwa don haka itama Chan hankalinta ya karkata gwara suyi nisa ko Allah ze sa su gujewa sharrin habu zuwa garesu, Maman sulaimi da tunda aka fara labarin se yanzu tayi magana tace "Toh bar mishi gidan da ya kullen zasuyi? Da kuma wani kud'i zasu tafi har su samu su kimtsa komansu?"..................

Dada tace "akwai sauran kud'in gonan nan da Abul ya bani yana jikina yanzu haka dubu d'ari biyu da ashirin, ze ishemu In shaa Allah, gidan kuma ya rike shi da Allah ai hakkin marayu ne, in mun ce se mun kwace gidan zamuyi asaran d'an kud'ad'en da mu ke da ba tare da munyi nasara ba tunda ya kwace takardun ya tafi dashi"................

Ita de khairi ta kasa magana mamaki sam ya ki sakinta da jin wannan cakwakiya da wan mahaifinta ke son had'awa da kuma ita, a zuciyarta tace tab lallai da kuwa da ya d'aukarwa kanshi. Shi kuwa Abul sam be so tafiyan ba don ba yadda ze yi ne kawai, sun tsayar akan zasu wuce washegari inda khairi ta mike jiki a sanyaye ta fara had'a musu kaya.....................

********

Sam ransu ba daad'i suka sauko daga saman cikin shirin makaranta Amrah da Zaraah sanye da uniform yayinda Miemie take sanye da doguwar rigan atampha da madaidaicin gyale kokarin sa wayanta take a cikin Side bag dake jikinta tana kuma fidda car key, kaman basa so ransu a had'e kaman ba su ba suka cewa momma dake zaune parlon kasa "mun tafi".................

A sanyaye tace "Allah ya kiyaye" tare da binsu da kallo kaman ba su ne masu fara'a da wasa ko wanni lokaci ba, zaraah ce kawai da bata san me ke faruwa ba take aikin fara'a da surutu, fita sukayi inda suka shiga motan ya Musharraf da Miemie ke zuwa school dashi be ce ya bata ba amma tunda ta fara Jami'a ya bata keyn shi kuma ke tura mata kud'in petroleum a kai a kai, har pocket money....................

Amrah ma ta iya driving don tare ya sa aka koya musu amma ya gargad'i Miemie kan kar ta sake ta bawa Amrah key ko sau d'aya ne se ya fad'a, hakan yasa In har tana da lectures d'in 8 take sauke su kan ta wuce driver se ya je ya d'auko su da motan Momma..............

Suna fita suka shige motar 'kiran End of discussion, Miemie ta ja ta nufi gate, daga wajen gate d'in wani mutumi ne baki sossai yake kama da Nuriyya komansu iri d'aya sanye yake da jumpan da daga ka gani kasan a sabonshi ba karamin kud'i ya ci ba, amma yanzu yayi datti ya kod'e sossai mutumin a rame yake kaman ka hureshi ya fad'i kanshi ba hula se gashin da ya tara abun tausayi de.................

Ko kallon inda yake basuyi ba Miemie ta ja a d'ari tabbas da akwai kura a wurin ba abunda ze hana ya bule mutumin, daga ciki kuma momma tayi zurfi cikin tunani har bata ji saukowan nuriyyah ba se ji tayi ta dafa ta, a hankali ta d'aga kai ta kalleta tana barin hawayen idonta zubowa, zama nuriyya tayi a gefenta sanye take da kayan NYSC ta d'aura after dress akai baki me buttons daga sama har kasa, tare da yana gyalenshi hulanta da jakanta ta ajiye tukun ta fara magana...................

"Har yaushe momma?" Momma tace "ban son Allah ya kamani da laifin barinku kuna abinda kukeso bayan kuma ba daidai bane, tunda ya tuba kam baza kuyi hakuri ku kar'be shi ba?" Nuriyyah tace "hmm yafiya fa kikace momma? Har ya kai a yafe mishi duk laifin da ya aikata nan? Dan Allah momma ki dena sa kanki a damuwa duk randa yazo kin san yanayin hawan jininki wadda shine sila kar ki bari yayi mana ajalinki"..................

Ajiyar zuciya momma ta sauke tace "toh naji zan dena damuwa in shaa Allah kar ki fad'awa yaynki zuwanshi dan Allah" Kai nuriyyah ta gyad'a tare da mikewa tace "se na dawo" momma tace "Allah ya tsare ya bada sa'a" murmushi sukayi wa juna kan ta wuce, motar ta da hamma Musharraf ya bata kyautanshi 'discussion continue' red color ta shige tare da jan motan ta fice Ko kallon gefen da mutumin yake itama batayi ba ta bar unguwan....................

Seda tayi nisa da unguwar tukun ta parker tare da fashewa da kuka sossai take kukan duk cikinsu ita kad'ai Allah ya d'aurawa kaunar mahaifinta har cikin ranta amma laifinshi a garesu ba na yafiya bane har se ya je an yanke mishi hukuncin da ya dace da abunda ya aikata, nan kam dole su bishi da ad'uar dacewa da rahamar ubangiji despite manyan laifukanshi a duniya................

Seda tayi kukanta ta koshi tukun ta d'aga waya ta danna kiran hamma Musharraf ko bata fad'a mishi ba su miemie ko zaraah se sun fad'a mishi gwara suyi magana ta fahimta da shi tunda yafi sake mata.................

*******

Shigowarshi office kenan yana zama ya jawo files files na gabanshi ya fara dubawa a tsanake yana cikin na farkon ne yaji kiran nuriyyah seda kiran ya kusa tsinkewa tukun ya d'aga da sallama a bakinshi amsawa tayi daga bangarenta ta gaidashi ya tambayeta su momma se tayi shiru ya sake cewa "bata da lafiya ne?"....................

Ya fad'a yana kokarin controlling kanshi don take yaji hankalinshi yayi mugun tashi Allah ne kad'ai ya san yadda yake son mahaifiyarshi, "a'a hamma, baba ya zo" In a very angry tone yace "what??? Ya zo? Me ya kawo shi?? And wa ya nuna mishi gidana???" Nuriyyah tace "ban sani ba wallahi yaya amma na sa me gadi ya koreshi, shine nake so ka kira momman ko hankalinta ze d'an kwanta na de yi iya kokarina"..................

Idonshi da yayi jaa ya kara kankancewa ya lumshe tare da cewa "Ohk" ya kashe wayan be kira momma ba se da ya kira gate man d'insu ya kashe mishi kashedi akan In ya kara bari mutumin nan ya shigo mishi gida wallahi a bakin aikinshi cikin tsoro ya amsa don ya san ran mai gidan nashi a 'bace yake sossai.................

Sanadin barinsu unguwan tudun wada kenan sbd baban na yawan zuwa Chan mai gadinsu na da kuma se ya barshi ya shiga, bayan duk kashedin da Musharraf ya mishi, randa ya zo last a ranan Musharraf ya sayi gidansu na yanzu suka tarkato suka dawo ya kuma kori wancan mai gadin duk kuwa da irin rokonshi da yayi tayi, a bakin driver yaji wannan labrin ai tun farko ma bai san shi bane da wlh be barshi ya shigo ba..................

Bayan Musharraf ya gama waya da gate man a take ya danna kiran momma tana zaune a inda nuri ta barta se sake sake take taji kira ya shigo wayanta tana kallon Musharraf ne taji wani tausayinshi ya rufeta, sam bata ga laifinshi ba don yace baze yafewa wadda ya lalata mishi rayuwa ya kuma jiyar dashi wahalan rayuwa ba, amma tana tsoron kar Allah ya kama ta da laifin gujewa mijin aurenta duk da kuwa ba sonshi take ko son zama da shi ba, amma hakkinshi na kanta tabbas abinda ke sata cikin damuwa kenan In har ya kusanci inda suke....................

Da sallama ta d'aga ya amsa a sanyaye daga bangaren shi, cikin kasa da murya yace "momma me yasa kike son sa damuwa a ranki a duk sadda mutumin Chan ya matso garemu? Ba de har yanzu kina son shi ba?" Girgiza kanta kawai tayi tana mamakin halin musharraf a matsayinta na mahaifiyarshi yakewa irin wanchan tambayar? Ta san ba laifinshi ba ne haka yake birkicewa In har yaji labarin babanshi sam bata so wa kanta da 'ya'yanta irin wanchan uba ba amma ya ta iya ba laifinta bane Allah ne ya za'ba musu...........

"In Ina sonshi Musharraf laifi ne? Ko ka manta mijina ne kuma uban 'ya'ya na? Jininshi ke yawo a jikinku duk irin tsanar da kuka mishi kuwa ba yadda zakuyi da jinin nan ko ka manta har yanzu sunanka "Abubakar Mahmoud Adam?" Ku natsu ku maida hankalinku jikinku don kun yafe mishi ba abinda ze chanzu a jikinku, ku kiyaye kuma ni na riga na yafe mishi kuma In har ya sake dawowa zan bishi inda yake rayuwa muyi rayuwa tare tunda baka da manners".................

Kit ta kashe wayan, da karfi ya bugi hannunshi da table d'in dake gabanshi tare da cewa "shiiiittt!!!!!" Wlh ya manta da wa yake dealing yayi mata irin wancan tambayan, tana da saukin kai amma tana da zaafi wurin tarbiyya don shine shaida sbd yafi kowa dakuwa a hannunta kasancewar shi me fad'an duk abinda ya zo bakinshi wa mahaifinshi................

"Goddamn it!!!!!!!" Duk randa mahaifiyarshi ta komawa mahaifinshi a ranar tabbas za'a d'auki

gawanshi safa da marwa ya fara yana kiran numbernta amma sam ta ki d'agawa hannunshi ya tusa a tulin gashin kanshi idonshi na cikowa da hawaye, da sauri ya isa gaban briefcase d'inshi ya bud'e tare da d'auko cigarette ya kyasta mata liter zu'ka biyu ta kare ya jefar ya kara d'auko wani.................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

*this page goes to yhu sweet sis haneefa Muhammad Gurin, thanks for the support and care, yhu are such an angel dear I love yhu so much😘*

Page➡️2️⃣2️⃣▶️2️⃣3️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Ganin yayi ta kiranta bata d'aga ba yasa yayi reporting a office be da lafiya ya tafi, tarkata komanshi yayi ya fice, ranshi a matukar 'bace wannan fushin da mommanshi tayi da shi duk baba yayi blaming sbd da be zo ba da hakan be faru ba, haushinshi yake ji har kashinshi............

Yau be taho da driver ba so da kanshi ya ja motan ya jefa ta titi, har ya isa gida ranshi tafasa takeyi ji yake kaman yayi tsuntsuwa ya ganshi gombe..........

***

Ita kam momma tunda sukayi haka da Musharraf ta ajiye wayan a parlorn ta haura sama, wanka tayi ta fito da alwala tare da gabatar da walaha, tana idarwa ta shafa mai tare da shiryawa cikin wata dakkakkiyar lace black and red tare da feshe jikinta da turarukanta masu sanyin kamshi..............

Saukowa tayi hankalinta gabad'aya se ya koma ga Musharraf ta sanshi sarai In har tayi fushi da shi toh be da natsuwa sam, seda ta shiga wanka tukun ta tuna da wayan da ta bari a parlor ta san yayi ta kira, tana shirin d'aga wayan ta duba kenan se mai aikinsu hanne ta shigo da sallama...........

Zama momma tayi tana amsa sallaman har kasa hanne ta du'ka ta gaida momman, momma tace "hanne me yasa yanzu baki son zuwa da wuri yanzu past 9 fah duk wanke wanken safe na tare kin san girkin safen ma kanki yake Ina yi ne kawai amma In Musharraf ya sani kema kin san sauran"..............

Hanne kanta a kasa tace "hajiya kiyi hakuri kwanan nan duk shirye shiryen buki na akeyi yau ne ma ake kawo lefe" cikin mamaki momma tace "shine ba sanarwa hanne? Yanzu yaushe ne d'aurin auren?" Hanne tace "nan da sati biyu kuma a kaltungo zamu zauna".........

Kai momma ta gyad'a tare da yi mata adu'an zaman lafiya, hanne ta mike ta wuce tana amsawa a zuciyarta, bayan wucewanta ne momma ta shiga tunanin inda zasu samu wata mai aiki me amana da gaskiya irin hanne ko ma fiye da ita............

"Yaaa salaam" ta furta tana me kara kallon fuskan wayanta 20 miss calls na Musharraf shi da baya kiran mutum fiye da sau biyu!!! Danna kiranshi tayi amma a kashe tayi ta nemanshi bata

samu ba Haka ta zauna jugum cikin tunanin wani hali yake, ita ba da gaske take mishi ba ai ko maza sun kare ta gama zama da mutum irin Mahmoud amma da gaske ta yafe mishi duk laifin da yayi mata...........

******

A yau suke da nufin barin taraba state jakukkunan kayansu guda uku suka fitar sulaimi da khairi se kuka sukeyi haka dada da ummi 'maman sulaimi' ma zaman shekaru dayawa rana d'aya ace za'a rabu da ciwo kuma zaman amana sukayi...........

Haka suna ji suna gani suka rabu baba ne ya kira musu napep shata har roadblock inda ake hawa motocin tafiya, ba su kara minti biyu ba suka wuce, sienna suka samu se suka kama back seat gabad'aya wato guda uku, khairi, dada da Abul suka zauna a sit, Abul ya d'auki nabeel inda Khairi ta d'auki nabeela................

Awanni kusan 7 ya kaisu gombe daga cikin jalingo sbd rashin hanya sam hanyar ba kyau, tunda suka hau motan drivern yake saka wa'azi na malamai daban daban akan marayu, cin hakkinsu da hukuncin masu cin kud'i da gadonsu, sossai jama'ar motan suka natsu suka ji har suka isa.................

Suna sauka tasha Khairi ta tsayar da drivern inda ta bashi labarinsu In brief, sannan ta kara da "muna so ne ka taimake mu, mu samu gida karami daidai na talaka mara tsada mu saya" girgiza kai kawai drivern keyi yana mamakin halin rayuwa seda ta kai aya tukun ya sauke ajiyar zuciya yace "kar ki damu zan taimakeku nima ina dillalancin gidaje akwai wani gida da zan sayar wa wani dama se mu je ku gani".......................

Godiya sossai suka mishi ya d'auke su a motanshi har tudun wadan fantami chan ciki suka shiga zuwa wani karamin gida me d'akuna biyu d'aya a chan ciki se d'aya a zaure gidan. gidan jan kasa ne irin ginin gomben nan filin tsakar gidan d'an karami ne sossai da karamin bayi, amma duk an shimfid'e da siminti se kitchen na langa langa.................

Sunyi ciniki inda ya ce su kawo dubu d'ari nan ma ya rage musu sossai don sossai suka bashi tausayi, haka Dada ta cire kud'in ta mika mishi ya kirga tare da komawa mota ya d'auko musu takkaddun gidan ya damka musu Abul da khairi suka saka hannu, suka ma drivern godiya ya wuce...............

Gidan ba komai se wearing na nepa hakan ya sa Dada ta damkawa Abul 15 thousand inda khairi ta rubuta mishi abinda ze sayo musu na kwanciya da anfanin gida, fita yayi ya tafi..................

*******

Bayan yayi ta kiran momma bata d'aga ba se kawai yayi jifa da wayan cikin takaici da haushin kanshi, rayuwanshi gabad'aya na da ya shiga dawo mishi daki daki, wani irin kuka ne ya zo

mishi amma yana ta kokarin mayarwa, kukan ne ya kwace mishi tuna irin ba'kar wahalan da momma ta sha a kanshi ba irin sana'an da batayi ba don ganin ta ceceshi amma se da mahaifinshi ya tabbatar ya tura shi prison tare da azaba me tsanani...............

Sossai yayi kukan tukun yaji zuciyarshi ya d'an yi sanyi a duk lokacin da ya tuna rayuwanshi na baya se yayi irin wannan kukan, mikewa yayi ya fad'a wanka se da ya share akallah 40mins a bayin tukun ya fito d'aure da sea green towel a kwankwanso da wani fari a kanshi yana tsane gashin kan nashi, a gaban dressing mirror ya yada zango tare da jan kujeran ya zauna...............

Hand dryer ya d'auko ya busar da gashinshi tare da shafa masu mayukansa masu tsada, yana gamawa da kai ya dawo jiki inda ya shafa man sama sama tare da feshe fatan jikinshi da mahaukatan turarukanshi, yana ganawa ya nufi wardrobe d'inshi ya zaro wani three quarter blue da sleeveless shirt black d'aukan kwalin cigarette d'inshi yayi da liter ya karasa inda ya hurgar da wayan shi ya d'auka tare da kunnawa.................

A tsanake ya gangara stairs d'in gidan nashi zuwa kitchen dake kasa ta kofan baya ya fita zuwa karamin garden d'inshi dake gidan a chan ya samu wuri ya zauna kan grass carpet tare da kunna tabanshi ya fara zuka, kallon time yayi almost 12 danna kiran momman yayi luckily kuwa ya samu ringing biyu ta d'aga.............

"Am soo sorry momma" ya furta cikin sanyi da shagwa'ba murmushi tayi me sanyi da har yaji tace "apology accepted" ya kara cewa "plz momma ki janye maganganunki na d'azu plzzzzzz" tace "na ki, I thought kana office oya concentrate in ur work" dip ta kashe wayan ta barshi da waya a kunne murmushi yayi tare da saukewa ya san wasa take mishi tun farko daga tune d'inta kuwa se yanzu yaji natsuwa ta sauko mishi, ci gaba da shan tabanshi yayi................

*****

Yau ne gobe ne, yau ne gobe ne tun suna sa ran ganin Abul har suka cire hankalinsu ya tashi sossai gashi su nabeel sun fara kukan yunwa, har akayi isha Abul be shigo ba mikewa khairi tayi ta fara safa da marwa, ganin takwas yayi yasa ta fara hawaye innalillahi wainna ilaihi rajiun take ta maimaitawa a zuciyanta kallon Dada dake share hawaye ba tare da tace komai ba tayi tare da cewa "Dada bari In dubowa su nabeel ko awara ne a wajen nan in zo"..................

Dada tace cikin tsoro "A'a khairi mu jira dawowan Abulkhairi d'in de" khairi ta share hawayen idonta tace "ba nisa zanyi ba, In har ban samu abu anan kusa ba zan dawo" hawayen idonta Dada ta goge tana gyad'a kai a hankali tace "Dan Allah ki dawo In baki samu ba" Kai khairi ta gyad'a tare da sa kai ta fice, bayan ta kar'bi 500 wurin dadan, bata kuwa yi nisa ba taga mai awara nan ta tsaya ta sayi na 200, ta karasa wani shago dake gefe ta sayi pure water bag d'aya sbd kama ruwa ga sallolin kansu ma duk basu sauke ba sbd ba guga a cikin rijiyar dake manne da toilet dinsun................

Sannan ko akwai gugan ba butar da zasuyi alwalan dashi, bayan ta gama sayan abinda zata

saya ne ta fara tambayar mutanen wurin ko sunga wani yaro me kama da ita, kowa se yace mata a'a wani ne daga karshe ta samu yace mata ya ganshi ya tsare machine ya hau, godiya ta mishi tare da komowa gida a inda ta barsu nan ta samesu, awaran ta bud'ewa su nabeel a take suka fara ci hannu baka hannu kwarya................

Ita kam bata bi ta kan awaran ba ta d'auki ruwa tayi alwala tare da bud'e jakansu ta fiddo wani zaninta ta shimfid'a tare da tada sallah, dada ma alwalar tayi da taimakon nabeel ta tsaya kusa da khairin tare da tada nata sallahn, bayan khairi ta idar lokacin su nabeel sun gama ci tare da bajewa kan varendar tsakar gidan har bacci ya fara d'aukansu Dada na zaune gefe tana azkar adu'anta d'aya Allah ya dawo mata da d'a gida lafiya................

D'akinsu ta nufa tare da shimfid'e bargo mara nauyi a kasa ta d'auko nabeel da nabeela ta kwantar da su a Kai ta fito ta janyo kofan sbd sauro dama bata bar kofan a bud'e ba tun zuwansu, wurin Dada ta nufa ta zauna tare da d'auko wani kullin awaran da pure water tace "Dada bismillah da nyamdu en nyama"( ga abinci mu ci).................

Kai Dada ta girgiza tare da cewa "bazan iya ba khairi, ko wani hali d'ana ke ciki? Nima nayi kuskuren barinshi fita shi kad'ai a wannan gari da be san kowa ba, oh wani irin IGIYAR RAYUWA ne wannan? Daga wannan se wannan? Yaushe ne zanga fari a rayuwana? Iya tsakankanin zama na da umaru? Ya Allah na tuba in wani laifin na aikata a gareka ka yafemin ya Allah, ka kular min da d'ana ya Allah na tabbatar yana inda be bukatar taimakon kowa se naka ya Allah ka taimakeshi........"..............

Kuka sossai Dada ta fashe dashi khairi ma na tayata wayan Abbansu dake hannunta ne ya fara kara d'agawa tayi ganin baba ne suka gaisa inda ya tambayesu ko sun samu gida? Cikin rawar murya ta amsa mishi, a tsorace yace "lafiya?" "Abulkhairi majji(ya 'bata) baba" ta karasa da kuka "innalillahi wainna ilaihi rajiun" baba ya dinga nanatawa "ta yaya? Me ya faru? Ya akayi Kuka rabu?" Kit wayan ya mutu ba tare da ta ba baban amsa ba.......................

Dada kuma bata da numbern baban sulaimi, haka sukayi zaman kurma kurma har 12 ganin sauro na shirin cinyesu ne yasa Dada ta cewa khairi "kamani zuwa d'aki" kama ta tayi har kan shimfid'ar da tayi musu suka kwanta, sun jima suna juye juye kan bacci yayi awon gaba da su.........

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️2️⃣4️⃣▶️2️⃣5️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Three days later

Sossai suka susuce damuwa yayi musu tsananin yawa a cikin kwana ukun nan, har gwara ace mutuwa Abul yayi da irin wannan 'batan shiru shiru sun yi zaman jira har sun gaji sun yi kuka sossai suna kuma kai wa Allah kukansu, a kwana na biyu da 'batanshi khairi ta samu ta lalla'ba Dada inda da kyar ta barta ta tafi police station tayi musu bayani amma se suka nemi raina mata wayau bayan kud'in da ta basu................

A zuciye ta dawo gida tana takaicin banzan hali irin na wasu daga cikin forces na nigeria, a kwana ukun da sukayin nan suna rayuwa ne a matukar takure ba abinda suka saya na anfanin gida kullum sede ta fita ta saya musu abinci shima ba wani na kirki ba, inda sukayi sa'a sun sami makwabciya me matukar mutunci da karamci maman hamdeeya, ta shigo musu sau biyu ta kuma turo musu abinci sau uku ganin yanayin rayuwansu..............

Duk da ba sanin su tayi ba, amma halin rayuwansu yana bata tausayi duk shiganta sau biyun nan samunsu cikin wani hali take, nabeel da nabeela duk sun zama wani iri kaman ba su ba masu wasa da dariya amma sun koma shiru shiru...........

**
Ta bangaren Musharraf kuwa ya ci gaba da rayuwanshi yadda ya saba na kad'aici da shan taba da ya zama mishi aboki kuma kawa da ya ji yana shiga damuwa in ya tuna rayuwanshi na baya se ya zauna ya d'irki na d'irka In ya gaji kuma se ya mike yakai kukanshi ga Allah..........

****
Yau ma kaman kullum zaman shirunsu suke ko taburma ba su da se kayansu da suke shimfid'awa su zauna ko shara gidan be ta'ba gani ba sbd ba tsintsiya, guga da sukaji ana sayarwa a unguwan suka saya se wani bokitin da ta aro musu wurin maman hamdeeya da shi suke wanka suyi alwala da guga...............

Ajiyar zuciya khairi ta sauke tare da kallon Dada tace "dada zaman da mukeyin nan ba shine mafita ba, kud'in da muke kashewan nan tafiya suke ba wadda ke shigowa In har kud'in nan suka kare a haka Toh ba karamin tashin hankali zamu shiga ba, adu'a zamu ci gaba da yiwa d'an uwa, in shaa Allahu baze fad'o kasa banza ba"...................

Ajiyar zuciya Dada ta sauke kan ta fara magana "na san hakan khairi kin rigani furtawa ne kawai ni ce ya kamata in karfafa muku gwiwa a matsayi na na mahaifiya kuma babba amma na sawa kaina damuwa wadda ya shafi har ku, ni uwa ce na fi jin zafin 'batan Abulkhairi akan rasuwar mahaifinku, ban san wani hali yake ciki ba, ban san wani rayuwa ze fad'a ba, yana raye ko mace Allah shine kawai masani" hawaye ta share kan ta ci gaba...............

"Ki shiga gidan maman hamdeeya ki roke ta ko Allah ze sa ta raka ki kasuwa ki sayomana abinda ya kamata se kuma muga sauran chanjin ko Ze ishemu Sana'a" da "toh" khairi ta amsa kan ta mike ta shige d'aki ta d'auko hijab d'inta a natse ta fice tana kallon su nabeel da suke kwance gefen Dada abin tausayi, da sallama ta shiga gidan, wata chocolate color mata ce ta amsa mata wacce na tabbatar itace maman hamdeeya sbd d'umbin fara'a.................

Da ta tari khairi dashi cikin tsokana tace "nayi fushi se yau zanga idanunki?" Murmushi khairi tayi tukun tace "afuwan maman hamdeeya ba gashi na shigo ba, Ina er fara?" Ta karasa tana dube dube "yanzu suka fita da dadynta zasu gidan kakanninta, ki karasa parlor mana bari In gama shanyan nan gani nan zuwa" cewar maman hamdeeyan, murmushi khairi ta saki kan ta nufi parlorn maman hamdeeyan.................

Duk da baza a kirasu masu kud'i ba amma kai tsaye za'a iya kiransu masu rufin asiri gidan ciki da parlor se band'akuna biyu d'aya ciki d'aya a waje, se karamin get d'insu na karfe ba kaman su khairi masu kofan buhu ba, bayan ta gama shanyan ta shigo parlorn da sallama, suka gaisa inda khairi tace "maman hamdeeya dama zuwa nayi in roki alfarma dan Allah in da hali Ina so ki

rakani kasuwa In sayo mana d'an abun anfani"..................

Murmushi maman hamdeeya tayi kan tace "haba khairi raka kasuwa ne se kin ta had'a ni da Allah? Dama yanzu gama shanyan nan da nayi wanka kawai zanyi in tafi kasuwa hakan ya sa ma na aika hamdeeya gidan kakanninta, ga remote yi kallo kan na watsa ruwa se mu wuce" murmushi kawai khairi tayi kasancewarta ba me yawan magana ba....................

Bayan ta fito ne suka wuce seda suka biya gidansu ta kar'bi kud'i wurin Dada kan suka wuce, sun jima sossai inda suka saya abubuwa masu yawa kusan fiye da rabin kud'in sun sayi kananan katifu uku, buta, bucket, tukwane biyu, karamin turmi, ludayi, plates, spoons, labulaye masu saukin kud'i sossai sbd sauro, kondon kife kwanoni, murhun karfe, karamin taburma, da dai abinda baza a rasa ba.................

Ganin da d'an sauran kud'i yasa ta ware 50k ta ajiye, sauran ta auna musu d'an kwanon shinkafa, masara, wake, borkono, ta sayi maggi da gishiri, daddawa, kuka, ku'bewa busasshe da 'yan d'anyun kayan miya ba masu yawa ba se albasa.............

a wheelbarrow suka zuba duka kayan ya kaisu har bakin hanya suka samu taxi suka wuto gida, godiya sossai sukayiwa maman hamdeeya kan ta wuce, khairi ta cire khimar nata ta hau shirya duk abinda suka saya a inda ya kamata, ta saka labulayen da igiyoyin da ta saya da su, ta sa katifun tare da shimfid'e musu bedsheets da suka zo dashi a kayansu, duk abin kitchen ta shigar..............

Nabeela ta kama ta raka ta gidan maman hamdeeya inda suka samu hamdeeyan ma ta dawo da gudu 'yar yarinyar da bata wuce 3years ba tazo ta rungume khairi d'an shigowan da suka yi da mamanta har ta saba da ita sossai, juya ta khairi tayi a sama tana mata wasa sossai yarinyar ta ringa dariya tana kiran maama, da ita a hannu suka karaso ciki.............

A kitchen suka samu maman hamdeeyan tana tuka tuwo kujeran tsuguno ta jawo ta zauna kusa da ita tana cewa "san da aiki maman hamdeeya" cikin fara'a tace "yauwa ai ke za'ayiwa sannu na san kin aikatu" murmushi kawai khairi tayi tana sauke hamdeeya dake ta tsalle a cinyanta tana mikawa nabeela hannu, wasa suka fara inda khairi ta maida hankalinta kan maman hamdeeya..................

"Maman hamdeeya kina ganin wani sana'a zamuyi a unguwan nan wadda ze kar'bu?" D'an shiru maman hamdeeya tayi tukun tace "Ina ga kuyi na kayan miya, irinsu maggi, borkono, kuka, kubewa, gishiri, busasshen tattasai, daddawa, albasa, attarugu da dai sauransu ku kukulla irin na goma, ashirin da hamsin zan taya ku tallah a unguwan nan samu a san kuna sayarwa sbd su ne ba'a samun masu sayarwa sossai a layin nan"................

Cikin tsantsan farin ciki khairi tace "mun gode sossai maman hamdeeya Allah ya biyaki, mu kam muna sa'an makwabta" su hauwa da mamanta ne suka fad'o mata a take hawaye suka gangara a idonta bata san sadda ta furta "Allah ka saka mana" ba, da mamaki maman

hamdeeya ke kallonta a natse cikin damuwa tace "lafiya kuwa khairi?" Share hawayen tayi kan tace.............

"Klau kawai na tuna da rayuwan mu na baya ne" "wannan ko wani irin rayuwa ne da ze saka ki kuka lokaci d'aya haka?" Ajiyar zuciya ta sauke "hmmm zan baki labari amma ba yau ba, a Ina ake sayar da itace?" "Toh shikenan, daga gidan nan ki Kirga gida d'aya, biyu, uku shine na masu sayarwa" Kai khairi ta gyad'a kan ta mike tana kallon nabeela tace................

"Nabeela 'yan dilla"(mu tafi), juya kai nabeelan tayi kan tace "Eyyah useni Adda khairi acham ha d'o min d'o fija be hamdeeya"(Eyyah dan Allah Adda khairi ki barni a nan muna wasa da hamdeeya) ta'be baki khairi tayi kan ta juya ta fice seda ta je ta saya itacen tukun ta juyo gida tana shiga ta tura nabeel gidan maman hamdeeya don ta san baza ta ta'ba cutar da su ba............,..

Girki ta d'aura inda tayi musu tuwon masara da miyar busashiyar kubewa tana yi suna er hira da Dada, anan take fad'a mata yadda sukayi da maman hamdeeya akan Sana'an da za suyi ilai kuwa ta aminta da hakan tace se gobe khairi ta koma kasuwa tayo sayyayan da sauran kud'in hannunta, da Toh kawai ta amsa, seda ta ga magrib ya gabato tukun ta shiga ta taho da su nabeela sukayi sallah sukayi karatun da suka saba tun suna happy family seda sukayi isha tukun suka baje abincinsu suka ci suka koshi kan hira ya biyo baya................

****

Zaune take kan d'an sallayanta sanye da hijab d'an karami fari sol hannunta a sama tana adu'a hawaye na zuba daga idonta, turo kofa akayi aka shigo da sallama, da tsantsan mamaki momma ke kallon zahra da take ta kuka tana motsa baki, da sauri ta karasa ta zauna kusa da ita jin hakan yasa ta shafa adu'anta tare da fad'awa jikin momma ta kuma fashewa da kuka..............

A natse momma ke shafa bayanta cikin rarrashi tace "me nene damuwanki takwara? Me akayi miki? Wa ya 'bata miki rai?" Zahra tace "granny mommy na na tuna friends d'ina ko wacce tazo mommy tayi min kaza tayi min kaza, mommy kaza amma ni kam se de granny, paapi ko Anties" ta karasa da wani hawayen.............

Momma ta share mata cikin tausayawa tace "zahra kwata kwata shekarunki nawa da zaki zauna kina wannan tunani? Yarinya dake? Ba na ce miki maman ki ta rasu ba? Toh me ya kamata kiyi mata? Zahra tace "adu'a nake mata don akwai hadisin da akayimana a school an ce

"عن ابي  هريرة رضي الله عنه قال: قال رسول الله صلى الله عليه  وسلم 'إذا مات ابن ادم انقطع عمله الا من ثلاث، صدقة خارية أو علم ينتفع به أو ولد صا لح يدعو له"

"An kar'bo daga baban huraira Allah ya yarda dashi yace, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi yace 'idan mutum ya mutu dukkanin ayyukanshi sun yanke se guda uku 'Sadaka mai gudana' 'ko ilimi wadda ake anfani dashi' 'ko d'a na gari wadda ke mishi adu'a"

granny ina mata adu'a kullum kuma Ina son Allah ya bani kud'i masu yawa don na yi mata sadakatul jariya malam yace sune rijiya, bohol, massalatai, bishiyu ko qur'anan da ake karatu da su a massalaci................

Karkata fuska tayi a shagwa'be tace "na sha yiwa paapi magana tunda yana da kud'i ya bani in mata ko yayi mata amma kullum sede ya had'e rai, ko ya daka min tsawa, granny shima In mishi adu'ar rage fushi?" Ta karasa da iyakar gaskiyarta duk da hawaye ya gangaro daga idon momma amma seda tayi murmushi tana sharewa ta gyad'a kai...............

Sossai take mamakin wayau da Allah yayiwa zahra da kaifin basiranta ko da shike d'an na gada yafi d'an na koya halinsu d'aya da Musharraf yana karami, lallashin zahran tayi har bacci ya sureta kan ta mike ta fito, tana shiga room d'inta ta d'auki wayanta ta danna kiran musharraf bayan sun gaisa tace cikin kakkausan murya "na baka nan da wata biyar ka fidda mata cikin waenda suke binka da sunan soyayya gasu dayawa cikin dangi da waje In ba haka ba kuma na aura maka wacce raina yaso" bata jira cewarshi ba ta kashe waynta tana runtse ido ta san ta saka shi a mawuyacin hali amma ba yadda ta iya, dolene ya samawa zahra farin ciki ya kuma samwa kanshi natsuwa ba duka aka taru aka zama d'aya ba.................

*barkanmu da sallah en uwa, fatan anyi sallah lafiya? Allah ya maimaita mana, Ameen *

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️2️⃣6️⃣▶️2️⃣7️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Wayan ya jima sakale a kunnenshi bayan ta kashe kan ya sabule ta a hankali ta fad'i kan katifan gadon da yake kai ba tare da ya bud'e idonshi dake lumshe ba ya dafe kanshi da hannunshi, cikin tsananin tashin hankali yake murza goshinshi da hannunshi dake kai.............

Aure fah Aure kuma? Yanzu? Daga muryan momma ya fahimci wannan karon da gaske takeyi, gaskiya be shirya ba, ya gama aure, ya rufe babin mace a rayuwanshi ya gama yarda da mata a duniyan nan, hawaye ne ya cika idanunshi, a fili yace "Surayyah baki min adalci ba, bakiyiwa kanki adalci ba, Allah ya Allah" gam ya runtse idonshi yana kokarin hana hawayen idonshi gangarowa................

Hannunshi ya mika bedside drawer ya janyo kwalin Aspen tare da liter ya kunna ya fara sha ba ji ba gani, yana tuna masu sonshin maryam, salima, zainab, Afreen. Shi duk cikinsu ba wacce tayi mishi dabiunsu duk na en boko ne ba na kad'an kad'an ba ze iya rantsewa ko za'a shakuresu baza su ta'ba karanta maka fiye da izu biyu na qur'ani ba da ka ko da qur'anin, Lallai yana cikin tsaka mai wuya................

****

Washegari da sassafe khairi ta tashi dama akwai sauran tuwon jiya da miya, dumame tayi musu me daadi tana saukewa ta d'aura ruwan wanka ta fito ta fara shara tana gamawa ta juye ruwan ta taso nabeel da nabeela tayi musu wanka kan tayi nata ta kuma surkawa Dada ta kai mata, seda ta taimaka mata ta shiga tukun ta dawo ta shirya cikin wani atampha ganta/maso da shima yaji jiki ja da green d'inkin riga da skirt seda hawaye ya zubo mata tuna wadda ya mata d'inkin (Abulkhairi)................

Ta d'aura d'ankwalin a kanta lokacin har su nabeel sun shirya cikin kod'add'iyar shaddansu iri d'aya, abinci ta shigo musu da shi tare da ajiye roban yaji a gefen nata da na Dada don dukkansu masu son yaji ne, su nabeel sun jima da fara cin abinci kan Dada ta fito ita ma atampha marar tsadar kudi ta saka riga da zani be wani kod'e sossai ba zama tayi, suka fara cin abinci da bismillah suna gamawa bayan sun wanke hannu sun shaa ruwa khairi ta dubi Dada tace....................

"Dada Ina ga ya kamata mu koma makaranta, su nabeela kam ma boko da islamiyya ya kamata mu mayar da su" ajiyar zuciya Dada ta sauke tace "toh khairi In kin je kin sayo abinda ya sawwaka na sana'a In kud'in ya saura se mu duba maakarantun a cikin unguwan nan don bana so kuyi nisa"................

Murmushi khairi tayi cikin jin daadi tace "ze yi ma Dada makarantun gomnati ba a Biyan wasu abin kirki haka islamiyya ma be wuce kud'in laraba ba" Kai Dada ta gyad'a tsam khairi ta mike ta d'auki roba hijab d'inta red color ta sanya tare da zura roba silifas d'inta tana duban Dada tace "na tafi kasuwan Dada" dada tace "zaki gane ko? In fa baki gane ba ki dawo fah" Kai khairi ta gyad'a se kace dada na kallonta, ta fice Dada na binta da adu'ar tsari....................

A natse take tafiya har ta samu napep ta tsare ta hau ya kaita har bakin kasuwa ya ajiye, 200 ta mika mishi ya zaro chanji ya bata se bata had'a cikin kud'in hannunta ba ta soke shi cikin d'ankwalinta don ta san halinta In chanji sukayi yawa a hannunta zubewa suke, straight ta nufi layin masu sayar da abubuwan da ta zo saya  don bata manta ba, ita da wuya tazo wuri sau d'aya ta manta..................

Taje ta saya kuka, daddawa, da kubewa duk na 2/200 ta d'ago hannunta tana zarar masa kenan taji an wabce kud'in gabad'aya tare da artawa a guje, ido ta zaro waje tare da bin bayan saurayin tana ihun a taimaketa kud'inta duk cikin masu sayar da abu a layin ba wadda ya motsa don sun san in ana irin wannan abun kace zakayi taimako kaima yasheka za'ayi........................

Se daidai kun matasa dake tsaye ne suka bishi da niyyan kamashi amma ko sama ko kasa an nemeshi an rasa, hannu khairi ta sa akai tana ambaton sunan Allah hawayen idonta kuma yaki tsayawa, ganin da gaske bashi ba labarinshi yasa ta sulale kasa dabas ta fashe da kuka

bilhakki, sossai tayi kuka har mutane dayawa suka tausaya mata amma ba me cire naira biyar d'inshi ya bata sbd wannan rayuwa kowa kanshi ya sani.................

Wasu sede suce "se hakuri yarinya ze biyaki a inda ba kud'i" bata kula kowa ba tayi kukanta ta gaji tukun ta mike ta nufi me kayan daddawa da ta fara saya dama ta riga ta mika mishi 1000 yana ganin tana share hawayenta yace "yarinya In sa miki a leda?" Bata kula shi ba se fisge dubu d'ayanta da tayi, ta juya a fusace tana jin yana dariya yana cewa "ba ni na kar zomon ba ko rataya ba'a bani ba ehe" wani sabon hawaye ne ya gangaro mata jin makwabtanshi sun kwace da dariya................

Sauri sauri ta isa bakin hanya ta tsare napep ta fad'a mishi unguwansu tare da shigewa, tana jin zafi a zuciyanta gwara zafin kwace kud'inta da zafin abinda en kasuwancan sukayi mata, ta tsani wulakanci tana da tsan tsan riko duk da tana da saurin yafiya adu'a ta ringa musu Allah ya had'asu da ibtila'i fiye da nata da na en uwanta, kukanta ta dinga yi har suka iso...................

Da kud'in cikin d'ankwalin ta ta biyashi tana ji yana cewa "malama rayuwan yanzun se hakuri fah" bata kula shi ba ta fad'a gidansu da gudu ta zube jikin dada tare da kuma sa kuka In ta tuna shine last kobonsu ashe gwara ma da Allah ya sa ta sayi d'an kayan abinci wadda In har ya kare bata san inda zasu samu kud'in sayan wasu ba..................

Cikin tashin hankali Dada ke shafa fuskanta da ya kumbura suntum tsabar kukan da ta ci take cewa "me ya faru khairi?" Shiru khairi tayi har dada bata san sadda ta dakawa khairi tsawa ba "nace me ya sameki ummulkhairi?" Ta karasa da hawaye a fuskanta hannunta kuma na rike gam da ita cikin kuka khairi tace "Dada an kwace kud'in gabad'aya dada, wani marar imani dada ya wabce kud'in yayi tafiyanshi"....................

Salati Dada ta saki tana tafa hannu sam batayi wani kukan ba, se cewa da tayi "khairi kukan ya isa haka Allahn da ya bamu wanchan d'in yana sane da mu kuma bakin da Allah ya tsaga baya hanashi abinda ze Sa a ciki sede In ya rena".................

Shiru khairi tayi tana ajiyar zuciya a lokaci d'aya ta sulale ta kwantar da jikinta kan taburma tare da d'aura kanta kan kafan Dada tana sauke ajiyar zuciya inda hannun Dadan ke kanta tana shafawa bata wani jima ba bacci ya sureta................

*****

"Hajiya zulai barka da yammaci ya gd ya yaran?" Banji abinda aka ce daga d'ayan 'bangaren ba nade ga momma na murmushi cikin dariya tace "aiko kaman kin sani daughter nake son ki turomin tyi min kwana biyu" banji mai aka kuma cewa ba, se godiya da momma tayi tare da kashe wayan.............

Hajiya Aisha ta kira yadda sukayi da hajiya zulai haka sukayi da hajiya Aisha, haka ma hajiya rabi da hajiya Asiya, tana gamawa ta saki murmushi a fili tace "wannan karon kam sede ka

fashe musharraf dear" ya ce mata ze zo ran Friday gobe kenan shi yasa ta jaji'bo mishi gayyan en mata masu tsananin sonshi inda biyu suke 'ya'yan yayyun mahaifinshi biyun kuma 'ya'yan kannenta...................

Har gwara 'yayan kannentan ma yana basu fuska sabanin yaran yayyun mahaifinshi da yake jin haushinsu ba wai tsana ba, maryam er hajiya zulai da Alhj nasir Adam ne wa ga mahaifinshi, se salima er hajiya Aisha da Alhj Ahmad Adam shima wa ga mahaifinshi, se Zainab tahir Abubakar er kaninta se Afreen Isma'il er kanwanta...................

Mayen son Musharraf ke kad'asu amma be ta'ba basu fuska ba se tsan tsan wulakanci da yake zuba musu ba ji ba gani, mikewa tayi ta nufi kasa don bada sakon abinda za'a sayo mata wadda zata girkawa d'an nata sbd jirgi ze biyo wannan karon kuma shigowar safe..................

******

Bayan ta tashi daga bacci ne take tambayar dada Ina su nabeela bata gansu ba, Dada tace "suna gidan maman hamdeeya" cikin fad'a khairi tace "haba dada ya za'ayi su tafi su barki ke kad'ai bayan baki gama sanin gidan ba In wani abu for god sake ya sameki fa?" Murmushi dada tayi tana cewa "kar ki d'auko wani hali da ba naki ba ki yafawa kanki ummul ki sawa zuciyarki salama komai ya faru da ke damu yana cikin igiyar kaddaranmu da se yanzu muka iso cikinta...................

Mu godewa Allah wasu tasu IGIYAR RAYUWAN ta ninke namu ta shanye ki yawaita istigfari hailala, da salati zakiji sauki, sannan yanzu ba inda ban sani a gidan nan ba gidan da ba wani girma yake dashi ba kuma akallah yau kwana na biyar cikinta taya za'ayi bazan san ko Ina ba!!!!"....................

Shiru khairi tayi kanta kasa gaskiya ba wacce ta kai mahaifiya a rayuwa duk da ba kallonta take ba amma ta fahimci halin da take son jefa kanta, mikewa tayi tana cewa "Toh na gode dada bari In d'aura mana abincin rana In na gama se in dubo su"  murmushi kawai dada tayi, a natse ta hura wuta ta d'aura musu shinkafa da mai da yaji.................

Tanayi suna hira jefi jefi da dada har ta gama ta kwashe musu a d'an kulansu tare da d'aurawa kan karamin tiren silvernsu ta sa cokula ta ajiye kan tabarman da dada take duk da rana tsaka ne amma garin sam ba rana se duhu kaman hadari ruwan se yawo yake a sama, fita tayi ta shiga gidan maman hamdeeya daga bakin kofa ta fara jin kamshi na tashi kasancewar maman hamdeeya na sana'an turaruka humras, collecture, turarukan wuta da na tsuguno hakan yasa kana doso cikin gidan kamshi ze bule ka................

A lokaci d'aya kuma ita tela ce, da sallama khairi ta shiga da gudu yaran suka zo suka rungumeta 'nabeel, nabeela da hamdeeya' se kawai ta suri hamdeeya ta fara juyi da ita se wangale hakori take, da murmushi maman hamdeeya dake had'a turarukanta a kan varender ta tare ta "barka da shigowa uwar alkhairi idonki kenan?"................

Khairi na kokarin zama gefenta bayan ta ajiye hamdeeya sun ci gaba da wasan su tace "hmmm kede bari maman hamdeeya wani ibtila'in ne ya sake sauko mana d'an kud'in da ya saura mana duniya wani ya kwace" salallami maman hamdeeya ta fara tana tafa hannu inda take tambayar khairi garin yaya hakan ya faru? Tsab khairi ta bata labari har da abinda sukayi niyyan yi da sauran kud'in wato komawa school da islamiyya..............,

Zagin da maman hamdeeya ta yiwa wancan saurayin ko kud'inta ne albarka, "dan Allah khairi ki ban labarin rayuwanki?" Khairi tace "yau kuwa don na yarda dake d'ari bisa d'ari baza ki ta'ba cutar da mu ba, amma bari inje In ba su dada abinci, Ina zuwa" ta mike ta sa su nabeel a gaba suka fice hannunta d'auke da hamdeeya..............

Bayan sun gama cin abinci sauran da ke cikin kula ta kullawa mai da yaji ta bawa nabeel suka fice zuwa gidan maman hamdeeya kaman yadda suka zo Dada kam ma bacci tace zatayi, da murna maman hamdeeya ta karbi abincin ta fara ci inda take cewa khairi "kaman Kin san wannan shine favorite na" murmushi kawai khairi tayi, bayan maman hamdeeya ta gama cin abincinta ta sha ruwa ta fuskanci khairi tace................

"Ina jinki" a natse khairi ta fara bata labarin rayuwansu idonta na kan su nabeel tun daga kan labarin iyayensu zuwa nasu bata boye mata komai ba, da mamakin khairi se gani tayi maman hamdeeya na kuka tsakaninta da Allah share hawayen idonta khairi tayi tana murmushi me ciwo da kyar ta samu maman hamdeeya tayi shiru a hankali tace "da d'an sana'an da nakeyi nayi alkawari daga yau na d'auki nauyin karatun islamiyyan su nabeel har su gama" cikin tsantsan farin ciki khairi ta rungumeta dama karatun addinin shine yafi damunta..................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad Gureen

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️2️⃣8️⃣▶️2️⃣9️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Washegari

Misalin karfe 10 na safe jirginshi yayi landing a birnin gombe, bayan ya gama checking ya janyo brown medium size trolley d'inshi tafiya yake cikin izza da tsantsar takama daga nesa In ka hangeshi zaka san lallai gayen ma'abocin gym ne don yadda kayan da yasaka suka mugun fidda yanayin jikinshi................

sanye yake da farin long sleeve shirt masu buttons da black crazy jeans amma ba irin crazy me munin nan ba, rigan sossai ya kamashi ya 'balle buttons biyu na sama, kanshi da ya sha gyara se kyalli yake daga nesa, tun fitowanshi ya sheda motar mommanshi sede ya tamke fuskan nan tamau sbd ba ita bace yake hange..................

Da gudu zahra ta taho ta rumgume shi dukawa yayi ya d'aga ta sama yana juyi da ita duk hankalin en matan wurin ya karkata gareshi wasu na kallonshi da tsantsan burgewa wasu kuma na kallonshi da tsantsar so dariyan da yakeyiwa ershi ya mugun tafiya dasu, yana sauke zahra

ya kama hannunta suka karaso jikin motan yana karewa Afreen dake tsaye jikin motan kallo..................

Sanye take da long sleeve peach color shirt me buttons kaman na maza ta kama kasan ta d'aureshi a cikinta har  fari kal din vest dinta na bayyana, se straight skirt brown me tsagu har cinya se turban brown, seda ya kare mata kallo daga sama har kasa kan yaja tsiririn tsaki ya bud'e gaba ya shige ko sannu da zuwanta be amsa ba..................

A ranshi yake tunanin yanzu wannan ce ze aura? Gsky ya cire ta lissafi Allah yayishi me tsananin kishi shi kallon tsirara ma yake mata don ba maraba a fili ya saki tsaki, tunda suka gaisa da drivern momma be kara magana ba har suka isa gida ko gaisuwan Afreen d'in be amsa ba haka duk surutun da zahra keyi be tanka ta ba dama ta saba...................

Ana parking be jira komai ba ya sauka ya nufi main parlor yana ganin yadda Afreen ta bishi da ido kaman zata cinye shi, da gudu zahra ta zo ta rike hannunshi suka karasa tare, tare da barin Afreen da dakon akwati. "Salamu alaikum my momma I miss y..........." maganan ne ya makale ganin Maryam, salima da Zainab baje a parlorn ko wacce taci ado kaman masu zuwa gasan kyau...............

Ba laifi dukkansu kuma kyawawa ne farare sossai irin farin gomben nan, amma duk cikinsu ba wacce ke da ki'ba ko dirin kirki, Zainab sanye da riga me had'e da wando na atampha ta cakara d'auri a gaban goshi tana zaune kan two seater hannunta rike da waya kirar iPhone X, se salima dake kwance kan doguwar kujera sanye da wando jeans pink da pink shirt d'an karami ba d'ankwali kanta se gashinta da ta raba gida biyu ta kamasu da manyan ribbons................

Se Maryam da yayiwa lakabi da er rawan kai ko ya ce mata kaza kanki da motsi tsaye gaban tv hannunta rike da remote tana chanza channel sanye take da straight gown da yabi jikinta ya fidda karamin shape dinta black hannunshi na vest, fuskanta kam mad'au yaji makeup kaman ba gobe se gashinta da tayi parking tsakiyar ka yana lilo...................

Ganinshi ya sasu tasowa da gudu kowacce na niyyar rungume shi, ganin da gaske fah suke yasa shi daka musu tsawa "what nonsense!!!!!" Birki ko wacce ta ja tana shagwa'be fuska, Zainab tace "sannu da zuwa sweet bro" a nyamutse yake kallonsu d'aya bayan d'aya akan salima ya tsaida idanunshi don a ganinshi ta fi su hankali yace "Ina momma?" A yangance cikin murmushi ganin duk cikinsu ita yayi wa magana tace "tana upstairs hamma" ba tare da ya tanka ba ya haura hannunshi rike da na zahra ya san ba me mishi wannan abu se momma yanzu ita momma cikin waennan taga matar aure?.................

******

"Dada Ina ganin zan nemi aikin aikatau sbd mu tsira da mutuncin mu"  'bata fuska dada tayi tare da cewa "inaaa khairi bazan yadda ba, ba abinda ya kai aikatau kaskanci ba wai don aikin ba a'a irin masu kud'inmu na yanzu rabi da kwatansu en wulakanci ne, ba zan juri kije inda za'a na

wulakanta ki ba, ga kuma yanayin jikinki wani abin ya faru wadda ba shine ba bazan ta'ba jin daad'i ba".................

Ajiyar zuciya khairi ta sauke tare da yin shiru tana zurfafa tunaninta kan maganan Dada ta san da gaskiyanta amma zamansu hakan ba ze ta'ba yiwuwa ba, "Dada kiyi hkr bamu da wani option bayan wannan In d'an kayan abincinmu ya kare ina kike tunanin zamu samu kud'in wasu? Sannan Dada Ina da burin ci gaba da karatu na da na kanne na, kaman yadda mahaifinmu yaci buri kan rasuwarshi, Dada na yi miki alkawari zan kula ba zan ta'ba bari wani abu ya kai ga zuciyata bama balle ya 'batan rai har wani abu ya faru, ki ci gaba da min adu'a in had'u da mutanen kirki waenda bazan ta'ba kuka da su ba"....................

Dada tace "shikenan khairi Allah ya za'ba mana abinda ya fi alkhairi" karamin murmushi khairi tayi tare da sa'ba hamdeeya dake bacci kan cinyanta a kafad'a tace "Ameen dada bari In shiga wurin maman hamdeeya" kai kawai dada ta gyad'a, khairi ta fice, da sallama ta shiga gidan ganin maman hamdeeya tayi kan keke tana d'inkin uniform da yafi kama da na islamiyya gefenta kuma nabeel da nabeela ne zaune suna cin d'an wake.................

Da murmushi khairi ta karasa tana cewa "eyye autocin dada d'an wake ake ci?" Nabeel yace "eh Adda khairi ke ma ki zo ki ci baki ji daad'in da yayi ba Ammi ce ta mana" Ammi suke kiran maman hamdeeya jin haka hamdeeyan ke cewa kuma sossai take jin daad'in hakan, khairi tace "toh shine ko tayi babu" nabeela zatayi magana kenan maman hamdeeya tace "Ke ni kyale min yara su ci abinci kin wani zo kin fitine su".................

Dariya Khairi ta kwashe dashi tare da Cewa "Lallai ma wato haka kikace? Kar ki yi wasa yanzu su jefa ki rana In de su nabeel ne" murmushi kawai maman hamdeeya tayi tana kallon hamdeeya dake hannunta tace "wai wani wankan kika kuma mata? Ai dole ta shantake tata bacci taji ruwan zafi, in kuwa ta hana mu bacci da dare ta katanga zan jefo miki ita".............

Murmushi kawai khairi tayi tare da karasawa parlor ta kwantar da ita, ta kuma fitowa ta ja kujera zata zauna kenan maman hamdeeya tace "karki zauna karasa kitchen ki d'ibo d'an wake" nufar hanyar kitchen d'in tayi tana cewa "aiko ci zan yi ba wani fulaku dan yana cikin favorites d'ina" murmushi kawai maman hamdeeya tayi bayan ta d'ibo ta zo ta zauna inda tayi niyyan zama tun farko ta fara ci....................

Bayan su nabeel sun gama sun wanke hannunsu ne maman hamdeeya tace "twins ku d'auki cooler d'in chan ku kaima dada d'an waken ta ne" d'auka nabeela tayi suka fice bayan fitansu khairi ta kalli uniform d'in da maman hamdeeya ke d'inkawa tare da cewa "wannan fah?" Maman hamdeeya tace "uniform d'in su twins ne na islamiyya" murmushi khairi tayi cikin jin Son matar tace "kin ko gama mana komai mun gode" hararanta maman hamdeeya tayi inda ita kuma ta saki murmushi..................

"Yauwa maman hamdeeya ya kike ganin aikatau a garin nan ana saurin samu?" Da mamaki maman hamdeeya ke kallon khairi tace "ba de aikatau zakiyi ba?" Cikin murmushi khairi tace

"wallahi dariya kuke ban ke da dada wai nafi karfin aikatau ne? Ni wace? Ko kin manta rayuwan yau da gobe ga masu sana'a da aikin gomnatin ma ya bare mu? Ba bu ta yadda za'ayi mu zauna haka maman hamdeeya" ta kara da maganganun da tayiwa dada.................

Seda tayi shiru tukun maman hamdeeya tace "hkne khairi kinyi tunani me kyau wai nake gani da de irin sana'un hannun nan kuka rike amma se kuma na tuna ba ku da jaari tabbas da Ina da kud'in kirki da ba abinda ze hana In baki jari duk da ba ko yaushe ake samun ciniki a sana'an hannun ba" khairi ta kara da "kuma bukatun mu ya wuce nan maman hamdeeya ko mai lalla'bawan mu baze ishemu ba"..................

D'an shiru maman hamdeeya tayi na mintuna tukun tace "ga shi kuma ban san wata dake aikin d'iban masu aikatau a garin nan ba" murmushi khairi tayi tace "ai alkhairunki yawa gareshi wadda kikayi a baya ma Allah ya biyaki, abinda nake bukata kawai ki fad'a min unguwannin masu kud'i na garin nan ni kuma In shaa Allahu zan bi gida gida da izinin Allah kuma zan samu"...................

Ba tare da maman hamdeeya ta so ba tace "toh yaushe zaki fara?" Khairi tace "gobe in Allah ya kaimu" "Toh Allah ya kaimu" cewar maman handeeya, sun d'an ta'ba hira tukun khairi ta wuce da albishir wa dada akan gobe su Nabeel zasu fara zuwa islamiyya dake nan cikin unguwan sun daga kasa ba wani nisan kirki.................

*******

Da sallama ya kutsa kai cikin d'akin na mahaifiyarshi dake tashin kamshin turarukan wutan ta masu tsananin kamshi, amsa sallamanshi tayi fuskanta cike da murmushi a gaban gadonta ya karasa ya duka tare da cewa "Barka da gida momma mun same ku lafiya?"  "Lafiya klau son ya aiki?" Yace "Alhamdulillah" d'an shiru sukayi kan tace "tashi muje ka ci abinci" cikin 'bata fuska yace................

"Momma dan Allah me ya kawo waennan yaran?" Itama 'bata fuska tayi tace "Ina ruwanka? Wurinka aka gaya maka suka zo? Sannan ni da kaina na kira iyayensu suka turominsu ba zuwan banza sukayi ba, kuma maganan da mukayi da kai d'in nan kar ka zata wasa nake maka wannan karon Musharraf ka fita idona" runtse idanunshi yayi tare da bud'esu lokaci d'aya ya watsa mata su a take sun sauya kala kau da idonta tayi tana ta'be baki................

Tana jin tausayinshi har ranta sede ta tabbatar In ba nuna mishi 'bacin ranta take ba baze ta'ba d'aukan maganan serious ba, tana mugun son ganinshi cikin kwanciyan hankali irin na ko wanni na miji dake sa'anninshi, duk da be ji daad'in yadda momman tayi mishi ba amma ya ya iya? Basar da maganan yayi inda yace "Ina su Amrah?" Momma tace "suna school nuri na wurin aikinta" kallon zahra yayi se yanzu ya tuna yau Friday a kausashe yace................

"Me ya hana ki zuwa school?" Dukar da kai tayi cikin rashin gaskiya ta san yau da kyar In bata zanu wurin paapinta ba bata gama tunani ba taji ya daka mata tsawa "ba da ke nake ba?" Kame

kame ta fara momma tace "ka ganta nan ba yadda banyi da ita ba ta tafi taki wai sbd zaka zo baza ta je makaranta ba" Da gudu zahra ta koma bayan momma ta san a nan ne kad'ai bazai bita ya buga ba, aiko be ce komai ba ya mike ya fice..........

Ko kallon su salima dake zazzaune be yi ba ya fice zuwa site d'inshi yana shiga ya fad'a gado tare da runtse ido hannunshi dafe da goshinshi, ya kusa shafe sa'a a haka kan ya karkata ya zaro wayanshi daga aljihu wani contact ya danna da na ga an rubuta haidar, cikin sa'a numbern ya shiga ba kaman yadda yayi ta gwadawa last two weeks a kai akai baya shiga ba............

A speaker ya sa hakan yasa ana d'agawa naji na d'ayan 'bangaren yace "Shege d'an iska se yau ka tuna dani?" Had'a girar sama da ta kasa musharraf yayi yace "zan ci ubanka haidar Ina wasa da kai? Ko ni sa'anka ne?" Dariya haidar din ya fashe dashi sossai seda ya tsagaita tukun yace "sannu gembo uwar son girma sati d'ayan da ka bani ne kake ganinshi da wani yawa ko?"................

"Mtseww ko minti d'aya ne girma de girma ne, in ba iskanci ba ba tun last two weeks ka ce min zaka hawo land ba?" Cewar Musharraf, cikin muryan zolaya haidar yace "hmm ka san abinka da me mata Ina dawowa ta kwace wayan ta kashe hutuna na one month ne so ta d'auka wa kanta ni na two weeks" tsaki me karfi musharraf ya ja hakan ya sa haidar kwashe Wa da dariya...............

Ze yi magana kenan yaji musharraf ya kashe wayan, se da yayi kira kusan uku kan musharraf ya d'aga haidar yace "daga magana......" kan ya karasa musharraf ya katse shi "ban son iskanci ka san ni fad'i." haidar yace "tukuna kana Ina ne?" Musharraf yace "gombe" haidar yace "Ohk gani nan zuwa amma se matata ta cika min....." Kit ya ji an kashe wayan hakan ya sa shi fashewa da dariya yana mamakin hali irin na musharraf duk da ba sanin yau ya mishi ba amma kullum da sabon halin da ze ganshi dashi, mikewa yayi yana d'aukar keyn motanshi a gurguje ya fice bayan yayi kissing chicks na matarshi, cikin farin ciki ta mishi Allah tsare...........

Afuwan🙏🙏

#share
#comment

#vote

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*An kar'bo daga baban musa Allah ya yarda dashi yace: manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi yace "mumini ga mumini kaman gini ne saashi yana karfafa saashi" Bukhari ya rawaito*

Page➡️3️⃣0️⃣▶️3️⃣1️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Kusan mintuna 20 da gama wayansu yaji an turo kofa an shigo ko be d'ago ba ya san haidar ne, yana nan yadda yake d'azu a kwance rigingine banbancin kawai yanzu akwai taba a hannunshi yana zuka, haidar Abokinshi tun na yaranta Haka iyayensu mata da mazan abokanaine sanadin mahaifinshi momma ta san mahaifiyar haidar sede zumuncin iyayensu maza ya gama ta'bar'barewa ne sadda mahaifinshi ya shayar da su ruwan mamaki da har

abada baza su manta ba, sati guda musharraf ya ba haidar banbancinsu kuwa haidar su biyu kawai iyayensu suka haifa daga shi se kanwanrshi Hafsa sa'ar miemie ita ma de tana jerin masu son Musharraf amma har ita be bata fuska ba duk kuwa yadda suke da yayanta.............

Haidar na da mata d'aya Islam da 'ya'yansu biyu Abdallah da Abubakar wadda ya ci sunan musharraf suna kiranshi Mu'allim, haidar sojan ruwa ne in an turashi aiki se yayi 5months,6 ko ma shekara kan ya waiwayo gida.............

Yana karasowa ya sa hannu ya fisge taban yana hararan musharraf yace "har yaushe? Baka san ba kyau ga lafiyarka ba? Me ya sa baza ka maida qur'ani abokin debe kawarka ba se taba abinda da kafi tsana" harara musharraf ya banka mishi yana cewa............

"Kaga kar ka fara daga zuwa? Ai ba gidanka na je nake sha ba a cikin gidana nake, d'an iskan banza kawai" yana maganan ne yana kokarin fisge taban shi daga hannun haidar da gudu haidar yayi kofa ya tsaya tare da danne taban a jikin gini a take ya mutu..........

"Me yasa zaka kashe min kayana? Ai naga ba haramun bane daga kai har momma kun sani gaba da maganan taban nan don ma na dena shan sauran kayan maye!!!" Kallonshi haidar ke yi cike da tausayawa ya san adu'a da tsantsar tsayawa ta mahaifiyarshi ya sa ya dena shan kayan maye da har so yayi ya zama addicted to drug Allah ya takaita musu............

A hankali yace "toh Lafiyar jikinka fah?" Tsaki musharraf yaja yana zama a bakin gadon yace "Afuwan doctor Haidar bazan kara ba" dariya haidar yayi ganin yadda musharraf din yayi magana kaman da gaske shi din doctor ne, girgiza kai kawai yayi tare da karasawa ya zauna ganganshi yace "naga kaman kana cikin damuwa lafiya kuwa?"...........

Ajiyar zuciya musharraf ya sauke a sanyaye yace "ba lafiya ba haidar wai fah aure momma ke son nayi nan da wata biyar kuma tsakaninta da Allah wannan karon, wallahi Ina cikin damuwa bayan duk abinda surrayah tayi min na kuma yarda da wata mace?............

Har na bata amanar kaina, 'yata, dukiyata da family na? Never haidar an shaa ni sau d'aya na kuma warke" haidar ya dube shi da damuwa "Musharraf se aka ce ma duk mata halinsu d'aya? Ka gwada ka gani in shaa Allahu Allah baze kara had'aka da irin surayyah ba, kuma na tabbatar kaima kanka kana da bukata, a yadda na sanka musharraf baza ka ta'ba zama har karshen rayuwanka ba mace ba sede In harkar zina zaka fad'a wadda bama fata, sannan ka dubi little tana da bukatar uwa kusa da ita ka kara duba lamarin ni de Ina bin bayan momma ko dole ne se mun maka d'an iska In ka ga dama ka tasata a gaba ka ta kallo kaman hoto"...........

Murmushi ne ya kubcewa musharraf haidar d'an iska ne komai seriousness dinka se ya kawo maka barkwanci kaman ba soja ba, "ni de ban shirya wani aure yanzu ba in ba so kuke mu koma gidan jiya ba" girgiza kai kawai haidar yayi sanin halin abokin nashi In ya kafe twankarashi se Allah se kuma momma.............

Kallon time yayi a agogon dake d'aure tsintsiyar hannunshi kan ya d'ago ya dubi musharraf "tashi ka shirya time na juma'a ya karato" ba tare da ya tanka ba ya mike ya nufi toilet yana 'balle Buttons din rigarshi..........

Haidar ganin zaman da yayi ze sa shi fad'awa duniyar tunanin qaddara irin ta musharraf yasa shi jawo system din musharraf ya kunna ya san baze rasa American film din kallo ba don ya San musharraf mayen American films ne..........

Ilai kuwa ya samu the state union yayi playing tare da fara kallo, har musharraf yayi wanka ya fito ya fara shiri cikin dark green shadda da yaji guga se sheki yakeyi tare da kafa hula a kanshi me adon green takalmanshi sau ciki black ya fiddo tare da d'aura wristwatch d'inshi na gucci me tsada, collection na turarukanshi ya feshe jikinshi dashi...........

Yana jin yunwa amma mayun nan yake tunani In har ya je parlorn Chan se sun mamayeshi sun sa ranshi 'baci ba gaira ba dalili, kiran numbern Amrah yayi ya san zuwa yanzu ta dawo ita ko nuri, ringing d'aya ta d'aga don ta sanshi sarai ta bari ya katse bata d'aga ba ta shiga uku............

"Salamu alaikum" cikin kasa da murya don shi ba ma'abocin d'aga murya bane mussaman in yana waya ko namiji haka yake waya da shi "wa'alaikissalam kin dawo?" Da sauri ta amsa "Eh hamma" "ohk kawo Min abinci" kit ya kashe wayanshi............

Kusan 15mins suna zaune yana danna waya haidar na kallo, sallama yaji daga parlor daga jin muryan ya san ba na Amrah bane wato don tsabar iskanci da reni ya sata aiki ita kuma ta aiko wata hmmm Allah had'a idonta da nashi, don tsabar rashin kunya zainab dinma bata jira amsa sallaman ba ta kusto kanta cikin d'akin da idonshi ta fara cin karo yana aiko mata da sakon harara...........

Ita har ga Allah tana son idanunshin nan mussaman In yana harara kyau idon keyi na fitar hankali, murmushi ta sakar mishi tare da nufar gefenshi ta ajiye tire din hannunta tare da d'aukan plate da niyyar serving d'inshi............

Cikin husky voice dinshi ya fara magana kaman ba da kowa yakeyi ba yace "mutum naci naci se kace talauci ban san ko ana so dole ba, ni kam ma Allah ya sawwaka In auri sa'ata" haidar dake kallo dariya ke cinshi be so yayi zainab ta kara kuluwa don ya san ta kulu, sa'arshi fa bayan ya san nuri ma ta girmeta da wattani dariyan da yake dannewa ne ta kwace lokcin da musharraf ya ce "baaa de ni baa" da kamar waka yayi shima murmushi na subuce mishi.............

Dangwarar da plate din Zainab tayi a zafafe tace "haba hamma yanzu don mutum ya so ka lefi ne? Wannan wani irin wulakanci ne don Allah ni ce talaucin?" Ya San abinda ta fi tsana kenan talaka da talauci ko shi da ze zama talaka ko kallo baze ishe su ba daga ita har mahaifanta, cikin murmushi idonshi akan waya yace "d'aye manna!!!!!" Wani dariyan haidar ya sa har yana

ture system d'in gabanshi, a zafafe Zainab ta fice daga d'akin wulaknci kam ta shashi a kan musharraf ba kad'an ba se tayi zuciya kuma ta sake dawowa shi yasa yake kiranta "d'aye manna" wani lokacin ma har karawa yake da "an d'aye kin manne, an d'aye kin manne Allah yayi mutum marar zuciya anan" amma yau kam ta ci alwashin ko mutuwa zatayi ta rabu da shi har abada wai itace sa'anshi? Amma Allah ya isanta............

Da kuka ta shiga main parlor ba wadda ya tanka ta cikinsu se ma murnan da sukeyi d'akin nuri ta shiga da ya kasance masaukinta ta had'a akwatinta da ta taho dashi ba tare da neman mayafi ba ta fice zuwa motarta tare da fisga ta bar gidan in a very high speed..........

****

Bayan sun idar da sallahn azahar khairi ta zauna ta natsu tana tunanin da wani unguwa zata fara cikin waenda maman hamdeeya ta lissafo mata ta yi zurfi cikin tunani taji Dada na magana............

"Ni kam khairi hankalina be kwanta da aikin nan ba, Ina tsoro wani abun yaje ya sameki a inda baki san kowa ba kin san yanayin jikinki khairi" Shiru khairi tayi na en mintuna itama tana tsoron abinda dada ke tsoro sede kuma ba yadda ta iya hakan ne kad'ai mafita zatayi iya kokarinta ganin bata bar ranta ya 'baci ba wannan alkawari ne................

"Karki damu Dada adu'arki kad'ai nake bukata in shaa Allah ba abinda ze faru" "Toh khairi Allah ya sa" da Ameen ta amsa tana duba wayan dadan don kaiwa maman hamdeeya ta sa musu a chargi tun washegarin zuwansu da ya d'auke basu sake sata chargi ba kasancewar basu da charger...........

******

Tsabar dariya har hawaye haidar yayi shi ko gogan tun murmushin na biyu be sake ba sema fuskan da ya had'e ya san yanzu momma zata kirashi ta ci mai mutunci but hakan shine kad'ai option don duk cikinsu ba wacce ze iya aura kuwa har gwara hafsa ma da bata furta mishi Kalman so ba sede alama amma banda waennan marasa kunyan nan.............

Abincinshi yake ci cikin kwanciyar hankali seda haidar ya gama dariyarnshi tukun yace "baka da kyau mutumina ko kayi wanka" harara musharraf ya watsa mishi cike da haushin dariyan da yake tayin...........

Ai ko be gama cin abincin ba ya ga call d'in momma yana d'agawa tace "na gode musharraf kuma ka sameni yanzu a d'akina" bata jira cewarshi ba ta kashewarta ajiyar zuciya ya sauke tare da ci gaba da cin abuncinshi hankali kwance seda ya koshi tukun ya mike yana kallon haidar yace "zamu je ne ko inyi tafiyata" haidar yace "rufamin asiri kanason momma ta had'a dani? Ai se ta gama da kai zan shigo inyi kaman bana d'akin komai ya faru"..............

Ta'be baki kawai yayi tare da ficewa kaman ka'ida suna baje aparlon ko wacce jira take ya shigo ko kallonsu be yi ba ya nufi sama se su ne ma suka bishi da na mujiya kaman zasu cinye shi, a karshen steps suka had'u da Amrah da sauri ta juya zata gudu ya kuwa yi azamar chapke hannunta tare da murd'ewa baya kara zatayi ya wara mata mayun idanunshin nan nan take ta sa d'ayan hannun ta rufe bakinta...........

Cikin kasa da murya yace "yaushe na fara wasa dake? In aikeki ki aiki wata?" Hawaye na cika idonta tace "kayi hkr Hamma musharraf Wlh momma ce tace na bari ta kai Dan Allah kayi hakuri zafi" rankwashi ya sake mata a kai tare da sakar hannunta ya ci gaba da tafiyanshi kaman ba shi ba, da gudu ta koma d'akinsu tana kuka, ta'be baki yayi tare da knocking d'akin momman yana tuna saura zahra se ya mammaketa na rashin zuwa makaranta yau be manta ba sam............

Seda yaji momma ta amsa tukun ya tura kofan ya shiga da sallama shagwa'be fuska yayi duk da kuwa yadda yake ganin 'bacin rai shimfid'e a fuskanta "me kayiwa er mutane?" Dafe kirji yayi yace "oh ni me tace na mata?".............

Harara ta zabga mishi "Musharraf wai kakanka na zama ne? Ko Ina wasa da kai" karkata kai ya kuma yi kaman yaro yace "ni fah ban mata komai ba In na mata ta fad'a mana" momma tace "kuka fa taje take tayiwa mamanta ban ma san tafiyanta ba kuma daga aikarta kai maka abinci ne".............

D'an zaro ido yayi "oh na tuna momma cewa fah kawai nayi ni de bazan auri wacce take sa'a na ba ko ma ta girme ni" zaro ido momma tayi tana mikewa "Zainab dince sa'anka ko ma ta girme ka?" Baki ya tura ya san in yayi magana ba abinda ze hana momma make keyanshi baya ya ja zuwa jikin kofa ya kuma cewa "na kuma tuna na ce mata naci kaman talau........." da azama ya fita yana murmushi ganin momma tayo kanshi, se da ya fitan tukun itama ta sake murmushi a fili tace "Allah ya shirya min kai"...........

#share
#comment
#vote

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*An kar'bo daga Aisha tace : madallah da mataye matayen madina, waenda kunya bata hanasu da suyi tambaya game da addininsu kuma su fahimta a cikinshi. Abu dawood ne ya rawaito*

Page➡️3️⃣2️⃣▶️3️⃣3️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Washegari

Da wuri khairi ta tashi, tayi duk wani aikinta ta gama inda ta musu d'umamen tuwon jiya bayan sunyi wanka sun shirya suka zauna karyawa, su nabeel ma yau zasu fara zuwa islamiya sun shirya cikin uniform d'insu milk da brown sunyi kyau sossai, bayan sun gama karyawa khairi ta dubi dada tace "dada in ban dawo da wuri ba ko ya zakuyi da abincin rana?"...............

Murmushi dada tayi tare da cewa "karki damu kekam ba akwai sauran d'umamen nan a kula ba ki ajiyeshi kusa kawai, in su nabeela sun dawo zata d'uma mana ko kin manta ta iya hura wuta?

Ni kuma se in dinga fad'a mata abinda zatayi" murmushi khairi tayi tana zura khimar d'inta tace "Toh shikenan mu mun wuce, zan tafi da su nabeela don ganin islamiyar tasu".....................

Adu'ar sa'a dadan tayi musu da fatan dacewa, suka fice se murna su nabeel ke yi, suna fita gidan Maman hamdeeya sukayi wa tsinke inda a get suka gamu da mijinta suka gaisa cikin mutunci ya fice, a shirye suka same ta so ko zama basuyi ba suka fito da kafa sukayi tattaki zuwa islamiyar su nabeel d'in inda a gaban khairi Maman hamdeeya ta cike komai har en littatafan da ba za'a rasa ba ta saya musu dama tun gida ta saya musu jaka me ABCD din nan da 20leaves kowa d'ai d'ai da pencil.............

Bayan an musu interview aka turasu aji biyu don yaran yara ne masu tsantsan ilimin addini don sossai malaman suka yaba da background d'insu, Asabar da lahadi zasu dinga zuwa daga 7 zuwa 12, yayinda sauran ranakun makaranta kuma 2 zuwa 5. Cikin kwanciyar hankali khairi tayiwa Maman hamdeeya sallama inda ta tari adaidaita ta shige tana ce mishi "Arabian estate"..................

Tafiyar minti goma shabiyar ya isar dasu unguwan, unguwa ne me kyau don yayiwa khairi kyau duk ginin iri d'aya ne se roof dinne suka banbanta layi d'aya red yayinda d'ayan layin ya kasance blue shiru wurin kaman anyi ruwa an d'auke ba kowa, "d'ari da hamsin" me napep din yace da kyar ta samu ya kar'bi d'ari tana mamakin tsadar kud'in napep na gombe..............

Gashi bata iya hawa machine ba ta san da ya fi sauki amma tunda akayi wani gomna na taraba, ya hana machine a cikin jalingo shekaru dayawa bata kara hawa machine ba. She's so curios ta rasa ta Ina zata fara, seda ta shafe kusan mintuna 20 a tsaye kan ta yi shahada ta nufi house no 1, knocking tayi ta jima tsaye kan wata ta zo ta bud'e mata sanye da riga daban zani daban hannunta rike da mopper kallon sama da kasa tayiwa khairi kan ta ce "lafiya" ba tare da ta amsa gaisuwan da khairin tayi matan ba.................

A sanyaye khairi tace "dama aikatau nake nema Dan Allah ko shara da wanke wanke ne a taimaka min" harara matar ta zabga mata duk da itama er aikince amma hali irin na d'an Adam se cewa tayi "bamu bukata akai gaba" tare da rufe kofan da karfi, ajiyar zuciya khairi ta sauke kan ta wuce gida na biyu nan ma wata buduruwace ta bud'e mata amma daga ganin ta er gayu ce itama a yatsine ta amsawa khairi da basa bukata tare da rufe kofan...............

A haka khairi ta dinga bi gida gida har kusan azahar amma bata samu Ko kallon arziki ba, ga kishirwa tana ji, tsayuwarta a kofan wani gida yayi daidai da kiran sallahn da aka kwad'a daga Chan bayan estate d'in a hankali tayi knocking wani matashin saurayi ne ya bud'e mata kyakyawa sanye da shorts da vest kau da Kai khairi tayi kan ta gaishe shi, yadda yake kallonta har ya so ya razana ta a shakiyance yace bayan ta gama gaya mishi bukatanta................

"Baby a yadda kike da kyaun nan? Ki zo kawai na kilar dake yarinya kiga irin kud'in da zaki dinga chaka a wurin manyan garin nan" yana wani kakkashe ido ya karasa maganan, da sauri khairi ta ja baya tana cewa "se anjima" tare da fara tafiya sauri sauri tana waiwayen baya ajiyar

zuciya ta sauke tare da zama akan dakalin wani gida................

Se da ta huta sossai tukun ta mike ta kwankwasa kofan gidan, wata matashiyar mata ce sanye da khimar har kasa murmushi shimfid'e a fuskanta khairi tayi saurin cewa "Ina yini?" Matar ta amsa da "lafiya ya gida?" Khairi tace "lafiya, don Allah aiki nake nema ko da baku da mai muku shara ko wanke wanke ko kuma girki ki taimaka don Allah"..............

Matsa mata matan tayi tare da cewa "bismillah" shiga tayi a d'arare ta samu kasan carpet ta zauna matar ta karasa ciki na mintuna kan ta fito da tire madaidaici a hannunta ta ajiye gaban khairin tana sakar mata murmushi tace "bismillah ci abinci kiyi sallah se muyi magana" d'an shiru khairi tayi tana tunani seda matar tace "ni musulma ce er uwarki wallahi bazan cuce ki ba" tukun khairi ta fara ci...................

Bata wani ci sossai ba ta ajiye matar ta nuna mata bayi dake parlorn taje tayi alwala a parlon tayi sallah tana idarwa matar tace "baiwar Allah kiyi hakuri kinji? Na san kina bukatar aikin nan hakan yasa bazan iya ce miki babu kai tsaye ba, ni ni kad'aice se mijina ni nake komai nawa bana bukatar me aiki kiyi hakuri ga wannan ki hau machine" ta bata five hundred a ladabce khairi ta kar'ba tana yabon kirkin matar har ranta taji daadi ba wadda yayi mata irin wannan karamcin, kin kar'ban kud'in tayi da kyar matar ta sata ta kar'ba kan ta fice...................

Haka tayi ta bi gida gida amma bata samu ba wulakanci kuwa ba irin wadda bata gani ba har ta yardar wa kanta matar Chan ne kawai me karamci a gabad'aya estate d'in, se yamma likis sannan khairi ta shige gidan karshe shi kam irin me fence d'in nan ne tana tura karamin get d'in kare ya biyota a 360 ta fito se kuma tayi wawancin barin kofan a bud'e kare kam ya fito dama ta wuce wasu biyu a gefen bolan gidan a take suka rufa mata baya................

Khairi tayi gudun da bata ta'ba yin irinshi ba a rayuwanta bata dena gudu ba har seda taga ta fita daga get d'in estate din tukun ta tsaya haki a lokaci d'aya ta fashe da kuka, ita ba gudun bane ya sata kuka se wasu matasa dake zazzaune saman mota a kofar gidan matan nan me mutunci su uku suka fara fashewa da dariya kan d'aya daga cikinsu dake danna waya ya d'ago duk da be fashe da dariya ba amma tana juyowa don kallon karnukan suka had'a ido inda ya sake wani shu'umin murmushi da ya fi kona ranta akan dariyan da sauran suke harda rike ciki.................

Seda tayi kukanta ta koshi tukun ta fara tafiya don ganin magrib ya gabato, harara ta bankawa securities din dake gadin gate din kan ta wuce, se kace su suka kar zomon😅 bata wani jima ba ta samu napep ta hau ta wuce haki kam har lokacin bata dena ba, ga kishi ga ko sallan la'asar bata yi ba..................

*******

Zaune ta ke a bakin gadon d'akin tana kallon wata kyakyawar mata da zasuyi sa'anni chocolate color ce daga ganinta er gayu ce kaman momman fatar ta kad'ai In ka kalla ka san kud'i sun

zauna, less d'in jikinta kawai abun kallo ne bare gwalagawaln da suka fi komai d'auke hankali akanta, "ban san yadda zanyi da musharraf ba hajiya rukayyah rashin auren shi na mugun damu na".................

Wacce aka kira da hajiya rukayyah tace "hajiya Fatima ban ga ta yadda rashin auren yaron nan ze d'aga miki hankali ba, tunda ba neman mata yakeyi ba hasali ma Ko kallo mace bata ishe shi ba ko kin manta aure lokaci ne? Idan lokacin yin na biyun yayi ba se kin mishi magana ba, sannan idan kika mishi na dolen ma kina da tabbacin xe riqe? Baze rike ba sbd be so, wacce yake son ma kinga abinda ya faru"................

Cikin nazari momma tace "na san In har na mishi auren ze riqe amma har yanzu ban samu macen da ta kwanta min da shi ba amma Ina ci gaba da dubawa In har na samu dole in mishi don sam hankali na be kwantawa da ganinshi hakan wlh" ajiyar zuciya hajiya rukayyah ta sauke tukun tace "Toh Allah ya za'ba mana abinda ya fi alkhairi" momma tace "Ameen"................

Hirarrakinsu suka ci gaba dayi na kawaye har suka gangaro kan auren da me aikin su momma zatayi inda take fad'a mata tana neman wata ma bata san ko zata samu nan kusa ba. Suna cikin hiran aka kira sallahn la'asar suka mike suka gabatar kan momma ta fara shirin tafiya dama tun 12 ta zo, har wurin mota hajiya rukayyah ta rakata inda sukayi sallama driver ya ja mota suka fice Ina ta aikin mamakin yawan securities na gidan.................

*****

Ana kiran magrib tana sallama a kofan gidan da gudu nabeel ya zo ya rungumeta cikin muryarshi ta yaranta yace "Adda hato a dilli a acci amin nabeela wuli ha jungo tun nane o d'o woka"(Adda Ina kika tafi kika barmu gashi nabeela ta kone tun d'azu take ta kuka)................

zaro ido khairi tayi tare da kama hannunshi cikin sauri suka karasa ciki Ai kuwa kuka ta samu nabeela nayi rike da hannunta dada na mata fifita..................

Karasawa gabanta tayi ta rike hannunta hawaye na cika idonta tace "garin yaya nabeela?" Dada tace "wai fa cewa nayi ta hura wuta ta d'aura mana d'umamen nan ban san yadda akayi ba naji suna musu da nabeel akan yadda ake sa itace bayan wutan ya ruru kan nayi magana naji ihun nabeelan nan ma ya sa'be don Maman hamdeeya ta sa mata kamu a wurin"...............

Juyawa khairi tayi tana kallon nabeel tace "kona er uwarka kayi?" Zaro ido yayi yana girgiza kai wani hawayen na zuba mishi don haka suke in d'aya na kuka to fa dole d'ayan ma ze yi kuka "A'a Adda kawai na sa hannu Ina kokarin gyara mata itacen se kawai tayi saurin fisgewa shine bata sani ba ya d'alli hannunta d'ayan" had'e rai khairi tayi tace "me ya kai ka bakin murhun tun farko, ko yari ma jaulero mivi?"(me ya kai ka kitchen din nace)................

Cikin muryan tausayi yace "wad'u munyal Adda mi metata nastugo"(kiyi hakuri Adda bazan kara shiga ba) khairi tace "good" tana mikewa tace "Dada ha mi jula mi yaramo chemist"( bari inyi

sallah In kaita chemists) da Toh Dada ta amsa. Seda sukayi sallah tukun khairi ta kama hannun nabeelan suka fice inda suka bar dada da nabeel.............

Magani aka shafamata a wurin suka kuma bata na sha don ta konu ba laifi,  suna hanyar dawowa khairi ta tsaya ta saya musu taliya leda d'aya suna da d'an kayan miya se ta tafasa musu, suna shiga kuwa himar kawai ta cire ta nufi kitchen in less than 40mins ta gama musu jollof na taliya seda sukayi sallahn isha tukun suka ci anan dada ke tambayarta ya aikinfa an samu? Da a'a kawai khairi ta amsa sam bata fad'a mata komai akan tafiyanta ba.....................

Da kyar ta samu ta taimakawa su nabeel da wajibul manzeel d'insu (assignment) tsabar gajiya da bacci suna ganawa, tayi alwala ta shiga ta kwanta, sede me!!! tana rufe ido fuskanshi ya fad'o mata yana wannan shu'umin murmushin da sauri ta bud'e ido tana ambaton sunan Allah, lokaci d'aya ta ajiye a ranta don haushin da ya bata ne yasa fuskanshi ke dawo mata amma tana mamakin irin kyaun da Allah ya zuba mishi juye juye tayi tayi da kyar ta samu baccin ya d'auketa.................

#share
#vote
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️3️⃣4️⃣▶️3️⃣5️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Yau kwana biyu kenan khairi na fita tana aikin neman aikatau amma bata samu ba wulakanci kam ba wadda bata gani ba amma da yake ta sawa zuciyarta neman aikin ya zama wajibi a kanta hakan be dameta ba, babban damuwanta ma kayan abincinsu da suke barazanar karewa don be wuce ya musu kwana biyu ba.................

Tare da su nabeel suke fita ta ajiyesu islamiyya ta wuce kasancewar basu shiga boko ba ta roka su dinga zuwa da safe ma ko ran makaranta ne kan su shiga bokon dayake yara ne masu shiga rai har sun saba da islamiyyar kamar sun shekara cikinta, hannun nabeela ya sabe sossai sede be warke ba, daga randa nabeela ta kone kullum kan ta fita se tayi musu abincin rana take fita, tana kuma iyakar kokarinta don ganin batayi magrib a waje ba...................

Yau ma kaman kullum bayan ta gama shiri tayiwa dada sallama suka fito hannunta rike da su nabeel se da suka shiga gidan Maman hamdeeya fishaa kan suka fito suka wuce kasancewar kwana d'aya kenan basu had'u ba, bayan ta ajiye su nabeel ta tari napep ta shige kud'in hannunta saura 300 duk ranta a jagule tana tunanin In bata samu aiki yau ba bata san da wani kud'in zata fita gobe ba, amma bata cire rai ba Allah na nan..............

Cikin mintuna kad'an suka isa low cost cikin d'ari d'ari ta sauka sbd duk cikin unguwannin da take zuwa ba wadda gidajen suka tsoratata kaman waennan ga ko wanni gida da securities, wani gate ta fara knocking gateman din ya fito sanye da uniform yake tambayarta lafiya? Tace "don Allah matar gidan nake son gani" ta san in tace zata dinga fad'awa gate-mans abinda yake tafe da ita zasu dinga mata bukulu ne.................

Kallon sama da kasa ya mata kan ya bata hanya ta shige duk da ya san madam dinshi bata harka da talaka aiko khairi na shiga tana fad'an abinda ya kawo ta matar ta mata korar kare ta had'a harda gateman d'in ta zage tas, a tsorace khairi ta shiga gida na biyu nan ma wulakanci aka mata haka ta dinga yawo duk gidan da ta shiga koranta ake, wasu kam ma har cewa suke ko an aiko ta spying ne, wasu harda barazanar rufe ta a police station sukeyi......................

A haka har akayi azahar ta samu panpom gefen wani gida tayi alwala tare da komawa gefe ta shimfid'a d'ankwalinta dukda bata san gabas anan ba amma haka tayi sallanta, bayan ta idar ta jima sossai zaune a wurin duk damuwanta na kan rashin samun aikin nan ga kud'in hannunta sun kare ga kayan abincinsu na hanyan karewa, babban damuwanta school tana mugun son su koma makaranta ko shedan gama secondary d'inta ta samu...............

Bayan ta gama sake sakenta ta mike ta ci gaba da tafiya a sad'ad'e har ta samu wani shop sadakarwa tayi ta karasa ta sayi pure bliss da pure water d'aya ta samu wuri ta zauna taci ta sha ruwan kan ta ci gaba da roaming har gab magriba la'asar ma a wani gindin bishiya tayi, ganin magrib ya gabato yasa ta fara neman napep don komawa gida amma ko d'aya bata gani ba ga hadari da ya had'u lokaci d'aya..................

A mugun tsorace take kalle kalle ko gilmawan mutum d'aya babu securities da suke kofan gidaje dayawa ma babu duk sun koma daga ciki tafiya ta fara sauri sauri tana aduar Allah ya sa ta samu ko machine ne, duk hankalinta ya tashi akwai wani gidan da ta wuce d'azu da ko marmarin shiganshi batayi ba sbd yawan securities din da ta gani kofan gidan akwai kaman rumfah haka wurin taje ta tsaya amma ko minti biyu batayi da tsayuwa ba wani katon security ya fito ya koreta..............

Hawaye ta fara ganin iskan ruwa ya taso gadan gadan kana ji ma ruwan na zuwa, ci gaba da sauri tayi batayi aune ba taji an 'barke da ruwa kam kaman da bakin kwarya ci gaba da tafiya a haka tayi ruwan na dukanta, daga nesa Chan ta hangi wasu matasa su kusan biyar suna zuwa zuban ruwan be damesu ba sam se ma wani irin tafiya da sukeyi na kasaita da ji da kud'i dukda In ka zuba musu ido ka lura sossai zaka san a buge suke................

Ci gaba da tafiya khairi tayi kanta a kasa har ta iso kusa da su batayi aune ba taji an chabke hannunta a razane take kallon wadda ya riketan zagayeta sukayi suna sheka dariya d'ayan yace "are yhu seeing this chick komai yaji yau akwai morewa" kokarin fisge hannunta takeyi amma ba rikon wasa ya mata ba a take suka cire mata khimar suka yasar kokuwa suka fara da su amma Ina sun mata yawa kuma aka ce sarkin yawa sun fi sarkin karfi.....................

********

"Ni wallahi sam ban so zuwa dukkun nan ba, duk momma ta bi ta matsamin da en uwan mutumin nan" inji fad'ar musharraf kenan yayinda yake driving da motar momma kwanansu biyu dukku wadda momma ce ta sashi dole zuwa duk rabin en uwanta a achan suke kuma en

uwantan de sune en uwan mahaifinshi don cousins suke, harara haidar ya sake mishi inda yace.................

"Ko min lalacewan masa de tafi kashin shanu" "mtseww could yhu imagine ni da bana karya ba na son me yinta amma ni ne da karya a office yau Tuesday amma ban koma ba, na fake da wani wai banda lafiya" shiru haidar yayi yana kallon hanya kallonshi musharraf yayi na seconds tukun ya juya kan tukinshi a fili yayi kwafa yana cewa "In miskilanci ne kaima ka san na dame ka na shanye don ma kaine yasa nake maganan".................

Cikin dariya haidar yace "toh musharraf me kake so in ce maka? Na riga da na saba jin wannan mitan a duk sadda na raka ka dukku har muje mu dawo kana mita abinda ban sanka da shi ba" Shiru musharraf ya mishi nan haidar ya dinga magana amma ko ci kanka musharraf ya ki cewa, ganin musharraf d'in ya d'auki hanyar GRA yasa haidar cewa "Kai gidanmu fah zaka kaini In d'auki matata don nayi kewarta".................

Harara musharraf ya sake mishi inda ya juya ya nufi Low cost ba tare da ya ce komai ba, a hankali yake tafiya kaman bayaso sabida karfin ruwan saman dake zuba yana covering view d'inshi hakan ya sa ya kure hasken lights d'in motar yana shawo kwanan street d'in su haidar hasken motarshi ya sauka akan shape d'in jikinta doguwar rigan material dake jikinta fitted one ne hakan ya sa da suka yaga saman rigan be zame ba, runtse idonshi yayi a lokaci d'aya ya bud'e akan black bra d'in dake jikinta ya kamata har tudun breast dinta ana iya gani daga nesa.................

Kallon haidar yayi yaga hankalinshi na kan waya be ma san me ke faruwa ba, takaicin matasan ne ya kamashi me yasa ga mata karuwai dayawa a gari se wacce bata sayar da kanta ba? Rage hasken motan yayi kan yayi kansu da mugun speed da yasa haidar d'agowa hakan yasa ya gane me akeyi, su kuma ganin motar tayo kansu yasa suka arci ta kare ita kuma ta du'ka a wurin tana boye fuskanta a tsakankanin cinyoyinta.................

Wani wawan birki musharraf ya ja a gabanta tare da juya kan motan cikin hanzari shi da haidar suka sauka sukayi kan yaran wani irin duka suka fara musu da ya bani tsoro don daga ganin yaran ba su da wani karfi ajeboters ne, duka sossai suka musu kan suka samu suka tsere, musharraf ya koma mota da sauri yana rawar d'ari don baya shiga ruwa sbd In ya shiga se yayi zazza'bi me zafi da mura kaman baze yi rai ba............

Heater din motar ya kunna yana kau da kai daga kan yarinyar, haidar ne ya karasa kusa da ita ya janyo hijab d'inta dake gefe cikin tausayinta yace "baiwar Allah" kuka takeyi sossai inda jikinta kuma ke tsananin rawa a hankali ta d'ago don ganin waenda suka taimake ta duk da ruwa ake hakan be hana haske tarwal a unguwan ba kasancewar ko wanni gida sun kunna kwayayen fitillunsu, had'a ido sukayi da haidar hannunshi rike da hijab d'inta yana mika mata..................

Kar'ba tayi har yanzu jikinta be bar rawa ba a kuma rud'e take, sa khimar din tayi dukda

wuyanshi ya yage sossai haka ta sa tana chukuikuye shi a kirjinta hannunta ya kama shi ko damuwa da ruwan be yi ba shi da yake watanni cikinshi ta Ina ze damu, a hankali ta mike ta bishi don haka kawai taji a jikinta she's safe with them ba abinda ze same ta................

Bayan motar ya bud'e mata ta shiga, ta zauna wani kamshi da dumi da ya buge ta ya sata sauke ajiyar zuciya motar ya d'auki dumi sossai ita bata ta'ba shiga mota me fidda sanyi bama balle zafi, d'aga ido tayi don kallon d'ayan se suka had'a ido ta mirror wani d'an banzan hararan da ya buga mata yasa tayi saurin kau da kanta zuciyarta na bugawa................

Tabbas shine toh me ya kawoshi nan bayan a chan estate ta kalleshi, kau da zancen tayi ta koma tunanin wani hali dada zata shiga In taga har yanzu bata dawo ba ga ruwa anayi tunaninta da kukanta ya yanke ne sadda taji me murmushin iskanci da ta sawa suna da haka wato musharraf na cewa "what are yhu doing? Where are yhu taking her to after the help"................

Haidar yace "haba musharraf are we leaving her at this rain and that street after all that happened to her? I'm taking her to Maami she will know what to do with her" su duk a zatonsu batayi makaranta ba ganin shigan jikinta suna ganin ko tayi ma to irin government dinnan da basa aikata aikin Chas a boko.............

A zuciyarta take magana "Lallai wato sunanshi musharraf kuma be da kirki be da tausayi, tsurewa tayi ganin sun nufi gida me rumfa da aka koreta a cikinshi duk da taji yace ze kaita wurin Maami amma seda taji cikinta ya d'uri ruwa, horn ya buga ba 'bata lokaci wani ya fito ganin motar yasa ya koma da sauri aka wangale gate din suka kutsa kai har gaban entrance na parlorn gidan musharraf ya Parker haidar ya juya ya kalli khairi yace "muje ko" fita tayi shima ya fita da sauri suka haura steps na kofan parlorn shi haidar ya d'auka musharraf dinma ze shigo se gani yayi ya ja motar a guje ya fice daga gidan..................

Girgiza kai kawai yayi yana shiga parlorn da sallama khairi na biye dashi har yanzu kuma tana share hawaye, hajjiya rukayyah ce zaune kan kujerun parlorn a had'e take cikin leshi me tsada da ya amsa sunanshi dukda mijinta baya gari kwalliyan nan de baya barin jikinta murmushi ta sakarwa haidar da ke tsaye.................

Tana nuna mishi set din kujerun ledan dake gefenta ganin jikinshi a jike baza ta yadda ya zauna mata a royal cushion ba, murmushi shima yayi yana zama dama ya sani, a kasan tiles khairi ta zauna tana takure jikinta idon Maami a kanta har tayi sallama da mijinta tukun ta kalli haidar ta kuma kalli khairi ya gane me take nufi hakan ya sa ya bata labarin abinda ya faru................

Ta tausayawa khairi sossai dayake Allah yayi ta mai tausayi da jin kan talakawa tace "en mata ya sunanki?" A hankali khairi tace "ummulkhairi" jijjiga kai Maami tayi ta kuma cewa "ummulkhairi me ya fito dake da dare kuma cikin ruwan nan har mummunan abu ya so samunki ba don Allah ya turo su haidar ba" a natse ta fad'a mata abinda ya fiddo ta.................

Cikin tausayawa Maami ke kallon khairi kan tace "kar ki damu bari In had'a ki da autata kiyi wanka ki chanza kaya ki ci abinci gobe se akai ki gida" tun kan Maami ta karasa khairi ke girgixa kai tace "mahaifiyata makauniyace kannena kuma basu wuce shekara biyar ba na san suna chan hankali tashe bazan iya kwana ba kiyi hakuri hajiya".................

Cikin tausayawa Maami tace "toh za'a maida ki gida amma se kinyi wanka, zaki kuma tafi muku da abinci gobe In shaa Allahu zan tura drivern da ze kaiki yau ya d'aukeki zuwa gidan wata aminiyata dake neman er aiki" cikin tsantsan farin ciki da ya gaza 'boyuwa khairi tayi ta godiya, Hafsat maami ta kira ta had'ata da khairi, hafsa ma tana da kirki kaman en gidansu Cewar khairi dake wanka kenan bayan hafsa ta nuna mata yadda zata yi anfani da duk toiletries d'in...................

Tana fitowa hafsa ta bata doguwar riga da gyalenshi ta saka tayi kyau sossai kuwa komawa parlorn sukayi ta samu Maami ta sa an shirya mata abinci cikin basket bata ga haidar ba don ya jima da shigewa part dinshi dake gidan duk da yana da gidanshi amma zamansu gidan iyayenshi yafi yawa sbd yanayin aikinshi kuma be son dinga barin matarshi gida ita kad'ai da yara..................

Driver Maami ta kira lokacin karfe tara na dare kuma ruwan ya tsaya, ya d'auki basket din khairi ta bi bayanshi kan ta fita Maami ta kirata ta dawo kud'i ta d'auko da d'an yawa ta bata Tace "inji haidar, ga wannan" ta bata wani leda da bata san me a ciki ba godiya sossai tayi kan ta fice ranta kal................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad: Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️3️⃣6️⃣▶️3️⃣7️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Har kofan gida drivern ya kaita tayi mishi godiya sossai kan ta fice, da sallama ta shiga gidan hakan yasa Dada da ta zuba tagumi sauke nannauyar ajiyar zuciya tana zaune ne kan turmi dukda sanyin da garin ya d'auka ta tabbatar damuwar da mahaifiyarta ta shiga baze fad'u ba a hankali ta kira sunanta "ummulkhairi"......................

A raunane ta amsa sbd tuno abinda ya so faruwa da ita awanni kad'an da suka wuce tabbas da ya farun da bata san wani hali zasu shiga ba ita da waennan en uwa nata, hawayen fuskanta ta share tare da gyaran murya jin dadan ta fara magana cikin sanyi "khairi me ya ajiyeki a waje haka  kin san ba magriba kukeyi a waje ba yanzu fah goma saura".................

Bata jira Cewar khairin ba ta kara da "lafiyanki ko? Ba wani abinda ya sameki? Wallahi tun fitanki gabana ke ta aikin fad'uwa" murmushi khairi tayi hawaye na kuma zuba mata ta karasa gaban dadan tana Jan er kujerar tsugunonsu ta zauna kan tace "lafiyata kalau dada kin ga ma albishirinki?" Dada tace "goro" khairi tace "Dada na samu aiki, matar ce ma ta riqeni ganin

hadari se da ruwa ya tsaya tukun ta had'ani da drivern ta ya dawo dani gobe ma in shaa Allahu shi ze zo ya d'auke ni"...............

Ta karasa with so much excitement in her voice, ta boyewa mahaifiyarta ibtila'in da yaso afka mata, farin ciki sossai ya bayyana a fuskan dada a fili tace "Alhamdulillah, Alhamdulillah ya Allah ka ci gaba da rufamana asiri duniya da lahira ba don halinmu ba"  cikin murmushi khairi tace "Ameen mamanmu, Ina su nabeel ne ban ji su ba" Dada tace "suna ciki sallah sukeyi tun d'azu suke jiran dawowarki da kyar na sasu yin magrib kin sansu da kafiya Toh isha dinma se yanzu suke mika ta".......................

Khairi ta gyd'a Kai ta kuma cewa "Allah ya sa ba abinda kuka ci don hajiya ta had'oni da abinci don naki ci a chan gidantan harda abu a leda ta ban kinga ko bud'ewa banyi ba" cikin jin daadi ba wai don abincin ba se don jin daadin khairi ta samu uwar d'aki me mutunci don a wannan zamani me mutuncin ne kawai ze iya maka haka, dada tace "aaa harda d'awainiya Toh Allah ya saka, ai ko an gode dama  ba wani abinda muka d'aura".............

Khairi tana cikin bud'e coolers din su nabeel suka fito da gudu suna cewa "oyoyo Adda" fasa bud'e flask din khairi tayi tare da taran kannenta cikin murmushi tace "oyoyo chutu'ben dada" (chutu'be means en biyu da fulatanci) rungumesu tayi tana jin kewar kannenta bayan ta sakesu tace "Dada ya kamata mu koma ciki wajen nan akwai sauro ga sanyi".............

Komawa ciki sukayi Allah ya sa akwai wutan nepa tarwal a gidan bayan d'auke ruwa suka dawo dashi, plates khairi ta d'auko musu da serving spoon ta zo ta bud'e coolern fried rice ne had'add'e da pepper chicken se cowslow a gefe da yaji kwai, a lokacin In kaga fuskan waennan familyn zaka tabbatar suna cikin farin ciki saka musu tayi yadda ze ishe su sukayi bismillah suka fara ci a natse.................

Har suka gama ci ba wadda yayi magana a cikinsu daad'in abincin kam ya wuce misali, bayan sun koshi suka ajiye saura a kitchen kan nabeela ta dawo ma khairi ta bud'e ledan aiko designers abaya ne masu kyau guda biyu se turaruka arabian perfumes guda biyu, se kud'in da haidar ya basu 10 thousand..................

cikin jin dad'in karamcin maami da haidar khairin ta d'aurawa Dada kayan akan kafa tatta'bawa dada tayi tana sharara musu adu'a kan ta mayarwa khairi kayan khairi tace "Dada baza ki dau d'aya ba?" Dada tace "a'a ernan rabani ni kam Ina ni Ina kayanku na zamani balle ni da ya kamata in d'au nauyinku bayan kushewar mahaifinku se kece ke d'awainiya dani ni Ina nan bani da anfanin komai".................

Ta karasa da sanyin murya da alamun abun na damunta, da sauri khairi tace "haba dada me yasa zaki ce haka ke kika fi komai anfani a garemu a yanzu haka dan Allah ki daina daurawa kanki damuwa dama tun asali d'a ne ya kamata ya ji kan iyayenshi bayan ya mallaki hankalin kanshi bare ke da lafiya bata isheki ba" murmushi kawai dada tayi tace "hmmm khairi kenan d'awainiyar ya mace bai barin kan iyayenta har se sun damka ta a hannun mijinta, don ba

yadda zanyi ne kawai, ki d'au rigunanki turaren ma ki d'au d'aya kya bar mana d'ayan mu dinga fesawa da kannenki..................

Sannan kud'in ki cire mana na kayan abinci se ki duba makaranta anan kusa na gomnati ki sa kannenki, daga baya ke kuma maga yadda Allah ze yi" khairi tace "Hakan yayi Allah ya shige mana gaba" ta mike ta cire na jikinta wadda hafsat ta bata ta had'a da sauran ta adana kan ta fita tayo alwala tazo tayi isha dama tayi magrib gidansu haidar kan suka kwanta sbd sanyin da gari ya d'auka, tsintar kanta tayi da tunanin wadda aka kira da musharraf ajiyar zuciya ta sauke tana lumshe ido view din kyawawan lumsassun idanunshi da yake hararanta da shi ya dawo mata tsab kaman wadda ta d'au videon ta ajiye tana kallo a haka har bacci ya d'auke ta.................

*******

Da kyar musharraf ya kai kanshi gida jikinshi na tsananin rawa hakwaranshi na had'ewa duk da zafin da motan ke fitarwa hakan be hana shi jin sanyi ba, horn ya danna malam d'ahe ya zo da gudu ya bud'e mishi kan motan na galau galau haka ya shiga da ita be iya shiga parking lot ba ya Parker ta tsakiyar gida, zama yayi a motan yana kallon ruwan dake zuba har isowarshi gidan.............

Shahada kawai yayi ya bud'e motar ya fita sede ya kasa sauri hakan yasa ruwan ya ci gaba da dukanshi har ya isa d'akinshi zubewa yayi kan gado yana Jan bargo duk da jikinshi dake a jike...............

Zaune suke a parlor suna jiran shigowarshi tunda ya danna horn zahra ke tsalle kwana biyu kennan bata sa mahaifinta a ido ba tayi ta kiran wayanshi yaki shiga, ita, momma, Amrah, nuri, miemie, salima se Maryam ne kawai zaune a parlorn yayi nasaran koran Afreen, da Zainab inji ta fad'ar momma..............

Ganin har mintuna 10 sun shige da shigowarshi ne yasa momma mikewa taje ta bud'e kofar parlorn tana duba waje, don In har Musharraf ya shigo gari be ta'ba biyawa wani waje be fara zuwa wajenta ba, sede In ba lafiya ba, yadda taga parking na motar kad'ai ya sanar da ita ba lafiya ba, da sauri ta fita tana kira nuri tare suka fita zuwa part dinshi ko wuta be kunna ba seda suka shiga ne suka kunna...............

Suna shiga d'akin tun daga bakin kofa suke iya ganin yadda jikinshi ke rawan sanyi da kuma atishawar da yake ta jerawa da sauri momma ta karasa tana yaye blanket din jikinshi a d'an rud'e tace "Musharraf me ya shigar da kai ruwa bayan ka san yanayinka? Ina shi haidar d'in yake har ka shiga ruwa ba tare da saninshi ba? Musharraf ka fa san yadda ruwa ke wahal da kai?".................

Shiru yayi nuri ce tace "momma ki sa shi ya cire jikakkun kayan nan sanyi na kara shiganshi da

su bari inje In dubo me zan iya bashi da first aid" da yake nuri likita ce, da sauri ta fice momma ta taimaka mishi ya mike da kanta ta ciremai rigan taje drower dinshi ta d'auko mishi sweater riga me had'e da wando na cotton me taushi blue tazo ta mikamai tana cewa "lalla'ba ka tashi ka je ka watsa ruwan zafi zaka rage jin sanyin".............

Da kyar ya mike ya nufi toilet momma ta bishi da towel da kayan, ruwan zafi ta had'a mai tare da ajiye mai kayan da towel din kan mirror stand dake bayin ta fice a d'akinshi ta zauna zaman jiran shi be fito ba har nuri ta shigo hannunta d'auke da tire da d'an madaidaicin flask da cup a kai se wasu magunguna a gefe, ajiyewa tayi akan bedside tana cewa "momma ga wannan se ki bashi in ya fito, bari inje inji da namesyn kin nan kin san yanayinsu d'aya da babanta amma se rikici takeyi wai se ta zo ta ga paapinta"...................

Murmushi momma tayi tana cewa "'yar kwal uba da kin barta ta biyoki In yaso su had'u su kwanta tare" nuri na murmushi ta fice, fitan nuri ba da jimawa ba wayan momma ya d'auki kara haidar ne ke kiranta dama yanzu take tunanin kiranshi taji ya akayi musharraf ya shiga ruwa haka, d'auka tayi suka gaisa ta tambayeshi gajiyar hanya inda yace "gajiya yabi jiki momma, dama musharraf nayi ta kira inji ko ya isa gida lafiya amma baya d'agawa"..................

Momma tace "Ina ko ze d'aga bayan yana fama da ciwon shin nan de, me ya shigar dashi ruwa hk haidar?" Nan haidar ya bata labari ya kara da "gani nan zuwa In ya so se in kwana dashi" momma tace "Allah sarki Allah ya ci gaba da kare mna 'ya'yanmu mata da irin waenchan maza Allah kuma ya saka muku taimakon da kuka mata, sannan ba se ka zo ba kai da kayi tafiya ka dawo matarka na bukatar kulawarka kayi zamanka zan kula da shi"..................

Sallama sukayi bayan haidar ya mishi adu'ar samun lafiya, suna cikin waya da haidar ya fito sanye da kayan sanyin da suka mishi kyau sossai, gado ya hau ya zauna yana kame jikinshi atishawa kam yayi su ba adadi ga muryanshi ya dishe makokoronshi se zafi yake mishi yana jin kaman an shake shi, kaman ze yi kuka yake kallon momma yana jiran tayi mai fad'a se ji yayi tana cewa "sannu ga coffee nuri ta kawo maka ka samu ka sha se ka had'iyi magani"..................

Tsiyaya mishi tayi a cup ta mika mishi kar'ba yayi yana sipping a hankali jikin rau kaman wuta, a zuciyarshi kuwa ba masifan da be yi ba duk ya d'aura laifin kan khairi da ya lakabawa suna da 'kantin ball' 🤣 Wai idonta kaman kantin ball (inji musharraf fah ba ni ba tohm😅) so sunan da yake kiranta kenan a fili kuma yayi tsaki yafi dubu.............

Bayan ya gama shan coffee d'in ya sha maganin tare da sulalewa ya kwanta momma taje wardrobe dinshi ta samo socks ta zo ta saka mishi tare da ja mishi blanket ta rufe shi, kanshi ta dawo tana ta'ba temperature d'in jikinshi a hankali tace "sannu babana Allah ya biyaku taimakon da kukayi, Ina wayanka?" Yace cikin dashewar murya "yana mota" tace "bari inje In d'auko maka zuwa anjima In na tafi kaji jikin ya matsa maka se ka kirani koh?" Shiru yayi ita kuma ta juya ta fice..................

Washegari🌚🌚

Yadda khairi ta saba tashi a kwanakinnan haka ta tashi tayi komai yadda ta saba tayiwa su nabeel wanka suka shirya cikin uniform d'insu na islamiyya ta rakasu har islamiyyan tana dawowa ne ta tsaya gidan Maman hamdeeya suka gaisa tayi mata albishir samun aikinta ta tayata murna sossai............

Bayan khairi ta koma gida ta fara zaman jiran driver jefi jefi suna hira da Dada ta matsu sossai ta ganta gidan tana son zuwa wani government day secondary school da ta gani daga Chan farkon unguwan ta duba me da me zasu bukata na admission din su nabeel amma tana tsoron kar ta tafi driver ya zo...............

Se around 11 sukaji an kwad'a sallama khimar khairi ta d'auka ta sanya tana shewa dada "se na dawo" Dada tace "Allah ya tsare ya bada sa'a" fita khairi tayi ta shiga motar tana gaida drivern din cikin fara'a ya amsa ta kan ya tada motar suka bar unguwan...............

Masha Allah take ta furtawa ganin unguwan da suka shigo gidajen cikinshi masu tsananin kyau da d'auke hankali unguwan shiru sossai, a tsanake drivern ke tafiya har ya iso gidan ya danna horn malam d'ahe ya wangale gate d'in suka shige kan su shiga ma drivern ya tsaya suka gaisa yace mishi kar ya rufe ajiyeta kawai ze yi ya tafi...........

Ai ko yana ajiyeta ya juya d'ago kan da zatayi idonta ya fad'a cikin nashi a tare zuciyarsu ya buga da tsananin karfi da har seda ta hard'e da kayan jikinta ta kusa fad'uwa kan ta d'ago kuma bata ganshi ba, kofar da ta tabbatar shine na asalin cikin gidan ta nufa, a hankali ta fara knocking, ta kusa five minutes a tsaye tukun taji an bud'e.................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*~~dedicated to MU KARU DA JUNA group, a gaskiya Ina jin daad'in comments d'inku, bani da abinda zan biyaku dashi tabbas ba don ku ba da na jima da dena rubutu, but yhu always support me kune karfin gwiwana thank yhu so very much for the care and support Allah ya bar kauna~~~*

Page➡️3️⃣8️⃣▶️3️⃣9️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Wata kyakyawar yarinya da baza ta wuce sa'ansu nabeel bace ta gani tsaye cikin shigan kananan kaya Jeans da pink tshirt, kanta kitson kalba masu kyau an sa mata beats, murmushi ta sakarwa khairin hakan ya sa khairin ma sakar mata murmushi...........

"Hey cutie I'm fatima Abubakar Mahmoud but yhu can call me zahra or little, yhu are beautiful" murmushi kawai khairi tayi mata kan tayi magana taji ance "little wanene a kofan?" Matsawa little tayi khairi ta shiga tana karewa parlorn kallo, a kan three seater idonta ya fara sauka, kwance yake rigingine yana kallon sama, fuskanshi ta kalla idonshi lumshe fuskanshi jajazur

musamman kumatu da kan hanci, kuma se gyaran murya yakeyi kaman me tsananin mura, kau da kai tayi tana sauke idonta akan momma dake zaune kan one seater tray d'aure akan cinyanta Da wani roba me kyau da tsabta tana yanka fruits..................

Murmushi ta sakarwa khairi dukda bata sheda ta ba da fara'a tace "sannu da zuwa lale" khairi tace "yauwa" tare da sulalewa kasa ta zauna tana karawa da "Ina yini?" Momma tace "Lafiya klau ya gidan naku?" Khairi tace "lafiya" se kuma tayi shiru, atishawar musharraf yafi biyar kan su gama d'an maganan nan hakan yasa hankalinta komawa kanshi a ranta tace bade taimakona da sukayin nan bane ya ja mishi mura haka don taga irunsu basuyi kama da masu shiga ruwa ba................

Maganan momma ne ya katse ta daga tunanin da ta fad'a inda tace "sede kuma ban sheda ki ba" khairi tace "sabuwar me aikin da Maami ta turo daga Chan gidan su Hamma haidar" don haka taji hafsa na cewa, momma tace "ohh Ohk na gane dama ke ce? But kinyi karama da aiyukan nan zaki iya kuwa?" Cikin ladabi khairi tace "zan iya In shaa Allah hajiya" little dake zaune kasa kusa da khairi ta zura mata ido tace "momma baki tambayi name d'inta ba tana da kyau"................

Momma tace "aiko little, ya sunanki?" Khairi tace "ummulkhairi" momma tace "masha Allah, toh kinji little sunanta Anty ummulkhairi" little ta turo baki gaba tana kad'a kai tace "uhm uhm ni de cutie zan dinga kiranta Anty ummulkhairi yayi yawa" dariya momma da khairi sukayi, kai a kasa khairi tace "yaushe zan fara aikin hajiya? Kuma Ina rokon alfarmar Ina zuwa da safe in koma da yamma"..................

Momma tace "ki dinga kirana momma ohk? Sannan zuwa da dawowan nan ze yiwu? Dukda tsohuwar me aikinmu ma haka takeyi amma abubuwa dayawa se ni ce me yi shiyasa nake son samun wacce zata zauna da mu anan" little tayi tsulum tace "Ayyah ki dinga kwana cutie plz plz plzzzzz" khairi na murmushi tace "kiyi hakuri hajiya hakan baze yiwu ba sbd mahaifiyata na da lalurar ido bata gani kannena kuma sa'annin little pretty ne"......................

Little ta daka tsalle "yeeeeeeeyyyyy cutie am I that pretty???" Kai khairi ta gyad'a mata tana murmushi little zatayi magana kenan suka ji muryanshi da ke shake sbd muran da yakeyi yace "zahra!!!" A tare suka juyo se idonta ya fad'a cikin nashi saurin kau da kai tayi tana lumshe ido ta rasa wani irin abu ne wannan da in suka had'a ido kad'ai se taji wani iri daga yatsan kafanta har kanta ga bugawar zuciya da take fama dashi In har suka kasance cikin inuwa d'aya................

Kallon da ta mishin nan kawai ta tabbatar da zarginta na ta sanadinta mura ya kamashi sossai haka idonshi ya sauya kala sossai haka lips d'inshi sun kara turwa daga light maroon zuwa dark maroon, sanye yake cikin sweater farare riga da wando masu taushi haskensu har d'auke ido yakeyi, ajiyar zuciya ta sauke jin maganan momma tana cewa "ba damuwa khairi zaki iya kina zuwa kina komawa d'in, se ki kiyaye latti sannan albashin dubu ashirin da biyar ne" godiya khairi tayi momma ta kara da...............

"Sannan zaki iya bari se jibi ki fara zuwa, ga wannan ki hau machine se jibin in Allah ya kaimu" godiya sossai khairi tayiwa momma tana kar'ban five hundred da ta bata don hawa abin hawa, mikewa tayi tana cewa "se anjima hajiya" murmushi kawai momma tayi mata tana me ci gaba da aikinta, har ta fita bata sake satan kallon inda yake ba....................

Tana fita suna cin karo da little murmushi ta sakar mata tana cewa "zan tafi little pretty se na zo jibi" little na murmushi tace "Ohk cutie see yhaa" tana d'aga mata hannu da son yarinyar ta wuce, gskiya yarinyar akwai shiga rai, a tsanake ta dinga tattaki har ta samu napep ta shige zuwa government day secondary school dake nan farkon unguwansu..................

A kofar makarantar ya sauketa ta biyashi kud'in shi ta shige, da tambaya  ta karasa office d'in principal bayani ta mishi akan kannenta da take so su fara zuwa karatu anan bayanin abinda zata biya ya mata ta kuwa biya a take don ta fito da gabad'aya kud'in Allah ya taimake ta ma four thousand ya kar'ba tunda primary one duk zasu shiga se kuma ya nemi su zo da tsintsiya, buta, se cup kowa d'ai d'ai godiya ta mishi ta fice..................

Wani napep din ta kara tara ta nufi kasuwa dukda yadda zuciyarta ke bugawa tuna abinda ya faru da ita achan amma haka ta karasa tunda ba wadda ze je musu In ba itan ba, sayayya ta musu da d'an yawa na kayan abinci yadda zasu kwnaa biyu basu nema ba, se en chanji da ta rage na napep din zuwa wajen aiki har yadin uniform da littatafai ta sayawa su nabeel da pencil................

Ta dawo gida around three duk a gajiye da kaya niki niki, da murna su nabeel suka tare ta su suka ringa tayata har ta shigar da komai da ta saya ta sallami me napep din, bayan ta shiga gida ta kimtsa duk abinda ta saya suna hira da Dada tana bata labarin karamcin matar da zatayi aiki da ita....................

Bayan ta gama ta kama nabeela suka shiga gidan Maman hamdeeya "oyoyo Adda khairi, nayi missing dinki d'azun na shiga wurin Dada ai ta cemin kin tafi gidan aiki" khairi na murmushi tace "kede bari gari yayi zafi, amma Alhamdulillah duk Adu'ana Allah ya amsa min nayima su nabeel registration yanzu ma uniform d'insu na kawo dinki inji kud'in kuma"................

Hararanta Maman hamdeeya tayi tana cewa "ko ba kud'in dinki ba, khaih Alhamdulillah na taya murna Allah ya ci gaba da rufa asiri a yau kuwa zan d'inka musu don gobe su fara zuwa"...................

Cikin jin daadi khairi tayi mata godiya, kan ta mike tana cewa "bari inje In d'aura mana abincin dare, kar magrib ya min a kitchen" Maman hamdeeya tace "toh tafi min da hamdeeyan nan plz in tayi kuka se ki dawo da ita samun In yanka abun nan sharp sharp in na gama girkin dare se in zauna In had'a ko ban gama yau bama da asuba zan karasa kan de suyi wanka su shirya.."................

Sa'ban hamdeeya da dama take kan kafanta tayi tana cewa "toh mun gode, se anjima" suka fice suna dariyar Maman hamdeeya dake cewa "kin manta godo ne ba gode ba"...................

************

Bayan tafiyan khairi momma tace tana duban musharraf "babana kaga Allah ya bamu me aiki me hankali da natsuwa ga duk kan alamu yarinyar ta samu tarbiya me kyau", a hankali musharraf ya bud'e lumsassun idanunshi a zuciyarshi yace Lallai momma me kantin ball d'ince me hankali shi kam be gani ba a ganinshi ma she's the craziest person he ever met in his life don wallahi ganin marar hankali yake mata had'uwansu na farko tana aikin gudu a cikin estate da tsakar rana bata kunyan idon jama'a................

Had'uwa na biyu wasu gardawa na shirin keta mata haddi cikin ruwa da kuma magriba In me hankali da tarbiyace wasu iyayen ne zasu bar ersu fita zuwa irin low cost da magriba ko don hadarin da suka gani be isa su ce ta zauna a gida ba.............

Had'uwa na uku daga suka had'a ido mahaukaciyar ta nemi hantsilawa tsabar shirme da shiririta na cinta, sannan the most annoying part shine aikatau da tazo yi shi yana ganin iyaye masu son abin duniya ne ke tura yaransu zuwa aikin bauta a gidan wasu ko lokacin da suke shan wahalan rayuwa be ta'ba yadda momma tayi aikatau ba duk da kuwa ta so yin, Ina babanta In ubanta useless ne irin nashi Ina yayanta In bata da yaya ina en uwanta ko da shike shima nashi en uwan watsar da su sukayi a lokacin da basu da komai..................

Despite the fact that su suka ja musu ko ma menene tunda auren dole sukayiwa mamanshi da babanshi, but duk da haka he see no reason da ze fito da katuwar buduruwa aikatau me yasa baza tayi Sana'a ba and aikataun nan fa gani yake kaman tauye hakki ne tunda ba ta yadda mutum ze had'a karatu da shi....................

"Musharraf magana nake" boyyayiyar ajiyar zuciya ya sauke yana cewa "ni de ban gani ba momma, yarinyarn nan bata da hankali, ni de I don't like her" hararanshi momma tayi tace "sannu a Ina ka Santa da ka san bata da hankali? Kuma daga ganin mutum sau d'aya se kace baka sonta ba kyau fa musharraf wai ni me matsalanka da mata ne".................

'Bata fuska yayi yana pouting mouth yace "toh momma ni me nayi" "laaaaaa paapi kaima kanawa granny shagwa'ba but ni kana hana In maka" little da gangarowanta Kenan ta fad'a on top of her voice, had'e rai musharraf yayi yace "zo" zaro ido tayi tana kallon momma dukda tana jinsu amma shiru tayi tana me ci gaba da aikinta................

A sanyaye ta karaso don ganin ba dariya a face dinshi seda ta iso gabanshi tukun ya sa hannu ya kama kunneta ya murde, ihu ta tsala tana rike hannunshi cikin dashewar murya yace "Ina wasa dake? Am I your mate?" Da sauri ta girgiza kai hawaye na cika idonta kau da kai yayi yace "and last Friday kinki zuwa school sbd zanzo again yau wednesday amma kinki zuwa school wai don bani da lafiya, zaki sake missing school with no reason?"................

"A'a bazan sake ba I'm sorry paapi" hararanta yayi yace "lastly ban hana ki In manya na magana kina sa baki ba? And the fact of calling that crazy girl cutie ewwww" se ya dakata da maganan yana kwa'be fuska irin disgusting din nan, kan yayi ci gaba little dake hawaye sbd har yanzu be sakar mata kunne ba tace "but she's cute can't yhu........" "shut up!!!!" Ya daka mata tsawa kukan gaske ta fashe dashi hakan ya sa ya sake mata kunne tare da fasa fad'an abinda yayi niyyan fad'a................

tare da sulalewa yayi kwanciyarshi, jikin momma taje ta shige tana kuka kasa kasa don ta san in ta kuskara yaji kukanta dukan da be mata ba toh se yayi mata shi, a wurin tayi bacci momma ta ajiye abubuwan hannunta tana mikewa da ita a hannu zuwa kan two seater ta kwantar da ita, ta dawo ta d'auki traynta tayi kitchen...............

Washegari🌚🌚

Da wuri khairi ta tashi yadda ta saba ta kimtsa komai na gidan tayi musu breakfast bata samu sayawa su khairi lunch box ba haka zasuyi hakuri zuwa albashinta, wanka tayi musu kan ta sawa nabeel vest da boxers ta turashi gidan Maman hamdeeya aiko mintuna kad'an ya dawo da kayansu a leda kar'ba tayi ta bud'e tare da zarowa ta fara sa musu....................

Red plain trouser da milk riga, shine na nabeel wandon be kai kasa ba, se nabeela red trosern da milk riga se wani karamin hijab iya kirjinta sunyi kyau sossai jakansu na islamiyya ta d'auko ta cire littafin islamiyyan ta sa musu sabbi 20leaves guda uku uku da sabon pencil d'insu abinci suka ci kan suka sallami Dada khairi ta raka su har school da yake gaba kad'an da islamiyyansu sede ta baya................

Seda ta dawo kan suka karya ta tattara kwanuka ta wanke tazo ta zauna suka hau hiran rayuwa da dada, a lokaci d'aya tunanin d'an uwanta ya fad'o mata da kyar ta hana kanta kuka tayi mishi adu'a kan ta fad'a tunanin musharraf da muryanshi me sanyi da daad'i a zuciyarta tace "Allah sarki na mishi sanadiyar shiga ruwa na barshi da wahala" tuna irin atishawar da yayi tayi zuwanta se ta kuma jin ba d'aad'i ta tabbatar daren jiya beyi bacci ba...............

Tsaki tayi a fili tana bugun goshinta tace "meke damu na ne?" Wani tsakin ta kuma ja, Dada tace "lafiyanki kuwa khairyya?" Murmushi tayi tana cewa "klau Dada ba wani abu" ci gaba da hiransu sukayi bayan tayi iya kokarinta wurin cire tunanin musharraf a ranta....................

#comment
#vote
#share

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️4️⃣0️⃣▶️4️⃣1️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Friday

Haka kawai khairi ta tsinci kanta cikin farin ciki da ta rasa dalili har take alaqanta hakan da aikin da zata fara ne wadda ta tabbatar da yardar Allah shine rufin asirinsu, da wuri ta tashi tayi musu

breakfast tana sauke breakfast ta d'aura jollof don ya zama na rana tunda bata nan, tayiwa su nabeel wanka ta shirya su cikin uniform d'insu seda ta sa musu breakfast d'insu kan ta shiga wanka tana fitowa jollof d'inta yayi ta kwashe musu a karamin cooler d'insu ta kai d'aki ta ajiye................

Cikin A shape gown material ta shirya tana sa kayan tana tunanin d'an uwa don shi ya d'inka mata, sossai gown din ya mata kyau, ponytail style tayi parking gashinta da ta manta when last ya ga kitso black silky hijab da iya karshi cinya ta saka ta zura black robber silifas d'inta, wani paper bag ta samu ta zuba d'an abinda zata iya nema In taje Chan, fiskanta fayau ba komai ko d'igon baki d'aya baza ka gani ba haka jikinta ma................

Cikin sauri ganin bakwai da rabi tayiwa dada sallama, dada tace "Allah ya tsare ya kiyaye, ya kuma bada sa'a ki ci gaba da kula dan Allah, ki kuma rike mutuncinki kiji tsoron Allah a duk inda kike, sannan ki gujewa 'bacin ranki don kin san sakamako" a sanyaye khairi tace "In shaa Allah" ta kama hannun kannenta suka fice, napep ta tara musu don bata son suyi latti seda suka biya ta ajiye su kan ya wuce da ita GRA................

Yana ajiyeta ta biyashi kud'in shi ta nufi gate din gidan gabanta na fad'uwa a kai a kai, knocking tayi malam d'ahe ya bud'e a mutunce suka gaisa inda yake tambayarta wurin wa ta zo ta sanar dashi itace sabuwar me aikin gidan, maraba yayi mata tare da bata hanya ta wuce, taku takeyi cikin salon tafiyanta da kaman tana tausayin kasa ta nufi main entrance na gidan a bakin kofa ta tsaya tare da knocking.................

Wata bakar buduruwa ta gani da ta san zata girme mata da shekaru masu yawa duk da baza ta haife ta ba, murmushi buduruwar ta sake mata Tace "sannu" da sauri khairi tace "Ina kwana" nuri tace "lafiya wurin momma kika zo?" Khairi tace "a'a ni ce sabuwar me aikin gidan" khairi ta d'auka zata ga nuri ta chanza fuska se taga ta fad'ad'a fara'arta Tace "Ohk sannu da zuwa bismillah"...............

Shiga khairi tayi cikin jin daad'i don bata ga alamun wulakanci a gida ba kwata kwata, a kasa ta samu wuri ta zauna tana gaida miemie da Maryam dake parlorn cikin fara'a miemie ta amsa ta yayinda ko kallo bata ishi maryam ba, nuri na kallon miemie tace "je ki kira mata momma" Miemie ta mike ta haura stairs ba jimawa se gata da momma, cikin fara'a tayiwa khairi sannu da zuwa khairi ta gaida ta, ta amsa tana tambayarta gida da mamanta, amsawa khairi tayi da "suna Lafiya Alhamdulillah" momma tana nuna khairi tace "ga fa sabuwar me aikinmu ummulkhairi sunanta"..................

Miemie ta d'aga mata hannu da murmushi itama ta mayar mata da murmushi, nuri tace "momma ina kika samu me aiki kyakyawa er fulani haka?" Momma tace "hajiya rukayya ce ta turomin ita wlh" Miemie tace "and she looks cool and innocent" momma na murmushi tace "ai itace little ke ta baku labari" wara ido miemie tayi tace "dama itace cutie? Ashe da gaskiyan little masha Allah"................

Maryam dake kallonsu da haushi da kuma mamaki ta ja tsaki, tare da mikewa ta haye sama da kallo suka bita kan miemie ta ta'be baki, momma tace "tashi ummu muje In nuna miki d'akin da zaki dinga ajiye abubuwanki" mikewa khairi tayi ta bi momma d'akin kasa dake daura da kitchen ta nuna mata ita kuma ta shige, tiles ne shimfid'e a kasan d'akin se babban katifa guda d'aya dake manne jikin inda window yake daga Chan gefe sallaya ce shimfid'e, se fanka dake ta aikin juyawa shikenan se toilet...............

Jakan hannunta ta ajiye ta fito, kanta a kasa take tambayar momma meza'a d'aura musu na breakfast ta tabbatar ba wadda ya karya a gidan, momma tace "nuriyyah nuna mata kitchen da store, ki de nuna mata abinda ya kamata" mikewa nuri tayi anan khairi ta san sunanta, bin bayanta tayi zuwa kitchen a tsanake nuriyyah ta nuna mata duk abinda ke kitchen d'in da store ta kuma nuna mata yadda zata kunna gas da electric cooker se hot plate.................

Nuri tace "ki d'aura doya da kwai se ki dafa mana black tea da kayan kamshi" Kai khairi ta gyad'a nuri ta fita, store khairi ta nufa ta d'auko doya ta fara ferewa se kuma ta tuna da bata san yawan yadda zatayi ba kar tayi yayi kad'an ko kuma yayi yawa, fita tayi maryam kad'ai ta gani zaune a parlorn gabanta ta karasa tace "Anty Dan Allah ya yawan doyan da zan dafan?"..................

Tafi mintuna biyu a tsaye kan maryam ta d'ago ta watsa mata harara a tsawace tace "kinga na miki kama da sa'arki ko ta uwarki da zaki zo ki tsaya min a ka?" Baya khairi ta matsa tare da sake murmushi dukda taji zafin sako dada da tayi amma ko a fuskanta be nuna ba ta juya ta nufi komawa kitchen din kenan taji muryan momma tana cewa "lafiya khairi?"..............

Dukda taji abinda maryam din ta ce mata hakan kuma be mata daadi ba amma se ta fuske da tambayarta me take so, khairi tace "dama hajiya yawan doyan da zan dafa nake tambaya" momma tace "mu biyar ne a gida ki dafa daidai yadda kika san ze ishi mutane biyar" Da "toh" khairi ta amsa tare da shigewa kitchen din tana mamakin maryam daga tambaya, ta'be baki tayi ta fara aikinta sharp sharp ta dafa doya ta baza shi tire ta d'aura mai tare da kad'a kwai, a d'ayan hot plate ta d'aura wani tukunyan ta zuba kayan kamshi da lipton bayan man yayi zafi ta fara jefa doyan a kwai tana sawa cikin mai.................

Ba 'bata lokaci ta gama ta zuba a wani babban cooler da ta gani cikin kitchen carbonate ta d'auka ta fito ganin dining table daga chan gefen parlorn an rufe wurin da labule shara shara milk me ado sossai, kan ka haura se ka taka steps akallah hudu, bayan ta ajiye ta koma kitchen ta d'auko flask da ta zuba black tea din ta kuma kaiwa kan dining, ta kara komawa ta d'ibo plates da spoons da fork se cups ta kuma kaiwa a kan dining din ta ga roban yaji da kuma na sugar se kawai ta gyara musu zama ta kuma komawa kitchen din.................

Abubuwan da tayi anfani dashi ta wanke tana gamawa ta bud'e kofan da ta gani a kitchen din bayan na store se taga waje ne wurin akwai dakali da manyan bafs a gefe se pampo a chan gefe kasan wurin kaman ana wanke wanke idan suna dayawa, kujeran tsuguno da ta gani a gefe taja ta zauna tana tunanin rayuwanta................

Sossai take jin kad'aici tana missing su sulaimi tana missing d'an uwanta tana missing Abbanta, hawaye ne ya fara gangaro mata 'Allah ka saka mana ya Allah kayi mana sakayya' a fili ta furta hakan tana fashewa da kuka ta jima batayi kukan Abbanta ba amma abun kullum yana zuciyarta yanzu da take zaune bata komai ne suke fad'o mata..............

Daga kanta taji ance "lafiya khairi kike zaune ke kad'ai anan?" Da dabara ta goge hawayenta tare da sake murmushi tana juyowa tace "Lafiya klau momma, me za'a d'aura na rana" momma tace "shinkafa za'a yi da miya se cowslow amma yanzu ki had'awa musharraf fruit salad hope kin iya?" Khairi tace "Eh na iya" momma ta kuma cewa "kaman baki d'ibi doyan ba" a ladabce kaman de yadda take magana da momman tun farko tace "na riga na karya a gida bana jin yunwa".............

Momma tace "Ohk" har ta nufi komawa se kuma tace "akwai fruits a fridge karamin nan a ciki zaki samu su cabbage, sannan a deep freezer akwai kayan miya a gyare suke a wanke blending kawai zakiyi, and naman kaza shine a blue leda, naman rago a orange leda, se naman sa a green, kifi d'anye kuma a black, suma de a wanke suke zubawa kawai zakiyi in zakiyi anfani dashi leda d'aya muke anfani da ko wani meal, se farare na tuwo su kuma wankakkun shuwaka, yakuwa, se zogale ne a cikinsu".................

Khairi tace "toh hajiya" momma tace "ki ce min momma, ban san dalili ba but duk cikin masu aikina kinfi ko wacce shiga min rai jinki nake kaman su Amrah" murmushi kawai khairi tayi itama tana jin son momman, mikewa tayi taje ta d'auko tray da roba da kuma knife ta dibo kankana, ayaba, lemu, mangoro se gwanda, a verender din ta dawo ta zauna ta fara cire kwallon kankanan tana yankawa kanana kanana.................

Bayan ta gama da kankana ta yanka sauran duk a kai kanana bayan ta gama ta duba kitchen din a fridge ta samu peak milk na gwangwani, a wurin spices ta samu foster clark da kuma wani gwangwanin sugar bayan na dining d'auka tayi ta koma ta zuzzuba wadda ze isa ta juya sossai ta d'auka ta kai fridge ta ajiye................

Ta koma wurin freezer ta fiddo kaza, da kayan miya, cikin lokaci kankani ta gama stew daad'i take ji sossai In tana girki haka take jin cikin d'in kaman nata, a tsabtace take komai har ta gama rice, tana son duba time amma ba waya hannunta balle agogo, diban kayan cowslow din tayi ta koma kan varender ta fara yankawa a natse har ta gama tayi grating carrot, kitchen ta koma ta fara dube dube har ta samu wani robber me kyau sossai ta had'a a ciki ta rufe da foil paper.................

Daga parlor taji momma na kiranta, da sauri ta fito sede ta d'anyi turus jin yadda bugawar zuciyarta ya chanza da sauri ta d'ago se idonta ya fad'a cikin nashi kallon seconds biyu ya mata ya d'auke kai, zaune yake kan one seater kafanshi zube a kan center table sanye yake da wata arniyar gezna milk anyi ado da black zare a gaba ya kafa hula black, yayi kyau sossai..................

Har ranta take mamakin na miji da irin wannan haske da kyaun, a gaban momma ta duka tace "gani momma" ta'be baki musharraf yayi a zuciyarshi yace 'karere se kace ita ta haifeta' ci gaba da danna wayanshi yayi, yana ji momma tace "kawowa Musharraf fruit salad dinshi" tana mikewa tace "Ina yini?" Ko d'ago kai be yi ba balle ya amsa, har ta wuce a bowl ta zuba mishi ta sa spoon tare da d'aurawa a kan karamin tray ta fito............

Har ta nufi saukewa a kasa se taga ya zame kafanshi yatsotsin kafanshi dogi masu d'an kauri ta bi da ido, masha Allah kafanshi ya mata kyau, a kan table din da ya janye kafan ta ajiye, ta juya ta nufi kitchen kenan taji an turo kofa muryan little taji ta shigo da gudu tana ihun paapi, paapi, suna had'a ido ya sakar mata harara da sauri ta koma tace "Assalamu alaiikuum" murmushi ne ya kubcewa musharraf, momma da khairi jin irin sallaman da tayi kaman waka a lokaci d'aya idonshi ya sauka akan kumatunta da ya lotse sossai se fararen hakwaranta da suka bayyana kaman bata san wani abu wai shi cin abinci ba tsabar farinshi.............

Da sauri ya d'auke kai yana maidawa kan little da ta karaso tana cewa "paaapi na a yi Anty Amrah na o......."(paapi ba ka ga Anty Amrah ba ta......) maganan ya katse ne sadda idonta ya sauka kan khairi se kuma ta waro su tare da daka tsalle "cutieeeee oyoyoooo" Da gudu ta nufi khairi ta rungumeta, d'aga ta khairi tayi tana mamakin rashin nauyinta tace "oyoyo little pretty, ya kk" kallonsu yayi na mintuna kan ya d'auke kai ya maida kan fruit salad dinshi...............

Sede duk hankalinshi na kansu yana mamakin me yasa little da bata da saurin sabon da mutane duk da tana da surutu amma ta saba da khairi a gani d'aya baki ya ta'be, yana jin little na cewa "cutie yau ke zaki min wanka ki shiryani, and feed me couse am starving" murmushi khairi tayi zata yi magana taji momma na cewa "a'a little ki je Anty nuri tayi miki duk waennan abubuwa don khairi de aiki ne da ita".............

Khairi ta ce "momma na gama aikina gabad'aya na rana, zan iya mata" momma ta d'an wara ido ta ce "Lallai haka kike da saurin aiki?" Murmushi kawai khairi tayi tana duban khairi tace "where is ur room dear?" Little tana kallon sama tace "upstairs cutie" saman khairi ta nufa a sace ya bi su da kallo lokaci d'aya yana mamakin turancinta abinda be ta'ba zaton tana ji ba balle tayishi fluently haka, ta'be baki yayi tare da ci gaba da shan fruit salad dinshi.............

A chan d'aki kuwa wanka khairi tayiwa little se surutu take zuba mata tana amsawa kaman bata so, bayan ta shirya ta cikin kananan kaya da ta san ta fi sakawa a hankali tace "little pretty naji kina cewa ya musharraf paapi is he ur father?" Little tace "yes he's my father, momma my grandmother, And my anties are Anty nuri, Anty miemie and Anty Amrah".............

Faduwa gaban khairi ya dinga yi da ta rasa menene dalili ko don tana mamakin kaman musharraf ne wai ya haifi 'ya kaman little ne ko me, maganan little ne ya dawo da ita daga tunaninta a hankali tace "and ur mom?"................

*SORRY* 🙏🙏🙏

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️4️⃣2️⃣▶️4️⃣3️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

"Mamana ta rasu" cikin tausayawa khairi tace "sorry pretty Allah yaji kanta" murmushi kawai little tayi, tana shafa cikinta tare da yin puppy face murmushi khairi tayi tace "Ohk mu je ki ci abinci" suna bud'e kofa ana bud'e na d'akin momma had'a ido sukayi da wata buduruwa da bata sani ba, wani kallon banza ta watsa mata a d'age tace "who the hell are yhu?" Kai a khairi ta kawar tace "house help" waro ido tayi tace "and yhu have the guts na hawan upstairs baki san maids basa hawa nan ba".............

Little tace "o'o Anty salima I invited her here, and momma ta sani" harara saliman ta watsa wa khairi kan ta wuce ta sauka, suma sauka sukayi ran khairi ba daadi tana tunanin su waye waennan en matan gwara ma salima ta d'anyi kama da mutanen gidan amma banda maryam kuma bata ji little ta kira sunansu a cikin mutanen gidan ba...........

Little na ganin Amrah zaune parlor tana cin abinci tace "Anty Amrah see the cutie I was telling you about" kallon khairi Amrah tayi tana murmushi tace "hi cutie" murmushi khairi tayi tana tabbatarwa kanta Lallai tayi sa'an gidan aiki don duk yaran momma bayan musharraf suna da tsananin kirki haka momman ma, Amrah na sa spoonful na abinci a bakinta tace "yhu cooked?" Kai khairi ta gyad'a waro ido Amrah tayi cikin sauri ta had'iye abincin tace "wow you cooked well Amma kinyi catering school a abroad ko?"...........

Dariya khairi da little sukayi yayinda salima ta ta'be baki ta ci gaba da danna wayan da takeyi, a fili tace "I don't think ko airport maid din nan ta ta'ba zuwa" Shiru Amrah tayi, little ta kuma rike hannun khairi tana kallonta, khairi na murmushi tace "thanks, bari In sakowa little" tare da nufan kitchen, Amrah tace "yana dining na fitar"............

Chan khairi taje ta sakowa little ta dawo parlorn a kasa kan rug ta zauna little ma tayi irin zamanta, a baki ta dinga bata har ta ce ta koshi Amrah na zaune gefe ta gama cin abincin tana kallo...........

Bayan ta gama bata ta had'a plate din Amrah da wadda little taci tayi kitchen ta had'a da kwanukan safe ta fara wankewa, biyota little tayi tana taya ta da surutu har ta gama ta share da towel me tsabta ta ajiyesu mazauninsu...........

D'akin da aka bata taje tayi alwala tayi sallahn azahar kan ta kwanta, wani bacci bacci take ji har ta fara lumshe ido taji an shigo, d'ago kai tayi se taga maryam ce tsaye tana yatsina tace "am not interested da abinda kika dafa, I want jollof na couscous with vegetable" bata jira Cewar khairi ba ta fice...........

Mikewa khairi tayi ta fito, kitchen ta shiga ta fara had'a mata dayake daidai na mutum d'aya ne in less than 30mins ta gama ta zuba a plate ta kawo mata parlorn a kan center table ta ajiye tare da jawo mata gabanta..........

Turo kofa taji anyi ko bata juya ba bugawar zuciyarta da kamshin turarenshi ya sanar da ita waye ne ya shigo runtse ido tayi don har ga Allah ita bata son encountering dashi, sallama kawai yayi maryam ta amsa, ya nufi dining.........

Kujera yaja ya zauna tare da fiddo waya ya fara dannawa ran nan a had'e har ta juya ta nufi d'akinta taji maryam tace "ruwan fah ko ni zan kawo wa kaina?" Fridge din dake gefen dining taje ta d'auki drinks d'aya da ruwa ta koma kitchen ta sa a tray ta d'aura cup tana fitowa taga maryam ta koma kan dining tana ta zuba duk da bata jin me take fad'a amma ta san da musharraf takeyi bayan ko d'ago kai be yi ba tun zaman ta balle ya tanka..............

Taje ajiye tray din taji maryam na cewa "haba ya musharraf ya za'ayi in zauna Ina ta magana kaki ko kallo na se kace baka sanni ba?" Shiru ya kumayi ta kuma cewa "ko ma menene ni de Ina sonka so kuma na aure, and am very sure zanyi nasara se na koya maka sona daga baya".............

A zafafe ya d'ago yace "leave" shagwa'be fuska tayi tana cewa "am sorry sweet......" "I said leave" ya kuma fad'a mikewa tayi tana tura baki zata wuce yace "and abincin nan wa kika barwa? Ko ke kike sayan kayan abincin da zaki sa a dafa ki tashi ki barshi a wurin? Common my friend take this food and finish it now!!!!"............

Ya karasa da d'an tsawa har khairi ma seda ta tsorata ajiye trayn hannunta tayi da sauri ta juya one step tayi taji ance "Ke!! Serve" juyowa tayi don ta san da ita yakeyi zuciyarta na bugawa ta fara zuba mishi abincin hannunta se rawa yake duk da idonshi akan waya yake amma yana kallon yadda jikinta ke 'bari bayan ta gama sa mishi ta tura gabanshi d'an daidai ta sa sam bata cika mishi ba..........

Ja yayi ya fara ci kaman baya so, tana juyowa suka had'a ido da maryam tana aiko mata da sakon harara bayan d'ura abincin gabantan kawai takeyi ba wai don tana jin yunwa ba, murmushi ne ya kubcewa khairi da sauri ta bar wurin tana murmushi sossai..........

Maryam kuma ganin murmushin da khairi tayi se taji kaman da ita takeyi haushin yarinyar ya kara ninkuwa a ranta dama tunda ta d'aura ido a kanta taji bata sonta, wannan couscous din da ta saka ta yi ma kawai don ta bata wahala ne se gashi ita aka had'a da wahalan d'urawa don da d'an yawa a plate din gashi musharraf ya wulakanta ta a gabanta, takaici ne ya zo mata har wuya hawaye ya cika idonta a haka kuma ta ci gaba da d'ura couscous............

Khairi na shiga d'aki ta fara dariya don abun ya bata dariya lokaci d'aya kuma ya bata haushi ace mace tana tallatawa na miji kanta yana dizga ta, khaih Allah ya sawwake wasu matan ke

bada sauran mata, ita kuwa abunda baza ta iya ba kenan koman son da takeyiwa namiji baza ta iya fara fad'a mishi ba matukar ba shi ya fara ba, tambayar kanta tayi to ma me son ne oho..........

Ta karasa da ta'be baki tana me kwanciya kan katifa juye juye ta dinga yi tana tunano maganganun da maryam ke fad'awa musharraf wani ta'be baki kawai takeyi se murmushi jefi jefi, ganin baccin ba zuwa ze yi ba ta mike ta fito, nuri da Miemie ta gani zaune kan dining suna cin abinci Amrah na kwance kan doguwar kujera tana kallo salima ma na zaune tana chat, bata ga maryam ba haka musharraf ma baya parlorn amma da alamu be jima da ficewa ba don har yanzu kamshin shi be bar parlorn ba............

Sannu tayiwa Amrah da salima, Amrah ce kawai ta amsa da "ai ke za'ayiwa sannu cutie" murmushi khairi tayi tana cewa "kema cutien zaki na cewa?" Amrah tace "tab ai dole in little ta sawa mutum suna bakwa kira kun ta fad'a da ita kenan har kuka se tayi" murmushi khairi tayi tace "Lallai little pretty, bari nayi wanke wanke, plz Anty Amrah ko kin san me za'ayi da dare?"...........

Amrah tace "Ke ma Antyn?? A'a ki kirani Amrah na plz ni ba babba bace" Ta karasa da turo baki, dariya khairi da Miemie dake dining suka sake, had'e rai Amrah tayi tace "Ke kuma wa ya sa bakin ki?" Miemie tace "oho dai kunne na ya ji kuma se naki dariya?" Khairi tace "toh yi hkr Anty Amrah fad'amin me za'ayi da dare"...........

Amrah tace "Again!! Ni de in zaki ce min Anty Toh zaki shekara magana ban amsa ba don bazan amsa ba Allah na san in bamuyi sa'anni ba sede ki girme ni" nuri ma murmushi tayi tace "cutie karki yarda ma ki ce mata Anty don I'm very sure kin girme ta, and naji momma na cewa za'ayi tuwon semo da miyan zogale da gyad'a" Kai khairi ta gyad'a kan ta karasa dining din ta fara tattare kwanukan don ta tabbatar sun gama ci...........

Bayan ta gama wanke wanke ta d'aura tuwo cikin lokaci kankani ta gama ta sassaka a leda ta shirya a cooler, seda taje tayi sallan la'asar ta dawo kan ta d'aura miya, tana cikin daka tarugu taji an rungume ta ta baya ko bata juya ba ta san little ce murmushi tayi tana juyowa tace "little pretty har kin tashi daga baccin?" Tura baki gaba tayi tace "Eh momma ce ta tashe ni wai la'asr yayi kuma ba kyau bacci bayan la'asar"..............

Khairi tace "hakane ai little pretty, yanzu kinyi sallah?" Tace "Eh, cutie kin iya zobo drink Ina so na sha kuma paapi na ma yana so, nace momma tazo ta mana wai In tambaye ki In zaki iya kiyi mana" khairi tace "worry not pretty zaki sha zobo" tsalle little ta fara cikin jin daad'i...........

Haka ta ci gaba da damun khairi da surutu har ta gama aikinta har zobon, a wani farin roba ta sa ta sa a fridge, duk inda tayi little na bayanta, yarinyar ta shiga ranta sossai ta lura little dinma na sonta...........

Bayan ta gama komai ta wanke duk abinda ta 'bata ta kuma goge kan kitchen island, gas

cooker da hot plate. little ta ja ta wai suje su zagaya gidan tunda bata san ko Ina a ciki ba, haka ta bita suka dinga zagayawa har garden, sun jima sossai a chan kan suka wuce boysquaters anan suka samu matar malam d'ahe inna laure  ita ke share share da goge goge a gidan da sassafe take shiga tayi komai kan gari ya gama haske ta gama ta koma bata sake lekowa se washegari...........

Gaisawa sukayi da khairi daga nan suka dawo cikin gida, a parlor suka samu momma tana kallon khairi tace "wai sannu ummulkhairi naga har kin gama ayyukanki gabad'aya, harda zobo kikayi na tabbatar wannan yarinyar ce ta saki yi dole"...........

Dariya kawai khairi tayi, momma tace "zaki iya tafiya, se ki d'ibar muku abincin a food flask, ya sunan kannenkin?" Khairi tace "nabeel da nabeela" momma tace "twins ne" khairi tace "Eh" momma tace "masha Allah ki duba store akwai gora se ki diba muku zobo zaki ga wani maroon coolar me d'an miya a ciki da karamin basket se ki sa muku abincin a ciki"..........

Khairi tace "toh mun gode" ta mike taje ta sako musu, ta fito d'akin da aka bata ta shiga ta d'auko jakanta ta fito d'ari biyu momma ta bata tayi kud'in napep godiya ta mata, tayiwa su Amrah sallama har get little ta raka ta kan ta dawo...........

A natse take tafiya kaman me tausayin kasa kanta kasa kaman ance ta d'aga kai se idonta ya fad'a cikin nashi ya sauya kaya daga manya zuwa kanana, milk jeans da maroon shirt me guntun hannu kafanshi sanye da normal shoe na maza, zaune yake saman mota shi kad'ai hannunshi rike da taba yana zuka............

"Subhanallah gentleman like him da shan taba? Be son lafiyan jikinshi ne?" A fili tayi maganan tana ji mishi takaici da haushi ta tsani taban nan kai duk wani kayan maye ma, tsintar kanta tayi da adu'ar Allah ya sa tabar kad'ai yake sha...........

Satar kallonshi tayi se taga shima ita yake kallo da sauri ta kawar da kai tana jin tafiyar na mata wuya natsuwa na neman barinta tsabar karfin kwayar idonshi a kanta.........

Shi kuwa ko a jikinshi kallonta yake shi kad'ai ya san me yake karanta a jikinta, dukda ya ga ta kasa tafiyar yadda ya kamata sabd kallon da yake mata hakan be hana shi ci gaba da kallonta ba. Allah ya taimake ta se ga napep da sauri ta tsare ta shige tana sauke ajiyar zuciya, kau da kanshi yayi ya ci gaba da shan tabanshi hankali kwance.............

Tafiyar mintuna a kalla 20 ya kawo ta gida, sauka tayi ta sallame shi ta shige gida, da gudu su nabeel suka rungumeta suna mata oyoyo ajiye kayan hannunta tayi ta tarbe su da murna itama tana tambayarsu ya school da lafiya suka amsa ta..........

Ta karasa tayiwa dada san da gida tana zama gefen taburman da take kai, nan ta fara ba Dada labarin duk abinda ya faru a ranar duk labarin little ne da yadda yarinyar ta shiga ranta se mutuncin mutanen gidan...........

Suna nan zaune suna labri har aka kira magrib suka mike sukayi sallah, yadda al'adarsu take karatu ne bayan magrib hakan kuwa sukayi seda akayi isha suka ci abinci, khairi tayi wanke wanke don akwai kwanukan abincin rana da su nabeel suka ci............

Ta shirya kwanukan momma a basket din ta Adana basuyi wani hira ba suka kwanta don kowa ya gaji..........

Kwance yake kan gadon momma yana aikin  danna waya, turo kofan akayi d'ago kai yayi se yaga momma ce tace "wai ni ka zo ka min bake bake a gado bayan ka san lokacin bacci na yayi a kanka kake so in kwanta?"..........

Murmushi ya sake yana cewa "momma zan tafi jibi flight na 10 zan bi, if possible a rubuta duk abinda babu gobe se nuriyyah suje su sayo, zan basu kudin shopping dinsu a goben ma" momma tace "Ohk toh se da safe wannan kam, and Musharraf In kaje ka daure ka dinga cin abinci plz In ka dawo bana jin daadin ganin yadda kake raman nan, ko de har yanzu kana sa damuwa a ranka
ne?"............

Murmushin yake yayi yace "ko d'aya momma" jin yadda ya amsa mata a takaice yasa ta san be son maganan shiru tayi ta kudurta a ranta a gobe ita da khairi zasu mishi danbun nama, donuts da duk wani abinda ta san baze 'baci nan kusa ba ya tafi dashi kila ya taimaka mishi..........

Mikewa yayi yace "seda safe mother" tace "good night and kar a manta da alwala da kuma adu'ar kwanciya yana murmushi ya fita a zuciyarshi yace se kace little?............

A parlor ya samu su nuriyyah nan ya fad'a musu gobe zasu je shopping ko wacce ta rubuta abinda take so ze duba a goben, godiya suka mishi ya fice ba tare da ya amsa musu ba...........

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*wipe away the tears of the orphans in order to attain the pleasure of the most merciful and a house in paradise*

Page➡️4️⃣4️⃣▶️4️⃣5️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Washegari

Karfe bakwai da rabi dai dai yayiwa khairi a GRA, duk gidan ba wadda ya tashi bacci kasancewar weekend ne, d'akin da aka sauketa ciki ta shiga ta ajiye bag dinta, tare da komawa

kitchen ta fara dube dube duk tunaninta ya tafi kan ko me zasu ci da safen? Tana d'aura hannunta kan kitchen island se taji paper an d'aura karamin robbern tumeric a kai d'auka tayi ta bud'e se taga an sa "kiyi pepper soup na kifi, za'aci da bread se kiyi tea but na soya beans" gyad'a kai tayi kaman a wurin aka bata umarni tare da fara aikin.................

Cikin lokaci kankani ta gama tare da shiryawa a dining ta koma kitchen ta wanke duk abinda ta 'bata, tana share kitchen din taji zuciyarta ya buga gabanta ya fara fad'uwa da sauri ta juya se kuwa idonta ya fad'a cikin nashi da sauri tayi kasa da kai tare da cewa "Ina kwana?" Kaman baze amsa ba se kuma yace "Lafiya" tare da ci gaba da tsayuwarshi.............

Juyawa tayi ta ci gaba da goge kan gas se kuma taga kaman hakan be kyautu ba se ta juyo tace cikin tsiririyar muryarta "ranka ya dade akwai abinda kake bukata ne?" Juya idonshi yayi tare da ta'be baki yace "just coffee" Kai ta gyad'a ya juya ya fita, coffeen ta had'a mishi tare da sa cup din kan karamin tray fari ta fita dashi a kan one seater ta Ganshi zaune se lokacin ta samu zarafin kallonshi da kyau sbd kanshi dake kan waya...............

Sanye yake da jallabiya coffee color me guntun hannu da ya matukar amsar fatan jikinshi, duk da be yi wanka ba amma kamshin shi duk ya cika parlorn, ganin ze d'ago yasa tayi saurin karasowa ta janyo center table ta ajiye mishi, ko kallonta be yi ba har ta juya ta fice, komawa tayi bakin aikinta Bayan ta gama goge gogen ta fice varender ta fara wanke mop din da tayi anfani dashi bata hankara ba taji an rungume ta, juyowa tayi ta d'aga ta sama "morning cutie" khairi na murmushi tace "morning pretty, ya kk?" Little tace "lafiya klau cutie Ina friends d'ina?" Khairi tace "sun je islamiyya, ke bakya zuwa ne?" Little tace "a gida malam ke zuwa ya mana da Anty miemie da Anty Amrah, ko wani weekend da yamma" kai khairi ta gyad'a tace "wa ya miki wanka?"...............

Little tace "momma tare muka sauko ma she's at the sitting room" khairi ta ajiyeta a kasa tare da kama hannunta suka fito, cikin ladabi ta gaida momma nan ta shaida mata ayyukan dake gabansu yau, da kai kawai khairi ta amsa, se misalin karfe goma su Amrah suka fita da, gabad'ayansu har little, da su salima.............

Ba sune suka dawo ba se azahar sayyaya kam sossai sukayi, a lokacin khairi ta jima da gama abincin rana har tayi donuts, naman ta ma yana wuta, da gudu little tayi kitchen da leda a hannunta "oyoyo cutie" khairi na murmushi tace "oyoyo kun dawo?" Little tace "yes cutie gashi na sayo miki tsarabar chocolate" khairi tace "aiko na gode" bata fiddo daga leda ba kawai lekawa tayi murmushi shimfid'e a fuskanta, bata kai ga magana ba taji momma na kiranta................

Fitowa sukayi inda momma ta bata umarnin tattare kayayyakin kitchen ta kaisu wurin zamansu d'iban sayayyan ta fara da kad'an kad'an har ta gama, yau kam bata gama aikinta da wuri ba sam sbd ayyukan da suka mata yawa se bayan magrib ta gama goge kitchen a gurguje ta koma d'akin da yanzu ya zama nata duk da ba kwana takeyi a cikinshi ba, ta d'auko bag dinta ta fito..............

Momma dake zaune parlor ita da su Amrah da little tace "sannu khairi yau kam Kin sha aiki, gashi har dare ya miki bari inyi magana da driver se ya mayar dake gida sbd baza ki samu napep da daren nan a unguwan nan ba" kan khairi kasa tace "Toh na gode momma" little tace "Ayyah momma tunda da driver za'a kuma daga chan nan ze dawo In bisu mu dawo da driver?" Amrah tayi saurin cewa "Eh Allah nima zanje" momma tace "Toh shikenan kuje se kun dawo"................

Da gudu Amrah taje ta d'auko gyalenta ta gangaro don ita kam Allah ya d'aura mata son khairi ba kad'an ba, Jan hannunta tayi little ta d'auki basket din abincinsu suka fito suka wuce, har kofan gida khairi tayi mishi kwatance yana parking suka fito Amrah tacewa drivern "Dan Allah bari mu gaishe su mu zo baba Adamu" yana murmushi yace "toh 'yata" sossai yake jin daad'in aiki da su momma sbd mutuncinsu sam basa rena na kasa dasu, dukda a karkashinsu yake kuma motarsu amma se sun had'a shi da Allah akan aikinshi............

Khairi na sallama nabeel da nabeela suka taso da gudu suna mata oyoyo itama rungume su tayi na mintuna kan ta sake su tana cewa "ga friend na maku" wara ido sukayi suna kallon Little dake makale da hannun khairi, nabeel ne ya fara cewa "hi" se nabeela ta fad'a murmushi little tayi tace "hello twins kuma kuna da kyau kaman cutie amma baku kaita ba, sunana Zarah and yhu?" Nabeel yace "am nabeel" nabeela tace "nabeela"...........

Amrah ce da ta gaji da tsayuwa tace "hi twins I'm Anty Amrah Adda khairi's best friend" waro ido sukayi har khairi kan suka fashe da dariya yayinda khairi ke murmushi, shagwa'be fuska Amrah tayi tace "au ni ba kawar ki bace?" Khairi tace "babba ma kuwa" nabeel yace "but Adda sulaimi min andi"(Adda sulaimi muka sani)"............

Har khairi zatace bata jin fulatanci se ta tuna jiya taji little nayi, Amrah tace "ha toi Adda sulaimi mai woni?"(a Ina Adda sulaimin take?) nabeela tace "ha jalingo"(a jalingo) Amrah tace "Toh kunga wadda yake nan dashi akeyi nice a nan sulaimi a jalingo" zasu sake d'auko wani maganan khairi tace "kinga Adda Amrah muje ki gaida dada dare nayi kar momma tayi fad'an kun zauna"............

Karasawa wurin Dada sukayi a cikin d'aki da tun d'azu take jinsu kasa Amrah ta duka tace "'yan nyalli jam na dada?"(mun yini lafiya dada?) dada tace "jam noi shomri noi saare"(lafiya ya gajiya ya aiki?) Amrah tace "jam wala ko d'ume"(lafiya kalau ba komai)...............

Tana mamakin me yasa ta amsa mata bata kallonta se wani direction d'in bata gama tunanin ba idonta ya fad'a kan sandar dada da take anfani dashi wani tausayinsu ne ya rufeta don ta tabbatar Dada bata gani gashi bata ga alamun akwai wani namiji a gidan ba don d'akin dai kwaya d'aya dashi ake anfani d'akin zaure a rufe............

Duk tana Chan duniyar tunani little suka gaisa da dada, har seda khairi tace "Adda Amrah lafiya?" Firgigit tayi tana cewa "lafiya Adda khairi, dada ba kinga khairi ba na hana ta ce min

Anty ta dawo Adda bayan kuma ta girme ni" ta karasa da tura baki kaman tana gaban momma.............

Dariya sauran yaran sukayi har khairi dada kuma tana murmushi tace "Toh khairi kinji bata son Adda ko Anty ki ce mata Amrahn ta" Amrah tayi saurin cewa "yauwa dadanmu" tana yiwa khairi gwalo dariya suka sake yi...........

Khairi ta mike tace "bari In kawo muku ruwa" Amrah tayi saurin cewa "Ke yi zaman ki, tafiya zamuyi mun bar baba Adamu a waje yana jiranmu oya little lets go"..........

Sallama sukayiwa Dada tana ci musu albarka, har mota nabeel da nabeela da kuma khairi suka raka su, suna d'aga musu hannu har suka tafi...........

Da hira suka shigo parlorn se kuma sukayi shiru ganin musharraf zaune kusa da momma yana shan coffee, little ce ta karasa tana hawa jikinshi tace "I miss yhu paapi" yana gyaramata zama yace "ba wani ba kin samu wata Chan kin manta da ni ba" little ta shagwa'be fuska tace "waye kuma wata Chan paapi" har ze kira sunan khairi se kuma ya Basar yace "you better start saying sorry"............

Tace "sorry paapi" yace "Ohk then" hiransu momma ne ya d'auke mishi hankali duk da sam be yi kaman yana jinsu ba inda Miemie ke cewa "Ina kuka je ba ni?" Amrah  tace "Ina zaki sani kin shiga d'akin Adda nuri maula" hararanta mimie tayi tana nuna musharraf da baki wato ba don shi ba da ta gane.............

Momma tace "kun dawo?" Amrah tace "Eh momma baki ga gidansu ba abin tausayi amma they live happily na lura ba wani namiji babba a gidan ga mamansu makauniya siblings dinta kuma sa'annin little ne" momma tace "Ayyah" Miemie tace "Allah sarki next time in za'a kaita nima zani" Amrah tace "Ohk" mikewa musharraf yayi yana cewa "good night momma" momma tace "Allah tashemu Lafiya da zarahn zaku kwana?" Yace "Yeah amma Amrah kiyi mata wanka ki sa mata nightwear se ki kawota".........

Tsalle little ta dinga yi don tana mugun son kwana da shi shikuma ba ko yaushe yake yadda ta kwanan ba, fita yayi yana amsa seda safen miemie...........

Yana kwance yayi zurfi cikin tunani wadda ban san na me ba se ga little ta shigo ta kwanto jikinshi tana bashi labarinsu cutie be hana ta ba sam sema hankalinshi da ya bayar kanta dukda ba amsa ta yakeyi ba, a haka ta gaji tayi bacci............

Washegari

Bayan sun gama breakfast yam and sous se tea da khairi tayi musu da misalin karfe 9:30 ya fiddo akwatinshi aka sa a mota, sanye yake da well ironed three pieces suit navy blue da ya matukar amsarshi, yayi kyau sossai har ya gaji yana shigowa parlorn kamshinshi ya bule ko

Ina.........

D'akin momma yaje tayi mishi adu'a suka fito tare da su Amrah little se shagwa'be fuska takeyi alamun kuka don wannan karon ya d'an jima, sun fita daga parlorn har sunje wurin mota yace "opps Ina zuwa" ya juya ya koma parlorn direct kitchen ya shiga tana tsaye tana chopping carrot kawai taga mutum a kanta, sake gaisheshi tayi duk da ta gaidashi da Safe amsawa yayi, yana nufan fridge ruwa ya d'auka dukda ya san akwai ruwa a fridge din parlor amma haka kawai ya tsinci kanshi a kitchen, bayan ya d'auko ruwan ya 'balle murfin ya kafa a baki dukda sanyinshi be cire ba seda yayi rabi kan ya juya ya fice...........

Yana fita ya samu haidar ya zo gaisawa sukayi kan ya shiga mota shima rakiyar mota uku suka mishi har airport, seda sukaga departing d'insu kan suka dawo............

One month later

Zuwa yanzu khairi ta saba sossai da gidan aikinta da ma mutanen gidan gabd'aya sossai suke kawance da Amrah har ta san labarinsu bayan alkawarin baza ta gayawa kowa ba, khairi na iya kokarinta ganin bata wuce matsayinta ba, sun saba sossai da little In baka sani ba se ka d'auka mamanta ce..............

Tunda musharraf ya bar Gombe almost month kenan be sake zuwa ba sede suyi waya da 'yan gidan yana Chan yana rayuwan da ya saba na kad'aici se shan taba iyakarshi da mutanen office d'insu gaisuwa se kuma In aiki me muhimmaci ya had'aku daga mazan har matan, har gwara mazan ma da mata kam, me makon abun ya ragu amma se karuwa yake..........

Rayuwa tayiwa su khairi daadi don zuwa yanzu ba abinda suka nema suka rasa albashinta na farko da ta d'auka last week ta saya musu duk abinda zasu bukata har kayan sawa ta kara musu kad'an, sauran kud'in da ba wani yawa ta cire kud'in napep dukda momma na yawan bata kud'in napep amma ba kullum ba gwara ta dinga rikewa In an batan ma se ta ajiye na wurinta sauran kud'in sukayi savings...........

Matsalan da ta fara fuskanta na d'aya a gombe wadda ya girgiza ta shine cewa da mijin Maman hamdeeya yayi yana sonta, a wata ranan laraba ta fita don zuwa gidansu musharraf ya tare ta a daidai kofan gidan shi, inda ya furta mata shi de yana sonta kuma soyayya ta aure, bata tsaya kulashi ba ta tare napep ta wuce ranan ta wuni jimami da tsoro tana tsoron kar Maman hamdeeya taji don bata san ya zatayi ba............

Yanzu sati biyu kenan rabonta da shiga gidan kuma ta kasa fad'awa dada, har yau da ya kasance Friday kuma a ranan musharraf ze zo don momma ta fad'a mata tun jiya da ta shirya yau akwai aiki sossai a gidan..........

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*Alhamdulillah Ala kulli haalin, thanks for your prayers🙏*

Page➡️4️⃣6️⃣▶️4️⃣7️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Tunda garin Allah ya waye take jin gabanta na fad'uwa kaman yadda yake mata de in jikinta ze tashi ko kuma mutanenta suna kusa, kaman ta ki zuwa wurin aikin amma In ta tuna momma tace akwai ayyuka dayawa yau sbd dawowan musharraf se jikinta yayi sanyi bata so su sha wahala.............

Dada ta fad'awa bayan sun gama breakfast dada tace "ki yawaita azkar a zuciyarki kuma ki kiyaye duk abinda kika san ze ja miki 'bacin rai, Allah ya tsare de kar suyi miki sanadiyar aikin nan" khairi tace "Ameen" a sanyaye ta gama duk abinda zatayi suka sallami dada suka fito ta ajiye su nabeel makaranta ta wuce GRA............

Yanzu sunyi time table sbd saukaka mata base ta dinga tambaya ba musamman breakfast, yau Irish potato za'aci da kwai se black tea duk me so se ya zuba madara da bournvita, aikinta ta fara cikin natsuwa tunda kitchen din a goge a share ta sameshi, kan lokaci ta gama ayyukanta tare da shiryasu kan dining, ta dawo kitchen ta wanke duk abinda ta 'bata ta kuma share kan gas d'in.................

Bayan ta gama ta koma d'aki taje ta kwanta har wa yau zuciyarta be dena bugawa ba, adu'a kawai takeyi a cikin ranta, ta jima sossai a haka ita ba bacci ba ita ba ido biyu ba, tana jin muryoyin su momma a parlor amma ta kasa tashi ta fita, tanaji momma ta turo Miemie ta dubo ta ko lafiya, har Miemie ta shigo bata iya ta tashi ba seda ta jijjigata tukun ta bud'e ido Miemie tace "khairi, khairi tashi momma na magana" ta juya ta fita, a hankali ta mike ta sa khimar dinta ta fito..................

Har kasa ta duka tace "Ina kwana momma?" Momma tace "Lafiya klau ya gajiyar aiki? Da su dada?" Khairi tace "duk Lafiya klau Alhamdulillah" gaisawa sukayi da nuri tukun Miemie, Amrah da little kam sun tafi school, salima da maryam kam sun jima da komawa gidajen iyayensu, khairi tace "me dame za'ayi momma?" Momma tace "eh toh zakiyi pepper soup na kifi, se tuwon semonvita da miyan ku'bewa d'anye, se zobo da fruit salad" kai khairi ta gyad'a tace "bari na fara wasu abubuwan yanzu kar lokaci ya kure" da toh momma ta amsa tana cewa "nuri da Miemie ma zasu shigo su tayaki"..................

Tashi sukayi suka rankaya kitchen din gabad'aya ko wacce ta fara aiki, cikin lokaci kankani suka gama, nuri na kallon khairi tace "Ke kuwa khairi lafiyanki kuwa yau? Na ganki duk wani iri" khairi ta d'anyi murmushi tace "lafiya klau Adda kawai kaina ke d'an ciwo amma na san zuwa anjima ze yi sauki" miemie tace "subhanallah sorry bari In kar'bo miki magani wurin momma"...................

Ficewa tayi Ba'a jima ba ta dawo da panadol biyu a hannunta nuri ta miko musu ruwa ba yadda ta iya haka ta kar'ba ta sha, karasa had'a zobon dake gabanta tayi tana jin miemie da bata dad'e da fita parlorn ba na cewa "Adda nuri har sun shigo gombe fah, inaga tafiyar asuba sukayi

amma wannan karon sunyi sauri yanzu 12 fah" nuri dake kitchen din bata ce komai ba se had'a fruit salad d'inta da ta ci gaba................

Khairi kuwa jin sun shigo se kawai ta juye zobon a wani plastic robber me d'an girma ta d'auka ta sa a deep freezer wai don ya d'an yi sanyi kan ya karaso, nuri kuma ta zuba fruit salad din a jug ta saka mishi kankara ta had'a akan tray da cups ta fitar zuwa dining, wanke wanke khairi tayi tare da share kitchen din ta goge ya fita kal kaman ba'ayi aiki a ciki ba...................

Tana shiga d'aki taji shigowarsu parlor, shi da Amrah da little sun had'u a gate ne se kawai suka shigo tare, momma dake zaune a parlor ne tayi mishi sannu da zuwa, samun wuri yayi kasan kafanta ya zauna yana cewa "mun sameku lafiya" se da gabanta ya fad'i jin muryanshi, ba abinda ya sauya a ciki yana tashi cikin sanyi da amo.................

Momma tace "Lafiya klau Alhamdulillah ya hanya? Ya kuma wurin aikin naku?" Yace "Alhamdulillah" yana shafa cikinshi yace "momma am starving Allah ko breakfast banyi ba" waro ido momma tayi tace "me kakeyi haka ya hanaka karyawa" murmushi me d'an sauti ya saki yace "kawai momma, nayi kewarku" murmushi itama tayi kan tace "oya muje ka ci abinci se kayi wanka kayi shirin juma'a gabad'aya" mikewa yayi suka nufi dining, Little da ta haura bata ga khairi a saman ba ta gangaro tace "momma Ina Adda khairi I want to eat with paapi, tazo ta min wanka da wuri"..................

Dariya momma tayi tace "Toh sannu mamanta, duba d'akin ta kanta ke ciwo In baza ta iya ba ki zo nuri ta miki ko miemie" d'akin ta nufa tana kwala kiran "cutie cutie" har ta shige mikewa khairi dake kwance tayi tare da zama tace "wannan irin kira haka pretty?" Tura baki gaba tayi tace "Toh ba ke bane cutie kinki kizo ki min oyoyo yadda kika saba ba"..............

Khairi tace "ohh sorry dear baki ji momma tace headache na damuna ba? muje In miki wankan anan tunda akwai kayanki koh? samu ki ci abinci da paapinki kan ya gama" da gudu ta nufi toilet dama daga ita se pant ta gangaro, towel d'inta khairi ta d'auka tare da binta bayin tana murmushi, wanka tayi mata suka fito se surutu take zuba mata amma khairi ta kasa magana se uhm ko uhm uhm, ciwon kanta ya fara yawa ga faduwar gaba dake ta kara damunta................

A Haka ta shirya little cikin short gown dinta blue me kyau tare da gyara mata parking din kanta don kanta a tsefe yake tayi mata parking din gefe tare da bud'e jakanta ta fiddo powder, ita ba gwanar kwalliya bace amma tana yawan sayan powder da lip glose se kajal, tana ma saka su jankanta ne sbd nabeela idonta idon kayan kwalliya se ta 'bata mata su.................

Shafawa little tayi tare da saka mata kajal da man baki tayi kyau kuwa sossai, da gudu ta fita ta kuwa samu paapin na jiranta be fara ci ba, zama tayi tana kallon momma, Amrah, miemie da nuri da suka kusa cinye nasu, ta'be baki tayi tana cewa "ba kunki jirana ba to de paapi na ya jirani" momma tace "ku ta dama daga ke har paapin naki mu de baza mu zauna da yunwa don ke ba da In kin zaunan ma ba cin kirki zakiyi ba"................

Dariya su Amrah sukayi musharraf na murmushi yace "khaih momma, kin de ki jiranta don bakya so tazo ta ci dayawa ta fiki kiba da tsai" momma na murmushi tace "wa wannan d'in? Tab ai wannan da take kaman bebin robannan ko rabin kiba na bazata yi ba bare tsaho" tura baki gaba little tayi tare da raurau da ido da sauri musharraf yace  "oya open ur mouth in baki kiyi maza maza ki ci kifi momma kiba da tsai" Ai ko da sauri ta bud'e bakin hakan yasa su kwashewa da dariya banda musharraf da murmushi kawai ya saki.................

Ita ala dole ita so take tafi momma kiba da tsaho, khairi dake jinsu daga d'aki ta saki murmushi hawaye na gangaro mata tana tuna lokacin da suke happy family, Ashe dama yana wasa da dariya da family dinshi? Da sauri ta mike tana cewa "subhanallah" shap ta mance da zobo bata kai musu ba, d'aukan khimar dinta tayi ta saka tare da fitowa, Amrah na hanganta tace "Tbest yanzu nake ta sauri In gama In zo In d'ura miki naki, tunda naji momma na cewa kina headache na san baza ki wani ci abincin rana ba".................

Murmushi kawai khairi tayi tana jin idanunshi a kanta Ai ko hakan ne kallonta yayi na akallah 30 seconds kan ya d'auke kanshi, da sauri ta shige kitchen tana sauke ajiyar zuciya, robbern ta d'auka ta fito zuciyarta na tsananta bugawa kanta kaman ze tsage sauri takeyi ta ajiye musu ta koma d'aki duk abinda ze sameta ma gwara tana d'aki bata hankara ba tayi missing step na haurawa wurin dining kuma skirt ne a jikinta hakan yasa ta hantsila robbern ya kubce mata.................

Se jikin musharraf gashi farin tshirt ne jikinshi da farin Jeans a take suka rine da sauri ya mike yana furta "subhanallah, ya Salam" ya karasa a hankali yana lumshe ido don cooling temper dinshi, ganin ta sulale ta duka wurin tare da rufe ido yasa haushi ya kamashi a lokaci d'aya ya daka mata tsawa "Ke wace irin mahaukaciya wawiyar yarinya ce da zaki watsa wa mutum abu a jiki kuma ki ki ce mishi komai??? I hate nonsense wallahi, useless human being" duk en dining din mikewa sukayi tun sanda zobon ya zubewa musharraf din a jiki...............

Momma zatayi magana kenan taga Khairi ta mike ta tsaya tare da bud'e idanunta da suka rine ta kafe musharraf da shi, fuskantan nan kaman bata ta'ba dariya ba, little ce ta nufe ta tana cewa "sorry cutie paapi ne ya 'bata miki rai ko?" Wani irin turewa da tayiwa little seda duk suka tsorata ba don musharraf yayi saurin tare ta ba da tayi mummunan fad'uwa a tsorace ta fashe da kuka tana kallon khairi da har yanzu musharraf take kallo....................

Nuri musharraf ya mikawa little cikin kasa da murya yace "ku tafi parlorna kuyi kallo" kar'ban ta tayi jikinta na rawa, binta da ido yayi jikinshi na sanyi har suka fita daga parlorn, runtse ido yayi yana jin tsanan mahaifinshi na kara ninkuwa mai, a kullum In yaga nuri se ya tausaya mata in ya tuna wai banzan halin mahaifinsu ya ja mata aljannu, da basa mata da wasa in sun tashi don ma yanzu sunyi sauki sossai don magungunan ya dinga nema mata kasashe kasashe....................

A hankali ya bud'e idonshi dake lumshe ya d'aura akan na khairi da har yanzu kallonshi takeyi ko kifta ido babu, tun daga kallon farko da ya mata ya san ba ita ba ce sbd yana da tabbacin

baza ta ta'ba iya juran kallon cikin kwayar idonshi na fiye da minti d'aya ba, hakan yasa ya saci kallon nuri ganin hannunta na rawa yasa ya tabbatarwa kanshi zargin da yake hakan ne yasa ya tura nuri part dinshi don kar nata ma su tashi...................

Tunaninshi ya katse ne ganin ta nufo shi cikin zafin nama ya rike hannayenta da take shirin shako shi dasu kokuwa suka fara, ganin tana shirin fin karfinshi ne yasa ya sa duk karfinshi ya ja ta tsakiyar parlorn tare da tad'iye kafanta yayi saurin sa hannunshi a kwankwasonta a tare sukayi kasa, se shi ya sauka da guiwanshi d'aya ita kuma ta sauko kan kafan, d'ayan kafan yasa ya danne ta tare da, danne hannayenta da duk hannunshi biyu don ya lura ba karamin karfi ne da aljanin jikintan ba.................

Kallon momma dake kallonsu cikin tausayawa yayi yace "momma a d'auko hayakin nuriyyah plz ayi sauri" ya kalli Amrah dake hawaye yace "yi sauri ban ruwa kad'an a cup" da sauri ta nufi kitchen momma ma ta nufi sama, adu'o'i ya ci gaba da mata kan saukowan momma, yanayi yana kallonta a rayuwanshi be ta'ba tausayawa wata mace ba bayan kannenshi da mamanshi da ershi se wannan wani irin tausayinta yake ji.................

Yana ta kallon yadda take ta fad'an kwachewa har Amrah ta kawo ruwan, a hannunta ya dinga adu'a yana tofawa yana cikin yi momma ta fito da wani rober a hannunta burner ta nufa ta zuba garin tare da kunnawa ta kaishi karshe, a take hayakin ya fara tashi zuwa lokacin ya gama adu'ar da ze yi, yace "watsa mata" Amrah ta zuba a hannu ta watsa mata wani irin kara tayi da ya sashi lumshe ido sam be son hayaniya amma ya ya iya, ihu ta ci gaba da yi na fitan hankali sake ta yayi tayi ta birgima a wurin har suka tafi, hannunta ta sa ta dafe kanta tana mikewa zaune a hankali ta bud'e ido ganin kallon da suke mata da halin da take ciki yasa ta fashe da kuka sossai, karasawa Amrah tayi ta rungumo ta a jikinta hakan ya sa ta kara karfin kukanta tana boye fuskanta....................

Mikewa yayi ya fice yana jin tausayinta sossai na yawa a zuciyarshi, part dinshi ya shiga ya ga nuri na kwance little kwance a jikinta har bacci ya d'auke ta, karasawa yayi ya d'agata ya kaita d'aki ya kwantar a kan gadonshi ya dawo parlorn yana adu'ar Allah yasa nata basu tashi ba don In hakan ya faru akwai matsala, a natse yace "nuriyyah" a hankali ta bud'e ido yace "me ya faru?" Kanta ta nuna mai, mikewa yayi ya nufi karamin table dake parlorn akwai jug da ruwa a ciki se cup ya d'auka ya tsiyaya................

Tare da komawa kusa da ita ya zauna adu'o'i sossai yayi a ruwan tare da mika mata kar'ba tayi ta sha dayawa ta shafa sauran a jikinta, kallonshi tayi taga irin kallon da yake mata hakan yasa tayi murmushi tare da cewa "thanks hamma" mikewa yayi ya shige d'akinshi, ta sanadinta ya iya adu'o'i dayawa na ruqya, cire kayan jikinshi yayi tare da d'aura towel ya shige toilet...................,....

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️4️⃣8️⃣▶️4️⃣9️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Ba irin rarrashin da Amrah bata mata ba amma ta kasa dena kuka gani take ta rasa aikin nan, aikin da dashi take taimakon kanta da en uwanta, aikin da ta sha wahala kan ta sameshi, rufin asirinsu kenan aikin nan, a hankali momma ta kira sunanta "ummulkhairi" d'agowa tayi tana kallonta ba tare da ta amsa ba tana jira taji ance ki tattara ya naki ya naki ki tafi kin gama aiki damu se ji tayi momma tace "Ashe baki yarda da kaddara ba?" Da sauri khairi tace "wallahi momma na yarda da kaddara me kyau ko marar kyau, ai bazan ta'ba zama cikakkiyar musulma ba se na kasance me yarda da kaddara"..................

Momma tace "good, toh me yasa kike kuka haka? Imani yana da hakika, hakikaninsa kuwa shine kaddara, Allah yana cewa a cikin suratul qamar "mun hallici komai da qaddara" ya kuma cewa a suratul A'ala "shine wadda yayi hallita, kuma shine ya daidaita ta, kuma shine wadda ya qaddara abubuwa, kuma ya shiryar dasu" ya kuma cewa a suratul Furqan "kuma ya hallici ko wani abu, kuma ya qaddara shi, qaddarawa" kiyi hakuri kiyi shiru da kukan nan dan Allah, ko basu ta'ba tashi bane se yau?"...............

Share hawayen fuskanta khairi tayi tace "na gode da tunatarwanki momma hakika na yarda da qaddara, da ban yarda dashi ba da ban kawo nan a rayuwata ba, na yarda qaddara ce ta sa na tankawa hauwa har idi yazo ya tadda mu ya d'auki hukunci, na yarda qaddarar abinda ke jikina yasa na murd'ewa Maman hauwa hannu har hakan ya fusatata ya kuma tunzurata ga ja mana sharri a idon duniya, qaddara shi ya d'auke min Abbana a sadda ban yi zato ba, ban ta'ba tsammanin zan iya rayuwa ba shi ba seda qaddara ya nuna min komai me yiwuwa ne..................

Qaddara shi ya rabani da d'an uwa na wadda muka rayu ciki d'aya mahaifa d'aya na watanni tara, muka fito duniya a tare muka kuma rayu a tare na shekaru 17, muka yi jimamin rashin mahaifinmu tare me makon ya barmu muyi wahalan rayuwa tare a wuri d'aya se ya d'auke mana shi, ya kaishi inda bamu sani ba" kuka ne yaci karfin ta, hannunta momma ta rike tana kallonta cike da tausayawa tabbas tun randa ta fara ganin khairi ta san tana cike da damuwa na wani abin..................

Wadda bata san ko menene ba, haka kawai take jin tsantsar tausayinta, za kuwa ta so jin wacece khairi, maganan khairin ne ya katse mata tunani inda take cewa "Ina kewarsu, Ina kewarsu sossai kuma Ina ganin ni ce sanadiyar komai da ya faru damu a rayuwa, na rasa yadda zanyi, na rasa wadda zan tunkara da damuwata, na rasa wadda zan kwanta a jikinshi inyi kuka iya yina be d'aga hankalinshi ba, Dada baza ta Jura ba, In har ta san ina cikin damuwa

itama hankalinta baze ta'ba kwanciya ba, nayi iya kokarina don ganin na boye abinda ke ci na a rai amma abun na shirin fin karfina"..................

Momma tace "zaki iya ummulkhairi, dukda ban san wacece ke ba, na tabbatar bakiyi sanadiyar mahaifinki ba sbd yanayinki da tarbiyarki be nuna hakan ba, In ba zaki damu ba Ina so ki bani labarin rayuwanki, Ina son zama miki gini wadda zaki dafa ki tsaya har ki kai ga cimma nasara a rayuwanki" khairi tace "toh momma zan fad'a miki wacece ni, amma yanzu azahar yayi bari In munyi sallah" Da toh momma ta amsa kan ta mike ta haura, miemie ta zo ganganta ta dafa kafad'arta tare da bubbugawa kan ta wuce itama, Amrah ce ta taimaka mata ta mike sukayi d'akin khairin...................

Anan sukayi sallah tare, bayan sun idar sukayi adu'o'i suka shaafa Amrah tace "bari In debo miki abinci kici kan momma ta sauko" abincin taje ta d'ibo mata, bata wani ci mai yawa ba ta ture, da Amrah suka fito yayi daidai da saukowar momma, miemie, da nuriyyah, zama sukayi, momma a two seater, Miemie a kasa kan rug, don bata cika son zaman saman ba haka Allah yayi ta, se nuri da ta zauna a one seater.................

Amrah bata zauna ba tace "bari In d'aura mana abincin dare" sam bata son sake jin labarin khairi don kuka sossai yake saka ta, don a sadda taji na farko ta jima batayi bacci ba tayi kuka har idonta ya rine seda momma ta tambayeta me ya sameta amma ta boye da abu ne yafad'a ciki, "jollof rice kiyi da nama, se pepper soup din cow-tail" Cewar momma, kitchen din ta shige.....................

Gyara zama khairi tayi akan rug din parlorn ta fara da "kamar yadda kuka sani sunana ummulkhairi sunan mahaifina Umar sanda sannan mahaifiyata sunanta safiyya Ali gamji........." sallamar musharraf ce ta katse ta, a hankali ta d'aga kai ta kalleshi shima cikin sa'a kanta idonshi ya fara fad'awa, sanye yake da kananan kaya da alamu be samu yaje sallar juma' a ba sbd ita, tun kafin sallamanshi kamshinshi ya sanar da ita kusantowarshi haka sauyawar bugun zuciyarta, sanye yake da black jeans da red polo shirt me guntun hannu, ba tare da ya tanka kowa ba ya samu doguwar kujera ya kwanta tare da lumshe ido................

Ba yadda khairi ta iya haka ta ci gaba da bada labarinta daki daki, tun daga kan labarin iyayenta har nasu, har zuwansu gombe da abinda ya faru dasu 'batar d'an uwanta, neman aikinta zuwa ga fyaden da ya so afkawa cikin rayuwanta su musharraf suka ceceta kawo yau.................

Kuka nuri da miemie ke yi bilhakki yayinda silent tears ke bin fuskan momma, musharraf kam be bud'e idonshi ba ma balle In san wani hali yake ciki, khairi ma kukan take momma ce tayi karfin halin share hawayenta tace "kuyi shiru dan Allah kuna kara mata ciwon abinda ke ranta" se shiru su nuri sukayi amma hawaye yaki dena fita sossai tausayinsu khairi ya kamasu, momma ce ta dinga lalla'ba khairi da kalamai masu daadi har ta samu tayi shiru................

Duk abunda sukeyin  nan idon momma na kan musharraf tana son sanin halin da ya shiga jin labarin khairi amma yaki bata daman sanin hakan, don ko motsi be yi ba balle ya nuna alamun

yaji komai, tun kan ta gama jin labarin khairi take kitsima abu a ranta kuma tana fatan tabbatuwarshi sede bata San ko khairi zata amince ba....................

A hankali tace "ummulkhairi zaki iya auren d'ana musharraf???" Ba khairi da musharraf ba har miemie da nuri seda maganar ta dake su, da sauri ya mike ya zauna yana warowa momma idanunshin nan, harara ta sakar mishi tana kau da kai tace "ba zan tilasta ki ba, sbd banda wannan hurumin amma Ina mai tabbatar miki ba yabon kai ba d'ana ze iya zama miji na gari a gareki sbd kyawawar halayyanshi, duk da rayuwa ya chanza min shi, amma har yanzu shi dinne de daga ciki, I want my old son back, Ina kwad'ayin miki samun miji kaman shi, a lokaci d'aya Ina mishi kwad'ayin samun mace irinki me kyau, baiwa, ilimin addini da tarbiya..................

Zaki iya zuwa kiyi tunani kuma kiyi shawara, be wise and chose what will be best for yhu and ur family daughter, all the best dear" musharraf ze yi magana kenan suka ji hayaniya daga waje gashi an fara yayyafi duk da musharraf be son shiga ruwa haka ya mike ya fito su momma suka biyo bayanshi, daga kan varendern parlorn ya tsaya yana kallon mai gadi na kokuwa da wani da be sani ba ko don be lura da kyau bane oho................

D'aga hannu yayi ya yafito me gadin hakan yasa ya sake mutumin suka nufo wurinsu tare, yana matsowa kamanninshi na fitowa, wani irin tsawa da ya tsorata dukkansu musharraf yayi inda yace "me ya kawo ka!!!! Me ya kawoka inda muke??? Ka manta mu marasa anfani ne? Ka manta mu kashin tsiya ne? Ka manta ni marar tarbiya ne? Ka manta uwarmu ballagaza ce?"...................

Kuka mutumin da khairi bata san wanene ba ya fashe dashi yana durkusawa kasa ga ruwan se kara karfi yake, cikin sanyin murya yace "na tuba Abubakar ku yafemin, fatima ki taimakamin don Allah na kwanta da yardar 'ya'yana da kuma adu'arsu a kaina, wallahi na chanza ba senator Mahmoud Adam da kuka sani ba ne a da, I'm so sorry for all my mistakes, plz find place in your heart to forgive me ko ba don ni mijinki ba ko ba don ni cousin dinki ba, ko don ni musulmi d'an uwanku"....................

Momma da ta fara hawaye musharraf ya kalla tare da lumshe ido a hankali ya bud'e har sun sauya kala a zafafe yace "baza mu yafe ba, ka fice ka bar min gida wallahi na tsaneka, tsana mafi muni a duniya da Allah ya bamu daman kisa ko da na mutum d'aya ne da kai zan fara kashewa a rayuwata, tirrrr tirrr Ina ma ana chanza uba? Nayi Allah wade da ranar zuwanka du..........." tasssssss tasssss momma ta d'auke musharraf da mari hagu da dama a zafafe tace "baka da hankali Abubakar mahaifin da ya tsuguna ya haifeka kake gayawa irin wannan magana? Irin tarbiyan da nayi maka kenan Musharraf??" Baya baya ya fara har ya sauka daga kan varender din ruwa ya soma dukan shi sossai don ruwan ya fara karfi....................

Da tsantsar mamaki yake kallon momma ya manta when last ta d'aga hannu a kanshi a rayuwanshi gabad'aya amma yau yau sbd wannan mutumin mommanshi me ji dashi ta iya d'aga hannu ta mareshi har sau biyu, hawaye ne ya fara zuba a idonshi wadda In ba ka kula sossai ba baza ka gani ba sbd ruwan dake zuba a kanshi...................

Da sauri nuriyyah ta zo gaban momma tace "momma me yasa zaki d'aga mishi hannu bayan ya fad'i gaskiyar abinda ke ranshi? Ba hamma musharraf kad'ai ba ko ni bazan iya yafewa wannan mutumin ba ko kin manta halin da ya jefaki a ciki? In kin manta naki na san baza ki ta'ba manta nawa ba, In kuma shima kin manta na tabbatar ko za'ayi duniya sau nawa ne baza ki ta'ba manta na hamma musharraf ba, yanzu akan wanchan azzalumin kika mari hamma?"
..................

Juyawa tayi kan baban nasu tace "A rayuwana ban ta'ba ganin mutum me son kanshi irinka ba, duk abinda ka mana be ishe ka ba se ka dawo ka raba kan mu? Hakan da kakeyin kana tunanin ze sa mu soka? To Albishirinka hakan sede ya kara mana tsananka, tsana kuma wadda tafi ta yanzu" momma tace "nuriyyah plz" nuriyyah da yanzu take kuka on top of her voice tace cikin tsawa "then he should leave and never come again"....................

Kallonshi tayi tace "leaveeeee!!!!!" Cikin muryan kuka kuma a tsawace, mikewa yayi yana kuka ya fice, musharraf dake tsaye kaman gunki ne ya fara layi basu ankara ba se fad'uwarashi suka ji, da gudu sukayi kanshi momma dake kuka sossai ne ta fara jijjigashi tana kiran "musharraf musharraf Dan Allah ka tashi, no plz kar ka min haka wallahi ba da niyya na mareka ba, musharraf! Musharraf!! Musharraf!!!"...................

Mai gadi ne yaje da gudu ya kira drivern momma da na musharraf din suka zo suka sashi a mota, Amrah da zuwan baban nasu ta fito itace taje da gudu ta d'auko musu hijabai, momma ta kalli khairi tace "plz khairi ki kula da zarah dake site din musharraf" bata jira amsanta ba ta bisu, da gudu suka fice zuwa asibiti, FMC suka je take family doctor d'insu ya kira wasu doctors din suka rufu kan musharraf da numfashi ke shirin barin kirjinshi................

*ga na gobe😊 don gobe baza ku jini ba*

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️5️⃣2️⃣▶️5️⃣3️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Musharraf ba shi ya farka ba se bayan magrib, a hankali ya bud'e ido yana kallon momma dake zaune kan sallaya tana karatun Qur'an a wayanta, mayar da idon yayi ya lumshe yana tunanin marin da momma ta mishi sbd mutumin Chan, duk tunaninshi yayi ya rasa me yasa momma ta mareshi don ya gayamishi abinda y dace dashi da rayuwanshi....................

A hankali ya mike ya zauna tare da gyara pillown da yake kai zuwa bayanshi ya jingina yana taune lips sbd kanshi da ke Sara mishi da jirin da yake ji, motsin shi ne ya sanar da momma farkawanshi tsayar da karatun tayi tana kallon gadon, ganin da gaske ya farka ne yasa ta mikewa tana cewa "sannu musharraf"....................

Kai ya gyad'a ba tare da ya kalleta ba, a hankali tace "wai kai se yaushe zaka girma ne ka san abinda yake daidai da wadda ba daidai ba?" Tura lips dinshi yayi ba tare da yace komai ba, seda ta kuma cewa "ba da kai nake ba musharraf?" Yace "Toh ni momma me kuma nayi bayan ba nine da lefi ba kika mare ni gaban kannena da masu aiki" murmushi momma tayi tana girgiza kai tace "Toh yanzu fushi kake da ni kenan?" Kara tura bakin yayi ita kuma ta saki murmushi tana cewa "Toh kayi hakuri, na san ba lefinka da be maka abinda ya maka ba da baka fad'amishi ko wacce kalma ta fito daga bakin ka ba"........................

Ajiyar zuciya ta sauke kan ta ci gaba "Ina kwa'bar ka ne don bana son Allah ya kama ka da laifi, sbd uba de uba ne ko min lalacewarshi adu'a ne kawai tsakaninku ba wai zagi ba, yanzu In ni ce nayi maka haka haka zaka dinga zagi na?" Had'e rai yace "subhanallah ki dena kwatanta kanki dashi plz momma, baza ki ta'ba ko da kwatanta abinda ya aikata ba" girgiza kai tayi tace "In yana cikin kaddara na dole hakan ya kasance ko da kuwa bana so, shi yasa nake so ka yarda kaddaranshi kenan, ku yafemishi tabbas ya tuba, don naga hakan" Shiru yayi be ce komai ba....................

Kanshi ta ta'ba jin jikinshi har yanzu da zafi yasa ta mikewa tace "bari na kira doctor zazza'bin nan be sauka ba" hannunta ya rike yace "a'a momma zanyi sallah tukuna ko la'asar banyi ba" duk maganganun da yake yin nan muryanshi ba wani fita yakeyi ba sbd mura da ciwon kai, bowl ta samo mishi a toilet da ruwan gora ta rike mishi yayi alwala don ba ze iya mikewa ba sbd jiri haka yake mishi In har jininshi ya hau...............

A zaunen yayi sallah yana idarwa ta sa mishi pepper soup da Amrah tayi, da kanta ta dinga bashi har ya ce ya koshi, magunguna ta 'balla mishi wadda bata jima da sayowa ba, yana 'bata fuska yana komai haka ta sashi sha dole, yana gama sha doctor na shigowa da fara'a ya mishi sannu da jiki amsawa musharraf yayi yana d'an murmushi....................

Dube dubenshi yayi kan yace "masha Allah, Dan Allah ka kwantar da hankalinka samun jinin da ya hauran nan ya sauka" murmushi kawai musharraf yayi ba tare da ya ce komai ba, fita doctor Aslam yayi don ba yau ya san halin musharraf ba, momma tace "ga jallabiya nan ko zaka chanza" kar'ba yayi ta fice daga d'akin bayan wasu mintuna ta dawo da waya sakale a kunnenta tana kallonshi ya chanza zuwa jallabiyan brown color sossai ya mishi kyau kaman ba shine

mara lafiya ba.......................

"Eh yaya, amma da sauki sossai a'a hawan jinin ne de, toh mun gode se da safe" tana kashe wayan ta kara danna wani layin bayan an d'auka suka gaisa tace "Rabi'ah ya kk ya su afreen?" Be ji me aka ce daga d'ayan bangaren ba se momma da tace "Toh gashinan de musharraf ne Wlh ba lafiya muna asibiti" Shiru tayi kan tace "Eh amma da sauki sossai, Ohk toh se kinzo"...............

Bayan ta kashe ta kuma yin wani kiran "hello taheer ya kk?, ya su takwara na? Eh dazu da mukayi waya da yaya Ahmad ya fad'amin.......... Ohk toh dama musharraf ne ba lafiya yana nan FMC......... wlh hawan jinin de........ Ohk toh se ka zo se da safe"..............

Zatayi wani kiran taji an rike hannunta d'ago kai tayi tana kallon musharraf tace "lafiya de ko?" 'Bata fuska yayi yace "momma dan Allah de wayan ya isa, na san yanzu gobe d'akin nan ze koma kaman kasuwa wlh kuma kin san bana son hayaniya" waro ido tayi tana cewa "don baka son hayaniya se bazan fad'awa dangi ba? Yanzu dakata bari inyi waya da hajiya ruqayyah se muyi wata magana tunda na ga kaji sauki"...................

Yana saurarenta har ta gama waya da hajiya ruqayyan ita ma rashin lafiyanshi ta fad'awa kan ta kalleshi tace "An kawo tambayan Saliman Yaya Ahmad" karamin murmushi yayi a zuciyarshi yace ta gaji da jiran gawon shanu kenan, a fili kuma se yace "Allah sanya alheri" momma tace "Ameen amma yaushe rabonka da gidan yayyun mahaifinka da kannena?" Yana 'bata fuska yace "momma In na zo ba lokaci kema kin sani, last zuwana ma seda na shiga time din aikina da kika sani zuwa dukku wurin grannys" momma tace "wannan ba hujja bace dukkansu cikin gombe suke ba wani gari ba balle kace akwai tafiya me yawa tsakani wallahi ka gyara halinka musharraf"..................

Zamewa yayi ya kwanta yana dafe kai, tace "Toh ba wannan ba ma, musharraf Da gaske nake har zuciyata Ina maka kwad'ayin auren khairi, In har kana son farin ciki na da kwanciyar hankalina toh ka aureta" Shiru yayi na mintuna tukun ya sauke ajiyar zuciya kan yace "In haka kike so momma so let it be, Allah ya sanya alheri" murmushi tayi tana jin son d'an nata har cikin ranta duk abinda tace take so ko da baya so haka ze yi shi.................

Maganan da take son mishi na gaba shine na shan taba amma tafi son se an sallameshi sun koma gida tukuna, abinci ta di'ba taci suna hira jefi jefi har ta gama, bargo ta d'auko ta lullu'ba mishi, ta kuma shimfid'a wani akan sallaya ta jefa pillow ta kwanta tana rufuwa da hijab dinta, cikin tausayawa yake kallonta Eyyah uwa de ko ya take bata gajiya da d'awainiyar yaronta tun daga yarantan shi har girmanshi yanzu dubi a kasa zata kwanta da girmantan nan bayan shi yana kwance akan gado..........................

Washegari

Kamar yadda khairi ta saba da wuri ta tafi wurin aikinta, duk basu tashi ba, ta fere dankali ta

soya da kwai, ta dafa black tea da yaji kayan kamshi, ta san dole akai na asibiti hakan yasa bata jira tashin su nuri ba ta shirya a basket ta fito ta ba driver ya tafi dashi, sauran ta shirya a dining, ta gyara kitchen din, bata jira komai ba ta d'aura abincin rana, dambun shinkafa tayi da sous na hanta, se tayi pepper soup na kayan ciki da fruit salad.......................

Lokacin da ta gama 11 yayi, tana fitowa parlor su nuriyya na saukowa duk a shirye suka sauko har little sun shirya ta cikin duguwar rigan atampha orange da black se white hijab da white shoe tayi kyau sossai, da murmushi ta musu barka da safiya suna nufan dining suna kuma gaisawa, Amrah na tambayar khairi ya su nabeel da dada, tana amsawa da suna lafiya.................

Little da ke rike da hannunta ne tace "cutie I want to see them plz come with them 2morrow" nuri tace "gaskiya nima Ina son ganin twins din nan da su miemie suka dameni da kyaunsu" khairi tace "Adda Ai suna zuwa islamiyya ne shiyasa ban ta'ba zuwa dasu ba" little tace "plz plz plz cutie su hakura da na gobe kawai su zo mu yini plzzzzzzz" Amrah tace "yes plz Tbest" miemie tace "please" nuriyyah ma tace "plz Adda khairi" a tare suka sa dariya har khairin tana girgiza kai tace "Toh shikenan zan zo dasu In Allah ya kaimu" "yeeeaahaahhahhhhhh💃💃" little ta dinga rawa da tsalle..................

Khairi ta ja kujera ta d'auke ta ta d'aura ta akai tana cewa "oya ci abinci tukun ki tsayawa mutane da rawan" wani dariyan sukayi tana kallonsu tace "Toh yanzu Anties breakfast zaku ci ko lunch?" Miemie tace "khaih kar de har kin gama lunch?" Khairi ta gyad'a kai tana murmushi nuri tace "weldon khairi na asibiti fah?" Khairi tace "tun 8 na bada driver ya kai musu" nuri tace "masha Allah sannu da kokari" murmushi kawai khairi tayi.....................

Amrah tace "nide chips zanci se in mun dawo hospital se inci lunch ko kuma inyi achan don na san su Anty rabi'ah zasu kai abinci" miemie tace "nima" little ma tace "me too, Anty Amrah who's at hospital? Naji kince su sauban zasu je" nuri tace "just eat bana son surutu and sauban ba uncle dinki bane kike kiranshi gatsau haka?" Pouting lips tayi tana cewa "but Anty nuri we are mates, same class and everything be yi babba ba like yhu and uncle marwan" dariya su Amrah sukayi miemie tace "se yayi girma kaman mu kenan zaki kirashi uncle" little tace "yes, sauban, Anwar and sudais are not my uncles" tana 'bata fuska tace "no way"................

Amrah na dariya tace "yes way, sbd kannen paapi dinki ne kap d'insu yhu better start calling them uncles na gayamiki" kara tura bakin tayi wai tayi fushi a haka har suka gama cin abinci suna sauka daga dining din da niyyan tafiya momma na shigowa, da gudu little taje ta rungumeta tana cewa "oyoyo granny" momma tace "oyoyo namesy how was ur night?"...................

Tana kwa'ba fuska tace "hectic, I didn't see you and my paapi" momma tace "Eyyah sorry, yanzu kuje ku ganshi I will be on my way too" little na tsalle ta fice, gaida momma duk sukayi suna tambayar ya jikin nashi tace "yayi sauki Alhamdulillah, jinin ya sauka kila a sallameshi da dare ko gobe muran ne de se a hankali ze sakeshi" ajiyar zuciya suka sauke, nuri tace "ba

abinda za'a iya yi akan kidneyn yanzu?" Momma tace "babu munyi magana da doctor Aslam da safen nan yace ba wai ya kamu da wani ciwo bane yana barazana ne sbd baki da yayi" Amra tace "Toh Allah bashi lafiya"...............,,

Suka ce "Ameen" miemie tace "Toh da wa kika barshi?" Momma tace "wai Ai family sun cika d'akin pim, kuje nima wanka kawai zanyi in tafi, nuri kije d'akinshi ki d'auka mishi kananan kaya da sponge da soap ku tafin mishi dashi, basket nan fah?" Nuri tace "Ohk, lunch dinshi ne ciki" momma tace "sannu khairi, har kin gama kenan?" Khairi ta gyad'a kai kanta kasa, momma tace "to ki bi su kuje, nima yanzu zan biyo ku" tace "toh momma" dama da hijab dinta jikinta, so fita kawai sukayi momma ta haura sama...................

Little ta shiga motan nuriyyah, yayinda Amrah da khairi suka shiga motan da Musharraf ya ba miemie na zuwa makaranta, seda suka jira nuri taje part din musharraf ta dawo kan suka jera suka fita a tare, bayan sun isa suka nufi d'akin little da nuri ne gaba se miemie tukun Amrah da khairi a baya, da sallama nuri ta tura d'akin da gudu little tayi kan gadon ganin paapinta, d'aga ta yayi zuwa kan gadon tana cewa "me ke damunka paapi kake kwance a hospital?"....................

Yace "ba gaisuwa?" Tace "good morning paapi?" Yace "morning" yana d'ago kai se idonshi ya fad'a cikin nata da ta shigo a karshe da sauri ta dukar da kai tana jin jikinta ya d'au rawa, mutane ne a d'akin akallah sun kusa 30 yara da kanana kamshi ko ta Ina na turaruka daban daban, gaban gadon ta nufa da basket din abincin rana a hannunta kafanta har rawa yake jin yadda ido ke yawo a kanta..................

Kusan kowa kallonta yake a d'akin ganin bakuwar fuska har kasa ta duka,
Ta gaida wasu manya da ta gani su uku zazzaune akan plastic chair, da fara'a suka amsa mata, bayan ta ajiye basket din ta d'an saci kallonshi da sauri ta kawar da kai ganin shima kallonta yake, cikin kasa da murya tace "Ina kwana? Ya jiki?" A hankali shima cikin dashewar murya yace "Alhamdulillah".....................

Kan darduma ta karasa da ta ga mata hud'u zaune suna hira, a kasa ta duka ta gaishesu suma suka amsa mata ba laifi, baza ido tayi a d'akin tana duba inda zata tsaya don tuni su Amrah ko wacce ta samu abokiyar hira bayan sun gaggaisa da uncles d'insu da Anties d'insu, wasu matasa biyu kyawawa idonta ya fad'a kai suma ita suke kallo gaishesu tayi, d'ayan ya amsa da d'an murmushi d'ayan kuma ba walwala ya amsa yana mai da kai kan wayanshi.......................

Kusa da Amrah taje ta tsaya tana lura da yadda d'ayan saurayin ke kare mata kallo up and down, ganin kallon yayi yawa kuma en matan gefen Amrah na ta yatsina fuska yasa khairi ta nufi kofa, yana magana da little amma yana lura da irin kallon da sufyan ke bin khairi dashi, ganin ta fice daga d'akin yasa ya sauke ajiyar zuciya, yana mai me da hankali kan little, Amrah kuma ganin khairi ta fita se taji ba daad'i hakan yasa ta bi bayanta................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*wannan page d'in naki ne Sadiya (Maman khalil) ina jin daad'in comments dinki sossai, irin sossai d'innan plz keep it up dear, Allah ya bar kauna*

Page➡️5️⃣4️⃣▶️5️⃣5️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Dube dube Amrah ta fara bayan fitanta Chan ta hange ta zaune kan wani dakali daga bayan d'akin ta zabga tagumi, karasawa tayi ta zare tagumin hakan yasa khairi d'agowa tana kallonta..........

Murmushi sukayiwa juna kan khairi ta d'an matsa Amrah ta zauna, bayan ta zauna tace "family sun cika d'akin" khairi tace "Ai kam duk ban san su ba gwara su Anty salima" Amrah tace "eh su da iyayensu ne, bari nayi miki bayani dalla dalla kan ki shigo daga ciki" hararanta khairi tayi tace "Toh wa ya gaya miki zan amince balle har in shigo daga cikin?" Amrah na dariya tace "har se an fad'a!! Lallai ni kam har na hango wani boyayyen sirri" waro ido khairi tayi tace "wani sirri?" Amrah ta fashe da dariya tana cewa "na san baza ki ki bane kawai amma ba wani sirri" a tsarge khairi ke kallon Amrah kar de har ta har'bo jirginta............

Ganin tana shirin tona asirin kanta yasa tayi saurin cewa "uhm Ina jinki suwaye da waye a d'akin?" Amrah tace "Duk waennan family da kika gani Alhaji Mahmoud dukku shine tushensu da shi da matarshi hajja marwa wadda yanzu duk sun rigamu gidan gaskiya, Allah ya bashi 'ya'ya guda biyu rak a duniya kuma duk maza da kakanmu ta wurin uwa da kakanmu ta wurin uba, Alhaji Adam wadda shine mahaifin Abbanmu se Alhaji Abubakar wadda shi ya haifi su momma......................

Alhaji Abubakar da Alhaji Adam sun taso kaman en biyu sabida ba wani tazara bane tsakaninsu sannan komansu d'aya, da yake mahaifinsu sana'ar saida dabbobi yake hakan yasa suma suka tsunduma sana'ar mahaifin nasu inda sukayi shura a ciki har ya kai ga sunyi suna a dukku da ma gombe gabad'aya, a yawace yawancen da sukeyi na safarar dabbobi ne suka had'u da Aslamiyya da kanwarta shuwa a garin chad suma ya da kanwa ne iyayensu sun mutu sakamakon harin da aka kaiwa kauyensu..................

A wurin saida sauran dabbobinsu don tseratar da rayuwansu suka gamu inda Adam ya nemi su zo su koma tare don sossai ya tausaya musu jin labarinsu, tare suka dawo Nigeria inda hajja marwa ta tarbe su hannu biyu take basu kulawa sossai jin labarinsu haka Alhj Mahmoud ma

duk wani kulawan da uba ze bawa d'anshi yana basu daidai gwargwado a lokacin Aslamiyya na da shekaru sha bakwai yayinda shuwa ke da shekaru sha biyu a duniya......................

Inda Adam ke da 26, Abubakar kuma 24 wasa wasa soyayya me tsanani ya shiga tsakanin Adam da Aslamiyya sossai Alhj mahmoud yaji daadin haka ba'a 'bata dogon lokaci ba akayi musu aure, anan cikin dukku suka gina gidan irin na zamani babban gida ne me part uku, Adam a d'aya Abubakar a d'aya In yayi aure se na tsakiyar na iyayensu, da kyar suka shawo kan Alhj mahmoud ya yarda suka koma gidan gabad'aya...................

Alhj mahmoud yaga ranar haihuwa sossai don a lokacin ba abinda yakeyi na aiki haka hajja marwa en aiki baja Baja, a hk suka ci gaba da rayuwa cikin tsantsar kwanciyan hankali don basu da wani damuwa, har Allah ya azurta Adam da samun d'a na farko, Alhaji Nasir shine wadda kika gani daga daman ya musharraf sanye da fararen kayan nan In kin lura duk ya fi su tsufa, bayan shekara biyu da haihuwarshi suka sake samun wani d'a namijin shine Alhj Ahmad shima yana nan ciki da sky blue shadda...............

Bayan haihuwan Ahmad ne hankalinsu Alhj mahmoud ya fara tashi akan rashin auren Abubakar yayi mishi magana ba sau d'aya ba ba sau biyu ba, amma amsan d'aya ne a kara mishi lokaci, ba irin lokacin da bai d'ibar mai ba amma ba mata, da ya gaji kawai se ya had'a aurenshi da marwa a lokacin ta gama secondary anan cikin dukku....................

Zama suke kaman ba auren had'i ba don iya gwargwado suna kula da junansu, Allah be basu rabo ba seda suka shekara biyar da aure a lokacin, yayyunsu sun sake samun karuwa inda suka haifi mahaifinmu Senator mahmoud Adam, sossai farin ciki ya cika wannan familyn don sun damu sossai da rashin haihuwan nasu akan lokaci....................

Sossai cikin yaga gata ba na wasa ba, har ya kai lokacin haihuwa inda suka samu 'ya mace taci suna 'fatima' momman mu, bayan haihuwanta da shekara biyu suka haifi uncle taheer shima yana cikin room din sanye da black gezner, bayan shekara biyu suka kuma haifan Anty Rabiah, ita ma tana d'akin, tun daga kan babanmu su Alhj Adam basu kara samun wani haihuwan ba...................

Nasir, Ahmad, da mahmoud a ABU zaria sukayi karatu inda Nasir ya karanta business yayinda Ahmad ya karanci Education se mahmoud da ya karanta political science, sossai suka dawo da nasara mai yawa, a wurin bautan kasa suka had'u da matarshi Aisha a jihar bauchi inda suka kulla soyayyarsu mai tsabta, haka Ahmad ma ya samu matarshi zulaiha a nan cikin dukku dayake shi anan yayi service suna gamawa service aka sha buki na ji da fad'a inda duk suka samu gida a cikin Gombe................

Haka Allah ya basu Aiki cikin sauki basu wani sha wahala ba, sbd kyaun results d'insu, a nan Gombe state university uncle Ahmad ya samu karantarwa yayinda Uncle Nasir ya samu aiki a wani textile company, Bayan aurensu ne suka tashi da mummunar rashi na Alhaj Mahmoud Dukku, sossai suka jimanta rasuwar don tabbas sunyi rashi babba, bayan rasuwanshi da

wattani biyu hajja marwa matarshi ta bishi tashin hankalin da suka shiga ba'a magana amma se suka fawallawa Allah.....................

Abbanmu kuma ya tsunduma siyasa kuma be da niyyar aure sossai ya kashe kud'in mamaji (Alhj Adam) akan siyasan har ya samu nasarar samun kujeran chairman a haka ya dinga taka matsayi har ya zama ministern man petur na kasa a lokacin ran mamaji ya kai makura wurin 'baci da rashin aurenshi hakan yasa sukayi shawara da bappa (Abubakar) akan su aura mishi fatima wato momma................

A lokacin ta kusa kammala karatunta na NCE anan gombe tana zama gidan Uncle Nasir sam bata ce komai ba sbd ta kasance mai biyayya da ladabi ga hakuri da Allah ya zuba mata, a fili mahmoud ya dinga nuna kiyayyar shi ga auren har barazana ya dinga yiwa momma daga baya da yaga an fi karfinshi sai kawai yayi shiru amma da mummunar kuduri a ranshi game da momma duk da ba kyau ta rasa ba ba komai ba don duk cikinmu tafi kowa d'ibo kamannin shuwa arab dukda suma sauran suna da kyau kuma farare amma se Abbanmu ya fita chocolate color, Kinga Adda nuriyyah colornshi ta d'auko................"

Bazan iya baki labarin zaman auren da momma tayi ba wannan kam se ita ko yaya musharraf haka kuma bazan iya gayamiki takamamman laifin Abba ba..... sbd....." kuka ne ya sarke ta ta kasa karasa maganan, side hug khairi tayi mata tana bubbuga dantsen hannunta, seda tayi kuka akallah na two mins kan tayi shiru tana share hawayen fuskanta tare da karamin murmushi tace ...................

"Yaran Uncle Nasir da Anty Aisha hud'u hamma marwan wadda shine ze auri Adda nuri, se Maryam wacce kin Santa, se salim da muke sa'anni se autansu sudais sa'an Little, duk tazara mai yawa ne tsakaninsu don Anty Aisha In ta haihu se tayi planning na akallah shekaru hud'u kan ta cire. Se Uncle Ahmad babban d'anshi ya sufyan, salima itama kin santa se Rufaida, zainab waenda kusan kanmu d'aya autansu shine Ibrahim wadda yanzu yake 12years old................

Se Kanin momma Uncle taheer da matarshi hajiya Asiya 'ya'yansu hud'u Zainab wacce kin san ta se Farida da fatima da suke en biyu kuma sa'anninmu se auta Anwar sa'an little. Se er autansu momma Anty Rabi'ah mijinta uncle Isma'il 'ya'yansu biyu Afreen da itama sa'ar mu ce se sauban sa'an little" Ajiyar zuciya ta sauke tare da karawa da "Toh kinji familyn Marigayi Alhj Mahmoud dukku"..............

Murmushi khairi tayi tace "masha Allah what a huge family!! Allah ya kara had'e kanku" Amrah zata amsa kenan taji miemie tace "eyeeeh ku kuma nan kuka zo kuka 'boye kuna ta gulma momma na Chan ta damu ya Musharraf na ta cigiyarku" waro ido sukayi a tare suka ce "ya musharraf???" Dariya miemie ta fashe dashi harda kama ciki tace "irin wannan tsurewar? Ko de baku da gaskiya ne" harara Amrah ta banka mata tana mikewa..................

Khairi ma mikewa tayi zuciyarta na luguden bugawa a tare suka nufi d'akin, Ashe bayan fitansu

daga d'akin ba jimawa sufyan ya fita hakan ya sa zuciyar musharraf ta kasa sukuni da ya rasa dalili, har yaje yayi wanka ya sauyo kaya daga bayi ya fito yaga basu dawo ba, ranshi yaji yayi wani mugun 'baci ya dinga buga tsaki wadda se da kowa ya tambayeshi ko lafiya yace 'kanshi ke sarawa ga muran da yaki barinshi na toshe mishi kirji' duk sannu sukayi mai.................

Da kai kawai ya amsa har momma ta dawo be bar kananan tsaki ba, idonshi kuwa na kan kofa kur kaman me jiran wani abu mai matukar muhimmanci, ganin basu da niyar shigowa yasa yana kallon momma yace "Ina Amrah ne? I want to ask her something" Anty zulai tace "Ai sun d'an jima da fita da yarinyar nan da su farida suka ce mai aikinku ce ya ma sunanta?" Momma tace "au wai ummulkhairi?" Hannu Anty zulai ta juya alamun bata sani ba................

Wayan Amrah momma ta kira se sukaga side bag d'inta ma a d'akin ta bari, sallaman da su Uncle nasir ke yi musu ne yasa hankalin momma ya bar kan su khairi da d'add'aya suka dinga ficewa se da d'akin ya saura su yasu tukun momma tace "ni kam Ina yaran nan suka shiga ne?" Musharraf da tunda su uncle nasir suka fara tafiya ya sulale ya kwanta tare da lumshe ido yana ta yaki da zuciyarshi da ya rasa gane abinda yake ji se kokarin controlling kanshi yakeyi amma abun na neman fin karfinshi, jin momma tayi maganan dubosu yasa ya sauke boyayyiyar ajiyar zuciya.................

Be bud'e idon ba seda yaji sallaman miemie kofan ya kurawa ido, sam momma bata lura ba sbd ita kad'ai ce a d'akin da little dake bacci, Nuri kuma suna waje da marwan, Amrah ce ta shigo daga bayan miemie se Khairi daga karshe, had'a ido sukayi a tare gabansu ya fad'i da sauri ta kau da kai zuwa wurin momma dake cewa "Ina kuka shige ne haka?" Amrah ce tace "muna daga baya muna hira ne momma"................

Momma tace "Ohk" khairi tace "sannu da dawowa" momma na murmushi tace "yauwa khairi" Amrah na kallon musharraf tace "hamma musharraf gani" Shiru ya mata yana kallon momma yace "Am starving"  momma na shirin mikewa khairi ta mike ba wai don kanzagi ko wani abu ba kawai gani tayi be kamata sunanan momma ta dinga wani aikin na daban ba musamman ma ita da ta kasance er aiki.....................

Kusan basket shidda ne na abinci a d'akin hakan yasa ta bud'e duk coolers dake ciki, bayan ta gama ta d'ago ta kalleshi shima ita yake kallo kasa tayi da manyan idanunta tana mamakin yau wani irin kallo yake mata ne oho, cikin tsiririyar muryarta tace "wanne zan zuba maka?" Shiru yayi seda ta d'ago kai tukun ya kalli abincinta ya kuma kallonta....................

Cikin kankanin lokaci ta fahimci abinda yake nufi danbum shinkafar ta zuba mishi da sous din hantan ta d'aura akan karamin tray, a bowl ta zuba mishi fruit salad marar sanyi sbd murar da yakeyi, mikewa yayi ya zauna a hankali yana tankwashe kafa, a gabanshi ta ajiye mishi garin ajiyewa ne hannunta ya karkace saura kad'an trayn ya fad'i a tare suka kai hannu amma nata ya riga sauka hakan yasa hannunshi ya sauka akan nata.....................

A tare suka d'ago kai suna kallon juna basu san wani irin abu bane ya rike musu idanun cikin na

juna, sossai take kallon kwayar idonshi cikin 'batar basira wani maiko da bata san na me ba dake kwance a kwayar idanunshi, take kallo ta jima tana contemplating haka idonshi yake ko kuwa, se yau ta tabbatar da ashe haka idanunshi suke kaman an zuba ruwan zaiba.....................

Shima kallon manyan eye ball d'inta dake sakashi cikin wani yanayi da be san na mene ne ba yake yana jin wani tension na building inside him, rufe kofar da akayi ne ya dawo dasu daga thoughts d'in da suka fad'a, da sauri ta kawar da kanta a kunyace tana zame hannunta, satar kallon su Amrah tayi se taga duk sallah suke da alamu momma ce ta shiga toilet................

Wani munafukin murmushi ya sake he looks so charming with it sbd be bari murmushin ya gama mamaye fuskanshi ba iyakacinta gefen baki wadda yasa dimple d'inshi na dama lotsawa, a matukar kunyace ta zame ta zauna akan plastic chair tana boye fuskanta da hijabin jikinta, wayancewa yayi ya wani basar kaman ba shi ba tare da fara cin abincinshi.....................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Story and written by: fateemah Muhammad gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️5️⃣5️⃣▶️5️⃣6️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Da kyar khairi ta sake bayan wasu lokuta amma ta kasa cin abinci sbd wani fitinanniyar kunyarshi da take ji abinka da fulani, shi kam ko a jikinshi se ma yawan satan kallonta da yake, da ya gaji ma kwanciya yayi abinshi yana facing inda take zaune tare da lumshe ido, a jikinta take jin ana kallonta amma ta rasa waye ne ta kalleshi yafi sau abinda yafi se taga idonshi a lumshe...................

Tana cikin sake saken yadda zata tambayi momma labarin rayuwanta da kuma kaddaran musharraf taji an turo kofan, murmushi me kyau ta saki tana mikewa tace "sannu da zuwa mamie" mamien haidar ce tazo tana matukar ganin daraja da girman matan, mamie ma na murmushi tace "yauwa sannu ummulkhairi" gaisawa sukayi cikin mutumci, su Amrah ma suka gaisheta ta amsa musu tana tambayansu school, kusa da momma taje ta zauna suka fara irin gaisuwarsu ta kawaye.................

Nuri ce ta shigo da sallama ganin mamie yasa ta duka har kasa ta gaida ta, amsawa tayi fuska d'auke da fara'a tace "ya service?" Nuri tace "Alhamdulillah mamie mun kusa kammalawa" mamie tace "toh Allah ya bada sa'a daughter" tace "Ameen" tana kallon momma tace "momma inaga ni kam zan koma gida" momma tace "Ohk ku tafi da khairi ma sbd abincin dare" khairi na mikewa tace "toh momma, se kun dawo Allah ya kara sauki" momma tace "Ameen" sallama tayiwa mamie....................

Suka fice tana satan kallon gadon har lokacin idonshi a lumshe yake, bayan nuri ta bi tana mishi adu'ar samun lafiya, yinin ranan gabad'aya haka tayishi cikin wani yanayi da bata san na menene ba, a chan asibiti kuma bayan fitansu khairi momma ta mike tana cewa hajiya ruqayya

"zo muyi wani magana" mikewa hajjiya ruqayyah tayi ta bita.............

Mota suka je bayan sun zauna hajjiya ruqayyah tace "menene aminiya da baza ki bari mu koma gida ba?" Momma tace "hmm Ina so inga komai ya tafi yadda nake so ne ruqayyah, matsalolin musharraf kara yawa suke bazan ta'ba iya barinshi ya kara wattani uku zuwa hud'u nan gaba ba mata ba sbd lafiyanshi" hajjiya ruqayyah tace "me ya faru?" Nan momma ta bata labarin duk abinda doctor ya fad'a, seda ta sauke ajiyar zuciya tukun tace "Ina mishi sha'awar auren ummulkhairi"........................

Waro ido hajja tayi tace "'yar aikin da na turamiki?" Momma tace "ita fa ko kina ga tana da wani aibu?" Hajjiya ruqayyah tace "a'a sam se hankali da tarbiyya da na lura tana da shi kawai de gani nake kaman musharraf be so mace me wayewa ba taya za'a yi yaso wadda ko primary bata dashi, dukda tana kyau da diri kam"................

Murmushi momma tayi tana tuna abinda ta gani d'azu tace "ze so ta ne, tana da hankalin da nake tunani ita ce kad'ai zata iya fiddashi daga halin da yake ciki gabad'aya, sannan tayi karatu zuwa ss2 In kinji turancinta ma zaki rantse private school tayi" hajjiya ruqayyah zatayi magana kenan momma ta fara bata labarin khairi tun daga na iyayenta har ita kanta, wlh se da hajjiya ruqayyah tayi hawaye................

Cikin tausayawa tace "khaih duniya!! Alhamdulillah Alhamdulillah, Allah mun gode da ni'imarka garemu" don wallahi labarin khairi imani ya kara mata, cikin tausayawa tace "ai ko na sami 'ya aminiya, na d'aukewa mahaifiyarta nauyin duk abinda uwa zatayiwa erta a bukin, sannan me ze hana In an tashi biyawa Amrah kud'in waec da zatayi nan da two weeks musharraf ya biyamata, don kin san yanzu karatu shine gatan kowa a duniyan nan"..................

Momma na murmushi tace "mun kuwa gode kuma zan fad'a mata, eh nima nayi tunanin haka In yaso bayan auren ta ci gaba da karatunta ko a wajen aikinshi ne, sannan Ina tunani su dawo gida gabad'ayansu mu zauna tare a matsayin en uwa" hajjiya ruqayyah tace "masha Allah, Allah ya tabbatar da alkhairi, ya batun Nuriyyah kuma?" Momma tace "dazu mukayi maganan da su yaya Nasir yace yana so asa bukin kawai nan da wata biyu tunda next month zatayi passing out, kinga se a had'a da nasu khairin don zuwa lokacin itama ta gama WAEC d'in"..................

Sun kara tattaunawa kad'an kan suka fito jin har an shiga sallan la'asar d'akin suka koma hajja ruqayyah tayiwa musharraf sannu da jiki tana zolayanshi wato sai abokinshi na nan yake zuwa gidan ta ko, murmushi kawai yayi bata jira tayi sallan la'asar ba ta wuce...............

Washegari

Da safe ya matsa aka sallameshi suka tattaro suka dawo gida, direct site dinshi ya nufa yayi wanka da ruwan d'umi yana jin daadin jikinshi, bayan ya fito ya shirya cikin kananan kaya ya nufi parlorn momma don Allah ya gani yanzu be son kad'aicewa sbd tunanin dake cika mishi

zuciya da kwakwalwa and he hate that.................

A parlor ya kwanta abinshi don ba kowa kasa, yana nan kwance yaji ana gudu a hankali ya d'aga kai se yaga little ce da wasu kyawawan yara guda biyu mace da miji masu tsananin kama da juna ga kyau da Allah ya zuba musu daga ganinsu kuma ya ba zuciyarshi kannen yarinyar nan ne don kamansu, wurinshi sukayo da gudu little ta fad'a jikinshi yayin da su kuma suka jaaa birki...........

Murmushi ya musu a tare sukace "Ina kwana uncle?" Baki little ta turo tace "he's not uncle he is paapi, paapi ga nabeel da nabeela cuties siblings" mikewa yayi zaune yana saukar da little kasa yace "morning twins, ya Dada?" Sukace a tare "tana lafiya, she said we should behave kuma mu gaisheku, and we thank yhu for everything" murmushi musharraf yayi yace "duka mu kad'ai?" Nabeel yace "yes paapi"................

Murmushi ya kumayi yana d'aukan nabeela sama yace "lets go" little ta fara diddira kafa tana turo baki tace "paapiii" Da sauri yace "shhhhhhh, oya wuce muje yawo" tsalle ta fara cikin jin daad'i ta bi shi don har ya riga yayi gaba rike da hannun nabeel, mota ya d'auka suka fice daga gidan.................

Da misalin karfe goma sha d'aya na Safe momma ta sauko kasa zuwa d'akin Khairi a bakin gado ta same ta zaune da sauri khairi ta zame kasa, tace "sannu da fitowa momma" momma tace "yauwa khairi kin gama aikinki kenan?" Khairi tace "Eh na gama momma" momma tace "Toh khairi bari na baki labarin rayuwarmu inda zaki ji daad'in yanke shawaran da ranki ke so, ba zan miki dole ba khairi don wallahi kaman 'ya na d'aukeki, Ina so in na gama baki labarinnan ki yanke hukunci zuwa gobe....................

Sbd Ina son musharraf yayi aure as soon as possible, kin de ji abinda likita yace a asibiti" Kai khairi ta d'aga momma zata fara bata labari daga asalin tushensu khairi tace "Amrah ta fad'amin a yayin da take min bayanin waenda na gani a d'akin asibiti jiya" momma tace "Ohk bari na fara baki daga auren da aka yi min, Tunda aka kaini gidan mijina dake Abuja en uwa ko wa ya koma muhallinshi a lokacin na gama NCE d'ina, dama tun kafin auren mamaji ya sa hamma mahmoud d'in samamin aikin koyarwa a wani secondary school........................

Na yi good two weeks ban sa hamma mahmoud a idona ba, sam ban wani damu ba damuwa na d'aya zaman kad'aicin da nakeyi duk girman gidan ba kowa se ni kad'ai a part d'ina, daga waje kuma daga mai bawa flowers ruwa, drivers, se gateman, tunda na shiga gidan ko kofan part d'ina ban fito ba................

Abun ya isheni hakan yasa kawai na shirya a wata ranar Monday na fito dayake ina da Lettern makarantan a hannuna hakan yasa na san sunan makarantan Ina fita driver ya zo da gudu ya tambayeni Ina zan je na fad'a mishi sunan makarantan aiko be yi kasa a gwiwa ba ya d'aukeni se makarantan nayi reporting..................

Na fara aiki da kwana biyu ina zaune a parlor naji an banko kofa an shigo da sauri na mike Ina kallonshi ban hankara ba naji saukan mari hagu da dama a tsorace nake kallonshi yayinda shi kuma cikin zafi yace "Ke!! Ballagaza, wa ya baki izinin fita aiki? In ba jahilci da rashin tarbiyya ba taya za'a yi ki fara zuwa aiki ba tare da izini na ba" a tsorace nace "kayi hakuri zaman shirun ne ya isheni shi yasa nayi tunanin fara aikin kuma naga kai ka ne......" "dakata, ban miki gargad'in aurena ba Kika nace? Wato kinga mai kud'i shine zaki makale mai ko? Toh bari kiji In fad'a miki kin shigo kabarinki ne wai har kina da bakin ce mini zaman kad'aici ya isheki."..................

Shiru nayi kaina a kasa, kafa yasa ya shure ni har seda na kai kasa, nyau ya tofa min kan ya juya ya fice ajiyar zuciya na sauke, hawaye na silalo min kuka nayi sossai na share hawayena, ba yabon kai ba amma Allah yayi ni me tsananin hakuri da juriya ga zurfin ciki hakan yasa ba wadda na fad'awa kuma ba wadda nake da niyan fad'awa, bayan kwana biyu dadda(Aslamiyya mahaifiyar Mahmoud) ta kirani bayan mun gaisa take tambayata ya aiki? Ban so fad'a ba sam amma se ta matsa jin na fara kame kame, kuma kaman uwa take a gareni don diddi na(mamanmu shuwa) haihuwana kawai tayi................

Wahalana da reno na duk dadda ce, cikin rashin makama nace "hamma mahmoud ya hanani Dan Allah dadda ki rokamin mamaji ya roka min shi zaman gidan ba daad'i" dadda tace "hanaki yayi?" Nace "eh" tace "Toh shikenan se anjima" bata jira cewana ba ta kashe wayan se lokacin naji na shiga hali na tsoro, karfa dadda tayi mishi abinda ze zo ya min abinda yafi jiya....................

Bayan na gama tunanuka na na tashi na shiga kitchen na d'aura ruwan zafi don yin girki, tunda nazo gidan da d'an sauran kayan miyan da kawayena suka sayo na kafa murhu, nake anfani Allah ya taimake ni ma a rayuwana na fi son mai da yaji akan komai, kuma dadda babban roba guda na yaji ta had'ani da shi a cikin gara na, toh a ranan kayan miyan yake karewa d'an wanda ya sauran nake gyarawa..................

Wani banko kofan da akayi se da na tsorata, a matukar razane nake kallonshi ganinshi da belt a hannu yana gyarawa kan inyi wani yunkuri ya rufeni da duka na fitan hankali yana yi yana maganganu a ciki yana cewa "wato had'ani da iyayena kika fara tun ba'a je ko Ina ba ko? Toh bari inyi miki me tushe yadda zaki ji daad'in kai gulma" yana cikin duka na garin kaucewa hannuna ya buge tukunyar da na d'aura se jikina Allah yasa be yi zafi sossai ba amma azabar wurin kad'ai ya isheni musamman hannun da na buge da shi d'in ganin haka yasa ya kyaleni yana huci yace "for your own information daga yau In kayan gararki suka kare ki nemi abinda zaki ci wa cikinki, tunda kince se kinyi aiki ko biyar na bazan kara kashe miki ba, wawiya jaka"..................

A ranan nayi kukan da ban ta'ba irinshi ba a rayuwana duk da haka ban fad'awa kowa ba nayi jinyar kaina na koma bakin aikina, In takaice miki khairi a haka muka shafe kusan wata biyu lokacin ni nake zuwa da kaina in sayi kayan abincin da zan ci kuma In biya kud'in mota da kaina sbd ya hana drivern shi tukani kwata kwata ma ya hana In ta'ba mishi ko mota ne, kullum In zan

fita zuwa makaranta haka zan ganshi da mata kala kala ba randa na ta'ba ganinshi da mace d'aya hakan yasa nake ta adu'ar Allah ya rabani da shi da gaggawa In kuma shi ne mijina na har abada toh Allah ya shiryaminshi.....................

Wata ranar laraba da har abada bazan manta ba, bayan na gama d'an girki na na dare kad'an na ci na sha ruwa, tare da shigewa d'aki shap na manta dawowana ban rufe kofan parlorna yadda na saba ba, na fito wanka d'aure da zani a kirji naga mutum tsaye a bakin kofan bayangidan yana ta layi a matukar firgice na juya da niyar komawa se ji nayi an riko ni, irin rikon da akewa 'barawo In takaice miki a ranan mahmoud yayi min mummunar fyad'e azabar da na sha Allah ne kawai ya sani....................

Sati nayi ina jinyar kaina har asibiti naje akayimin d'inki da nurses din suka tambayeni fyad'e aka min se ce musu nayi eh, sossai suka tsinewa wadda yamin hakan ban tanka su ba har suka gama aikinsu, nan ma seda na kwana da safe na koma gida Ina iyakar kokari na wajen ganin ba wadda ya fahimci irin zaman auren da nakeyi, a haka a haka rayuwa ya ci gaba da gurgurawa duk randa ya shawu ya bugu haka ze zo ya farmin kaman dabba se ya tabbatar ko numfashi bana iyawa kan yake kyaleni In naki bud'e mishi kofa kuwa duk sadda ya kamani se yamin dukan da ko tashi bazan iya ba................

A haka na samu cikin musharraf, cikin wannan wahalar rayuwan gashi ko nayi niyyan fad'awa wani se in kasa, don ma makarantan da nake aiki suna min uzuri sbd tausayamin da suke kullum fuska na a kumbure idona a tare da jini basu ta'ba tambayana wa yake min hakan ba sede su tausayamin suyi ta min sannu, cikin musharraf me tsananin wahalarwa ne hakan yasa na kara ramewa nayi baki kirin, har iska na iya d'auke ni In fad'i, ana cikin haka mukayi hutu yayi daidai da bukin taheer hakan yasa mamaji cewa dole se munje haka muka tattara muka nufi gombe bayan uban kashedin da nasha a wurin mahmoud kuma naji don sossai na tsorata da lamarinshi kwata kwata be da tausayi da imani don da cikin ma haka yake duka na yayi ta naushin cikin hakan ze barni da azaba, ban ta'ba tsammanin musharraf ze zo duniya da rai ba........................

*kuyi hakuri plz na jina da kukayi shiru jiya ba lallai gobe ma ku jini ba sbd younger brother na ba lafiya anyi admitting d'inshi kuma ni ke zama dashi, plz kuyi mishi adu'a bcos he need it*

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️5️⃣7️⃣▶️5️⃣8️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Ba irin tambayar da su dadda basu min ba ganin irin karewar da nayi kaman kud'in guxuri amma na ki fad'a musu shi ne ma yace musu Ai basu ga yadda nayi jiki ba farkon auren kawai yanzu cikin nan ne, ba yadda suka iya haka suka bar zancen ba wai don sun yarda ba, har kunyan shiga mutane nake ji don duk wadda ya ganni se ya tanka.................

A haka aka gama buki muka koma Abuja zama nake na hakuri da juriya har na haifi musharraf wadda tsananin rabo ne ya ajiye cikin, na shaa wahala sossai lokacin sbd nayi labour ba me taimakona da kyar na fito tsakar gidan, mai gadi na ganina yaje da gudu ya kira mahmoud seda ya 'bata lokaci sossai kan ya fito se juyi nake kaman bazan rayu ba, da ya fi to d'inma a kaina ya tsaya yana min kallon banza ganin zan iya mutuwa su dadda su tuhumeshi yasa ya d'aukeni ya wurga mota tare da figar motar zuwa asibiti.....................

Naquda me wahala nayi kan na haifo shi a lokacin ya kira gida ya sanar musu inda mamaji ya bashi umarnin maza ya biyamin kud'in flight in koma gida kar ya yarda yace mota zanbi, ba don ya so ba Se don ba yadda ya iya haka ya biya yazo ya bani ticket a wulakance ko fuskan musharraf be gani ba, da kanshi ya kaini airport wai baya so inje inyi missing flight in ja mishi asara, bayan mun isa airport kan na fita a motar nace "baka mishi hud'uba ba" wata uwar harara ya zabga min a zafafe yace "baki da uba ne? Ke kar ki yarda, don't you dare try me a airport nan, bayan duk asaran kud'i da nayi da wadda zanyi dole In kun je gida se kin nemi kakaba min banzan d'ankin nan to wallahi ki kiyayi biyan bashi na"................

A hankali nace "ni de d'ana ba banza bane" waro ido yayi kan yayi wani yunkuri na fita daga motan da sauri, kwafa yayi tare da juya motarshi ya fice, trolley na naja rungume da d'a na da tambaya har na gane yadda ake komai a airport se kuma karance karance a haka har na shiga jirgi na zauna a sit d'ina da karanbani na d'aura belt don ban ta'ba ba................

A jirgin na taune dabinon dake jaka na na saka mishi a baki tare da zuba mishi ruwan zamzam, hud'uba nayi mishi da sunan baba na, don na gane baki da uban nan da yace min yana nufin kar In saka mishi sunan babanshi, bayan na isa hamma Nasir da matarshi Anty Aisha suka zo suka d'aukeni bamu ma shiga cikin gari ba muka wuce dukku, Anty Aisha rungume da musharraf, ni kuma Ina rike da marwan lokacin yana da kwana hamsin a duniya....................

Bayan mun isa naga suna ta fiddo kayayyaki daga motansu anan na gane  sun yi min duk wani necessary sayyaya daga gombe, sossai su mamaji sukayi murnan ganin musharraf se tabarakallah masha Allah suke cewa, a part din dadda (mahaifiyar mahmoud) na sauka, ranan suna suka tambayeshi sunan yaro yace yana jin kunyan fad'a a tambayeni tsabar iya lauyanci, ba kunya nace "Da sunan bappa ya mishi hud'uba" don bazan bari mamaji ya sa sunanshi ba In je In shiga uku na ni kad'ai, sossai kuwa sukayi farin ciki da sunan, ranan suna mamaji ya bada shanu aka yanka, bappa kuma ya yanka mishi raguna biyu basu ma bi ta kan mahmoud ba da be zo ba be kuma kawo kudin rago ba sun ajiye hakan as kunya bayan kuma yi d'inne bazeyi ba............

Bayan kwana arba'in sossai nayi kyau nayi bulbulbul har bana so ace yau zan koma Abuja duk da sossai dadda ta fahimci be damu da ni da musharraf ba gashi tunda nazo bata ta'ba gani nayi waya da shi ba, randa na cika kwana arba'in na tafi gombe sati biyu kwarara nayi, sati na farko gidan yaya Nasir, kwana biyu gidan yaya Ahmad shima lokacin matarshi na da tsohon cikin sufyan.............

Sauran kwanakin kuma gidan taheer nayi su kan na tarkata na koma dukku a lokacin dadda ta kira mahmoud ta ci mishi mutumci daidai gwargwado don tunda na zo Gombe mahmoud be zo ba har yau, dadda ta kuma jaddada mishi bazan koma ba har se ya zo In kuma yaga baze iya ba Toh yayi ta zama shi kad'ai yana fakewa da aiki.............

Ba yadda ya iya haka yazo ya d'aukemu su yaya Nasir suka kaimu har airport ran nan a had'e sbd fad'an da iyayenshi suka mishi a kaina, Ai ko isarmu bada jimawa ba ya min dukan da ba gaira ba dalili ya kuma biya bukatarshi da ni a wulakance............

Renon musharraf na cigaba da yi har ya kai shiga makaranta na saka shi a makarantan da nake koyarwa duk waennan shekaru mahaifinshi be kashe ko naira biyar akan komai nashi ba, idan ya shigo site dinmu musharraf na nufanshi ze hankad'e shi wani lokacin har ciwo yakeji tun yana zuwa wurinshi har ya daina, abu na farko da na lura musharraf na da shi kenan zuciya yana d'an shekara uku idan har mahaifinshi ya bugeni haka ze zauna yayi ta kuka kaman ze had'iyi rai inyi lallashin duniyan nan baze ta'ba shiru ba ban san ashe tsanan mahaifinshi na ginuwa a zuciyarshi bane............

Rayuwa na gurguwa dayake albashina me tsoka ne hakan yasa ba abinda muka nema muka rasa da d'ana improvement da na samu kuma shine cire damuwar mahmoud a zuciyana tun wani mahaukacin hawan jinin da nayi kaman ba zan rayu ba, gashi ba wadda ya sani a gida..........

Daga lokacin na cirewa zuciyata damuwanshi hakan yasa na d'anyi kyau dukda raman na nan se kuma haskena ya dawo, In kuma kinga munzo nan gombe to babban abu za'ayi se muyi shekara bamu je ba, a haka musharraf ya shekara bakwai In kin ganshi zaki rantse d'an shekara sha uku ne sbd tsawo da Allah ya bashi zaki sha mamaki In na ce miki bayan musharraf na d'auki ciki sau hud'u, biyu suka zube sbd duka sauran biyun kuma sbd rough sex ko ince miki raping.............

Kuma har yau ban ta'ba fad'an halin da nake ciki ba, haka musharraf sbd Allah yayishi ba me son magana ba kuma sam baya shiga harkar da bata shafe shi ba yasa be fad'awa su dadda ba ko a hira kuwa, a tsakanin ne aiki ya dawo da mahmoud gombe wani abinsu na siyasa da ban sani ba kuma 4years ze yi achan hakan yasa muka tarkato muka dawo sam ban so dawowarmu ba sbd tonuwar asiri ne a garemu, gashi ajiye aikana nayi, abinda yafi damuna kenan Ina zan samu kudin da zanyi enrolling musharraf makaranta? Kuma Ina zan samu kud'in da zan ci damu?.................

Bayan munyi settling a gidanshi dake gefen government house, naje gidan yaya Nasir da siyasa nace mishi Ina so in fara business kaman ya san kud'i nake nema a lokacin ya min transfern 200k sossai na mishi godiya haka mukayi da yaya Ahmad ma, shima 100k ya bani tare da sanya albarka business na fara na manyan leshuka da atamphopi, veils, shoes se perfumes irin na harkan manya de.................

Matan su yaya ahmad ne suka dinga had'ani da manya sossai harka ya bud'e har na samu shigarda musharraf makaranta a lokacin yana primary four, na kuma yi mana sayayyar kayan abinci, a kwana a tashi har mukayi shekara a Gombe business kawai na sa a gaba se kula da tilon d'ana, wata ranan alhamis muna zaune a parlor ni da musharraf Ina koya mishi assignment muka ji an turo kofa a tare muka d'aga kai ganin babanshi ne yasa suka ci gaba da abinda sukeyi.................

Toh kullum ya dawo se ta mishi sannu da zuwa amma be ta'ba amsawa ba tun tanayi ta zo ta gaji ta daina, dayake gidan sun nan se an shiga main parlor ake shiga part part na gidan wadda guda biyu ne se boysquaters, Ashe yaji haushin banzan da mukayi dashi a tsawace yace "Kai wawa marar anfani, baka ganni bane da baza ka min sannu da dawowa ba In ita uwarka taki min din ni ba ubanta bane, kai baza ka min ba Ina ubanka?" Shiru musharraf yayi.................

Yana matsowa yace "Kai don uwarka wannan ba magana nake maka ba?" Musharraf yace "bade uwata ba" cikin gunguni wani wawan mari ya sauke mishi da sauri ya nufi wurin tv ya fisgo wayar Av ya dawo Ina ta zungurin musharraf ya gudu amma wawan zuciyarshi ya hanashi tashi yana zuwa ya rufeshi da duka tunda musharraf ya nad'e kafafuwanshi ya d'aura kanshi a kai be kara motsi ba kaman itace ake duka.................

Abinka da uwa se na kasa jurewa na san tunda musharraf yayi haka baze ta'ba gudu ba kuma baze yi ihu ba, hakan yasa na rike Av Ina cewa "kayi hakuri yaya mahmoud" mari ya saukemin tare da komawa kaina ya fara duka yana yi yana masifa "duk ke ce me hure mishi kunne gaki uwar banza me koya mishi tarbiyar banza aka gaya muku da maganarku da rashinshi wani abu ze karamin ne, en iska kashin tsiya".................

Ya d'aga ze kai kenan yaji an rike Avn yana juyowa yaji saukan mari yaya Nasir ne da matarshi se d'ansu mari ya kife Mahmoud dashi hagu da dama yace "mahmoud irin tarbiyar da aka bamu kenan? Ko bare ce zaka sa ta gaba kana wannan dukan a gaban d'anta balle er uwarka? Me ta maka haka? Yarinya me hankali da natsuwa" mikewa musharraf yayi da gudu ya fad'a jikin uncle dinshi, kirjinshi se tashi yake yana sauka shi ba kuka ba shi ba shiru ba yace.................

"Uncle ka gayamishi ya fita harkar uwata da ni tunda baya karinmu da komai, uncle kullum mutumin Chan se ya duki momma bayan bata mishi komai, momma na ke saya mana kayan abinci, momma ne ke biyamin kud'in makaranta duk abinda nake so ita ke saya min ta kuma saya ma kanta to me yasa ze zo yayi ta dukanta?" Da matukar mamaki yaya nasir ke kallona ya kuma kalli mahmoud.................

Dukawa yayi yana kallon jikin musharraf da yayi rud'u rud'u da duka yace "son kayi kuka, kaji In kayi zuciyarka ze yi sanyi irin haka na sawa mutum ciwon zuciya, kaji yi kuka" kuka ya fashe dashi sossai yayi kuka, seda hawaye ya cika idon yaya nasir da matarshi, samun wuri yayi ya zauna muma muka zazzauna a hankali yace "Fatima gayamin rayuwarki na aure daga farko har yau" Shiru nayi, be ce komai ba ya fiddo waya yayi kira "duk inda kake ka zo gidan mahmoud

yanzu yanzu it's urgent plz" Shiru muka zauna se kallon mu yakeyi ya kalleni ya kuma kalli mahmoud..................

Ba'afi fives minutes ba akayi sallama Ahmad ne ya shigo zama yayi yana cewa "lafiya?" Hamma Nasir yace "ba lafiya ba" ya kalleni "ke fatima, kalleni Ina wasa dake??" Girgiza kai nayi yace "bani labarin rayuwan aurenki daga farko har yanzu" a hankali na fara bashi labari jin ba wasa a lamarinshi kallona suka dingayi kaman tv har na gama a tare suka maida idonsu kan mahmoud...............

Baki ya bud'e da niyyar maganan a tare suka sauke mishi mari d'aya haggu d'aya dama, Yaya Ahmad yana hawaye yace "irin tarbiyar da dadda da diddi suka mana kenan? Mahmoud me yasa zaka ci amanar aure ka san kuwa illar dukan mata matan ma matarka?" Yaya nasir kam kasa magana yayi, da kyar yayi mishi nasiha me ratsa jiki, Ahmad kam fad'a sossai yayi mishi kuma da zaran ya bud'e baki da niyar magana se ya d'auke shi da Mari a karshe yace mamaji ze fad'awa.....................

A hankali nace "kuyi hakuri hamma Dan Allah karka fad'a musu baza su ji daad'i ba kuma ka san mamaji nada hawan jini plz kar wani abu ya sameshi" yace "naji Amma In yana so muyi Shiru se ya sayo kayan abinci ya cika store sannan ko marinki yayi ki fad'a min wallahi zaka sha mamaki na banza marar tunani" juyawa yayi ya fara tafiya har ya kai bakin kofa yace "sannan ka cire musharraf a makarantar da ta sa shi da kud'inta ka maida shi wadda yafi tsada a gombe, zan zo gobe da rana inga bakayi abinda nace ba zaka sha mamaki na mahmoud" ya juya yayi tafiyarshi.................

Fad'a sossai da nasiha yaya nasir ya kara mishi don ya san yafi jin tsoro da kuma maganan Ahmad ya san dole yayi abinda yace, kaman kuwa nasihar ta shigeshi a washegarin yayi duk abinda yaya Ahmad yace kuma da gaske yazo ya gani sossai ya ja mishi layi ya mishi tijarar da ya bani tsoro don beda fad'a sam, Ashe jiyan ma don ganin yaya nasir ne...................

Ai kuwa sossai maganan yaya Ahmad ya shigeshi, ya ajiye mana kayan abinci sossai ya kuma sauyawa musharraf makaranta, kuma be sake min ko kallon banza ba, ba lefi kuma In yazo karban hakkinshi ba ya mata ta karfi, a haka na samu cikin nuriyyah, ranan na tashi da laulayi sossai Ina kwance zazza'bi ne ke damuna, dama tunda ya sayo kayan abinci dashi nake girki kuma yana ci................

So ya fito se be samu breakfast d'inshi ba, a zafafe ya shigo d'akina ina kwance cikin bargo ya janye bargon tare da cewa "ke!! Me kike nufi? In sayo kayan abinci kuma baza ki girkamin In ci ba? Ai ko baki isa ba karkiga kaman don na sararamiki kwana biyu ki zata tsoron su hamma nake wallahi yanzu se in tattakaki" a hankali nace "kayi hakuri bana jin daad'i ne" ban rufe baki ba ya janyoni kasa "ba ruwana da rashin jin daad'inki ki wuce ki samamin abinda zanci" kasa mikewa nayi yace "taurin kai ko? Ohk" belt na jikinshi ya zare ya fara dukana................

Kaman daga sama mukaji musharraf yace "baba me tayi maka kake dukanta? wallahi ka kara

dukanta se na rama mata da tsantar mamaki babanshi ke kallonshi jin furucin da ya fito daga bakinshi kan ya d'auke shi da mari, ganin ko gizau be yi ba sema kafa mishi ido da yayi yana kallonshi juyawa yayi ya fice a fusace kama ni yayi na mike ya taimaka min zuwa kan gado zan mishi magana akan abinda yayi yanzu se kawai ya juya da sauri ya fice.......................

*thanks for your prayers ya samu sauki sossai Alhamdulillah*

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

*This page is dedicated to yhu mama on this your special day, Ina rokon Allah ya karo miki shekaru masu albarka, ya biya miki dukkanin bukatunki na duniya da lahira, Allah ka bata tsawon kwanan da zamu faranta mata kamar yadda ta faranta mana kuma take kai. Yhu the best woman I've ever met and strong lady I've ever known. I love yhu so very much mama*

Page➡️5️⃣9️⃣▶️6️⃣0️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Musharraf ne ya kula da ni a ranan, dukkanmu da ni dashi tea muka yini sha sbd be iya girki ba ni kuma bazan iya ba, da dare mahmoud ya dawo ganin ba abinci a dining yasa ya nufi d'akina da belt a hannu Ina kwance cikin burgo ya yaye blanket d'in ya fara dukana, bai hankara ba kawai yaji saukan kwalba a keyanshi a matukar razane ya juya da tsantsar mamaki yana kallon d'anshi d'an shekara tara wai yana dukanshi.........................

Kwalban pepsin dake hannunshi ya bi da ido, belt mahmoud ya zuba mishi shi kuma ya d'aga kwalban da niyyar sake kwad'a mishi a firgice nace "innalillahi wainna ilaihi rajiun Abubakar!! Me zan gani haka? Me kakeyi" na karasa maganar cikin d'aukewar hankali ban kara sanin inda kaina yake ba se na ganni asibiti su hamma Ahmad suna tsatsaye kaina sannu suka dinga min...............

A kasalance na amsa Ina dudduba inda zanga musharraf baya d'akin, yaya Ahmad yace "sannu fatima, dukanki ya sakeyi ne? Musharraf ya kira mu da gaggawa wai yazo ya ajiyeku a asibiti

yayi tafiyarshi" girgiza kai nayi nace "a'a hamma be dakeni ba ban da lafiya ne, Ina musharraf d'in?" Yaya Nasir yace "yana waje yaki ce mana komai" ajiyar zuciya ta sauke tana runtse ido, doctor Aslam ne ya shigo yana kallon su hamma Nasir yace "congrats tana d'auke da cikin wata biyu" cikin jin daad'i sukayiwa Allah godiya..................

Nan suka tambayeshi yaushe ne sallama, yace za'a iya sallamanta zuwa gobe da safe, godiya suka mishi ya fice a take suka kira su dadda suka fad'a musu suma sunyi farin ciki sossai da sukaji da laulayi kuwa suka ce zasu bani dattijuwar me aikinsu ta kwana mini biyu, Ai ko washegari aka sallameni na samu ma mai aikin ta iso na bata d'aki cikin part d'ina tunda aka kaini asibiti musharraf be yarda mun had'a ido ba har aka sallamoni.............

Bayan mun dawo ne na samu ganinshi sossai na mishi fad'a da nasiha yace baze sake ba, a haka a haka na yi renon cikin nuriyyah har na haifeta tun daga sanda musharraf ya d'aga ma mahaifinshi hannun kaina be sake dukana a gabanshi ba sede yayi min hukunci a lokacin kwanciyar aure, abinda ya matukar bani mamaki kuwa shine ganin sa'banin yadda na gani a lokacin haihuwan musharraf......................

Allah ya d'auramishi son nuriyyah tun daga randa ya d'aura ido a kanta hakan yasa ta samu gatan suna sossai daga wurinshi har su yaya nasir suka zata ya sauya haline amma hausawa suka ce hali zanen dutse yana nan da kayanshi, seda nuriyyah ta shekara biyu tukun muka koma Abuja inda ya ci gaba da shaye shayenshi wadda da bayayi a gombe, ko da yanayin kuwa be ta'ba shigowa gida a buge ba...................

Sam jituwa be ta'ba shiga tsakaninsu da musharraf ba nayi iya yina da kokarina don ganin musharraf be tsani mahaifinshi ba amma ban ci nasara ba ganin abun na shirin kwa'bewa yasa na yi enrolling musharraf a boarding school don tun kafin mu dawo mahaifinshi ya dena biya mishi kud'in makaranta wai ba yadda za'ayi yana wahala da yaro bayan ci da sha ya kuma biya mishi kud'in makaranta amma yazo yana mishi rashin kunya ba...................

Sam musharraf be so ba da kyar na samu na shawo kanshi ya yarda don shi gani yake In baya nan babanshi ze samu damar ci gaba da dukana yadda yake so, shekaran nuriyyah hud'u na haifi miemie wacce asalin sunanta Aslamiyya muke ce mata miemie, seda mukayi rikici sossai kan ya yarda da sunan don seda na had'a shi da yaya Ahmad abunda ya mugun bashi mamaki kenan don be zata zan iya ba, shekarar miemie be cika biyu ba na samu cikin Amrah.................

A lokacin musharraf ya gama secondary school yayi jamb ya kuwa ci, sossai aikina ya taimakeni don tun dawowarmu Abuja na koma, da kud'ad'ena da nake tarawa na samu yi mishi chukuchukun samun University of Abuja, yanzu muna cin albarkacin son da yake yiwa nuriyyah yana saya mana kayan abinci, ya saya a makaranta me tsadar gaske, duk da rayuwan aurenmu be koma kaman na mutane ba amma ya bar dukana sbd nuriyyah tace bata so.................

Shekarar musharraf 24 ya gama jami'a har service inda ya karanci accounting a lokacin na

samu kawata hajjiya ruqayyah wacce tun zuwanmu Abuja muke mutunci sossai amma kawancen be yi karfi ba sbd ban bada fuska ba, sede 'ya'yanmu musharraf da haidar da suke abokai, itace ta kar'bi takardun musharraf ita da mijinta suka mishi hanyar samun aiki a CBN..................

Shekarar nuriyyah 15, yayinda miemie take 11 se Amrah 9, a lokacin kuma musharraf ya fara matsanancin ciwon ciki kullum muna hanyar asibiti Zaki sha mamaki kuwa In na ce miki har lokacin basa ga maciji da mahaifinshi ba irin nasiha da wa'azin da banyiwa musharraf ba amma ya riga da rike shi a rai, dayake zaman mu rabi gombe rabi Abuja yasa su nuriyyah suka saba da en gomben sossai, naji mamaki sossai da likita yace wai musharraf na da karfin sha'awa hakan yasa maniyyi ke taruwa mishi a mara wadda yake haddasa mishi ciwon ciki me tsanani....................

A tsakankanin ne komawa gombe ya kamamu, sabon gida muka koma me d'auke da part biyu manya a d'aya na gaban muka zauna, sam hankalina be kama da barin musharraf shi kad'ai a Abuja ba dukda na yarda da tarbiyar shi amma shed'an tana tsoron sharrinshi, Kiran musharraf nayi a waya nace In yana da buduruwa tayiwa su yaya nasir magana a tura gidansu................

Ce min yayi be dashi ya bani dama in za'ba mishi duk wacce naga tayimin, Anty Aisha na samu mukayi maganan inda ta ta had'amu da surayyah yarinya me hankali da natsuwa er gidan manya ba wai kud'i ba a'a Addini da tarbiyyah, a lokaci kankani aka yi komai aka gama mamaji yace tunda site biyu ne damu ta zauna a d'ayan kan musharraf yayi gini, sam musharraf be so ba amma ba yadda ya iya, shi abinda baya so shine anfani da komai na babanshi..................

Se ranan d'aurin aure musharraf ya zo, don gudun idon mutane yasa mahmoud had'a musu dinner na manya da yara a tsare yayi komai kuma naji daad'in hakan da kyar na shawo kan musharraf yaje, abinda na lura da shi sosssi a wurin dinner shine kallon da Mahmoud ke yiwa surrayah har abun yaso tsorata ni, amma ganin mun had'a ido se ya wayance be kuma sake kallonta ba.....................

Abuja suka wuce a chan suka ci gaba da zama har surrayah tayi nasarar sa musharraf fara sonta da kyakyawar d'abiyanta, duk hutu in ya samu gombe suke dawowa muyi tare, har ta samu cikin Zarah, Ashe musharraf da haidar suna business wadda ban sani ba seda ya saya gidan da muke cikin nan a yanzu haka...................

Seda ya kawo ni gidan kan yace "surprise momma, ga gidanmu" harararshi nayi nace "stop kidding me" musharraf na murmushi yace "wallahi da gaske momma, muna business na shigo da motoci da haidar wadda muka had'a share, ban fad'a miki bane kawai sbd Ina son yi miki surprise ki san d'anki ya girma" dariya nayi sossai cikin farin ciki na sawa business d'in albarka..................

Bayan haihuwan zarah da kwana arba'in cib cib wani ranar alhamis da tashin hankali ya shigo rayuwarmu me tsanani don ba wadda be azabtu da wannan ibtila'i ba a family d'inmu, tun bayan

haihuwan zarah da musharraf ya koma be dawo ba se ranan dayake a gida surrayah tayi wanka wata dattijuwa iyayenta suka turomata ta taya ta zama itama dattijuwar ranan ta tafi.................

Part dina straight musharraf ya sauka bayan isowarsu da murna na tareshi yadda na saba, mun d'an jima kan yace bari yaje yayi wanka a part dinshi ya dawo yana fita da kamar five minutes naga musharraf ya shigo a tsanin rud'e jikinshi na mugun rawa idanunshi sun kad'a zazur har hawaye na zuba a rud'e na mike nace "Lafiya musharraf?" Be iya amsa ni ba se part d'inshi da yake ta nuna min da hannu.................

Da sauri na bi shi tun daga parlor nake jin gurnani da nishi irin na masu yin sex a hankali na d'aga labulen d'akin tashin hankalin da na shiga ba a kwatantawa khairi kin san kuwa abinda na gani? Bata jira amsar khairi ba tace mijina da surkata tsirara kwance a kan gado turmi da ta'barya suna aikata mash'a a razane khairi ke kallon momma da kuka ya sarke ta seda ta samu tayi tukun taji nauyin zuciyarta ya ragu har seda ta saka khairi kuka dama tun daga farkon labarin take share hawaye..................

Ci gaba momma tayi da, yanke jiki nayi na fad'i ashe a daidai lokacin musharraf ya je kitchen ya d'auko wuka da niyyar da'bawa mahaifinshi duk da ya lura da had'in kan matar akeyi amma yafi ganin bakin mahaifinshi a kanta, Allah ya sa yana shigowa baban ya lura dashi da sauri ya mike ganin wukar da musharraf ya kawo setinshi hannu biyu yasa ya damki hannun musharraf dake rike da wukan a take suka fara kokawa hannun mahmoud ne a sama shiyasa ya zama kaman shi ke controlling juyawar wukan...................

Ganin musharraf na shirin fin karfinshi ne yasa ya saita surrayah dake kwance a sandare ta kasa komai ya ja musharraf da karfi wukan ya da'bu a cikinta be shiga sossai ba amma ba karamin azaba taji ba da ya sata sandara ihu, da sauri mahmoud ya saki wukan ya d'ibi kayanshi yayi bayi da gudu tare da danna sakata, bayan ya sa kaya ne ya kira police yake ce musu wai d'anshi ya kashe matarshi yana shirin kasheshi suyi sauri su zo..................

Shi musharraf tunda wukar ta sauka cikin surrayah ya daskare a wurin idonshi har lokacin be bar zubar da hawaye ba don ba karamin so yakeyiwa surrayah ba, a hankali ya sabule hannunshi daga kan wukan yana juyawa zuwa kan sofan dake d'akin ya zauna a tsananin rude ya ma kasa tuna ni Ina kwance a sume a d'akin, ita kuma surrayah ganin jini na zuba sossai yasa tayi kokarin tashi tana dafa gado hannunta ne ya gauce se jinta tayi a kasa tayi rub da ciki wukar ya gama shiga cikinta wani ihu da ta tsala seda ya tsorata musharraf da gudu ya taho ya juyata a lokacin polisawa suka cika d'akin suna saita musharraf da bindiga shi kuma se kallon surrayah yake cikin tsananin takaici da haushinta wa ya san ko tun yaushe ta fara mu'amala da mahaifinshi..................,,,

Kamashi akayi se a lokacin mahmoud ya fito yana ganina a sume ya fara ihun karya yana cewa "bade ya kashemin mata ba ko?" Police mace ce ta ta'ba wuyan Momma tace "bata mutu ba suma ce kawai" ruwa aka saka man na farfad'o kenan naga d'ana sanye da ankwa har biyu a

hannunshi a gaba suka saka shi Ina ta ihu da cewar baze aikata haka ba suka kamashi suka tafi dashi......................

In takaice miki gwagwarmaya sossai akayi a court wadda duk sheda ta nuna musharraf ne ya aikata komai kuma karya yake da yace ya samu mahaifinshi da matarshi turmi da ta'barya, da na so 'boyewa amma ganin ana shirin halaka min yasa na mike nayi shedar nima da nake matarshi na gani ido da ido rudewa kam su dadda sun yi shi wadda yayi sanadiyar kamuwarsu da hawan jini, mamaji kam har ciwon zuciya..................

Mutane wasu sun yarda wasu basu yarda, a take don ba sheda ga sawun hannun musharraf d'in jikin wukan aka yanke mishi hukuncin zama a gidan yari na har abada, a nan na yanke jiki na fad'i, da sauri aka d'aukeni zuwa asibiti jini yayi mugun hawa ba kad'an ba, su dadda da suma suke fama da jikinsu ne suka ci gaba da bani baki amma inaa d'ana namijin kwaya d'aya jal shine aka yaankewa zaman gidan kaso da har abada? Kuka sa me sauti bayan sati biyu aka sallamenu bamu zarce ko Ina ba dukku don na tsani zama da mahmoud a lokacin na san ko mutuwa yakeyi yana farfad'owa bazan ta'ba komawa gidanshi ba.................

Family meeting aka had'a inda anan na cire kunya na bada labari yadda Yaya mahmoud ya kuntata min ya azabtar dani, ya kuma zalunceni, ba wadda be yi kuka ba dadda kam har seda ta wanka min mari kan ta yake jiki ta fad'i mamaji ma ciwon zuciyarshi ta tashi a tare aka had'asu zuwa asibiti.........................

*kuyi hakuri plz saboda rashin wuta ne yasa kuka jini shiru shekaran jiya da jiya*

#vote
#share
#comment

**Not edited

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️6️⃣1️⃣▶️6️⃣2️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

In kika ce tashin hankali kin rage a abinda na shiga ko ince muka shiga gabad'aya family, mamaji kaman baze rayu ba ko da suka yi niyyar tsinewa Mahmoud Bappa da diddi ne sukayi tsayin daka wajen hanasu inda suka nuna musu ko basu tsine mishi ba abinda de ya shukan nan shi ze gir'ba sun amince baza su tsinemai ba amma kar ya sake tako kafanshi inda suke har abada In kuwa yazo to tabbas tsinuwa ce tsakaninsu, ba yadda su hamma nasir basuyi ba ganin an ku'buto da musharraf amma abin yaci tura abinda yaso haukatar dani kenan..................

Dadda da ta tashi yimin fad'a har kaman zata bugeni akan yadda na boye rayuwar aurena, se kuma suka d'aurawa kansu laifin suna rayuwa with that guiltiness, khairi In nace miki na zauna na natsu karya nake yi, tunda aka kai musharraf prison ban kara bacci da dare ba, kullum a tsaye nake a gaban ubangiji abinci se anyi da gaske nake ci su miemie kam ma ko kallonsu bana yi dukda basu san me ake ciki ba wacce ta fahimta ma nuriyyah ce haka In Ina kuka zata zo ta sani a gaba muyi tare...................

Da nasiha da adu'o'i da komai aka samu na d'an sake har muke zuwa prison ziyartar musharraf randa na fara zuwa halin da na tadda musharraf ya kusa yin ajalina, a buge ba yadda yake rungume shi nayi ina kuka kaman raina ze fita hakan yasa shima fara hawaye, inda da kyar na samu yayi min magana ya tabbatar min tunda abin ya faru kuka ma be samu yi ba se yanzu, a sanyaye na ce "musharraf me ya kaika fara shaye shaye da hankali da iliminka?" A yanayi na marar hankali yace "Toh me kike so inyi momma? Anan fa zan kare rayuwana sanadiyar sharrin mahaifina, na san yaushe zan mutu? Na san iyakar shekarun da zanyi a duniya? Momma dan Allah ki barni kawai abin nan yana rage min damuwa kaman yadda na ciki suka fad'a"......................

Ina girgiza kai nace "Inaa musharraf ka fawallawa Allah lamuranka shine kad'ai me iya rage maka damuwa ba shaye shaye ba, musharraf ba tarbiyarka ba kenan amma ban ga laifinka ba duk na mahaifinka ne" yana kallona da idonshi da suka rine da kayan maye yace "Ina rokon ki abu biyu a duniya momma, ki kularmin da little sossai momma ki kuma kwantar da hankalinki wurin tarbiyar su nuri kar laifin ubansu ya shafesu, sannan abu na biyu shine dan girman Allah karki komawa auren mahmoud don Allah" Ina gyad'a kai nace "naji musharraf naji, zanyi duk abinda kace" ya kuma cewa "sannan alfarma nake so kiyi min na komawa gidana na nan garin da zama, ki kula da su little a wurin ki ci gaba da sana'anki"...............

Nan ma kai na gyad'a mishi yana baya baya yace "and kiyi hakuri ganina ze dinga d'aga miki hankali hakan yasa na yanke shawaran bazan kara fitowa ba daga yau, am sorry" Ina ta kiranshi amma ko waiwayowa be yi ba ya wuce su hamma ne suka kama ni muka tafi, haka na dinga zama da kewan d'ana da kyar na samu na shawo kan su diddi suka barni na dawo cikin gombe da zama, anan na ci gaba da business Ina ci gaba da kula da su miemie, a lokacin ne kuma su hajjiya ruqayya suka dawo gombe, sossai ita da mijinta sukayi mana jaje, se kuma daga lokacin kawancenmu yayi karfi....................

Kullum In naje prison musharraf baya fita haka kuma bana kin zuwa ko letter in bayar akai mishi, sannan mahaifinshi ban kara ganinshi ba, kowani karshen wata se su hamma nasir da Ahmad se sun turo mana kayan abinci da kuma kud'i haka taheer ma, a lokacin ma anyi auren Rabi'ah har ta haifi afreen................

Bayan three years

Se bayan three years aka chanza mana sabon governor a gombe state inda yayiwa duk en prison afuwa wadda de ba'a saka mishi baza'a ta'ba sake shi ba a file se Allah ya taimakemu musharraf baya ciki, nuriyyah na zaune tana kallon Network news kawai taga an sanar da sake en prison da sabon governor ya bada umarnin ayi da gargad'i me tsanani In kuwa suka kuma aikata laifinsu toh za'a dawwamar dasu a prison din.................

Da gudu nuriyyah ta haura ta sameni tana kuka tana dariya hannuna ta kama cikin tsantsar farin ciki tama rasa me zata ce se tsalle take a d'an rude nace "lafiya kuwa nuri?" Tace "momma zo ki ga, zo ki gani" mikewa nayi ganin yadda take ja na, har gaban tv ta tsayar dani a lokacin ake maimaita kanun labarai, Ina gani na sulale nayi sujada ina mai mika godiyata ga Allah se kuma kukan murna ya biyo baya, su hamma Ahmad ne suka kirani suna tambayana ko na ga news cikin kuka nake ta gyad'a kai suka ce In jira suna zuwa...................

Cikin 30mins suka zo da matansu mu matan kam se kuka mukeyi hajiya ruqayyah ma tazo da mijinta wadda ya kasance a da abokin mahmoud amma tunda abunnan ya faru ya fita hanyanshi, a tare muka dunguma zuwa prison at last after good three years zan sa d'ana a ido, ashe he will be free one day, Ashe Ubangiji na ya amshi adu'o'i na, a bakin kofa muka tsaya jira har ya fito kasa karasawa wurinshi nayi se kuka................

Da kanshi ya karaso ya rungume ni, yayi baki sede ba rama a jikinshi se ma wasu packs da suka fito rad'a rad'a a cikinshi don ba riga ya fito, daga ka ganshi zaka san ya zama tantiri d'an shaye shaye, bakinshi yayi maroon duk da dayawa na cewa kyau ya karamishi, duk en uwa ma rungume shi suka dinga yi d'aya bayan d'aya, a lokacin mamaji ya kira yace mu wuce dukku..................

Ina rike da hannun musharraf kaman wadda aka ce ze gudu ko wani abun ze sameshi In ban rike shi ba muka koma gida, su little zamu d'auka se mu wuce dukkun mun kuwa samu sun taso daga school gabad'aya motan da muke suka shiga kasancewarshi babban sienna ne, kallon kallo little da musharraf suka tsaya yi Bayan nuriyyah ta rungumeshi ta sake miemie da Amrah da basu ganeshi sossai ba seda nuriyyah tace "Hamma musharraf" kan suka rungumeshi suma Amrah na cewa "Ina ka tafi ka barmu hamma, tun tafiyanka ba me kaimu shopping ba me saya mana chocolate and rest and kullum se miemie ta bugeni bayan ka hanata" ture ta yayi daga jikinshi ba tare da ya ce komai ba.................

Anan na lura da sabon miskilancin da ya koyo wadda da ba halinshi bane kuma na lura duk en uwana su taheer da su hamma nasir da kyar yayi musu murmushi, abin yaso sani kuka don ba haka yake ba yana da son mutune mussaman ma kannenshi duk da na san son sun a jininshi yake amma miskilancin da ya koyo baze sa ya nuna musu ba, tapping laps dina da yayi shi ya dawo dani daga tunanin da na tafi tare da maida idona kanshi...................

Little ya nuna min tukun ya nuna kanshi, alamun yana tambayana ershi ce? Kai na gyad'a mishi se naga murmushi a fuskanshi yana kallonta yace "hi little" kallona tayi nace "your paapi" Ai da gudu ta rungumeshi dama ta saba ganinshi a hoto kuma kullum se tayi magananshi inaga

duhun da yayi da kuma gashin dake kanshi da ya tara kaman ba Indiye don har bayan wuyanshi ya sauko se kuma lips dinshi da suka koma maroon yasa ta kasa ganeshi, nan ta dinga zuba mishi surutu wani ya amsa wani yayi murmushi har muka isa.....................

Abu na gaba da na lura ya shafawa kakkanninshi ta wurin uba laifin ubannashi don da In munje dukku wurinsu yake fara sauka suyi wasa da dariya kan ya wuce part dinmu amma wannan Karo ko kallon part d'insu be yi ba ya wuce namu, da suka had'u ma da kyar ya gaishesu suna mishi wasa ma ko murmushi be d'aura a fuskanshi ba balle magana, har kuka sukayi sbd hakan, sossai na mishi fad'a amma ba abinda ya sauya..............

Da iyayena kawai yake d'an wasan jika da kaka, kwana biyu mukayi muka dawo cike da alhinin sabon halin musharraf en uwan mahaifinshi da suka fito ciki d'aya ma ba magana yake musu ba bayan gaisuwa, muna dawowa kuma ya ci gaba da shaye shayenshi sossai fah kaman ba gobe sossai na tsorata na kira en uwana muka zauna hamma Nasir, Ahmad se Tahir da Rabi'ah sossai muka tattauna inda taheer ya bada shawaran kaishi gidan tauri................

Tashi d'aya na ki, hamma Ahmad ne yace akwai doctorn da ya sani yana treating irin abun ze tuntu'beshi yaji, sannan dole se mun dage da adu'a kuma tunda yana so na sossai duk duniya ba wadda ze girmama magananshi se ni, In dinga nuna mishi tsanata ga kayan maye sannan wa'azuzzukan da sukayi magana akan shaye shaye ki nema mishi caset din yana ji..................

Sossai na aminta da shawaran yaya Ahmad inda daga nan muka dage ana treating dinshi ina nuna mishi 'bacin raina ga wa'azi da dama ya sani amma yake takewa cikin wattanni uku mukayi nasarar sashi dena shaye shaye, se taba kawai da har yanzu be dena sha ba wadda muke fata ya dena,  a bayan hakan ya koma aiki ta hanyar mahaifin amininshi haidar wadda lokacin da shima yaji labarin an sakeshi ba karamin kuka yayi ba, Ashe kuma duk shekarun nan yana ci gaba da kula da business d'insu Inda yake wa musharraf savings din nashi share d'in account daban da ya bud'e mai da ya bashi atm card din, ba karamin murna mukayi ba gabad'aya har musharraf a lokaci d'aya ya mana hidima mai yawa har chanjin furnitures da sa na d'akinshi, motoci biyu da ya saya bayan tsohon nashi..................

Abuja ya koma da zama sede yana yawan zuwa weekend anan cikin nasara ya koma aiki don ana yawan tura shi assignment kasashen waje da haka yayi ta samun karin matsayi har zuwa yanzu ya kaini makka a first year dinshi na komawa aiki haka In an bashi assignment zuwa wani kasa se ya za'bi kanwanshi d'aya su tafi tunda d'awainiyar ba kanshi yake ba, Toh kinji khairi wannan ne tarihin musharraf kinji sanadiyar tsana da wulakancin da musharraf ke yiwa mata bayan ni kannenshi, ershi da mamana....................

Kinji sanadiyar da yasa ya dena sakewa en uwana mussaman waenda suke ciki d'aya da Mahmoud...........

*********

Kuka kam khairi tayishi ba kad'an ba, wani irin imani ne ya shige ta ashe nata rayuwan nafila ne da nasu sossai tausayin musharraf ya shigeta sam kuma bata ga laifinshi na tsanan mata da yayi ba kuma bata ga laifinshi na maganganun da yake yiwa mahaifinshi ba.................

A hankali tace "na Amince momma zan yi iya kokarina In shaa Allahu wurin ganin hamma musharraf ya koma rayuwanshi irin na da me cike da tausayi da son mutane, haka kuma In shaa Allahu baza ki sameni da halin cin amana irin na surrayah ba" hawaye momma ta share tana murmushi lokaci d'aya cike da jin daad'in kalaman khairi tace "na gode khairi, na gode" mikewa momma tayi ganin har magrib ya kusa basu yi la'asar ba ta fita tana istigfari Allah ya taimaka tacewa su Amrah suyi girkin dare................

Bayan tayi sallahn la'asar ta fito da azkar a bakinta na tuban rashin sallan la'asar a kan lokaci se lokacin take tunanin inda su nabeela suka shiga, a gaban wani door size enlargement d'inshi dake parlorn ta tsaya tana kare mishi kallo, sossai ya had'u a hoton sanye yake da three pieces suit dark blue da ya matukar fito da haskenshi, hoton tana ga ya jima don red lips ne dashi a cikin hoton se kuma kanshi a aske cikin askin low-cut gashin ya fara fita amma be cika kan ba................

Yana murmushi ne farin hakwaranshi sun fito reras se daga tsakiya wushiryanshi ya nuna sossai haka dimple dinshi ya lotsa kuma a d'an d'osane yake akan irin kujera marar baya me juyawan nan, a zuciyanta tace 'masha Allah he's so handsome kai more than handsome ma and at the picture he looks so young, adoring, charming, and sexy at the-same time' kusa da kunnenta taji muryanshi yana cewa cikin sanyi "ya dai en mata? Irin wannan kallo haka" zaro ido tayi tana juyowa murmushi ya sakar mata don ba karamin dariya ta bashi ba ganin yadda ta kwalalo ido kaman ze fad'o, kan ya wuceta yana barinta da tsananin kunya da kamshin turarukanshi.................

Tana nan tsaye kaman statue taji su little sun rungumeta suna ihu maida idonta kansu tayi tana murmushi tace "oyoyo Ina kuka shige ne?" A tare suka ce "wurin wasan yara and shopping" nabeela tace "mun sha wani abu mai daad'i Adda khairi ashe shine ice cream inji paapi" nabeel yace "paapi ya sayamana five five pairs of English wears kin gansu" little tace "cutie look at my new teddy bear" nabeela tace "and mine too" nabeel yace "look here Adda khairi my new aeroplane zan d'aukeki a ciki phewwwwwwwww to makkah" murmushi sossai takeyi ta rasa maganan wa zata amsa se kawai ta duka tana dudduba abinda suka sawo tana murmushi d'ago idon da zatayi ya fad'a cikin nashi yana jingine da bakin kitchen hannunshi rike da table water na faro, shima su yake kallo da murmushi a fuskanshi don sossai suka burgeshi dama yaran sunyi enlightening mood dinshi ganin sun had'a ido yasa ya d'aga mata gira d'aya asking what the look for, da sauri ta kauda kai tana murmushi.................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

'Yar mutan Adamawa

Page➡️6️⃣3️⃣▶️6️⃣4️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Bata kara kallon inda yake ba ta ja su d'akinta suna ci gaba mata da surutu, harhad'a komai nasu takeyi cikin sauri don kar magrib ya musu a waje bayan ta gama suka fito zuwa parlorn ba kowa hakan yasa ta ja su zuwa d'akin momma sallama sukayi mata ta kira driver akan khairi na fitowa ya kaisu gida, bayan sun fito ta shiga d'akin su Amrah ta musu sallama haka ma nuriyyah.................

Suna fita bayan sun shiga mota little ta sa kuka da mamaki khairi ke kallonta kan ta bud'e ta fito ta duka a kusa da ita tace "little pretty me yasa kike kuka haka?" Tana tura baki tace "I want to go with yhu plzz" khairi tace "sorry pretty ki zauna a gida kinji, ai gobe ma zan zo" tana kallonsu nabeela da suma sukayi raurau da ido tace "but ai bada su zaki zo ba" ba lallashin da khairi bata yiwa little ba amma tace ita kam se ta bi su.................

Tunda suka fara yana tsaye jikin windown parlornshi yana kallonsu yana murmushi da be san dalili ba, ganin taki hakura ne yasa ya had'e rai tare da fitowa ya tsaya a bakin kofa ya ce "little" juyawa tayi tana kallonshi kan ta fara tafiya zuwa wurinshi hannunta ya kama ba tare da yacewa khairi komai ba ya juya suka shige part d'inshi, ajiyar zuciya ta sauke kan ta shiga mota suka wuce.....................

Suna isa gida ana kiran magrib, hakan yasa sukayi alwala kawai kan suka shige d'aki sbd hadarin da ya had'e sama ga kuma sauro, bayan sunyi sallahn magrib dada tace "khairi Maman hamdiyya na nemanki tace dan Allah In kin dawo In ce ki shiga" mikewa khairi tayi tana tunanin ko lafiya? Ba tare da ta tsaya karatun bayan magrib ba tace "bari inje inji menene dada" da Toh dada ta amsa ta kan ta fice...................

Da sallama ta shiga gidan Maman hamdeeya dake tattare tattare tana murmushi tace "ke wallahi khairi kirkinki yayi yawa tun yaushe rabon da ki shigo gidan nan?" Khairi tace "afuwan Maman hamdeeya wallahi abubuwa ne suka had'e min gashi ba lokaci ba gashi na shigo ba" Maman hamdeeya tace "dama ke kullum akan bada hakuri kike daga kinyi laifi" murmushi kawai tayi a lokacin Maman hamdeeya ta gama tattare abunda ya sawwa ka tayi mata iso zuwa d'akinta..................

Bayan sun zauna ta matsa ta kama hannunta tace "Alfarma muke roko a wurinki khairi, Dan Allah kiyi hakuri ki amince da bukatarmu na auren baban hamdeeya" da sauri khairi ta zame hannunta tana mata wani kallo na baki da lafiya kan tace "Maman hamdeeya??? Wani irin magana ne wannan anya kuwa kina cikin hankalinki?" Maman hamdeeya na murmushi tace "Lafiya ta kalau khairi kawai de ina son hakan ne don haka ya bukata sannan ni wallahi er uwa na d'aukeki ki amince da auren nan yadda zamu cigaba da rayuwa tare cikin kwanciyar hankali" khairi ta had'e rai kan tace "bana sonshi" Maman hamdeeya ta waro ido tana cewa "ba kunya khairi a gabana kike cewa baki son mijina?"....................

Khairi tace "Au Ashe da kunya, shi be ji kunyar sanar dake yana so na ba? Abarma wannan maganan plz ni na samu wadda nake so yake sona aurenmu kawai nake jira" bata jira amsan Maman hamdeeya ba ta mike ta fito tana kiranta amma ko waiwayowa batayi ba ta tafi bayan ta koma gida ta d'an ta'ba karatu kad'an se kuma aka kira isha mikewa sukayi suka gabatar kan khairi ta saka musu abinci suka ci....................

Bayan sun gama su nabeel sun kwanta khairi tace "Dada Ina da muhimmiyar magana dake" Dada tace "Ina jinki khairi" khairi tace "Dada........ na samu wadda nake so ne, and kuma yace ba maganar 'bata lokaci yana so ayi aure cikin lokaci kankani" Dada kallon setin da muryan khairi ke fitowa baki sake tayi a hankali tace "aure? Khairi kin san kuwa me kike cewa?" Khairi tace "na sani momma, yana sona haka mahaifiyarshi na sona, haka en uwanshi kinga ba dalilin kin yin auren, In fa kin amince kenan, amma kan amincewarki Ina so in baki labarin waennan ahali inda zaki yanke hukunci ko In shiga cikinsu ko kar na shiga" Shiru d'akin ya d'auka se muryan khairi da ke fita cikin kuka da tausayawa don In itane kam Allah ta tuba baza ta iya jurewa ba, da kullum tana cikin kuka sbd ba karya Allah ya jarabce su...................

Dada ma seda tayi hawaye, tana mamakin wani irin juriya da hakuri ne ga wannan mata, tabbas momma da ahalinta sunga jarrabawa, a hankali tace "yana sonki khairi?" Khairi cikin hawaye don se yanzu labarin ya gama game ta tace "Eh dada" dada ta kuma cewa "kina sonshi?" Khairi ta kuma cewa "sossai dada" ta furta idonta a runtse................

Tana ji dada tace "Toh shikenan khairi Allah ya tabbatar da alkhairi, amma kin fad'a musu wacece ke?" Khairi ta kuma cewa "Eh" dada tace "toh Allah ya zaba mana abinda yafi alkhairi" Khairi tace "Ameen" kwanciya sukayi don dare yayi kowa da tunanin da yakeyi a ranshi..................

Washegari tayi duk house chores d'inta kan ta fito dada na mata adu'ar sa'a se kuma fad'an kare mutuncinta, ta rasa dalilin tashinta cikin farin ciki yau, bayan ta isa direct kitchen ta nufa ta fara aikinta cikin tsanaki tanayi tana er wakanta da fillanci har ta gama ta shirya akan dining tana sauka daga wurin taci karo da su miemie da saukowarsu kenan gaisawa sukayi cikin fara'a Amrah na tambayarta Ina su nabeel tace sun tafi makaranta................

Amrah tace "wai kin karyane?" "Eh wallahi na karya a gida, bari In karasa aikin nan In zo" wanke wanke tayi ta fito ta samu momma ma ta fito har kasa ta duka ta gaisheta amsawa tayi cikin fara'a tana tambayarta dada, tace dada na nan lafiya, momma tace "dama akwai maganan da nake so muyi yanzu ki shirya ku fita da Amrah Musharraf ze kaiku makarantansu yayi miki registern waec da neco, sbd kinga ba halin ci gaba da karatu mussamanma In anyi auren, zaki dinga zuwa lesson da Amrah na two weeks kan fara paper"....................

Cikin farin ciki khairi tace "na gode momma" momma tayi murmushi kawai ta kuma cewa "In kun dawo Ina so in d'aukeki zuwa gidanku Dan magana da dada" Khairi tace "Toh" tare da mikewa ta shige d'aki, tana shiga ta daka tsalle cikin murna dama tana da burin ci gaba da karatu a rayuwanta gashi burinta na shirin cika ba abinda zata d'auka don hijabinta na jikinta dama ba

cirewa take ba, fitowa tayi cikin zumud'i................

Se kuma ta d'an dakata hanganshi da tayi akan dining yana karyawa hannunshi rike da waya yana dannawa at same time, a tsakiyar parlorn kuma Nuriyyah ce da miemie da Amrah, nuriyyah sanye da kayan bautar kasanta se after dress baki da ta d'aura a saman, kanta sanye da half hijab fari, Miemie ce tsaye a gabanta tana mata magiyar dan Allah ta bata aron phone d'inta ta yi kira don wayanta ya fad'a ruwa ta gayawa Hamma musharraf kuma be ce komai ba...............

Bata sa ran samu nan kusa ba don Amrah ma tun kan ya koma wanchan karo wayanta ya Sami matsala shikam little ce ma ta yar, kuma ta fad'a mishi amma har yanzu fin wata be saya mata ba, harara nuriyyah ta sakar mata kan tace "bazan bayar ba fa gwara kin nemi me baki, kinga ma tafiyata" juyawa tayi ta fice tana mata gwalo, Amrah dake zaune tana ta aikin dariya ta watsawa harara kan ta wuce sama fuuu kaman guguwa...............

Musharraf dake zaune dining khairi ta kallah wadda yayi tamkar be san da wanzuwarsu a parlorn ba se ma harkan gabanshi da yake ran nan had'e kaman be ta'ba dariya ba, wurin Amrah ta nufa tare da zama a kasa Amrah tace "TBest ban son gulma fah da fulako me na zama a kasa bayan ga kujeru" harara ta bankawa Amrah akan lips d'inta tace "Ina ruwanki" waro ido Amrah tayi tace "eyeeeh ashe, na manta gwaninta be kar'bi kare ba" Shiru khairi tayi mata idonta na kan tv da ake maimaicin tarkon kauna a arewa 24......................

Itama Amrahn shi take kallo jikinta sanye da uniform tunda ta shiga ss3 zuwa makarantan se a hankali balle kuma da suka fara lessons kawai se kusan past 10 take tafiya ta dawo 2, mikewa musharraf yayi yana gyara rigan half jumpha na getzner dake jikinshi maroon color, kallon Rolex watch silver dake d'aure a tsintsiyar hannunshi dake cike da gargasa yayi kan ya zaro tissue ya goge bakinshi tare da saukowa daga kan dining d'in kallon Amrah yayi da kai ya mata alamar su tafi..................

Ta'ba khairi Amrah tayi tace "ke tashi mu tafi kinga yau na lura Hamma musharraf A dinne a goshinshi baki ga da yadda ya gaida momma ba kaman ana mishi dole" mikewa khairi tayi tana murmushi fitowa sukayi se suka ganshi a cikin motan momma da ya kasance light brown Mercedes benz, da sauri Amrah ta shige baya, tare da rufe kofan, d'an tsayawa khairi tayi kan ta bud'e bayan itama da niyyar shiga...................

Taji husky masculine voice d'inshi na cewa "uban waye driver d'inku?" Sake kofan tayi tare da bud'e gaba ta shiga, lumshe ido yayi yana mamakin kamshin turarenta a zuciyarshi yace "Ashe ba irin kazaman masu aikin nan bace" da oud 24hours take anfani oil d'inshi wadda be wuce 250 ba, duk kamshin jikinshi da kamshin motan be hana shi shakan sassayanyar kamshinta ba, ta'be baki yayi tare da yin reverse da motan ya fice...................

Gombe high school suka je, Amrah tayi hanyarta tana cewa khairi "se na dawo" tana kallon musharraf Tace "Hamma thanks" be ko kalle ta ba balle ta sa ran amsawa, bayanshi khairi tabi

ganin ya fara tafiya tana tafiya tana kallon en matan school din yadda suke ta kallonshi kaman sun ga sabon hallitta musamman en ss3 masu zanawa...............

Ta'be baki tayi tana sake tsiririyar tsaki ganin yadda en matan gabansu suka wani chanza tafiya daga d'aura ido akanshi, a haka suka karasa office na principal a take yayi mata registration na waec da neco ya kuma biya kudin uniform kala biyu, a take aka je da ita aka bata yana nan zaune ta fito ya mike yana ma principal d'in godiya cikin harshen turanci kan ya fice tabi bayanshi.................

Seda sukayi nisa da tafiya kan tayi gyaran murya a hankali tace "Ina kwana?" Seda ta fidda ran amsawanshi kan taji yace "se yanzu kika ganni?" Waro ido tayi kan ta ta'be baki tace "Dada tace In maka godiya taga kayan da ka sayowa su nabeel mun gode" seda ya nisa tukun don kanshi yace "ce miki akayi don ke nayi" Shiru tayi bata kara magana ba har taga sun shiga wani wuri da alamun filin saida wayoyine ba tare da ya mata magana ba ya fice...................

Kusan 30mins tukun taga ya shigo nan ma be ce mata komai ba yaja motar suka wuce gida yana parking taga ya ajiye mata wani Leda karami da bata san me a ciki ba kallonshi tayi da alamun tambaya tace "wa zan kai wa?" Seda ya ajiye kafanshi d'aya a waje hannunshi rike da irin ledan hannunta guda biyu yace "ki yar" kan yayi wucewarshi zuwa site d'inshi................,,

Baki ta turo gaba kan ta fito ta rufe kofan tare da nufan cikin gida a d'akinta ta yada zango tana bud'e ledan hannunta kwalin waya ta gani na Samsung galaxy A10s budewa tayi tana juya wayan a hannunta golden color ce da ya matukar yi mata kyau dannawa tayi se taga ya kawo haske harda mtn sim a ciki, murmushi tayi a fili tace "thank yhu" tare da d'auko chargarn ta makala ta kuma ajiye kwalin da earphone a kan gado.................

Fita tayi ta haura saman momma tare da knocking kofan daga ciki momma ta amsa tana cewa "har kun dawo khairi?" Khairi tace "Eh mun dawo ya min komai na gode, har uniform kala biyu aka bani" murmushi momma tayi tana mikewa hannunta d'auke da sky blue gyale tana yafawa kan orange and sky blue Swiss lace dake jikinta, tana cewa "muje khairi samun mu dawo da wuri ki d'aura girki" Khairi tace "Toh" tare da yin gaba.................

Musharraf ne ya fito don kaisu momma ta kame a baya khairi ta shiga gaba, ba me magana a motan se khairi dake mishi kwatance har suka isa kofan gidansu, ita da momma ce suka sauka yayinda shi kam ya gyara zamanshi a kan kujerar driver yayi kasa dashi tare da kwanciya, da sallama suka shiga dada dake zaune tsakar gida ta amsa tana cewa "Khairi me ya dawo dake da wuri haka?" Khairi tace "Da momma muke" dada tace "lale maraba sannu da zuwa" sossai momma ke kallon dada tana tunanin inda ta ta'ba ganin fuskan amma ta kasa tunawa hakan yasa ta zauna a kan sallayan da khairi ta shimfid'a mata...................

Zama tayi sossai kan suka gaisa da dada Bayan sun gaisa take sanar da ita kudurinta na son su koma gidanta da zama na har abada zata kula dasu kaman en uwan da suka fito ciki d'aya, tashi d'aya dada taki, ba yadda momma batayi da dada ba amma taki, khairi dake zaune gefe

bata ji daadin hakan ba sam, momma ce tace "ki cewa musharraf ya shigo ya gaisheta se mu wuce ko" Khairi ta mike ta fice mintuna biyu ta shigo kan ya shigo daga baya taugunawa yayi har kasa ya gaida ta, ta amsa da fara'a tana mishi godiya don daga jin sunan ta san shine ya sayawa su nabeel kaya kuma shine de surkinta mijin khairi, momma ce ta sanar dashi dada taki su koma gidanshi, cikin hankali da natsuwa ya fara tausar dada inda ya tabbatar mata ya san abinda take tsoro wato wulakanci da tozarci inda yayi alkawarin In har yana da rai duk duniya ba wadda ze wulakantata yana gani be d'au mataki ba, sannan ya tabbatar mata daga kan mommanshi, kannenshi da ershi ba me wani bakin halin da baza ta iya zama dashi ba sossai ya nuna mata illan zamansu anan su kad'ai In khairi tayi aure, jiki a matukar sanyaye dada ta amsa da ta amince zasu zauna tare da su da zuciya d'aya In shaa Allahu.............................

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION (home of peace, charity, honor and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

Page➡️6️⃣5️⃣▶️6️⃣6️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Da tsantsar mamaki da sha'awa take kallonshi a gaskiya ta yabawa kaifin basira da fasahan magananshi sbd sarai ta san Dada In ta kafe a kan abu to fah me tankwarata se Allah haka Abbansu ma duk zuciyar fulani ne dasu, maganan momma ne ya katse mata tunani da kallon da take mishi tace "Khairi tashi muje gobe in Allah ya kaimu se kuyi parking" mikewa khairi tayi dada na ta godiya suka fice...............

Kad'an kad'an momma da musharraf suka dinga hira har suka isa gida, kitchen ta fad'a ta fara girki don ganin rana yayi se kawai tayi musu faten shuwaka da gyad'a ta had'a musu soya beans juice da yaji flavors kala kala a dining ta shirya tana gamawa Amrah da little na shigowa da gudu little taje ta rungumeta sama ta d'aga ta tana dariya tace "pretty sannu da dawowa ya school?" Little ta fara zuba mata surutu akan abinda ya faru a makaranta tana jin labarin little tana magana da Amrah har suka haura inda take gayawa Amrah gobe itama zata fara zuwa school da su in shaa Allah.................

Ihu Amrah ta fara tana tsalle tace "yeeeeeeeh amma naji daadi sossai Allah ya kaimu akwai rocking kafin waec" hararanta khairi tayi tace "ba wani rocking  karatu kawai zanyi malama" waro ido Amrah tayi tare da fasa shiga d'akinsu ta nufo na little da sama nan zasu shiga da sauri khairi ta shiga tana danna kofa tace "ki wuce kije kiyi wanka duk tsamin zufa kike" Amrah na tsaye rike da kwankwaso tace "Lallai ma yarinyar nan amma kin sha ni dayawa ki guji had'uwarmu" murmushi khairi da little sukayi suna tafawa kaman sun yi wani abin kirki, bayi ta shiga da little tayi mata wanka................

A pink towel d'inta ta nad'ota suna fitowa taga mutum zaune bakin gadon little har tsorata tayi kan ta gama gane wanene ajiyar zuciya ta sauke tana ajiye little da niyyan ficewa, cikin husky voice d'inshi yace "zo ki ciro mata kaya" dawowa tayi ta nufi wardrobe d'inta shi kuma ya

kamata zuwa kan dressing mirror d'inta ya shafa mata mai tare da murza powder fari ya shafa mata a fuska tare da sa mata lip balm sunayi tana mishi hira murmushi kawai yake sakewa jefi jefi..............

A sace take kallonsu ta bar ma fitar da kayan se kallonsu da take yi kaman tana kallon tv ba karamin burgeta sukayi ba a natse ya taje mata kanta dake tsefe ya shafa mata mai tare da sa mata ruffle ta cikin madubin ya kalli khairi da tun d'azu ya lura da yadda take kallonsu yace "madam muna jira" a kunyace ta fiddo kayan ta miko musu tare da juyawa ta fice cikin sassarfa.................

Ta'be baki yayi yana girgiza kai, tare da sakawa little kayan, kasa suka sauko inda suka samu duk ahalin gidan a kan dining har khairi da momma ta sata zaman dole, sun ma yi nisa a cin abincinsu yayinda khairi ke juya chokalin kawai bayan sun zauna khairi ta mike tayi serving d'insu ta turawa kowa gabanshi a natse ya fara cin abincin ba tare da ya tankawa kowa ba.................

Bayan sun gama momma tayi musu bayanin dawowar su khairi da family d'inta gidan duk cikinsu ba wadda ya nuna 'bacin rai ko a fuska sema farin ciki da suka dinga yi, anan kuma ta sanar musu batun zuwa dukku da zasuyi sbd maganan auren Nuriyyah da Marwan se kuma na Khairi da musharraf tana so su zama danginta kawayenta kuma madogaranta hakan yasa zasu tafi gabad'ayansu tunda kwana biyu kawai zasuyi.................

Tsokana ne fal ran Amrah da Miemie amma musharraf na zaune ba halin yi, se de da ido suke gulman, a bazata musharraf yace "ke tashi kije ki d'auko mun irin ledan d'azu a parlor na" kowaccensu kallonshi take sbd basu san da waccce yakeyi ba, khairi da ta fahimci da ita yakeyi yasa ta mike ta fice yayinda Miemie da Amrah suka kalli juna tare da fashewa da dariya kasa kasa harara ya zabga musu tare da mikewa ya koma parlor ya zauna duk suma parlorn suka koma...................

Mintuna be wuce biyar ba khairi ta dawo da ledojin guda biyu a hannunta har gabanshi taje tace "gashinan" Seda ya gama shan kamshinshi kan ya kar'ba, juyawa tayi d'aki tare da d'auko wayan da ya bata da komai ta fito ta samu su Amrah na murnan nasu murmushi kawai tayi ta nunawa momma, godiya ta tayata murmushi kawai yayi wa momma duk hankalinshi na ga waya.................

Washegari bayan khairi ta zo tayi breakfast da sauri sauri tare da shiryawa cikin uniform da yayi mugun amsanta ta fito a parlor ta tadda Amrah na breakfast zama tayi a kan dining din tana cewa "yi da wuri mu tafi Amrah Dan Allah" kallonta amrah tayi tace "wow uniform nan ya kar'be ki waiiii omoooo wallahi zaki tsone idon mutane yau kinga yadda shape d'inki ya fito? Dama haka kike shiyasa baki ta'ba rabuwa da hijabi? Wowwww amma yaya musharraf ya mo............." da sauri khairi tace "kayyah Amrah surutunki yayi yawa, In kin koshi ki tashi mu tafi plz" ta'be baki Amrah tayi tana kallonta har lokacin haka khairi ta dinga damunta har seda ta mike suka haura sukayiwa momma sallama kud'i ta bawa khairi tace inji musharraf ta sayi

books da pen da de abinda ze taimaka mata a lesson d'in duk kuma za'a samu a school din, godiya sossai tayi kan suka fice...................

A kofan parlor suka gamu dashi a tare suka gaisheshi da lafiya kawai ya amsa su, khairi ce tace "Hamma musharraf na gode sossai" kallonta yayi na fisha tukun ya kauda kai yana nufan kujerun parlorn fita sukayi driver ya ja su suka fice Amrah na mitan itakam suyi suyi waec ta huta da fitan sassafen nan ita bacci baya isanta ga Miemie da Adda nuri ko tashi basu da niyyan yi itace kawai take fama da wani uniform............

Murmushi kawai Khairi keyi har suka isa, sossai makarantan ya mata daad'i yadda sukayi karatu kaman revision ko wanne malami 40mins ba su suka fito ba se 1:20 sukayi sallah tare da break na 20mins duk wadda ya kalli khairi In har ya san Amrah se ya tambayeta wacece wannnan beautiful girl dinnan se Tace sisternta ce, a haka suka koma suka kuma yin wani 40mins d'in kan aka tashe su, suna fitowa sukayi site d'in nursery school suka d'auki little sukayi gate a nan suka samu driver na jiransu suka shige suka dawo gida...................

Tana sa kai parlorn ta kalli nabeel da nabeela na wasa da mamaki take kallonsu su kuwa da gudu suka rungume Amrah suna gaisheta ko kula khairin ma basuyi ba suka ja little suka fara wasa, d'akin da yake a matsayin nata ta shiga da baki bud'e take kallon d'akin wani babban 6/7 tagani me shegen kyau dukda ba Italian bane na Nigeria ne amma ya had'u se wardrobe dinshi me murfi hud'u daga gefe brown color ne set d'in bed d'in, haka labulayen d'akin ma an sauya zuwa brown, an shimfid'a rug carpet a tsakiyan d'akin shima brown, se wani black mini bed da karamin wardrobe a  gefenshi shima black me murfi d'aya, d'akin se kamshin sabbin furnitures da turaren wuta yakeyi.................

Dada ta hango zaune a bakin gadon rike da sandarta da sauri khairi ta karasa kusa da ita tana kama hannunta tace "Dada yaushe kuka zo? Yaushe kuma aka chanza d'akin nan haka? Na su waye?" Murmushi dada tayi tace "khaih ummulkhairi duk wannan tambayoyi haka wanne zan amsa miki?" Khairi tace "duka" dada tace "kiyi ma surkuwarki godiya khairi, kinga d'akin nan duk da ba gani nakeyi ba amma na san ko yayi kyau, zaki ga wani karamin gado shine na nabeel, nabeela kuma a d'akin zarah zata zauna, sannan wai ya cire su a makarantan gomnati a inda zaki rubuta papper anan zasu ci gaba, ummulkhairi bamu da bakin godiya ga bayin Allahn nan se adu'a  kawai zamu cigaba da binsu dashi Allah ya biyamusu bukatunsu na alkhairi" ................

Kuka kawai khairi ta saka tare da rungume dada tana cewa "Alhamdulillah! Alhamdulillah!! Alhamdulillah!!! Ina d'an uwa? Ina Abba, ku zo kuga burinku, Abba burinka na ganin munyi karatu ko da sau d'aya ne a private school ya cika Abba, burinka na ganin mun zauna a muhalli me kyau ya cika amma baka duniyar, d'an uwa kana Ina da kake tunanin rayuwarmu baza ta sake yin kyau ba sema yafi baya ta'bar'barewa ga haske na shigowa cikinta amma kayi nisa ya Allah in yana raye ya Allah ka bayyana mana shi, In ko ya mutu Allah kaji kanshi ka gafarta mish, ya Allah..........." kuka ne ya sarke ta, haka dada ma sossai sukayi kuka har muryan khairi na dishewa kanta kuma ya fara matsanancin ciwo, fuskanta yayi jajazir abinka da farin

mutum......................

Dada ne ta fara share hawayenta tace "kukan ya isa haka khairi, Allah kuma ya amsa mana adu'arki don darajar Annabin rahama sallalahu alaihi wassalam" karasawa khairi tayi tana me share fuskanta wanka taje tayi tazo ta shirya cikin doguwar rigan atampha simple tasa hijabinta tare da cewa dada "bari na d'aura abincin rana dada" dada tace "Toh khairi" fita khairi tayi a parlor taga little na zaune kasan kafan babanta ta zabga tagumi cike da damuwa..................

'Dago ido tayi se kuwa ya fad'a cikin sexy/oily eyes d'inshi dake lumshewa yake budewa kaman me jin bacci, kauda manyan idanunta da yayi ja sbd kukan da tayi tayi, Chan gefen parlorn ta hangi nabeel da nabeela suna wasa sake kallon little dake zaune shiru tayi, har zata wuce se kuma taga rashin dacewar hakan cikin dashewar murya tace "little pretty wa ya ta'bamin ke" Da sauri ta mike ta nufo ta hawaye na cika idonta tace "cutie ba ke bane na shiga kimin wanka naga kina ta kuka, wa ya ta'baki paapi ya rama miki?" Hawaye ne ya sake cika idon khairi d'ago kai tayi ta saci kallonshi bata hankara ba taji hawaye sun fara zuba kaman panpo da sauri ta wuce kitchen tana rufe fuskanta da hijabi.................

Runtse ido yayi yana jin zuciyarshi na motsawar da ya rasa dalilinshi, me ya sameta? Kukan me takeyi? Duk ya rasa dalili shafa goshinshi yayi tare da fesar da iskan bakinshi waje, tare da sauke idonshi kan little da hawaye ya cika idonta pim, suna had'a ido kuwa suka sauko mikewa yayi ya kama hannunta suka nufi kitchen d'in, a gaban kitchen island suka ganta ta dukar da kanta tana shesheka.................

Kaman daga sama taji ance "dukkan tsanani yana tare da sauki matukar bawa ya dogara da Allah, kin san de matsalarki In kanki ya fara ciwo, ga prettynki nan ki san yadda zakiyi da ita tunda kin san dole damuwar ki ya dameta" be kara ba be rage ba ya juya ya fice se be tafi ba ya jinginu da kofar kitchen d'in, ita kuwa da sauri ta share hawayenta tana dukawa gaban little tace "sorry pretty na sa ki damuwa ko? Na tuna paapi na ne nima" little tace "ya rasu ne koh kaman yadda mamana ta rasu?" Kai khairi ta gyad'a................

Little tace "momma tace in mutum ya rasu adu'a kawai zaka na mishi shi ze nuna kana sonshi ba kuka ba, ki dinga mishi adu'a kinji?" Kai khairi ta kuma gyad'awa cikin rawar tace "Toh pretty" tafiya ya fara a hankali yana tuna duk wani labari nata da ta bayar yana had'ashi da nashi rayuwar tabbas itama taga jarabawar rayuwa, rayuwa ya bi dasu duk su biyun bisa wani IGIYA me wuyar tsallakewa for the very first time bayan kaddaran rayuwanshi ya fara tausayawa wata mace bayan mommanshi, a fili yace "Toh Ina d'an uwanta ya shige a garinnan?" Taune lips d'inshi yayi yana tuna first promise d'inshi da ta karya...................

A chan kuwa kitchen cikin lokaci kankani khairi ta sake sbd little se kuma tunanin maganganun da ya fad'a mata na dawo mata, ya damu ne da kukanta? me yasa ya za'bi ya mata magana bayan haushin auren chushen da ake shirin mata dashi? Don ta tabbatar baya so, da irin tunanukan ta gama girki, da kyar dada ta yadda ta fito suka had'u gabad'ayansu suka ci................

A washegari bayan sun dawo daga school suka wuce dukku inda gabad'aya family za'a had'u a chan, drivern musharraf ya ja Nuriyyah, dada, nabeel da nabeela a motar miemie, yayinda drivern momma yaja momma, Miemie da Amrah a motar nuriyyah, inda musharraf ya ja motan momma daga shi se khairi da little dake baya, duk wannan tsarin momma ne wadda be so ba amma ba yadda ya iya, zamansu kusa na mugun takura mishi wadda dauriya ce kawai irin nashi, shiru motar ya d'auka se wakan Lost In yhu na Praiz ft sammy ke tashi a hankali shima yana bi kasa kasa.........................

🤧🤧🤧🤒🤭🤐

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

*these page is dedicated to Amina Lawal shahud(Maman heedaya) bani da bakin gode miki sede inyi adu'a Allah ya bar zumunci. Thanks for your support and care Allah yaji kan hamdeeya yasa me ceto ce. Ameen*

Page➡️6️⃣7️⃣▶️6️⃣8️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

"Nothing I wouldn't do you're me one for two....... it's lonely the bend or crack but it's a whole world with i with you.... yes you underneath the blue light.. silver memories on the skyline... stars will be there to guid us through.. my hands will be there to lead you through.... if they put a brick wall in between us i'am ah be with you down to the pillar....

God's love is real it will free us... got me winning meet me at the temple.. if they put a brick wall in between us i am ah be with you to the pillar God love it real it will free us got me winning meet me at the temple....... nothing can change the way that I feel I will die for yhu.... nothing can change the way that I feel I am lost in you...." abinda yake ta maimaitawa kenan Haka kawai yake tsintan kanshi da kallonta minti minti, tayi luf fuskanta fayau Ba komai d'aya daga cikin dogon rigan da hajiya ruqayya ta bata ta saka, purple me stones sossai white da gyalenshi fuskanta fes Ba komai tana jingine da jikin kujera fuskanta na facing d'inshi.

Sam ba bacci takeyi ba kaman yadda ya zata, sede gabad'aya jikinta a mace yake da farko tunanin yadda en uwanshi zasu kar'beta take sbd taga akwai masu sonshi dayawa a dangi be auresu ba se ya buge da auren 'yar aiki? Me ilimin secondary, ta tabbatar gabad'ayansu sun gama degree ko suna dab da gamawa, sannan kakkaninshi tana tsoron da wani fuska zasu iya

ganinsu har su kar'bi aurenta ba tare da 'yan uwan mahaifinta ko guda ba, tunanuka ne fal ranta amma yana fara bin wakar nan da bakinshi se taji wani irin sanyi na shigarta, tunanukan na guduwa se wani rawa da zuciyarta keyi sam ya kasa zama wuri d'aya, kai harta tsikar jikinta tashi take..

A zahiri ta san ba da ita yakeyi ba wtkl wakanshi kawai yake amma ta kasa hana gangan jikinta da zuciyarta shiga nishad'i da amincewa da ita yakeyi, bata so sam ya san idonta biyu don kar ya dena hakan yasa ta ci gaba da rufe idon har suka isa, a hankali ta bud'e ido ta d'aura akan wani katon iron blue gate da suke danna horn a gabanshi zaka rantse gidan ba'a kauye bane a cikin garin Abuja ne tsabar kyau da had'uwarshi, bata tashi sanin kyaun gidan ba seda suka shiga ciki a cikin wani tabkeken parking lot sukayi parking inda motoci kala kala a ciki sun kai goma sha biyu..

Hakan ya tabbatar mata da duk en garin Gombe sun iso don ba karamin mota a ciki Parker nasu sukayi tana mamakin bud'in da Allah yayiwa wannan family In bata manta ba Amrah ta fad'a mata su maryam kowaccensu motan kanta take hawa daga yarinya ta shiga jami'a ake mallaka mata mota, girgiza kai tayi a zuciyarya tace 'arziki na inda yake' sauka tayi ganin duk su momma sun sauka, baya ta bud'e ta d'auki little a kafad'anta tare da d'aukan madaidaicin jakan da momma ta bata tasa abubuwan anfaninta, na su nabeel daban su biyu haka na dada, ta juya da niyyan tafiya kenan taji an rike hannun jakan har hanun wadda ya riken na gogan nata, wani irin electrical shock da taji yasa tayi saurin sakewa tana kallon shi..

Ba tare da ya kalli idonta ba yace "Ai abubuwan se su miki yawa" be jira cewarta ba ya zaro trolley d'inshi ya ajiye daga jikin motan tare da bin Bayanta cikin tafiyarshi na Izza da tsantsar kasaita se kace d'an gidan saraki, manyan parts guda uku ne a gidan cikin ko wani part akwai 2rooms and parlor, 2rooms and parlor akallah hud'u hud'u banda part na tsakiyan da ya kasance babban parlor d'aya se rooms guda goma cikin wani dogon corridor, na hagun shine na Abubakar da matarshi shuwa wato diddi da bappa, se na daman na Adamu da Aslamiyya wato mamaji da dadda, na hagun suka nufa momma ce tayi knocking tsadaddan door d'in part d'in bayan haurawansu babban varender me steps biyar ko wani angle.

Mintuna biyu aka bud'e Afreen ce tsaye sanye da doguwar rigan kanti ba ko d'an kwali a kanta ihu tayi tana cewa "oyoyo momma" a take sauran kannenta da yaran uncle taheer suka taho suka rungumeta suna ihu, murmushi kawai take musu ganin oyoyo ya ki karewa yasa musharraf dake tsaye gefen momma ya daka musu tsawa "wani irin rashin hankali ne wannan bakwa ganin da baki muke!!!" Da sauri suka saketa suna juyawa parlorn su khairi suka rufa mata baya, nuriyyah dake rike da sandar dada ta taimaka mata har ciki ta ajiye ta kan kujera.

Kallon khairi musharraf yayi da ta fara nishi sbd little da ta mata nauyi gashi tana shirin zama kasa, hakan yasa ya ajiye jakan hannunshi tare da karasawa wurinta beyi mata magana ba yasa hannu ya zame little wadda yasa khairi razana ya had'u mata da irin shock d'in d'azu don fatan wuyanta da hannunshi ya ta'ba saura kad'an ta fad'a mishi amma se tayi saurin dafa broad chest d'inshi, da mugun sauri kuma ta zame hannunta tana zamewa kasa kunya kaman

ta nitse ganin momma na kallonsu.

Lumshe ido yayi ya bud'e yana juyawa da sauri zuwa wani door dake facing d'in na shigowa. Wata kyakyawar farar mata ce da khairi bata lura da ita bama seda tayi gyaran murya tana cewa "sannunku da zuwa lale maraba, ga kishiyoyina" kallonta khairi tayi tana jinjina kyaunta dukda tsufan da ya nuna sossai a fuskanta hakan be hana tsantsar kyaunta fitowa ba.

Ga fara'a da ya cika mata fuska da tsantsar annuri alamu sun nuna tana jin daad'in wanzuwarta da 'ya'yanta a irin wannan lokaci, kasa momma ta zame tana gaida ta amsawa tayi tana tambayarta ya hanya, da Lafiya klau momma ta amsa, su Miemie ma gaisheta sukayi Amrah da tun shigowarsu take lafe jikin matan tace "kawas ya kk" hararanta tayi tana ture ta daga jikinta tace "matsa min anan marar kunya, ki kwace min miji sannan ki zo kina ce min wani kawas aka gayamiki ana kawa da Kishiya ne?" Duk parlorn dariya suka saka.

Khairi da ke murmushi sossai ta kalleta tare da cewa "Ina yini, mun sameku lafiya?" Amsawa tayi da fara'a tana mamakin Ina fatima ta samo kyawawa haka, a mutunce suka gaisa da dada inda momma tayi musu iso zuwa part dinta wato inda musharraf ya shiga, d'akinta ta isar da dada inda ta had'a su Amrah da khairi dakinsun me adaje ne irin na boarding kanana na katako guda 6 anan suka samu musharraf kishingid'e a jikin gadon da ya kwantar da little..

Duk jikinshi a mace hakan yasa da ya kwantar da ita ma ya kasa fita zuwa part d'insu na maza yana mamakin wani irin sabon abu ne yake ji ajikinshi game da yarinyar nan musamman In jikinsu ya had'u hakan na bashi mamaki se kace be ta'ba sanin wata mace ba, shigowarsu ne ya sa shi mikewa ganinsu duk da trolley d'insu kowaccensu ta nufi bakin gadon da ta saba sauka bayan ta mishi sannu, ba wacce ya amsawa se idonshi da ya bud'e yana kallonsu d'aya bayan d'aya gado Amrah ta nuna mata taje gefen gadon ta ajiye jakanta tare da satan kallonshi se kuma suka had'a ido..

Da sauri ta kawar da kanta mikewa yayi ya fice tare da ja musu kofa, ajiyar zuciya ta sauke tare da yaye gyalenta ta zauna bakin gadon a lokaci d'aya duk su ukun suka fashe da dariya hakan yasa khairi kallonsu da mamaki nuri tace "Kai irin wannan soyyayya" Miemie na dariya ta fara wakar "soyayya ruwan zuma kasha kaba masoyi" Amrah kam murmushi kawai takeyi tana tuna gulmar da sukayi tayi tun isowarsu gidan, kunya ne sossai ya kama khairi kaman ta nitse da sauri ta tashi ta fad'a kofan da ta gani tak a d'akin da alamun bayan gida ne, da karfi Amrah tace "gama ki fito don ni ban miki nawa ba" suka sa dariya a tare.

Bayan fitanshi straight mota ya nufa yaja trolleynshi zuwa part d'insu yana bud'e kofan yaga su marwan da sufyan zaune a parlorn suna hira bayan sallaman da ya musu yace "hi dudes" a tare suka ce "hello kun iso kenan" Da Eh kawai musharraf ya amsa tare da wucewa corridor din da d'akunansu suke d'aki na biyu by left ya shiga wadda shine nashi, a gyare yake tsab komai na d'akin fari akwatinshi ya ajiye tare da budewa ya fiddo towel, Sam be jin daadin yadda yake shashare kakarshi da take matukar sonshi, fitowanshi daga part din mommanshi ne ya Samu gaisheta sama sama amsawa tayi tana Jan shi da wasa kaman kullum amma ya kasa amsa

mata, kaman yadda ya saba dafe kai yayi yana tuna yadda suke a da, itama kenan da ta haifi mahaifiyarshi Ina ga dadda..............

Da wannan tunanin yayi wanka yana fitowa ana knocking da yes ya amsa aka turo kofan aka shigo Zainab ce, hakan yasa ya had'e rai tam kaman hadari cikin yanga tace "barka da zuwa Hamma musharraf" cikin husky masculine voice dinshi yace "ajiye abinda aka aikoki and leave, In kuma baza ki ajiye ba yhu can leave with it and ko pim kika kara cewa you will definitely regret it" sanin halinshi yasa ta ajiye ta fice sum sum sum..............

Tsaki ya buga tare da fesa turarukanshi ya janyo wayanshi yana zama bakin gado ba don ya d'auki leave a office na two weeks ba ba abinda ze hana shi tafiya Abuja, shi ya tsani irin wannan had'uwa gida d'ayan sbd waennan mayun en matan, haka ya ci gaba da zama a d'akin yayi sallahn la'asar dukda ya san se mamaji yayi fad'a sbd a irin wannan lokaci duk mazan familyn tare suke had'uwa a shiga masallacin dake kofan gidanshi gwanin sha'awa.

A chan cikin gida kuma bayan an aiko musu abinci daga babban kitchen don a irin wannan lokaci ba wacce akeyiwa girki a part d'inta sede ayi a babban kitchen a kuma shirya shi a babban dining area dake part d'in mamaji a chan ake lunch and dinner breakfast ne kad'ai ake turawa part part, momma ta shiga ta sanar musu ga abinci an kawo maza su fito su d'iba..

Fita sukayi suna ta dariyan kunyan khairi don da kyar ta fito daga toilet d'in kuma ta kasa sakewa har lokacin haka suka ci gaba da tsokananta tun bata sakewa har ta sake suka ci abinci tana mamakin Ina su nabeel, Bayan sun gama ne su Amrah suka jaata babban parlor anan ta same su suna ta wasa da sauran yaran gidan sa'anninsu, fita sukayi zuwa part d'in mamaji...........

A nan khairi taga ashe part d'in duk iri d'aya ne shima kofofi biyar ne dashi hud'u 2rooms da parlor se d'ayan kofan kitchen ne me girma dukda be kai na bayan gidan inda ake girkin buki ba, d'aya part d'in Uncle Ahmad da iyalanshi d'ayan kuma uncle nasir da nashi iyalan se d'ayan na momma da Abbansu musharraf amma tunda abun nan ya faru bata sake sauka a part din ba, se en matan da suke sauka ciki anan suka shantake dukda khairi bata magana se murmushi, dukda ta takura amma sam ko a fuska bata nuna ba ganin yadda yawancin en matan ke yi mata kallon uku saura kwata..............

Bayan magrib suka koma part din diddi achan sukayi sallahn magrib da isha Anty Rabi'ah ce ta had'a kan yaran part d'in gabad'aya zuwa parlorn dadda ran nan a had'e ta nuna khairi da su nabeel tace "ba'a gayyata da ku ba" tare da nunawa su Amrah hanya haka suka fita ba don sun so ba, khairi de bata ce komai ba sema gyara zama da tayi tana tunanin yanayin momma bayan dawowarsu daga d'aya part d'in ranta kaman a 'bace amma sbd bata da hurumin tambayanta yasa tayi shiru gashi Anty Rabi'ah ma fuskan nan kaman bata ta'ba dariya ba.

Ita bata ma damu da wai ance ba'a gayyacesu ba dama chan su ba familyn gidan bane so akan me zata damu wurin dada suka shiga sukayi zaune a kasa a gabanta suna shan hira daga

parlor akayi sallama ta mike ta fito me aiki ce da tire na abinci tace "inji momma" kar'ba tayi tare da godiya a d'akin suka ci sukayi kat suka ci gaba da hiransu har su nabeel sukayi bacci d'aukansu tayi d'aya bayan d'aya ta kaisu d'akin da aka saukesu tare da shimfide su su biyu gado d'aya, don ta lura kowacce da gadonta har little da suka fita suka bari tana bacci basu dawo sun Tarar da ita ba.

Ta kuma tabbatar spare gado guda biyu ne sbd kar ta takura musu yasa ta kwantar dasu a gado d'aya ita kuma zata kwanta a d'aya, komawa d'akin momma tayi tayi sallama da dada akan se da safe, tana fitowa parlor taga message ya shigo wayanta "sameni mana a parlorn diddi" dukda bata san numbern ba haka taje ta d'auko hijab ta fito ita duk a zatonta musharraf ne ze sata wani aikin, tana fitowa ta kalli sufyan gayen da yayi ta kallonta a asibiti cikin had'e rai tace "gani" murmushi yayi yace "haba beautiful had'e rai sam be kar'bi fuskanki ba, In kina dariya haske kike kaman tauraro plz kar ki hana ni anfana da wannan haske" ja baya tayi tana kokarin wucewa don ganin ya Matso dab da ita bata ankara ba taji ya riko hannunta a lokaci d'aya aka turo kofa d'ayan idon da zatayi se cikin na musharraf.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo

‘Yar mutan Admawa

Page➡️6️⃣9️⃣▶️7️⃣0️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Wani irin sharp idea ne ya fad’o mata dukda ta san it is not right a matsayinta na er talaka amma tana tsoron zargi ya shigo tsakaninta da musharraf In har ta aureshi kai ko bata auri musharraf ba ta san mutuncinta na ‘ya mace, cikin abinda be wuce kyaftawar ido ba ta d’aukeshi da wani wawan mari tare da fisge hannunta had’e gabas da yamma tayi, shi kuwa abun ya zo mishi out of blue, dayake bayanshi ne ke facing kofa se be ga musharraf ba, ganin tana kokarin wucewa bayan ta mareshi, shi da kowacce mace ke burin samu sbd kyaunshi irin na shuwa arab da kuma kud’in da yake dashi, don ma ya nuna yana sonta ba wai asalin so yake mata ba kawai de akwai abinda ya gani jikinta ne da ya kula ba wadda ya lura da hakan.................

Duk Laifin kanshi yake gani na kulata da yayi be danneta ta karfi ya biyawa kanshi bukata ba, cikin zafin nama ya damko hannunta tare da murd’e shi a bayanta wani d’an kara ta sake tana juyowa taji saukar hannunshi a fuskanta wadda har seda ta dena gani da ji na wucin gadi, d’ago hannun yayi da niyyar sake kaimata mari yaji an damke hannun, a zafafe ya juyo yana kallon

musharraf dake tafasa har fuskanshi yayi ja tsabar ‘bacin rai, shi karan kanshi ya manta last da yaji irin wannan ciwo da ‘bacin ran da yakeji daga kirjinshi har kan harshenshi.

Mamaki ne ya kama sufyan a saninshi musharraf baya shiga abinda be shafeshi ba amma gashi akan wannan banzar yarinyar ya hango abinda be ta’ba hangowa ba a idon musharraf tsantsar kishi da ‘bacin rai har rufe mishi ido yake, naushin da musharraf ya sake mishi a fuska ne ya dawo dashi daga tunaninshi zaro ido yayi yana kokarin fusge d’ayan hannunshi dake cikin na musharraf amma ya kasa................

Naushinshi musharraf ya dinga yi da hannunshi na dama shi kuma yana tarewa da na hagu ganin In be yi wani yunkuri ba fa musharraf ze iya illatashi hakan ya sa shi saka iya karfinshi ya fusge hannun tare da kaiwa musharraf naushi a fuska shima, Ai ko nan ran ‘yan maza ya ‘baci suka fara kaiwa juna naushi sede ba’a d’au lokaci ba sufyan ya galabaita abinka da wadda yayi zaman prison har ya zama kwaro a cikinsu............

Khairi kuwa ganin musharraf ze iya yin kisa yasa ta Kwasa a guje zuwa part d’in dadda ta san ko ta hanashi ba hanuwa ze yi ba balle ma baza ta iya ba sbd tsoronshi da ya shigeta lokaci d’aya, da karfi ta tura kofan parlorn tana cewa “momma ki zo, momma!! Hamma musharraf” tana magana tana nuna waje da sauri suka mike momma tayi saurin bin bayanta ganin ta kuma kwasa a guje, suna turo parlorn suka sake salati a tare...........

Da sauri momma tayi kanshi tana kamashi a lokaci d’aya tana kiran sunanshi, cikin ‘bacin rai ya ture hannun momma yana shirin komawa sufyan da be dena zaginshi ba, uncle Ahmad ne ya tsinka mishi mari yana cewa “baka da hankali ne da girman ku  musharraf? Me ya had’aku haka??” A zuciye musharraf ke kallon uncle Ahmad yana ta aikin sauke numfashi yayinda hannunshi ke a dunkule, wato ubanshi son kai zeyi me yasa be mari d’anshi ba se shi..........

Sufyan ne dake zaune kasa jini na d’iga a fuskanshi yace cikin alamun kuka a muryanshi “Abba wai akan wanchan banzar yar.......” “dakata!! Wallahi ka kiyaye ni na rantse da girman zatin Allah ka sake cewa abinda zuciyata ke SO banza zan kakkaryaka a gidan nan, In kuma ka Musa ka gwada inga uban da ya tsayamaka”...........

Shiru sufyan yayi don wallahi ya tabbatar tunda ya furta har yayi rantsuwa ba abinda ze hanashi karyashi hakan ya sashi iya bakinshi, wani irin shock khairi ta shiga jin yace ‘Abinda zuciyarshi ke so’ me yake nufi? Itace abinda zuciyarshin ke so? Ya Allah, Allah sa ba mafarki take ba, Momma ce ta daka mishi Tsawa “baka da hankali ne wai musharraf? ‘Dan uwanka kake maganan zaka karya a gabanmu? Kuma kace kaga wadda ze tsaya mai? To ni zan tsaya mai nice uban da zan tsaya mai In ka fasa karyashi” ta kalli sufyan tare da cewa “me ya had’aku?”..............

“Momma akan fah mai aikinkun nan ce” kallon khairi duk en parlorn sukayi har momma, ganin irin kallon da suke mata yasa ta maida kanta kasa tana shirin fara hawaye, ta shiga uku yanzu ta had’a en uwa kenan? Da ta sani da tun farko bata mareshi ba, wani farin dattijo me cikar

kamala ne ya bayyana a parlorn yana cewa “Wa ya ta’ba maza ne?” Ganin fuskan sufyan yasa yace “subhanallah me ya faru?”.

“Ummulkhairi ya mara tare da murd’e mata hannu bayan bata mishi komai ba ko aka gayamishi en aikin ba mutane bane? Wallahi In baka fita hanyar matar da zan aura ba, kuma yarinyar da nake so da kauna ba zaka yi dana sanin kasancewana d’an uwanka” baki sake en parlorn ke kallon khairi se kuma su kalli musharraf banda en gidansu da kuma Anty Rabi’ah da diddi, a take kananan maganganu ya fara tashi cikin en matan parlorn harda masu zuciyar barin parlorn...........

Anty Rabi’ah ce tace “yanzu fisabilillahi musharraf akan wanchar talakan ka daki d’an uwanka? Shi yaro karami ne ko be san me yakeyi ba? Ai In kaga ya mareta to tabbas da abinda ta mishi watakila ma seducing d’inshi tazo yi kaman yadda ta yi muku asiri kai da kafatanin gidanku, Allah ya kamata” runtse ido musharraf yayi yana ji kaman shi Anty Rabi’ah ke zagi wani irin zafi ne ke chakar zuciyarshi inaga ita? Idonshi ya d’aura akanta tana tsaye kanta kasa hawaye na zuba a fuskanta.............

Mamaji ne yace “uhm uhm Rabi’ah uhm uhm wani irin seducing? Kina da hankali kuwa In ma seduction d’in ne se a cikin gidansu” bappa ne ya kalli momma da wani irin haushin rabiah ke cinta yace “ban gane me take nufi ba Fatima wani irin asiri tayi muku?” Mamaji ne yace “a bar maganan nan se gobe yanzu dare yayi” kallon sufyan da musharraf yayi yace “In har na isa daku ban son ko kallon banza ya kara shiga tsakaninku har zuwa In yanke hukunci” juyawa yayi ya fice  dadda ta bi bayanshi, bappa ma ya shige part d’insu diddi ta bishi, Marwan ma ya kama sufyan suka wuce, nan fah maganganu suka fara tashi dukda basa son d’aga murya sbd musharraf dake tsaye sun tabbatar ranshi a ‘bace yake yau dinnan...............

ganinta a duke tana kuka yasa wani irin tausayinta da ya ninka na da kamashi, wurinta ya nufa tare da kamo kafad’anta ta mike hannunta ya kama tare da janta zuwa part din momma, Amrah da Miemie ne sukayi ihu tare da tafawa nuriyyah kam se murmushi, momma ma murmushi tayi farin cikin furucin musharraf na d’azu na kamata dukda haushin Rabi’ah da ta Shaka yau, sannan bata wani damu sossai da dukan da musharraf yayiwa sufyan ba ko kuma tace fad’a don shima musharraf d’in kasan idonshi ya tara jini............

A take en parlorn suka watse ko wacce da abinda take cewa mussaman hajjiya Zulai mahaifiyar sufyan harda habaici ta jefawa momma, girgiza kai kawai momma tayi tana shigewa part d’inta su nuriyyah suka rufa mata baya, suna shiga d’akin ya kaita har gaban gadonta tare da zaunar da ita ya duka a gabanta yana rike hannunta yace “me ya had’aku?” A dabarance ta zame hannunta tare da goge fuskanta, tana kokarin hana kuka kwace mata tace “wallahi sako na gani a wayana” ta d’auko wayan ta mika mishi amsa yayi ya karanta ta d’aura da, “duk zatona kai ne hakan yasa na fita, Ina fita ya fara yi min wasu maganganun da ban gane kai ba, shine nace mishi zan tafi ina kokarin wucewa ne ya riko hannuna kai kuma se ka sh.....”.

Kuka ta sakar mishi tana tuna abinda Anty Rabi’ah tace ‘wai seducing sufyan’ Allah ya sawwaka

mata and har zuciyarta bata ji daad'in kalman asirin da ta ambace su dashi ba, ya Allah wannan wani irin masifa ne kuma ke shirin kunnu musu? Anya amincewa auren nan da tayi ba wani igiya take kuma kokarin kullawa wanchan rayuwan da suke gudu ba? Lallausar tafin hannunshi da taji akan kumatunta ne ya sata dawowa tunaninta..............

A hankali yake share mata tears d'in idonshi na kan yatsun hannun sufyan da ya fito tas akan fuskanta taune lip d'inshi na kasa yayi yana sauke ajiyar zuciya, a hankali kuma ya maida idonshi cikin nata wani irin abu da be ta'ba gani ba a rayuwanshi ya gani suna fita daga cikin idanunta zuwa nashi itama cikin kwayar idonshi take kallo cikin d'aukewar tunani, a chan cikin wata duniya ta tsinci kanta me cike da furanni na soyayya😁😁 (toh fah anzo wajen).

Da sauri ta d'auke kanta tuna wadda ke tsugune a gabanta wani irin kunya na rufeta murmushi ya saki, a fili yace "kunya na kar'banki khairrr" ya wani ja khairr d'in In a unique way da ya sata murmusawa tana boye fuskanta, mikewa yayi yace "se da safe habeebty" Tace "Allah tashemu lafiya hamma, plz ka shafa ointment a kasan idon kan nan kan ka kwanta" Kai ya gyad'a mata yana ficewa daga d'akin a parlor ya ga su nuriyyah har little suna kallon tv, be kula kowaccensu ba ya fice, da gudu Amrah da Miemie suka shiga d'akin, har suna buge juna.

Turus sukayi suna kallon gadon khairin don kwance take taja borgo zuwa kirjinta tare da juya musu baya, Amrah tace "Eyyeh soyayya manya, ke Miemie kina ganin wani irin love? Wato har ya rarrashi abunshi tayi bacci ba tare da d'igon damuwa ba" Miemie tace "hmmm kede bari, amma wannan soyayyar na san ko lokacin maman little iyaka. Hamma musharraf da ke nuna baya so shine har da tada jijiyoyin wuya 'ummulkhairi matar da zan aura kuma yarinyar da nake so da kauna'" wani irin dariya Amrah ta sa ganin yadda Miemie ke magana wai tana koikoyon Hamma musharraf.............

Khairi na jinsu har suka gama tsiyansu Miemie ta shige bayi yayinda Amrah ta koma parlor, sossai take dariyar shirmen su Amrah tana kuma tuna kalmomin Hamma musharraf na d'azu, wani irin sanyin daad'i taji yana shigarta In kuwa ta tuna yadda ya ambaci sunanta se taji duk tsikar jikinta sun tashi, dukda zuciyarta na cike da damuwa amma d'an farin cikin da ta samu daga gareshi ya danne damuwar ya hanashi tasiri akanta har bacci ya kwasheta a haka............

Washegari

Da misalin karfe goma aka had'u a babban parlorn mamaji, kallon momma mamaji yayi yace "Da me kike tafe kika ce?" Momma tace "yarinyar da musharraf yake so kuma ze aura ita da familyn ta, mamaji inda hali so nake su zama cikin ahalinmu su kasance en uwa a garemu don basu da kowa" dadda tace "haba fatima don basu da kowa se su zama d'aya daga cikin ahalinmu? Inaaa baki san yadda duniya ta koma ba ko? Sannan a gaskiya bazamu aurawa musharraf ita ba, ba tare da en uwan mahaifinta ko danginta bayan uwa ba" Hajiya zulai tace "Ai ko da danginta baza mu yarda da auren ba don alamu sun nuna raba kan en uwa zatayi tun kafin ta shigo tunda gashi har ta had'a musharraf da sufyan fad'a"..............

D'aya bayan d'aya mamaji ke kallonsu ba tare da yace komai ba, har seda sukayi shiru tukun ya murmusa yace "ummulkhairi kaman haka naji musharraf ya anbata jiya ko?" Kai khairi ta gyad'a yace "Ina son sanin su waye ku? Da wani mugun nufi kuka shigo cikinmu?" Idon musharraf dake lumshe ya bud'e yana kallonta itama kallonshi tayi ya gyad'a mata kai cike da bata kwarin gwiwa.

A hankali ta fara bada labarin rayuwanta tun daga kan na iyayenta har ita duk parlorn anyi tsit ana jinta da kallonta har ta gama da kuka sossai a muryanta ta d'aura da "bamu da wani mugun nufi akanku sbd ban ta'ba zama da d'an uwana musulmi da zuciya fiye da d'aya ba, na tabbatar haka sauran ahalina" ta kai karshen maganan da sa bayan hannunta ta goge hawayenta, dada ma hawaye take, hajiya Aisha da mijinta uncle Nasir, diddi, salima, farida, fatima, da bappa se da sukayi hawaye tsabar tausayi da wannan ahali suka basu, Sauran en parlorn duk ta'be baki sukayi suna juya keya alamun basu yarda da labarin ba, mamaji kam cikin jimami yake kallon khairi da tunanuka fal ranshi, wadda shi kad'ai yasan abinda yake kullawa.............

Bayan shirun mintuna fiye da biyar yace "a haka kike so musharraf ya aureta?" Ya karasa yana kallon momma, Musharraf dake jin zafin kukan da khairi takeyi yayi saurin kallon mamaji, yana shirin magana yaji momma tace "Eh" cikin bada umarni yace "ban yarda ya aureta ba!!!!" ..

#vote
#share
#comment

‘Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

Page➡️7️⃣1️⃣▶️7️⃣2️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

"What!!!" Exclaimed musharraf with a mouth open agape, kallonshi momma tayi da alamun gargad'i hakan yasa yaja bakinshi ya yi shiru, cikin sanyin murya momma tace "ko sbd me yasa mamaji?" Mamaji yace "duk cikin zuriyarmu bamu da wata ko wani me aljannu baza mu fara daga kanta ya zamana gaado ba, don mu yarda da aurensu ba danginta Ba komai bane sbd ko iyayenku a haka muka auro su".

Kai dadda ta dukar cike da kunya shap ta manta da su a ya aka auresu take kokarin aibanta wasu sbd rashin dangi, murmushi momma tayi me cike da manufa tace "Ai ko inde haka ne marwan baze iya auren Nuriyyah ba" da mamaki suke kallonta bappa ne ya iya cewa "ko sabi

da me fatima?" Kai tsaye tace "sbd itama aljannun ne da ita, am sorry to say mamaji masu aljannun ba mutane bane? Ko akwai wadda ya ke d'aurawa bawa bayan Allah? Tuni ne kawai nake muku na san kun sani Allah ne ke qadarta wa bawa abu a yadda yaso, na boye muku nuriyyah na da aljannu ne sbd kwanciyar hankalinku.

Sbd In har kuka san dalilin samuwarsu a jikinta zaku ci gaba da d'aurawa kanku laifin komai ne" dadda tace "innalillahi wainna ilaihi rajiun, menene dalilin samuwarsun?" Musharraf yace "duk wani banzan aiki na ubanmu wadda ya shafi sihiri zuwa wurin boka don cin za'be, sun za'be ta ne sbd yafi sonta akan duk mu 'ya'yanshi a rayuwanshi" salati en parlorn suka d'auka dadda kam fashewa da kuka tayi tana Allah wadai da d'a irin mahmoud.

Mamaji ma shi kad'ai ya san halin da yake ciki, Bappa ne ya dinga musu nasiha cikin ilimi da fasaha ya nuna musu kar su karaya suce zasu tsine mai su ci gaba da adu'a shine ze taimaka mishi koda Hakki ze tashi kamashi ze zo mishi da sauki, da kyar mamaji ya nitsar da kanshi tare da mai da kwallan idonshi yace "tun yaushe take fama da su? Kun yi magani?" Momma tace "tun shekara d'aya da rabi da ya wuce, Musharraf ya taka rawan gani sossai akan maganninta I cannot ask the better for them bcos he's the best brother ever, ya tsaya sossai duk inda yaji wani malami ya kaita har abin yayi sauki ba kaman da da zatayi sati bata san waye kanta ba hallitarta duk se ya sauya ni kad'ai na san irin tashin hankalin da na shiga mah......" kuka ne ya kwacewa momma tuna irin wahalan da nuriyyah ta sha a tsakankanin kan tayi sauki.

Duk parlorn nuriyyah suka zuba wa ido cike da tausayawa hakan ya sata fashewa da kuka, duk yadda mamaji yayi kokarin maida hawayen idonshi hakan ya gagara se da suka zubo, bappa ma seda yayi hawaye yana godiya ga Allah da kaddarar ta, yana mata adu'ar samun aljannah sbd hakan don tayi matukar kokari wurin cinye jarrabawarta.

Musharraf da idonshi ke kan khairi ganin zata fara wani kukan yasa ya had'e rai ya zaro mata ido tare da girgiza kai, baki ta turo tana dukar da kanta a lokaci d'aya tana kokarin mayar da hawayen tunda yace baya so su zubo, maganan mamaji ne ya katse musu tunanukan da suka fad'a da kuma kukan da wasu daga cikin en matan ke yi, "Alhamdulillah Alhamdulillah, Allah na gode maka da ka bani irin wannan d'a, Fatima, Musharraf, nuriyyah bani da bakin baku hakuri amma Ina neman wa kaina da matata yafiyar ku, sbd duk mu ne silar komai da bamu nemi Abubakar da maganan son had'a fatima da mahmoud ba da hakan be faru ba don Allah Ku yafe mana kar hakkinku ya hana mu kwanciyar kabari".

Momma tace "Wallahi ni ban rike ku ba mamaji na d'auke shi matsayin kaddara, da IGIYAR RAYUWA na baya kulle da na mahmoud da hakan bata faru ba, so ni kam na yafe muku" Nuriyyah tace "mamaji baka min komai ba ni kam wallahi na yafewa kowa amma banda Abba" Shiru duk sukayi suna jiran jin ta bakin musharraf amma gayen nan yayi shiru abinshi kaman be san dashi ake yi ba, kuma yaki kallon bangaren momma.

Khairi ce ta kalleshi for the first time tayi niyyar bashi hakuri da sa baki a cikin harkanshi ita bata ga laifin su mamaji ba bare yace baze yafe musu ba, d'ago kai tayi se taga yana kallon ta hakan

yasa ta shagwa'be fuska tare da karkatar da kai alamun plz yayi magana, juya idanunshi yayi kan ya fiddo maroon lips d'inshi da ke cikin bakinshi yana tsotsa yace "Allah ya yafemana" murmushi tayi tare da kauda kanta daga kanshi se taga idon momma akansu a kunyace ta dukar da kanta.

Tabbas khairi alkhairice a garemu taci sunanta, taga alamun musharraf ya fad'a cikin kogin Sonta da kaunarta wadda hakan ze sa ta iya tankwarashi duk da a hakan ma ta san ze iya yiwuwa wani lokacin kuma baze yi ba, maganan mamaji ne ya katseta inda yace "shikenan In Allah ya kaimu goben se a yi komai na auren a saka date da komai" murmushi momma ta sake tana kallon musharraf amma shikam kaman be san me ake cewa ba don fuskan nan ba ko d'igon fara'a a de sake yake amma ba fara'a sam be nuna ba, Hajjiya Rabi'ah ce tace "haba mamaji ya za'ayi gida be koshi ba a bawa waje, yara en matan nan ba wacce bata son musharraf amma ya dinga zuba musu wulakanci kaman ba gobe yanzu kuma se ya d'auko wata bare marar tushe yace ita ze aura? Er aiki ce fah, Ina had'i biri......"

"Dakata Rabi'ah ban cike da halin iskanci, tun jiya da na miki maganan abinda nake son yi kike share ni da jefa min habaici, wai me ke damunki ne? Ina da er uwa amma bazamu ta'ba muyi maganan sirrin junanmu ba sbd baki so, na barki kuma yanzu ince ga wacce nake so kuma d'ana yake so a matsayin suruka kice bata yi miki ba? Ke zaki zauna mishi da ita? Ko ko auren dole za'ayiwa musharraf d'in?" A hasale momma ta karasa maganan don bata manta bakaken maganganun da ta dinga fad'a mata jiya ba kawai don ta zauna da ita da diddi ta fad'a musu manufarta akan su khairi da dada.

Diddi ce tace "baki da hankali Rabi'ah, ban kuma san yaushe zakiyi hankali ba, yau da hannunmu khairi ta fara sauka ko fatima da musharraf basu yarda ba se na aura mishi ita, ki natsu ki san me kikeyi er uwarkice" cike da haushi take hararan khairi Bappa ma fad'a ya mata, ganin kusan 12 yasa mamaji cewa "maganan karshe kan watsewarmu musharraf da girmanku me ya had'aka fad'a da d'an uwanka yanzu fisabilillahi kalli fuskanshi" kallon fisha yayiwa mamaji kan ya maida kanshi kan khairi yace "fad'a musu abinda ya faru" bayani tayi musu inda anan take babanshi Alhj Ahmad da tunda yayi opening prayer be sake cewa komai ba, ya rufeshi da fad'a sossai ya mishi fad'a Alhj Nasir ma yayi mishi nasiha tare da had'ewa da yaran gabad'aya ya musu nasiha sossai kuma ya tabbatarwa en matan Afreen, Zainab, sulaimi, maryam akan tare za'a had'a aurensu da khairi da nuriyyah don haka ko wacce ta turo maneminta auren baze wuce 2months ba.

Daga nan bayan an rufe taro da adu'a aka wuce dining, khairi ta kama dada suka nufi hanyar fita har sun kai kofa musharraf yace "ke!! Ina zaki bayan kina ga abinci za'a ci?" Juyowa tayi ta kalleshi ya nuna mata dining da kanshi juyowa sukayi suka dawo kowa yayi serving kanshi Ina khairi ta sa ma dada ta tura mata rice and stew ta sa mata tare da d'aura mata hannu akan chokalin, "saka min abinda zaki ci" kallonshi tayi kaman ba da ita yake magana ba kama ma bashi yayi ba.

Tuwon semo miyan kubewa ta saka mishi ta tura mishi tare da d'iba itama ta fara ci a hankali su

maryam dake dab da ita ne suke ta mita da masifa ta ya za'a had'a aurensu da wannan shashashar talakar tsab take jinsu amma ko a fuska bata wani ci na kirki ba ta mike ganin dada ma ta ajiye chokalin yasa ta kamata suka mike, diddi dake chan gefen bappa tace "bade har kun koshi ba me kuka ci?" Da fulatanci tayi maganan kan khairi ta bada amsa hajiya zulai tace "hmmm ba'a saba bane babu a house" hajiya rabiah tace "a toh Kin san irin haka in anci dayawa ciki rud'ewa yake" momma ce ta buga table d'in tare da cewa "enough, kar ku kaini makura wallahi akan cin mutuncin khairi da iyayenta ba abinda bazan iya yi ba" Hamma Ahmad ne yace "ku kiyaye don kun min farin sani be game ni naci mutuncin kowaccenku ba, zulaikha na sake ganin kin zagi yarinyar nan se ranki yayi mugun 'baci try me and see" shiru sukayi girgiza kai mamaji yayi yana kallon su dada da har sun fice ma, murmushi musharraf yayi haka yake so mommanshi ta koma baya son sanyinta nan, ya kuma lura akan khairi se ta fi haka masifancewa murmushi yayi yana me ci gaba da cin abincinshi.

Washegari da safe mazan suka zauna a take akayi komai har sadaki mazan suka bayar amma de ba'a fad'i kud'ad'en ba, na marwan da musharraf akayi na sauran se next week, kwana biyun da khairi tayi taga wulakanci kala kala cikin familyn masu sonta kad'an ne, daga familyn su musharraf se diddi, mamaji, bappa se su uncle Ahmad da nasir, se surkuwar nuriyyah matar uncle nasir hajiya Aisha amma banda yaranta marwan ne ma ba ruwanshi sufyan kuwa In har sun had'u kallon banza ke had'asu dadda ta biyewa hud'ubar su Anty Rabi'ah da Anty zulai ta tsani khairi ba gaira ba dalili.

Hakan yasa khairi ta auri zaman d'aki karfi da yaji taki fita ko dining ne, sbd hakurinta kad'an ne ba don ma halin rayuwa ba a cikinsu akwai wacce zata mata kallon banza ta Kyale, Toh yanzu ma tana kin fitan ne sbd maganin kar ayi kar a fara, kuma tunda akayi meeting na safe a washegarin da suka zo bata kara sa musharraf a idonta ba. A yau zasu koma ta gama had'a kayanta gabad'aya haka ta had'a nasu nabeel ta kai har motan da suka zo dashi don yadda aka zo haka za'a koma.

Da d'ad'aya da d'add'aya duk kowa ya wuce saura su kad'ai ita da shi don little ma su momma ta bi, tana zaune tana jiranshi suna hira da diddi, kamshinshi ne ya fara sanar da ita isowarshi kan bayyanar shi da sallama a bakinshi, kallon seconds sukayiwa juna kan suka d'auke kai, sanye yake cikin Ash suit ya sha polished cover shoe gashinshi da ya sha gyara se sheki yakeyi yayi kyau har ya gaji.

Ita kuma tana sanye da doguwar rigar atampha duk da ba me tsada bane amma d'an uwanta ya fidda d'inki a wurin A shape gown yayi mata da yaji pattern na kayan daga sama har wurin cikinta daga wurin kuma har kasan rigan stones ne baja baja dayake atamphar sea blue ce me adon orange a jiki se ta yafa orange gyale na wani dogon riganta cikin wadda hajiya ruqayyah ta bata, orange flat shoe ta zurawa kafanta wadda na Adda nuri ce ta bata kyauta yau da safennan da Amrah take had'a mata kayan da zata saka suka rasa takalmi.

Fuskanta fayau ba d'igon komai a hakan kuma tayi matukar kyau kaman a sace, dayake kanta ba d'ankwali se gyalen ya zauna sossai akan silk long hair d'inta irin na fulani da baya kitsuwa

ta dad'i, sallama sukayi da diddi inda suna fitowa suka gamu da su bappa sallama suka musu suma suna ci musu albarka suka wuce ta so su shiga suyi sallama da dadda amma tana tsoro tunda shi uban gayyan ko part d'in be kalla ba.

Suna shiga ya tada motar tana ji sadda yayi adu'ar shiga abin hawa da na matafiya hakan ya tuna mata itama tayi, a natse yake driving motan shiru sbd ba abinda ke kunne hankalinta gabad'aya ta mayar kan hanya tana kallon wurare wani irin murd'awa da taji maranta yayi ya sata ambaton "innalillahi wainna ilaihi rajiun" Da sauri ya kalleta da kyar ya iya cewa "are yhu okey?" Kai ta gyad'a mishi yace "words" tace "am fyn" dafe maran tayi tana tunanin rabonta da period tun last three months.

Dama haka yake mata inda aka cewa Abbanta aljannunta ne ke mata wasa da period don idan watanta yayi se tayi ta ciwon mara amma ba jini, tun suna neman magani har suka hakura, idan ta shafe wata biyu wata uku batayi ba baze ce ga randa ze zo ba amma In ya tashi zuwa kaman zata mutu da ciwon mara har karin ruwa ake mata, ajiyar zuciya ta sauke tana adu'ar Allah ya sa kar ya fi karfinta kan su isa, jujjuya kai ta fara hannunta na kan maranta gani take kaman ba driving yake yi ba gashi tana mugun rushing Allah yasa kar ta 'bata mishi mota kan su isa.

Duk abinda takeyi hankalinshi na kanta kuma ya fahimci abunda ke damunta amma se yayi kaman be san halin da take ciki ba, se ma cd da ya saka a motar ya kunna wakar All ever need na Austine mahone, ya fara bi a hankali, kasa jurewa tayi yasa ta fara mutsu mutsu hawaye suka fara tsere a saman fuskanta jujjuya kai kawai take tana ambaton sunan Allah, dukda cikin zuciyarshi cike yake fal da tausayinta hakan be sa ya tsaya ba don be san me ze mata ba.

Wayanshi ya d'auka ganin sun shiga wani d'an kauye ya kira Amrah don ya san itama tana wannan ciwon dukda be kai ko kwatan na khairi ba kuma yana ganin maganin da take sha amma be san sunan ba, tana d'auka ya tambaye ta maganin Mp fad'a mishi tayi ba tare da wani dogon nazari ba, fita yayi ya tambaya ko akwai chemist anan aka nuna mishi wani d'an karamin chemist zuwa yayi ya saya tare da dawowa motan da sauri fuskanshi na nuna damuwar halin da take ciki.

Ruwa ya d'auka tare da 'ballan maganin ya bata da kyar ta sha se aikin kuka takeyi ajiyar zuciya ya sauke tare da tada motar da hannu d'aya d'ayan hannun kuma ya sashi cikin nata yana matsawa a hankali, dayake ya kwantar mata da kujeran hakan ya sata kwanciya ta dukunkune tana cin azabar period pain, a haka bacci ya kwashe ta tana jin yadda d'umin hanunshi ke ratsa ta suna shigowa cikin gombe tana farkawa a gigice tare kokarin bud'e kofa.

Da sauri ya parker motar be gama tsayawa ba ta sauka da gudu ta fara sheka amai goran ruwa ya d'auka tare da fitowa yana mai tsananin tausaya mata yazo ya riketa, ko gyale babu a kanta tsabar ciwo bata san ta jefar da shi ba, tana gama aman taji kafanta ya kasa tsayuwa sbd ciwon da sukeyi wani murd'awan da cikin ya kumayi yasa ta saki kara tare da sulalewa ta zube a jikinshi a sume, a matukar rud'e yake jijjigata ganin da gaske suman tayi yasashi d'aukarta da gudu zuwa mota zagayawa yayi ya shige tare da figan motan zuwa FMC duk wadda ya ganshi

kaucewa yake sbd irin gudun da yakeyi cikin lokaci kalilan ya isa inda ya fita da sauri ya d'auketa yana kiran doctor da gudu nurses suka kawo gadon marasa lafiya suka kar'beta tare da yin emergency da ita, dafe kanshi yayi yana kiran sunan Allah.

*kuyi hakuri na rashin jina Kwana biyu idon ne ya karye 👓 ba kuma zan iya typing ba shi ba amma an gyara zaku ci gaba da jina In shaa Allahu kaman ko yaushe*

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

Page➡️7️⃣3️⃣▶️7️⃣4️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Bayan kaman 40mins doctor Aslam ya fito yana kallon musharraf yace "muje office" bin bayanshi yayi zuwa office Bayan sun zauna yace "dr ya jikin nata?" Doctor yace "da sauki sossai tana bacci ne yanzu haka sbd alluran da aka mata" fuskanshi d'auke da damuwa yace "Amma ba yadda za'ayi a cire mata ciwon gabd'aya Ina nufin next month kar tayi haka?" Doctor Aslam yace "itama sistern ka ce?" Dayake Doctor Aslam ya san en gidansu gabad'aya, har ze ce er aiki se yaji bakinshi ya furta "wacce zan aura" murmushi dr yayi yace "masha Allah, ciwon mara na period pain ba yadda zamu yi mu cire mata se Allahn da ya d'aura mata, wasu matan suna denawa ne daga sun yi aure wasu kuma har se sun haihu yayinda wasu har abada, yanzu de mun yi mata allurai da karin ruwa ruwan na karewa zaku iya tafiya".

Godiya ya mishi tare da amsan bill d'insu ya fita, biya yaje yayi kan ya dawo d'akin da aka kwantar da ita dayake sun san en gidansu duk amenity ake kwantar da su hakan yasa da ya shigo da khairi aka bata amenity, a bakin gadon ya zauna yana kallon fuskanta da yayi fayau farinta ya fito sossai, baccinta ya mishi kyau sossai musamman yadda idonta da bakinta suka bud'e kad'an.

Seda ya gama morewa kallonta kan ya koma kan plastic chair ya kishingid'a tare da lumshe ido yana tuna randa sonta ya fara shiga zuciyarshi, be san taya ba be san ta Ina ba kuma be san yadda akayi ya karya alkawarin da ya d'aukarwa kanshi da zuciyarshi na hana kanshi son wata 'ya mace ba, be san yadda akayi ta kakkarya duk wani takunkumi da kwado da ya sawa zuciyarshi ba ta shige tun kallo na biyu da ya mata randa ake shirin keta mata haddi, tunda kuwa yaji labarinta se yaji kaman ninka mishi sonta da tausayinta akayi yana sonta har be san iya adadi ba.

Yana kaunarta da dukkan zuciyarshi, babban abinda yasa ta zama numfashinshi kuwa shine

yadda take matukar son little tabbas duk wadda yaso little to shi ya so, abinda ya hanashi bud'e mata zuciyarshi kuwa shine yana tsoron sabarwa kanshi rayuwa da ita da soyayyar ta tazo tayi betraying d'inshi irin surrayah, gwara ya zauna be d'and'ani zakin soyayyarta ba zuwa ya gama yarda da ita 💯% karan wayanshi ne ya dawo da shi daga duniyar tunanin da ya fad'a a hankali ya bud'e idonshi dake lumshe ya sauke su akanta gashinta me taushin bala'i dake baje akan pillown da take don tuni tayi wulli da ribbon da kuma gyalen ta, wayanshi ya zaro daga pocket d'inshi yana kallon caller id d'in ganin "first love" yasa shi d'auka tare da karawa a kunne yace "hello" momma daga 'bangarenta tace "lafiya son naga baku iso ba har yanzu" idonshi na kanta yace "yarinyar nan ce ba lafiya tana FMC" momma tace "subhanallah me ke damunta haka?" Yace "period pain, ku taho yanzu am on my way too sbd flight d'ina 1 ne and yanzu 12".

Da Toh kawai momma ta amsa tana kashe wayan, mikewa yayi ya karasa bakin gadon yasa hannu ya mayar mata da gashin goshinta dake yawo a fuskanta, cameran wayanshi ya shiga yayi mata pics sossai kan yayi pecking goshinta ya juya kenan yaji an riko hannunshi a hankali ya juyo se yaga duk cikin bacci ne sabule hannunshi yayi ya juya ya fice cikin takunshin nan me sace zuciyar mata.

A parking lot yayi parking tare da fita straight wurin su momma dake shirin fita asibiti ya tsaya da ita da Amrah ganinsu ne yasa drivern tsayar da motan tare da sauke glass, momma tace "har ka dawo?" Kai ya gyad'a mata tace "Toh Allah ya tsare ya bada sa'a, a de dinga kiyayewa zamu yi waya kan ka tashi don na san ba asibitin zaka koma ba" kwa'be fuska yayi ya ki magana se kallonta da yakeyi.

Dafe kai tayi tace "yanzu kai yaro ne musharraf, da kullum se na maka nasiha kan ka tafi? Kuma se na ga tafiyarka?" Kuma 'bata fuska yayi yana kallon driver da Amrah ganin hankalinsu baya kanshi yasa yayi mata alamun plz da lips d'inshi, fita tayi tana cewa Amrah "kira nuriyyah a waya ku tafi in ya tafi zan zo, Miemie kuma ta kula da yaran nan da dada" a waya Amrah ta kira nuri yayinda momma ta bi Bayan musharraf zuwa part d'inshi, a parlor suka zauna tayi mishi nasiha sossai kamar yadda ta sabar mishi tun farkon samun aikinshi bayan ta gama ya mike yaje ya d'auko briefcase dinshi da ya zuba muhimman abubuwanshi sharp sharp.

Be yi sallama da little ba don ya san kuka zatayi kuma gashi khairi bata gida bare ta sata yin shiru da sauri idan su Amrah ne har ya isa Abuja tana kuka, dada ya shiga ya sallama itama adu'a ta mishi ya fito gudu gudu zuwa mota inda momma da driver ke jiranshi duk yadda momma ta so mishi maganan khairi sharewa yayi ya dinga basar da maganan har suka isa Airport har ciki ta raka shi tukun sukayi sallama ta wuce asibiti.

Bayan sati biyu

Rayuwa yayiwa su khairi daad'i sossai suke samun kulawa daga wurin su momma har momma ta samu wata me aiki yanzu ba abinda khairi take se in ita ta sa kanta da kanta, karatu kawai suka dukufa dayi ita da Amrah, wanchan sati momma tayi musu sayayyar kayan sawa sossai musamman dada, da su nabeel itakam har kayan kwalliya dukda ba kwalliyan take yi ba, su

nabeel ma sun koma school d'insu duk tare suke zuwa kuma suke dawowa dukda ba koyaushe suke fita da sassafe ba.

Bata ta'ba waya da Hamma musharraf ba sede taji suna waya da en uwanshi har nabeel da nabeela suna waya su kam ma kullum a wayan little se dada ma sun ta'ba waya sau biyu, hakan kuwa sam be mata daad'i ta rasa dalili, sam kaman yau da ya kasance juma'a tana gyarawa momma d'aki taji wayan momman na ringing d'agawa tayi se taga "Son" a fuskan wayan hakan yasa ta San musharraf ne amma kuma momma bata nan ta fita ta mance wayan, share wayan tayi ya kira kusan sau hud'u kan ta d'auka ta 'bangaren shi yace cikin shagwa'ba "tun d'azu nake ta kira kinki d'auka motherrr" cikin daburcewa khairi tace "ba ita bace hamma" lumshe ido yayi yana jin wani natsuwa na shigarshi.

Yayi kewarta da muryanta sossai amma haka yake hana kanshi kiranta, a sanyaye yace "Toh wace ce?" Tura baki tayi a zuciyarta tace Lallai ma mutumin nan wato muryanta ne ze ce be sani ba a fili tace "ummulkhairi" Shiru yayi na mintuna kan yace cikin husky voice d'inshi "baki iya gaisuwa ba kenan" Da sauri tace "Ina kwana Hamma musharraf?" Yace "bazan amsan ba seda na roka?" Be jira cewarta ba yace "Ina momma?" Tace "ta fita ta manta wayanta a gida".

Shiru yayi na mintuna kan taji kit ya kashe wayan, ta'be baki tayi tare da ajiye wa ta ci gaba da gyaran d'akin bayan ta gama ta sauka zuwa d'akinsu a bakin gado ta zauna dada na garden da su nabeel da Miemie. Wayanta ta d'auko se taga text message ya shigo.

"There has never been and will never be a time when God will desert you. Place all your fears in him" ta karanta text d'in ya kai sau biyar ta rasa wa ke tura mata wannan message d'in yau na biyu kenan, last friday ma taga wani shigen wannan wadda aka rubuta "Fasten your seat beats, your life is soon landing in Happyland!".

Ta rasa wa yake turo mata wannan messages d'in ta kuma kira numbern sau biyu ba'a d'aga ba, ya akayi wannan ya san tana cikin damuwa? Duk da damuwan a da ne yanzu damuwarta d'aya, yaushe d'an uwanta ze dawo? Tana son sanin wani hali yake ciki In ma mutuwa yayi tana son sani sbd ta ci gaba da mishi adu'ar samun rahamar Allah.

Bayan dawowar momma ta sanar da ita Hamma ya kira kuma ta d'aga da Toh momma ta amsa mata Bayan ta haura da mintuna talatin ta fito take ce musu next week Friday musharraf ze zo tsalle su little suka dinga yi cike da jin daad'i itama sossai hakan ya mata daad'i a zuciyarta sbd tayi matukar kewanshi musamman ma kamshinshi me tafiya da zuciyarta amma tuna ko tambayanta be ta'ba yi ba In suna waya da en gidan, kuma ya tafi ya barta a asibiti amma ko ya jiki ya ki mata dukda bata kwana ba ma a ranar aka sallameta.

Ta 'bangaren musharraf kuwa a daddafe yayi sati biyun nan, zuciyarshi cike yake da sonta da kewarta da ya mugun bashi mamaki sam be zata ze yi kewarta haka ba, seda yaji muryanta me makon kewar ta ragu se kuma tayi mugun karuwa shi da yayi niyyan se lokacin aurensu ze d'auki hutu ya dawo amma se gashi yana shirin dawowa be kai ko wata da tafiya ba, system

d'inshi dake sleep ya ta'ba se ga kyakyawar hoton ta ya bayyana kwance akan gadon asibiti wadda ya mata a ranar da ze taho, arrow key ya danna se ya tafi next tana tsaye tana serving abinci duk hankalinta na kan abinda takeyi, dannawa ya kuma yi se ga wani hotonta tsaye a kitchen tana girki wadda gefenta d'aya kawai ake iya gani tayi kyau sossi a hoton haka ya ci gaba da tafiya hotunanta kala kala duk kuwa bata sani ba amma sunyi masifar kyau.

Juma'a

Yau sun tashi da aiki sossai sbd dawowar shi yayinda suka riga suka fara waec tun last monday, yau basu da paper hakan yasa basu je makaranta ba inda nuriyyah ta tafi wurin aikinta Miemie kuma na school, daga ita se Amrah da momma se kuma sabuwar me aikinsu ce a kitchen d'in se aiki sukeyi suna hira lokaci lokaci har suka gama, pounded yam da egusi soup se waina da Miyar taushe da yaji tantakwashi se pepper soup na cow-tail da yaji cloves da garlic, daga karshe khairi ta mishi zobo, indo suka barwa wanke wanke da sharan kitchen din suka fice kowa ya fad'a wanka sbd huce gajiyar girki.

Bayan khairi ta fito daga wanka ta duba cikin kayanta ta zaro wani material d'inta me kaman atampha da akayimishi d'inkin fitted gown, sawa tayi a jikinta tare da shafa oil d'inta a hannu ta shafe bayan kunnenta da gefen wuyanta haka kawai ta tsinci kanta da shafa powder da red lipstick a bakinta tare da sa kwalli a idonta tayi kyau sossai kuwa abin ka da wacce bata saba kwalliya ba.

A parlor ta bar dada hakan yasa tayi komai cikin natsuwa amma kuma se ta kasa fita kunya sossai ya rufeta hakan yasa ta hau gado tayi kwanciyarta tare da ba kofa baya, tana nan kwance taji shigowarshi parlorn Amrah na mishi sannu da zuwa kin fita tayi tana ji suka gaisa da dada da kuma momma, momma tayi mishi iso zuwa dining tare da bud'e mishi kulolin pounded yam da egusi soup ya za'ba ta saka mishi tare da tsiyaya mishi zo'bo.

A natse ya fara ci, yana sa Loma d'aya a bakinshi ya san miyan nan ita tayishi haka zo'bon ma yana kur'ba ya san hannunta ne haka ya ci gaba da ci cikin natsuwa yana jin daad'in girkintan yana kuma mamakin me ya hanata fitowa yi mishi sannu da zuwa ya tabbatar In har tana d'akin chan to taji zuwanshi.

Har ya gama ci bata fito ba, hakan yasa ya mike ya fice daga parlorn zuwa part d'inshi yayi wanka ya shirya cikin kananan kaya zuciyarshi fal tunaninta dukda suna gida d'aya, Bayan ya gama shiryawa ya fita zuwa garden a hankali yake zagayawa yana shakan sansayyar kamshin flowers da na kasa da garden d'in ke yi kaman ance kalli chan se ya ganta tana tunkaro inda yake tana tafiya tana lullumshe ido da alamu weathern na mata daad'i, ajiyar zuciya me karfi ya sauke yana me kara kallon fuskanta da ya mishi kyau fiye da kullum da sauri ya 'buya a bayan mango three dake gefenshi ganin zata bud'e ido Ai kuwa bata lura dashi ba tazo zata wuce wurin kenan taji an fisgo hannunta tare da juyata ya manna ta da jikin bishiyar hannunshi d'aya yasa ya zagaye cikinta yayin da d'ayan hannun ke kan bakinta da ke shirin tsala ihu.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

*Am so sorry dearies wallahi wani important thing ne ya sha min kai kwana biyu kuka jini shiru, am very sorry for keeping yhu guys waiting🙏*

Page➡️7️⃣5️⃣▶️7️⃣6️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Manyan fararen idanunta da ta waro su sbd tsoro ya ke kallo da lumsassun idanunshi da kaman an d'iga mishi zaiba, a hankali ya saketa gabad'aya yana sauke boyayyiyar ajiyar zuciya kasa tayi da kanta tana motsa lips d'inta da sukayi matukar d'auke hankalinshi shiru yayi yaki magana har na kusan mintuna 3 ganin da gaske baze yi maganan bane yasa ta cewa "Ina kwana, ka dawo lafiya?" Kallonta kawai yakeyi ba tare da ya amsa ba, baki ta tura tana jujjuya idanunta murmushi kawai yayi ya wuce ta yayi tafiyanshi abunshi.

Tana ta kunkuni har ta isa d'akinsu don abun ya bata haushi tana mishi magana ya wani yi banza da ita, a fili tace "samu ma kayi na maka magana, d'an ba kara" zubewa tayi a kan gado gefen dada, dada tace "lafiyanki ko? Irin wannan fad'owa haka" Khairi tace "lafiya dada, dada Ina kewan d'an uwana, ko me ya sameshi ya hana shi dawowa garemu se Allah" Shiru dada tayi na mintuna kan tace "hmmm Allah ya bayyana mana shi nan kusa khairi ba ke kad'ai ke kewanshi ba, adu'a zamu ci gaba da yi har Allah ya bayyana shi".

Khairi zatayi magana kenan taji an turo kofa d'aga kai tayi se taga su little, mikewa tayi tana murmushi ganin yadda suke rige rigen mata oyoyo rungume su tayi gabad'aya na seconds kan ta sake su tana cewa "muje room d'inku maza In muku wanka ku samu ku ci abinci" jansu tayi ta bar nabeel nan yana cire kayanshi sama suka haura tayi musu wanka ta bud'e sif d'insu kayansu na wanke na jere tsab ta zaro musu riga pink da jeans blue se blue hula me kyau sossai, d'akin su Amrah suka shiga suka samu Miemie na bacci Amrah na kallo a system.

Gadon Amrah suka nufa tare da tsalle akanta ihu ta sake tana mikewa zaune Khairi na tsaye se dariya take musu, "what!!!! Lallai ma yaran nan, wato ke kika turosu ko?? Toh wallahi In kama yaro anan ku ga yadda ake ribiti" Ai da gudu sukayi waje har khairi suna mata dariya itama bayansu tabi tana d'akawa Miemie duka itama a fusace ta tashi ta bi bayansu don sun katse mata baccinta me daad'i.

'Dakin dada suka shiga da gudu yayinda khairi taja baya tana musu dariya sossai ta san dada na chan tana Shari'ah bata gama dariyan ba taji ance "what's funny?" 'Dan razana tayi don bata ji zuwanshi ba se magananshi kasa tayi da kanta tana cewa "babu" kafin ya kuma magana suka sake fitowa da gudu turus suka tsaya ganinshi, had'e rai yayi yace "baku da hankali ne? Katti da ku ku zauna kuna mana gudu a gida. Yara sunayi ku kunayi?" Shiru sukayi Miemie na tura baki,

Amrah na mata dariya a fakaice ganin hakan yasa ya gane Amrah ce ta nemi fad'a hakan yasa ya kama kunnen Amrahn ya murd'e da karfi ihu ta sake tana cewa "sorry Hamma" dariya khairi keyi sossai tana mata gwalo shagala yayi da kallon ta har Amrah ta zame suka gudu sama da Miemie suna mishi dariya da kallo ya bisu kan ya juyo yaga wayam ba ta nan, murmushi yayi yana shafa kanshi ya fice daga parlorn.

Washegari da karfe 10 suke da papper hakan yasa tayi wankin da take da shi da wuri dayake yawanci inner wears d'inta ne yasa ta nufan chan bayan garden don shanyawa, a natse ta karasa da bucket d'inta a hannu sanye take da cotton night wear masu taushi farare wando har kasa da riganshi se ta d'aura karamin farin hijab a kai kafanta sanye da fararen silifas.

A natse take tafiya har ta isa ta fara shanyanta tunda tazo wurin take jin warin taba ta tabbatar shine bata nemi inda yake ba don bata son ganinshi dashi a yana sha, zuciyarta taji ba daad'i duk ya chunkushe, Sam bata fata ya ci gaba da shan taban nan har aurensu bata san yadda zatayi ta sashi denawa ba be bata fuska ba gashi momma ta d'aura hope a kanta tana jin idanunshi a kanta amma taki juyawa se shanyanta take yi duk da kunyan da take jin kaman zata natse amma ranta dake 'bace ya hanata denawa.

Bayan ta gama ta kama hanyar ficewa daga wurin yi tayi kaman bata ganshi ba dayake dole se ta wuce ta inda yake zaune akan wasu kyawawan kujeru green color, kan ta fita daga wurin hakan yasa tana isowa daidai inda yake ta kara kau da kai be wuci taku d'aya ta wuceshi ba yasa hannu ya rike hannunta tare da janyota baya tayi kaman zata fad'i kan kafafunshi dake mike se yayi saurin janye kafafunshi ta zauna tana rintse ido don ta d'an ji zafi In a whisper yace "sorry" Shiru tayi mishi 'bata rai ta kuma yi tana motsa lips d'inta don har lokacin be dena busa hayakinshi ba.

Bata hankara ba taji babban yatsanshi kan lips d'inta da take ta motsi dashi, da sauri ta d'aga manyan idanunta ta zuba cikin nashi karkata kai yayi looking so naughty yace "I like your lips, in munyi aure it will be my something else" juya idanunta tayi tana ture hannunshi tare da kokarin mikewa, da sauri ya maidata ta zauna yace "wai menene kike ta 'bata rai?" Kallon d'ayan hannunshi tayi ta kauda kai.

Goshi ya dafe tare da yarwa ya take yana cewa "bakya so?" Kai ta gyad'a mishi yace "Toh shikenan In shaa Allahu daga yau na dena sha amma fah se kin min alkawarin har abada baza ki sani bakin ciki ba, ba kuma zaki sani dana sanin aurenki ba, ummulkhair maganan gaskiya bazan iya ci gaba da danne abinda nake ji a zuciyata game da ke ba, kece mace ta farko da ta karya padlock da na sawa zuciyata bayan mutuwar surayyah" ya fad'i surrayahn da wani d'aci a zuciyarshi da har tana iya ganewa.

Kallonshi kawai take ta kasa magana be kalleta ba yace "ban san ta ya ba ban kuma san yaushe kika shiga zuciyata kikayi kane Kane ba ko fili kad'an na wata mace baki rage ba, khairr Ina sonki da dukkannin zuciyata Dan Allah karki ta'ba cin amanata da soyayyata, tunda aka haifeni ban ta'ba jin irin son da nake mikin nan ba akan wata mace bayan mommana".

Numfashi ne ya nemi d'aukewa khairi she just can't believe, ya Allah ji take kaman ta tashi tayi ta taka rawa yayinda musharraf ya sake yake ta fad'a mata sirrin zuciyarshi, Sam be san nata zuciyarma cike yake da tsantsar soyayyarshi ba wadda ya fara har'bawa tun daga randa ta kalleshi a Arabian estate. Magananshi ya katse ta inda ya ci gaba da cewa "ummulkhairr kin gama da zuciyata tun daga randa na ganki a area d'in su haidar wasu banzaye na kokarin keta miki haddi wadda shine kallona na biyu dake, na kasa gasgata hakan seda naga nayi iya kokarina wurin hana son tasiri daga ranan amma abun ya ci tura, na kwana cikin matsanancin zazza'bi a lokacin amma zuciyata na gareki da duk tunanina na ko kin isa gida lafiya ko baki isa ba.

Ban ji hankalina ya kwanta ba seda haidar ya kira momma sukayi magana a gabana inda yake sanar da ita lafiyanki klau har hajiyarshi ta had'aki da driver don komawa gida, khairr ban san ta yadda zan misalta miki irin farin cikin da na shiga ba a sadda momma ta nuna tana min sha'awar aurenki a lokacin na tabbatar ta ga abinda na hanga a tattare da ke, da kika amince kuwa har azumin godiya ga Allah nayi ba tare da sanin kowa ba.

Ban san ta yadda zan fad'a miki irin so da kishin da nakeyi a kanki ba amma ke sheda ce a sadda wanchan banzan sufyan d'in ya rike min hannunki, Ina fad'a miki hakan ne sbd ban son a d'aura mana aure da shakku ko wani kokonto na junanmu sbd Ina son mu zama sirrin juna, aminan juna, masoyan juna, rufin asirin juna, Ina son a duk sadda wani abu ze faru ko ya had'amu mu zauna tare muyi solving duk wani issues d'inmu tare, kin san abinda ya ninka min son da nake miki daga farko har ya kasa boyuwa?" Girgiza kai tayi tana sake murmushi da tunda ya fara maganan shine a fuskanta.

Cikin kasa da murya yace "sbd irin son da kike yiwa familyna musamman little da momma, khair Ina kaunarki har ban san adadi ba" wani irin ajiyar zuciya ta sauke farin ciki na mamaye duk zuciyarta kokonton auren wadda baya sonta ya fice daga zuciyarta soyayyarshi ya kara ninkuwa a zuciyarta irin wadda bata ta'ba ji ba don bata ta'ba yin soyayya a rayuwanta ba se daga kanshi bata fata kuma yayi breaking heart d'inta.

Kaman yadda yake mata magana cikin kashe murya itama tace "ba matsala Hamma Allah ya shige mana gaba" 'bata fuska yayi yana cewa "ban gane ba fah, ummu cewa zakiyi nima Ina sonka sweetheart" ya karasa da kashe murya kaman wata mace, da sauri ta rufe fuska tana murmushi tace "I can't hamma" da sauri yace "nop yhu can say it, oya am all ears ko bakya sona ne na miki tsufa ko?" Sauke hannunta data rufe fuskanta tayi tana wasa da yatsunta tace "haba na isa?" Yace "har ki wuce ma".

Time ya kalla kan yace "I thought 10 kuke da papper?" Kai ta gyad'a ba tare da ta kalleshi ba, yace "Ohk je ki shirya karku makara but promise me In kin dawo zaki fad'a min kina sona" Kai ta gyad'a yace "ban yarda ba fah, se kin furta da bakinki tana murmushi tace "Ohk I promise" yace "uhm uhm fah" mikewa tayi tana d'aukan bucket dinta tace "na tafi" yace "take care" wucewa tayi zuciyarta fari kal kaman auduga wani iri take jin kanta kaman tayi ta taka rawa,

Alhamdulillah ta dinga maimaitawa tana jinjinawa rahamar ubangiji a garesu.

Duk wadda ya ganta a ranar ya san tana cikin farin ciki ba kad'an ba ko a school waenda suka d'an saba seda suka tambayeta ko kujeran hajji aka biya mata? Murmushi kawai take musu shine amsan amma bakinta yaki rufuwa Amrah ce tace "ni kam kode yayi proposing ne?" Da sauri ta rufe fuskanta shewa waenda suke zaune da su sukayi Amrah kam harda gud'a, kunya kaman ta nitse.

bayan sun gama papper suka fito don tafiya gida kenan me makon su ga driver se suka ganshi tsaye jingine da mota hannunshi rike da waya yana dannawa sanye yake da black jeans white shirt me guntun hannu se ya d'aura black jacket a kan rigan be wani rufe gaban rigan ba don kana ganin rubutun dake gaban fari kal d'in shirt d'inshi da aka rubuta "Just chill" da manyan bakin harrufa, kafanshi sanye da black combat shoe, 'Masha Allah' ta furta cikin numfashinta tana d'aura ido akan black silk hair dinshi da yaji gyara se sheki yake daga nesa.

Class mates d'insu da suka fito tare ne suka fara kusasu daga masu cewa "woowwww guy d'in Chan ya had'u karshe" se masu cewa "wayyo wallahi zuciyata ta har'bu Allah yasa wannan guy d'in ya zama nawa" se masu cewa "innalillahi kinga wani guy a chan Ina ma zece yana sona wallahi da kunga yadda ake zuba soyayya don na san wanchan karshene daga ganin alama" wata kam cewa tayi "wallahi se na mishi magana ko baze amsani ba, bari ki gani ma in fara da d'aukan hotonshi ba tare da saninshi ba irin wannan guy d'in sune ake mallaka ko ta halin kaka ko da kuwa mutum ze dangana ne da malam".

Idanunta da suka fara chanza launi ta d'aga ta zubawa yarinyar da tayi maganan karshe ai kuwa se taga ta d'aukeshi hoto kanshi ta maida idonta ranta na wani irin suya da bata ta'ba ji ba a rayuwanta har wani zafi zafi yake mata, a lokacin shima ya d'ago ganin sun nufoshi yasa ya maida wayanshi aljuhu yana mikewa daga jinginuwa da yayi da motar duk cikin waenda sukayi 'bangareshi ita kad'ai zuciyarshi ke gani ko za'a kashe shi bayan ita be san ko kalan fatan waenda suke gefenta ba har ta iso karamin murmushi tayi mishi wadda ko fuskanta be gama gamawa ba ta zagaya ta bud'e front sit ta shige.

Hakan ya tabbatar mishi ranta a 'bace yake don tun daga ganin farkon da yayi mata yake tunanin ranta a 'bace yake toh me ya 'bata mata rai? Gaisheshi duk sukayi a tare kaman baze amsa ba se kuma yace "lafiya" tare da bud'e mota ya shige baya Amrah ta bud'e ta shige tana mamakin wasu matan don duk abinda suka dinga fad'a akan wanta tana ji, har ya tada motan yaji ana knocking glass saukewa yayi yana kallon faran tsiririyar yarinyar da ta mishi knocking yana jiran jin me ke tafe da ita, khairi da ta d'ago taga yarinyar da ta d'auke shi hoton nan ce se kawai ta fara hawaye shi kam ma sam be lura ba hankalinshi na kan yarinyar tace "plz handsome in baza ka damu ba ka sa min number dinka wallahi daga ganinka naji abinda turawa ke cewa love at first sight" wani d'an banzan tsaki yaja tare da figan motan yana watsa mata kura, en matan da suke wurin suka kwashe da dariya suna nunata a kunyace ta juya sumi sumi ta nufi motar gidansu da yazo d'aukanta........

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, charity, honor and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️7️⃣7️⃣▶️7️⃣8️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Tunda ya d'auki hanya ko juyawa be yi ba balle ya ga hawayen da yayi cha'ba cha'ba a fuskanta duk tunaninshi ya tafi ga mata masu kaiwa maza kansu a wannan zamani, mazan yanzu ba kai ka fara cewa kana sonsu ba ma ya aka kare bare, mazan yanzu da basu san darajar mace ba? Ya tabbatar d'ai d'ai ne za'a samu masu bin koyarwan manzo a zamantakewar aure he just take a glance at her a lokacin da ya sha kwanan gidansu waro ido yayi a d'an rud'e yace "qalbee!! What happened to yhu subhanallah are yhu sick? Ko nayi miki wani laifi ne?" Ya karasa yana danna horn na shiga gida.

Me makon tayi shiru se ta fashe da kuka harda shesheka, Amrah dake baya murmushi kawai ta sake ta san ba wani abu bane kishi ne kawai ke d'awainiya da ita, kuma da alamu ze lalla'ba kayanshi da farko ma damuwa tayi da auren hammanta da khairi sbd sanin halinshi amma yanzu zuciyarta fes ashe hamma an iya soyayya harda wani qalbee😅

Yana parking ta fice daga motan khairi ma shirin fita take taji ya riko hannunta cikin damuwa yace "menene ummu?" Cikin kuka tace "ba kai bane ka saurari wasu" waro ido yayi shikam ma be gane inda maganan ta dosa ba hakan yasa yace "ban fahimta ba" tura baki ta kuma yi cike da rigima tace "har hoto fah ka bari ta d'aukeka, har fa cewa take ko da malam se ta mallakeka, amma tana knocking glass ka bud'e" dariya ya saki cikin dariya yace "jealousy jealousy, dama duk kukan na kishi na ne? Alhamdulillah" kukan shugwa'ba ta kara sawa da sauri ya bar dariyan da yake yace "sorry, am sorry sweetheart bazan kara sauraren kowacce mace ba bayan ke da muharramaina In shaa Allah kinji?" Kai ta d'aga yace "oya fulfill your promise" rufe fuskanta tayi da kyawawan yatsunta hakan yasa ya kurawa yatsun ido na mintuna kan yasa hannu ya sauke ya rike su cikin hannunshi yace "wallahi qalbee kina sa ni surutu dayawa In yi ta magana ki ki cewa komai".

Yanzu dinma shiru tayi ya sake cewa "shikenan tunda baza ki min magana ba you can go" ya fad'a yana sake mata hannu ganin kaman ranshi ya baci yasa tace "Ohk sorry, zanyi magana"

Shiru shima yayi tace "mi yid'i ma ha nder nberd'e am" tana karasawa ta fice da sauri tana murmushi, murmushi me sauti ya sake yana shafa kanshi zuwa kirjinshi a kan lips dinshi ya furta 'Alhamdulillah' ashe ze sake farin ciki a rayuwanshi? Cikin farin ciki ya fice ya shiga d'akinshi gobe da safe ze wuce hakan yasa ya d'an shirya abinda ze bukata.

Tana shiga parlorn ta samu duk ahalin gidan zaune su nabeel ne kad'ai basa nan suna islamiyya, har kasa ta duka tayiwa su momma da dada sannu da gida kan ta shige d'aki don yin wanka, a ranar da yamma suna zazzaune a parlor ana hira yayinda momma da hamma ke kallon news khairi kuma na tsaye daga wurin dining tana taya me aikinsu shirya abincin dare, su little suna game a waya amma basu sa volume ba, nuriyyah, Amrah da Miemie kam kowacce chatting take yayinda dada ke zaune shiru tana azkar.

Sanarwa aka farayi a tv wadda ya sa su maida hankalinsu gabad'aya akai "Abun al'ajabi wani hawan Allah ne wadda ada aka sanshi farin sani sbd yadda aka dama dashi sossai a siyasar kasarnan inda mukamin da ya rike daga karshe shine mukamin senator ba kowa bane se senator mahmoud Adam, ya mika kanshi ga hukuma akan abubuwan da yayi marasa kyau har gwara da alummah ma akan iyalanshi inda yace 'ya cutar dasu mafi munin cutarwa wadda baze fad'u ba amma yana rokonsu yafiya yayi hakan ne watakil ko zasu yarda da gaske ya tuba yabi Allah su taimaka In sunji labarin mutuwarshi su yafemishi haka iyayenshi su sashi a adu'ar su dan Allah duk san duniya ne da son zuciya se sharrin shaid'an ya ja mishi abinda ya aikata a garesu, yaci amanar aure yayi shaye shaye yayi cin hanci ba kad'an ba yayi zinace zinace.

Abu mafi munin da ya aikata kuwa shine zina da matar d'anshi yana rokon yafiyarshi ba don halinshi ba, don shi ba ya d'ubi girman Allah ya yafe mishi zina da yayi da matarshi dukda da yardarta, da asirinsu ya tonu kuwa me makon ya yarda se ya d'aurawa d'anshin namiji kwaya d'aya sharri har yayi zaman shekaru a gidan yari' senotorn de a shekaru biyu da suka wuce yayi sadaka da gabad'aya dukiyarshi inda ya koma talaka futuk a fad'arshi ya kwashe shekara biyu yana rokon Allah yafiya kan yazo a yanke mishi hukuncin zina, sannan ya kara da cewa matarshi kuma 'yar uwarshi fatima ta yafemishi tayi mishi takaba ko ze samu rangwami wurin Allah, inda a yau da safe aka yanke mishi hukuncin kisa ta hanyar jifa ga yadda abun ya kasance.

Da sauri khairi ta rufe fuskanta tana kuka sossai, Amrah da Miemie ma kuka sukeyi sossai yayinda momma ke hawaye tare da furta "Allahumma gafirlahu wa rahamhu, Astagfirullah" musharraf kam tunda aka fara jifan mahaifinshi ya runtse ido a hankali yace "na yafemaka Abba, Allah ya yafemaka, Allah ya amshi bakuncinka" uwar gayya nuriyyah kam yanke jiki tayi ta zube a sume.

Dukda laifin da ya musu amma gidan sunga tashin hankali sun kuma ji mutuwanshi sossai ba kad'an ba, kan kace me gidan ya cika da en uwa, a take su dadda suka kamo hanya cikin mintuna 30 suka shigo cikin gombe a lokacin har su hamma Ahmad sun kar'bo gawanshi, momma tasa hijabinta kato har kasa su hajiya Aisha duk sanye da manyan hijabai su Amrah ma na zazzaune hk dada ma, khairi kam na d'aki sossai ta tausayawa Abbansu duniya kenan,

musharraf na waje cikin masu amsan gaisuwa idonshi kaman gauta tsabar ja jijiyoyin kanshi duk sun tashi goshinshi rad'a rad'a da su be ta'ba sanin yana son mahaifinshi ba se yau adu'a sossai ya dinga mishi har aka mishi wanka aka shiryashi a part d'inshi, dashi da su uncle nasir se Mamaji da bappa ne suka mishi wanka suka kwantar dashi a parlor su momma suka shigo suka mishi adu'ar ban kwana sossai tayi mishi adu'a ta roka mishi yafiyar Allah inda ta dinga furta na yafemaka hamma, na yafe maka, duk su nuriyyah ma sun mishi adu'a itakam ma duk ta fice a hayyacinta tana sonshi sossai don yafi kula da ita akan kowa a gidan suna ji suna gani aka fita dashi zuwa gidanshi na gaskiya bayan an binneshi musharraf kasa daurewa yayi ya fashe da kuka sossai.

Da kyar su uncle Ahmad suka samu ya dawo gida inda suka kira Doctor Aslam gida yazo ya duba shi don zazza'bi ne sossai ya rufeshi, alluran bacci ya mishi me karfi tare da d'auramishi ruwa don jininshi ya hau sossai.

Bayan kwana bakwai

A yau akayi sadakar bakwan Abbansu mutane dayawa daga wurare dayawa sun zo musu gaisuwa har en office d'inshi, kuma har lokacin yana kwance khairi ce ke kulawa dashi shan maganinshi, cin abincinshi, tsabtar part d'inshi dukda exams din da suke zuwa ita da Amrah, ita ke tausanshi da kalamai masu taushi don kwantar mishi da hankali sossai ta cire kunya take kula dashi, momma ma sossai mutuwar ya shige ta ko yaushe suna tare da dada tana bata kalamai, nuriyyah ta zama so silent kullum marwan na zaryan zuwa kwantar mata da hankali, Miemie ma de mutuwar ya shigeta don tayi sanyi kaman ba me hayaniyar nan ba.

Su mamaji sun koma tun bayan sadakar uku, amma kullum suna kira suji lafiyarsu haka su hamma nasir kullum se sun zo da iyalansu, su ke kawo musu abinci, a haka akayi sati biyu zuwa lokacin musharraf ya warke har ya koma office kowa ya koma normal rayuwanshi banda momma dake takaba, soyayya tsakanin khairi da musharraf ya ninka da, musharraf da kanshi ya bada shawaran a d'aga bukinsu se momma ta fita takaba wata hud'u kenan, za'a kara wata uku akan d'ayan da ya saura zuwa lokacin ma su khairi sun gama neco ba ma waec ba.

Su mamaji sun yarda da hakan kuwa, a hankali rayuwa ya ci gaba da gurgurawa lokuta dayawa ana cikin farin ciki da saisaitar rayuwa musamman wurin su khairi yau suke gama neco a yau kuma mutuwar Abba ke cika wata uku da sati biyu saura wata guda bukinsu inda baza'a fasa duk wani events da aka shirya tun farko ba, zasuyi lalle day, bridal shower, kamu, walima ranar da aka d'aura aure se dinner washegari, dukda khairi bata so ba amma ba yadda ta iya gasu amaren dayawa ita kad'ai baza tace kar ayi ba amaren sun had'a Nuriyyah, maryam, sulaimi, zainab se khairi. Mazan biyu na gida ne yayinda sauran suka kasance waje, mamaji da bappa sun zauna sun tattauna tunda suncewa sufyan ya fidda mata yaki zasu had'ashi da Afreen uncle Ahmad ya nuna yana tsoron kar abinda ya faru da kaninsu ya faru da d'anshi tunda ya nuna baya so a kyaleshi.

Haka kuwa suka hakura suka barshi don sunga illar hakan, tunda musharraf ya sa kafa ya tafi

be sake zuwa ba se de waya sam be son ganin mommanshi na takaba yayi alkawarin baze dawo ba kuma se ta fita, soyayyarsu ba wadda be san dashi ba daga gida har wurin aikin hakan ke kara kular da Anty Rabi'ah musamman In tazo gidan taga yadda khairi ke kulewa a d'aki suna shan love, tayi ta hantararta kenan da gayamata munanan kalamai ba ita kad'ai ba har dada da su nabeel, kaman yau khairi na kwance a kuryan gado waya makale a kunnenta tana yiwa musharraf rigima "Allah honey nayi kewarka plz come soon am dying right here" ta bangaren shi yace "habaa rayuwata ki tausayawa bawan Allah mana, ko kina son ganin honeynki na kuka?" Cikin tura baki tace "uhm uhm" yace "am sorry nima Ina missing dinki sossai musamman wannan kunyan naki, nayi kewar idanunkin nan masu matukar kyau da tsari, nayi kewar well carved attractive lips dinkinnan baza ki gane ba baby am missing yhu more than someone can imagine".

Ya sauke numfashi kan yace "kawai ban son zuwa ne se momma ta fita takaba" tace "alright dear Allah nuna mana, ya shirye shiryen buki?" Murmushi yayi yace "Ai ku za'a tambaya wannan baby ba mu maza ba kune masu abubuwan yi amma fah na shirya mishi sossai sbd Ina so ya zama best wedding ever a gombe, huhhh dear am so tired wallahi tun safe aiki nake ban huta ba da kina nan kuma kin zama tawa da ina dawowa gida zan baje akan gado kiyi min tausa da hannayenkin nan masu taushi da albarka".

Murmushi me sauti ta sake tace "ka san ban ta'ba zata kana da surutu ba honey?" Wani sauti ya sake da ya sata jin tsikar jikinta ya zuba yace "Ai ke kika koyamin kuma se na gayaki da momma na" ya karasa da muryan da zata iya rantsewa ko little baza ta iya irin shi ba, lumshe ido tayi tace "I love yhu" cikin fisgar hankali yace "minfu mi yid'i ma boddi ha nder nberd'e am"(nima ina sonki beauty har cikin zuciyata).

Kira taji ana kwala mata hakan yasata cewa "I will get back to yhu baby, ana kirana" yace "waye?" Tace "Anty Rabi'ah" tsaki yaja don pendonshin ta fara fita ranshi sbd takurar da takewa khairi dukda ba ita ke fad'a mishi ba amma yana sane, cikin kasa da murya yace "ko menene ya 'bata miki rai ki tuna, Ina sonki zaki ji farin ciki, bye bye" ya kashe wayan murmushi tayi kan ta mike ta fito.

Ita da Afreen ta gani zaune a parlorn kasa ta duka tace "gani Anty" hararanta tayi tace "wacece Antynkin? Kije chan ki nemi Antynki munafuka, ba tun d'azu na kiraki ba? Wato se kinga dama zaki fito koh? Shege be iya samun wuri ba wallahi" Afreen tace "na rasa meyasa Anty fatima ta kasa gane munafurcin mutanen nan da gani sunan en gidan suka kai wurin bokansu na daji kiri kawai(mugayen fulani sune kiri).

Hawayen da ke kokarin zubo mata ta mayar don ganin dada da Amrah na shigowa murmushi tayiwa Amrah bata san sunji abinda su Anty Rabi'ah suke cewa ba Amrah ma ganin khairi bata nuna mata ba ysa ta sakar mata murmushi tare da ci gaba da tafiya da dada sandarta na hannunta ko kallon su Anty Rabi'ah batayi ba har suka shiga d'akinsu khairi, Afreen tace "ba kin gani ba mommy, suna shirin rabamu da en uwan mu" Anty Rabi'ah tace "kyalesu tsintacciyar mage de...." bata karasa ba se ma daka wa khairi tsawar da tayi tace "ki tashi kije ki dafamin

pounded yam bana son na gari, doya zaki fere ki daka, da miyar egusi se pepper soup kan sa da kunun Aya" mikewa khairi tayi ta shige kitchen tana d'an murmushin tuna kalaman musharraf.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, charity, honor and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️7️⃣9️⃣▶️8️⃣0️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Cikin natsuwa ta fara girkin don ita a ganinta ba wani abu me wahala suka bata ba kasancewarta me son girki, babban abunda ke damunta rashin tarbiyar Afreen tana ga se ta seta yarinyar ta kiyayeta a gidan ta rasa dalilin tarewarta a gidan tun last week, ga mamanta da kullum tana hanya, a fili ta furta "Au na manta ita da gidan pendonta!!" Tana ta sake sake tana girkin amma duk sadda ta tuna da musharraf se taji wani farin ciki wadda hakan ke kasa boyuwa a fuskanta bayan ta gama ta jera musu a dining ta shige d'akinsu tayi wanka da karamin towel ta fito d'aure a kirjinta tare da zama gaban dressing mirror ta fara shafa mai.

Tana cikin shafawa taji wayanta na ringing special ringing tone da ta sa don special man d'inta yasa ta gane me kiran seda ta ja ajinta tukun ta d'aga suka fara hira tana ci gaba da abinda take, tambayarta yayi me taje tayi nan ta gayamishi amma bata ce ga wacce ta sa ta ba, be ce komai ba don Amrah ta riga ta sanar mishi, sossai ya yabawa zuciya irin ta khairi da wata ce da se ta aibata pendonshi a gabanshi amma se ta dinga rufa musu asiri, hirar ta ne ya d'auke mishi hankali, inda take sanar dashi wai zasu koma gidan hajiya ruqayyah In ji ta achan za'ayi musu gyara na wata guda da ya saura, inda yake tambayarta karfe nawa zasu tafi tace mishi da dare driver ze kaisu.

Hakan ne ya hana musharraf kiran Afreen yaci mutuncinta, Ai ko da daren khairi da nuriyyah suka tafi da manyan akwatunansu, dada kam bata da abin cewa se godiya ga wannan bayin Allahn duk abinda tayi niyyan fad'a ko yi akansu kan ta aikata momma ta rigata, tunda tazo gidan bata komai se ci da kwanciya da kuma yawan zama da su Amrah a garden ko chan bayan boys quarters, shiyasa a duk sallollinta na farilla se ta sa mutanen nan a adu'a harda hajiya ruqayyah da ta d'auki nauyin kayan d'akin khairi gabad'aya ga na gyaran amare da zata musu.

A chan gidan kuwa hajiya ruqayyah part guda ta ware musu me komai da komai me d'akuna uku ta gayyato babbar me gyaran jikin nan Hajiya Jameela idrees daga chad don tayi mugun kwarewa a harkar se hajiya yasmeen Ahmad daga sudan duk dakuna d'ai d'ai ta saukesu se su khairi suka sauka a d'aya.

A ranar da suka zo a ranar aka fara musu abinda ya kawosu don manyan fridge d'in part din a cike suke da guzurin su hajiya yasmeen, da magungunan sanyi da infection suka fara, se gyaran fata wasa wasa kan sati biyu ya zagayo su khairi sunyi wani mugun chanzawa ga kamshi da ya mugun kama jikinsu ga wani d'an kiban da sukayi sukayi fresh dasu kaman d'anyen tomatos 🍅.

Toh su ci me kyau su sha me kyau ko abinda suke ci ma daban da wadda en gidan suke ci, su kwanta a Ac azo a dirje musu jiki da dilka a turarasu sama da kasa ko fita basa yi, yayinda soyayyarsu da musharraf kuwa ba'a magana kaman zasu kashe juna da love, har mamaki nuriyyah ke yi ba don ta san muryan hammanta ba da se ta karyata khairi akan irin soyayyar da suke zubawa.

Randa suka cika sati biyu a gidan a ranar momma ta fita takaba hakan yasa suka tarkata gabad'aya gidan zuwa gidansu harda hanan matar haidar da hafsa da suka saje suka zama kawaye matar haidar kam ma kusan da ita ake cinyewa da shanye kayan gyaran amaren, sossai momma tayi farin cikin ganinsu haka suna samun kulawa fiye da zatonta, ko su maryam da suma aka had'asu zuwa gidan uncle Ahamad don gyaran baza su nuna musu komai ba har ake wani kananan maganganu akan kaisu gidan hajiya ruqayyah da tayi, ta rasa me ke damun Rabi'ah wallahi har gwara zulai da dama ta san halinta ne.

Bayan an gama yiwa momma gaisuwa mutane sun tattafi khairi ta samu kebewa da dada inda suka fara magana akan gyaran jikin da ake musu se albarka dada ke sawa hajiya ruqayyah ko da ta'bi ta san jikin khairi ya chanzu balle kuma In ta wuce se kayi mintuna kana jin kamshinta, dada ne ta nisa tukun tace "Khairiyya ni kam maman hamdeeya ta san da auren nan kuwa?" Khairi tace "a'a dada" dada ta kuma cewa "Anya ma da na aikeki ki sallameta ki kuma bata adreshin gidan nan kinje?" Shiru khairi tayi hakan ya ba dada amsar tambayanta.

Cikin 'bacin rai tace "amma baki da hankali khairi shiyasa mana banga matarnan ta zo gidan nan ko sau d'aya ba, na san da ta sani da se tazo sbd mutunci irin nata, me ta miki haka da ta chanchanci wannan sakayyar daga gareki bayan duk kyautatawarta a kanmu anya rayuwa yace haka?" Shiru khairi ta kumayi hawaye na shirin zubo mata duk se bata ji daadin abunda ta aikata ba gashi ta bakantawa mahaifiyarta rai.

Dada ta sake cewa "ashe In kikayi kud'i na kanki har mu zaki iya mantawa da......." da sauri khairi tace "a'a dada kin fah san halina dada kin san abinda zan iya da wadda bazan iya ba, wallahi ba Haka kawai naki mata sallama da bata address ba, mijinta ne ya matsa yana sona dukda na nuna mishi bacin raina da kin amincewata amma se ya sameta ya kuma fad'a mata ita kuma ta kirani tana rokona In aureshi ana cikin hakan ne barin mu unguwan ya tashi, ban fad'a mata bane sbd kar ya kuma biyoni nan har yasa inyi abinda zan mutu Ina da na sani, don na san se ta fad'a mai, amma tunda ranki ya 'baci akan hakan yanzu zan samu driver ya kaini In gayamata, kiyi hakuri".

Bata jira cewar dada ba taja hijab d'inta ta fice driver ta samu ya kaita har tsohon unguwansu inda tace ya jirata ba jimawa zatayi ba, da sallama ta shiga gidan maman hamdeeya dake kitchen ne ta fito da sauri ganin khairi yasa taje da gudu ta rungumeta tana cewa "Alhamdulillah khairi ashe kuna nan garin duk na shiga damuwa da taraddadin me ya sameku? Ko kuna lafiya?".

Hawaye ne ya gangarowa khairi tace "kiyi hakuri mun saki cikin damuwa, muna nan lafiya" janta

maman hamdeeya tayi zuwa parlor suka zauna ta fita ta kawo mata ruwa dukda bata ga alamun wahala a jikin khairi ba sema hutu da jin daad'i da ya bayyana amma hankalinta yaki kwanciya akan lafiyansu klau, bayan khairi ta sha ruwa ta bata labarin duk abinda ya faru da dalilin barinsu, sossai ta bata hakuri akan abinda tayi inda ta fad'a mata dalilin yin hakan.

Dukda ran maman hamdeeya yayi ba daadi amma tayiwa khairi uzuri sbd tana ganin laifinta ne, da bata nemeta akan maganan auren mijinta ba da duk hakan be faru ba, adress d'in ta kar'ba tace zata zo In shaa Allahu, ta dinga tsokanan khairi har kofa ta rakota se da tazo fita tace "banga hamdeeya ba" maman tace "suna fita da babanta zuwa gidan kakanninta kina shigowa" "Eyyah a shafa min kanta se na ganku" hannu ta d'aga mata tare da komawa ita kuma ta shige mota.

Tana sauka a mota kiran musharraf na shigowa d'agawa tayi tanacewa "baby Alhamdulillah momma ta fita takaba yaushe zan ganka?" Murmushi me sauti yayi har tana ji tukun yace "se next week dear, ya kk?" Tura baki tayi tana nufan garden tace "opps na manta ana gaisuwa tsabar kewanka da nayi, Assalamu alaikum ina yini?" Wani murmushin ya kuma saki cike da shaukin sonta yace "lafiya qalbee, ni kam ana ta maganan anyi kewata ko me aka tanada min?" Fuska ta rufe da tafin hannunta d'aya murmushi yace "awwwn I guess kunyar sarauniya ya motsa" tsiririyar dariya ta sake tana zama akan grass carpet dake gyare fes ba ko digon dotti bayan ta jefa hijabinta cewa yayi "on your data" kashe wayan yayi ita kuma ta cika umarninshi na kunnawa, tana kunnawa call dinshi na shigowa video call bata damu da sa hijabi ba ta d'auka.

Sanye take da doguwar rigar atampha blue da aka mata wata arniyar dinki da ya bayyana wuyanta sossai zuwa kan kirjinta an yiwa rigan style da plain purple chiffon kanta ba dankwali se gashinta da tayi parking daga tsakiya yana lilo a bayanta, suna had'a ido ya sake nannauyar ajiyar zuciya yana kare mata kallo dukda ta waya ne hakan be hanashi ganin freshness da shiness na jikinta ba dukda ba komai a fuskanta amma tayi mishi wani balae'en kyau ji yake kaman yaja ranan aurensu yadda ze ganta zaune kusa dashi ta zama mallakinshi.

Zaune yake a office sanye da Ash color suit da white shirt a ciki me dogon hannu ya cire na saman na cikin kawai ya bari tare da sake neck tie dinshi ash, "wow qalbee kinga yadda kika koma kuwa?" Murmushi kawai tayi mishi ya kuma cewa "an kuwa ta'ba ce miki kina da kyau?" Girgiza kai tayi yayinda da waro ido yace "Toh kinfi kowacce mace kyau a duniya, yhu are the most beautiful African girl that I've ever met, Wallahi Ina sonki" and khairi can stop her self from blushing daad'i take ji har cikin ranta.

Tace "ba wannan ba yaushe zaka dawo?" Yace "au ina sonki ba important magana bane? And kuma baki amsa min bafa!!" Ya karasa da karkata wuya gefe, murmushi ta saki har yana kallon fararen hakwaranta da dimple dinta da ya lotsa, tace "ohk Ina sonka nima" lumshe ido yayi yana jin daad'in words din har cikin ranshi, kallonta da yakeyi yanzu ji yake wani abu na yawo cikin jikinshi, wani mutuwa jikinshi keyi a duk sadda ya ji sassayar muryarta, a hankali yace "randa zakuyi kamu ko menene zan dawo" juya ido tayi da sauri ya kawar da kanshi da ta san yadda

yakeji In ta juya idanuntan nan da bata mishi ba, bata ce komai ba ya san bata ji daad'in randa ze dawon ba.

"Momma zata tafi Abu Dhabi jibi da safe don miki sayayyar kayan aurenki ko zakuje tare zaki fi za'ban abinda kike so?" Tun kan ya karasa take girgiza kai dama ya san baza ta yadda ba sbd kunya ya gwadata ne kawai, cewa tayi "a'a wallahi duk abinda ta sayo Ina so, na San ta fini ma sanin abinda ze min kyau" kan yayi magana yaga little ta fad'a kanta cikin murna tsayawa yayi kallonsu khairi da bata san murnan da little ke yi ba tace "little pretty me muka samu ne?".

Little tace "cutie granny tace daga next two weeks zaki zama mommy na?" Satan kallon musharraf tayi hakan yasa little juyowa ihu tayi ganin paapinta tace "Paaaapiiii is it real that cutie will be my mommy?" Musharraf yace "yes dear ai kina so ta zama koh?" Cikin murna tace "of course yes paapi, I really love her" haka suka ci gaba da hira cikin son juna musamman little da murnanta ya kasa boyuwa kusan one hour sukayi suna shan hira kan sukayi sallama.

Da dare suka koma gidan maami, kaman yadda ya fad'a jibin momma ta tafi Dubai kwananta hud'u ta dawo da set d'in akwati guda masu tsananin kyau kaya kam har da kyar ake rufewa, a ranan aka kuma kawo na nuriyyah ita ma set ne me kyau, shirye shiryen buki ya kamkama Inda Za'ayi lalle day ranan Wednesday a gidan uncle nasir aka had'u gabad'aya hajiya yasmeen da ta kware a lalle da kwalliya ne ta chancharawa amare nuriyyah da Khairi da wasu manya har momma, don gabad'aya matan familyn suka had'u, masu lalle kusan hud'u amma na hajiya yasmeen yafi had'uwa, ba abinda ke tashi a gidan se kid'a cikin wakokin hausa yara se chashewa suke, su Amrah kaman za'a karya kwankwaso, wai juyawan da zanyi se naga en mukaru da juna group mota guda wai sun zo lalle.

Kama baki nayi ina kallonsu ko wa ya gayyato su oho, su maman khalil, Aisha lawal shahud, Zainab Ads, hauwa Adam(jiddo), Nagarta, Smeenerl, salmerhalee, Maijidda, salmer Auwal, saadah Sanusi da queen mai makon su je yin abinda ya kawosu se na hange su gaban dj mace da aka kawo se rawa suke harda kwaso shoki Maman heedaya na tsaye gefe tana d'aukansu video tana dariya sbd ta samu na status da turawa a Mukaru da Juna, ganin za'a gama lalle banda ita yasa ta zame taje ta zauna aka chanchara mata nata tanayiwa su maman khalil dariya don ganin sun kusa rasawa da kyar suka shawo kan hajiya Yasmeen tayi musu Bayan sun gama tikan rawansu amma be kai na maman heedaya kyau ba haka suka tafi da haushi.

#vote

#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️8️⃣1️⃣▶️8️⃣2️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Buki fah yayi buki ko wani gida mutane ne fal washegari da ya kasance bridal shower da safe suka tattara gabad'aya se dukku, dada kam kin zuwa tayi ba yadda momma batayi ba taje tace bazata ba ai suma dawowa zasuyi zuwa jibi, hakan yasa momma ta zuba akwatunan auren khairi da nuriyyah d'akinta ta rufe da key tare da kiran mai aikinta akan ta dinga kwana a gidan

da dada har su dawo don har su nabeela da nabeel za'a tafi.

Gabad'aya amaren da kawaye a part din momma na wurinsu dadda suka sauka duk a takure khairi take sbd bakaken magana da harara da su maryam da kawayensu ke jefanta, ganin Haka yasa nuriyyah ta jata da kawayenta zuwa d'aya room din su Amrah ma da Miemie nan suka koma, anan suka shantake suna ta hira tana mamakin karamci irin na su nuriyyah mamaki sam yaki sakinta ganin kawayen nuriyyah ne zasu zauna a matsayin kawayenta su da suka fita class da wayewa don daga en jami'a se wacce ta gama, Amrah da Miemie suna cikin kawayenta don abinda kawaye zasuyi anfani dashi duk sun d'inka.

Da yamma aka gayyaci kwararriyar decorator d'innan Muhsina maikano tayi decorating gabad'aya gidan da mutanenta mussaman inda za'ayi bridal shower din, shima taron ba maza, inda musamman chief cook din nan saadah sanusi tazo ta baje fasaharta tayi girki kala kala, momma uwar ango da amare biyu gabad'aya a busy take na saukar da mutanenta masu zuwa wasu tun daga Abuja waenda sukayi koyarwa tare, wasu mutanenta na nan gombe donma hajiya ruqayyah na taimaka mata.

Wow wow masha Allah shine abinda na furta ganin amaren nan da sukayi matukar tafiya da imanina dukkansu Allah ya zuba musu kyau ko wacce da kyaun da Allah yayita don Allah be hallici mummuna ba, amma kyaun khairi na daban ne, gabad'aya amaren anko sukayi haka kawayensu ba'a banbanta na wace da wace ba sanye suke cikin purple bridal gown me bits da kwalliyan pink, ko wacce an saka bata band daga kafad'a zuwa gefen kunkurunta light pink inda akayi rubutu da dark pink aka rubuta "Bride to be" sossai sukayi kyau sbd purple din ya kar'bi fararen fatansu, hajiya Yasmeen ta baje fasaharta wurin kyalliya da d'aurin khairi da nuriyyah wani d'an banzan hill suka saka pink da pose pink da suka rike a hannunsu a jere reras suka fito suka nufi filin bayan gidan da akayi decorating dj mace da aka d'auko ta sake musu waka me sanyi da taushi.

Nan fah taro ya fara tafiya yadda ya kamata amare kowacce ta samu gifts daidai gwargwado akayi hotuna da videos aka ci abinci daga karshe aka sake kid'a aka chashe, en Mukaru da juna ne gaba wurin rawa da suka ci ankon peach da orange se kace an gayyacesu, se na Queen bee da suka sha ankon light blue da dark blue, Chan na hango en Annur writers Association na chacewa daga baya se ga en Wattpad da nasu ankon red suka baje tasu basirar rawar su didi ta (haneefah muhammad Gurin) har kwankwasonta ya kusa karyewa, su Aisha Gurin duk miskilancinta da kunyarta seda ta zage ta kwashi shoki harda su zanku da gwara gwara.

Khairi de taga mutanen da ta rasa daga Ina kuma ba laifi sun sata nishad'i da farin ciki sossai, bayan taro ya watse ta kar'bi wayan Amrah ta tura duk hotunanta dake ciki tare da kunna data ganinshi online yasa tace "baby" ko seconds biyar be yi ba yace "qalbee ya gajiyan buki? Na san an gajiyarmin dake dayawa" murmushi ta turamishi kan tace "wallahi akwai gajiya Sweetheart ka samu tahowa ne?" Yace "Eh muna ma gida d'aya and I wanna see yhu right now" tura mishi emojin juya ido tayi da na shagwa'ba tace "akwai fah mutane dayawa a gidan

nan taya zanyi in fita Inzo wurinka?".

Yace "plzzz I wanna see yhu" ya tura mata emojin plzzz, batayi reply ba se tunanin fita da take ganin bata ce komai ba yasa yace "shikenan tunda baza ki fitoba, turomin pics din bridal shower dinku I know yhu looked perfectly good and the most beautiful bride of this century🥰" murmushi tayi tare da tura mishi "tnx love an am sorry" yace "no I understand ai an kusa kai mini ke gabad'aya mu rayu har abada yadda ba wadda ze min katanga da ke".

Murmushi tayi tare da tura mishi pics din aiko ya dinka tura mata emojis din love da sauransu dariya ta dinga yi ita kad'ai, su Miemie na kallonta da mamaki juya ido tayi tace "what" waro ido sukayi Amrah tace "eyee soyayya daad'i" Miemie tace "Allah samu a danshinku" dariya kawai tayi tare da cewa "Ina son yayankun nan sossai gaskiya and he loves me equally" shewa suka sake da sauran kawayen nuriyyah suna cikin wannan maganan ne Anty Rabi'ah ta shigo da wasu cousins dinsu ta bangaren uba tare da nunata tace "kun ganta nan, itace Adda fatima ke wani tada jijiyoyin wuya an zageta, gida be koshi ba an d'auka an ba na waje, na wajen ma marar asali da gata".

D'aya daga cikinsu tace "ikon Allah gashi ba kyau tafi en familyn nan ba Ba komai ba, watakil da boka aka had'a" khairi da kanta ke kasa ko d'agowa ta kasa ranta ke wani irin tafasa kanta ya fara saarwa cikin kasa da murya tace 'not now plz' d'aya daga cikinsu tana kallon Rabi'ah tace "kuma kikace mahaukaciya ce ko? Amma haukan tashi tashi?" Ba kunya Anty Rabi'ah tace "Eh wallahi, ita kad'ai aka gani fah da uwarsu se en biyun da na nuna muku, gashi uwarsu nakasashiya wa ya sani ko a yawon maula ta samosu duka".

Jikin khairi ne ya fara 'bari fuskanta yayi jajazir idonta a lumshe tana jin yadda kanta keyi kaman ana daddatsawa da arda ko wani makami, sama sama ta fara jin maganganunsu, da sauri miemie taja nuriyyah suka fice daga d'akin zuwa part din diddi, Amrah kuma ta d'aga waya ta kira musharraf yana d'agawa tace "Hamma kazo akwai matsala, khairi ce" bata rufe baki ba ya dira daga kan gadonshi tare da ficewa zuwa part din dadda.

Basu ankara ba basu ji tasowarta ba se ji sukayi an had'a kawunansu an gwara, ihu suka tsala tare da zubewa don ba karya sun bugu, a rud'e Anty Rabi'ah tayi kofa bata karasa ba khairi ta rikota ta shake wuyanta kam duk abinda takeyi idonta na rufe, ihu Anty Rabi'ah ta dinga yi na neman taimako gani take kan azo cecenta ta mutu don ba karamin shaka aka mata ba, a take mutane suka fara taruwa don ganin abinda ke faruwa, musharraf da ya iso ne ya tsaya kallonsu shi ya rasa me ke damun mata wallahi ya tabbatar cikinsun nan baza'a rasa masu shi ba amma sun iya taruwa ganin gulma, mamaji, bappa, uncle nasir, da uncle Ahmad ne suka shigo suka korasu kan musharraf ya shiga cikin d'akin ta'be baki yayi yana gyara tsayuwa tare da tura hannuwa cikin aljuhu ya zuba masu oily eyes dinshi yana kallo.

Mamaji da be shigo ba yacewa su unlce Ahmad "na San Musharraf ze iya kula da matarshi don haka muje In baku wani hayaki kowa ya samu kasko a je babban kitchen a d'ibi wuta a yiwa gidan gabad'aya hayaki sbd na tabbatar baza ta gaza yin kara ba kuma bamu san adadin masu

shi ba" ficewa sukayi da sauri don cika umarni bayan ya bawa kowa kullin hayakin yana da burin sama ma khairi da nuriyyah inganttaciyar magani in Shaa Allah.

Tsabar irin mugunta na musharraf seda yaga pendonshi ta kusa mutuwa tukun ya zare hannu a aljuhu yaje ya fara kokarin janye khairin da kyar shima ya samu janyeta tare da sanyata jikinshi ya matse don kar ta fisge tayi wani wurin, Adu'o'i ya fara tofa mata da alamu aljannin ba me wani fitina bane, cikin lokaci kankani ya tafi, tuna abinda ya faru yasa ta saka fuskanta cikin broad-chest dinshi ta fara kuka, bayanta ya dinga shafawa a hankali har ta tsagaita kukan tukun ya d'ago ta direct toilet ya shiga da ita ya sa hannu ya wanke mata face d'inta kan suka fito lokacin kusan 11 hakan yasa ya karasa da ita bakin gado ta kwanta ya lullu'bamata bargo tare da zama gefenta ya rike mata hannu.

Ba abinda yace mata itama haka har bacci ya d'auketa gyara mata blanket din yayi kan ya fice, direct zuwa parlorn diddi don duba lafiyar nuriyyah, Anty Rabi'ah ya fara tozali da se kuka take fuskanta yayi jazir idanunta sunyi zuru zuru, fad'a su mamaji suke mata akan abinda ta aikata, don miemie na shigowa da nuriyyah ta fad'awa su momma abinda ke faruwa daga ita har mahaifiyarsu cewa sukayi baza su ba a kasheta.

Bayan su mamaji sun gama hayaka ko ina shine suka zo nan din don sunga shigan Rabi'ah part din tana layi hannunta dafe da wuyanta, anan ne suka ji abunda ta aikata shine suke mata fad'a, bappa kam zagin cin mutunci ya mata har kaman ze mareta uncle nasir ne yayi ta basu hakuri har suka hakura, musharraf dake zaune gefe idonshi lumshe yana jin zagin da cin mutuncin da tayiwa hasken rayuwanshi yana tunanin da ya barta ma da khairin ya rufe kofar da key yayi tafiyarshi da keyn, kash wallahi yaji haushi.

Ita kam Anty Rabi'ah ba alamun nadama sema wani tukukin bakin cikin da takeji da aurenta da 'ya'yanta a zauna ana mata wannan rashin mutuncin sbd matar d'an yayarta duk waenda suke parlorn ji take kaman ta rufesu da duka har iyayen nata ko da tana buduruwa bazata iya tuna fad'an su bappa da diddi akanta ba sbd sanyinsu da hakurinsu amma gashi tsofe tsofe da ita an zauna ana yi mata fad'a kan wannan shegiyar da tunanuka fal ranta aka tashi taron.

Washegari khairi ta tashi fes ba wadda yayi mata maganan abinda ya faru jiya se ma hakurin da momma ta bata murmushi kawai tayi, da yammacin ranan sukayi walima inda manyan malamai da aka gayyato wasu tun daga kano sukazo suka baje fasaharsu a kan zaman aure da bautar da ke ciki, amare sun sha kyau cikin lafayarsu maroon me tsananin kyau da tsada, su hassana s Fagge na hango an natsu ana jin wa'azi, daga gaba gaba na hangi Anty wasia(ummu rijaal) itama zaune tana jin wa'azi da er joter d'inta tana jotting abubuwa masu anfani da ake fad'a, Chan na hango kawata sadiya muhammad sanye da orange lafayarta itama an natsu ana jin wa'azin.

Fatima Usman hadeija aka had'a da snacks da za'a ci a waliman inda tayisu masu shegen daad'i su samosa, spring roll, fish roll, fish pie, donuts da meat pie se drinks su aka ci a waliman, washegari da safe bayan an sauko juma'a aka d'aura aurensu d'aya bayan d'aya a

babban masallacin juma'an dake cikin garin dukku inda suka ga ruwan mahalarta wannan aure motoci kaman zasu fasa dukku sbd mutane to auren mutane biyar kuma ba laifi 'ya'yan masu harka da masu akwai.

Kwance take kan gado su Amrah da Miemie da wasu kawayen nurriyah cike da d'akin suna shan kwalliya sbd hoton da zasuyi kan wucewa gombe a ranar gabanta se fad'uwa yake da ta rasa dalili sanye take da tun kayan baccin safe ko wanka batayi ba bare maganan kwalliya, kaman a cikin dodon kunnenta takeji yadda masu busa algaita ke ta busawa maroka kuma nata shelan an d'aura an d'aura.

Tsaban gulma irin ta maroka na fad'i ba'a tambayeka ba suka dinga fad'an sadakin kowa, na nurriyah da aka fara d'aurawa dubu d'ari biyu, se na maryam dubu d'ari da hamsin, na zainab dubu d'ari, suna jira suji na khairi dubu hamsin se suka ji, "me gayya me aiki wato me kankat Alhaji Abubakar mahmoud Adam ya biya sadakin matarshi ummulkhairi farouq umar akan tsadadden set na gwal da kud'insu suka haura dubu d'ari shidda da hamsin" gud'a su Amrah da kawayen nuriyyah suka sake, momma kam seda tayi hawaye tsabar farin cikin abinda musharraf ya aikata don ko ita bata san sadakin da yayi niyyar badawa ba, hajiya ruqayyah kam seda ta tattaka don turawa Anty Rabi'ah da hajiya zulai dake zaune bakin ciki sadakin erta me uwa da uba da gata be kai ko rabin na wacce suke kira marar asali ba.

Shigowar text taji a wayanta a yayinda hawaye ke kwaranya daga ramin idonta zuwa kyakywar fuskarta, bata ta'ba tunanin zatayi aure me mutunci da daraja irin wadda tayi ba su momma sun gama musu komai, yayinda musharraf ya tabbata numfashinta, farin cikinta, sanyin idaniyarta ya kankaro mata daraja da ta tabbatar a fad'in family d'inta da nashi da kyar a samu wacce aka bada sadakinta da gold, karanta sakon tayi kasan makoshinta ga abinda sakon ke cewa "Alhamdulillah, finally Mrs Abubakar mahmoud Adam" kuka me sauti ta fashe dashi.

Su Amrah suka rufeta suna mata wakar ta zama d'auko riga, ta zama d'auko hula, ta zama d'auko kwano ta zama ta zama d'auko wando, wani kukan ta kara sakewa, bayan duk an wawatse zaune yake da dakakkiyar Farar Australian geztner da yaji d'inkin er ciki da babbar riga sabuwa gal har d'aukan ido yake kanshi sanye da hula zanna masu zare dark blue takalmin cover dake kafanshi ma dark blue hannunshi sanye da wata arniyar agogo ta kampanin Gucci golden se zoben zinari dake yatsarshi na tsakiya yayi kyau har ya gaji duk yadda ya motsa se kaji fitinannen kamshishi na tashi, wayan hannunshi yake kallo bayan ya tura mata sako datanshi dake kunne yake kokarin kashewa sbd sakkonin taya murna suke ta rige rigen shigowa, magana yake da haidar fuskanshi washe da fara'a kaman ba musharraf ba kowa ya ganshi ya san yau ranar farin ciki ne a gareshi.

Mistakenly hannunshi ya danna wani sako da number ne kad'ai har ze fita se kuma ya tsaya karantawa, a take ya mike, waro gabad'aya idonshi yayi kan wayan zuciyarshi na dukan tara tara ba ma uku uku ba, wani irin jiri ne ya d'ibe shi ba don haidar yayi saurin rikeshi ba da ya zube kasa Allah yasa ba mutane dayawa a wurin duk an tattafi, hannunshi haidar ya kama zuwa mota binshi kawai yake ba don ya san yanayi ba wani irin tashin hankalin da baze iya

kwatantawa ba yake ji, a haka suka shiga mota haidar na tambarshi ko lafiya amma ya kasa amsawa da kyar ya samu "Innalillahi wainna ilaihi rajiun" ya kubce daga bakinshi kan ya runtse ido hawaye ya fara gangarowa daga cikin kurmin idonshi.

2503 words

🤦‍♀️gosh nayi typing dayawa har hannuna na ciwo gaskiya harda na gobe😅 but idan naji ra'ayinku akan page din nan watakila ku samu gobe in Allah ya kaimu, me kuke tunanin musharraf ya gani ko ya karanta har ya shiga cikin wannan tashin hankalin?

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️8️⃣3️⃣▶️8️⃣4️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Gida haidar ya nufa dashi ganin yadda jikinshi ke rawa hawaye kuma yaki dena gangara daga fuskanshi, be ta'ba tunanin shi rago ne ba se yau ya kasa zuciyarshi ya kasa aminta da abinda ya gani sede ga sheda, suna isowa ya fad'a d'akinshi tare da datsewa don be son kallon fuskan kowa daga bakin kofan ya tsuguna tare da cire hulanshi ya tusa hannu cikin gashin kanshi duk jijiyoyin jikinshi a tashe yau ba don yayiwa momma alkawarin baze kara shan abun maye ba da ya sha giya, tuna akwai taba a d'akin yasa ya nufi wardrobe ya d'auko tare da cire babbar riganshi ya jefar anan ya zube ya kunna taban se kuma ya kasa sha, jefarwa yayinda karfi yana me naushin iska toilet ya fad'a ya sakarwa kanshi shower ba tare da ya cire kayan jikinshi ba.

Ya kusan minti talatin tsaye a wurin zuciyarshi be yi sanyi ba ji yake kaman an saka zuciyar a tukubar tsire tsabar Azaban zafin da yake mishi, why? Why? Why khair yake ta nanatawa da kyar ya samu yayi wanka zazzafan zazza'bi na rufeshi sbd abinda ya dami zuciyarshi da kuma ruwan sanyin da ya zubawa kanshi na about 30 minutes, a bayin ya kwa'be kayanshi tare da fitowa d'aure da towel ya zube kan gado yana lullu'buwa jikinshi kaman wuta.

Cikin tashin hankali haidar ke ta zarya a kofan d'akin don bugawar duniya musharraf ya ki bud'e mishi about 2hours kenan da shigowarsu tare ya barshi don yana tunanin yana son samun space in ya ware se ya dawo yaji abinda ke faruwa, amma har anyi hotuna mutane duk sun

watse an koma gombe don shiryawa dinner yanzu a gidan daga momma se su dadda da su uncle Ahmad, momma ma ta shirya zata wuce kenan ita da hajiya ruqayyah.

Da sauri haidar ya fita ya tare ta yana cewa "momma, maami akwai matsala" Da mamaki suke kallonshi a tare sukace "matsalan me? Ina musharraf?" Shiru yayi na mintuna kan ya fad'a musu abinda ke faruwa momma da tun d'azu take fad'an kin zuwan musharraf a d'auki hotuna kuma tayi ta kiran layinshi be d'aga ba, a rude tayi d'akin suka rufa mata baya itama maganan duniya musharraf be bud'e ba.

Su bappa ta kira a lokacin har hawaye ya fara zarya idanunta me musharraf ya gani haka? Da spare key din part d'in mamaji yazo lokacin duk waenda suka saura a gidan sun cika kofan, bud'ewa uncle Ahmad da ya kar'bi key din yayi a tare suka fad'a d'akin cikin wani hali suka samu musharraf da yasa momma kusan fad'uwa yana kwance ne kawai shi da gawa ba maraba kuka ta saka tana sulalewa kasa, dadda ce ta kamata haidar ya karasa da gudu ya ta'ba pulse dinshi yaji yana har'bawa a hankali ajiyar zuciya ya sauke yana cewa "he's alive we just need a doctor" uncle nasir yace "saka mishi kaya Aliyu se mu wuce cikin gombe kawai" nan suka fita dadda na rike da momma da ta kasa dena kuka se kace an ce mata musharraf din ya mutu.

Cikin lokaci kankani sukayi asibiti dashi inda suka bar mamaji, diddi da dadda a gidan, uncle Ahmad, uncle nasir, hajiya ruqayyah, bappa, momma se haidar ne suka wuce dashi, cikin hanzari akayi emergency dashi Doctor Aslam da wasu doctors din suka fad'a d'akin, sunanan zaune kusan hour uku a lokacin har magrib ya gabato doctors basu fito ba, uncle Ahmad ne ya d'aga waya ya kira marwan kai tsaye yace mishi "a fasa dinner din nan musharraf na asibiti ba lafiya" cikin damuwa yake tambayar me ya sameshi uncle Ahmad ya sanar dashi doctors basu fito ba har yanzu.

Abunka da gidan buki nan take maganan ya bazu ba dinner amma ance za'a kai amare gidansu a daren sbd musharraf ba lafiya shiyasa ba za ayi dinner ba, mutane dayawa sunji haushin hakan amma ya suka iya, khairi kwance a d'aki dada na zaune gefenta tana mata er nasiha da kad'an kad'an akan zaman aure don su se gobe zasu wuce Abuja a tsarin da sukayi tun farko don a Abuja aka shirya duk wani kayan d'akinta sbd musharraf be da wani gida anan part d'inshi kuma yayi karami amma In sun zo nan zasu dinga sauka.

Amrah ce ta fad'o d'akin ko sallama babu tace "Khairi musharraf ba lafiya yana asibiti" a zabure ta mike ta zauna tana dafe kirji tace "innalillahi wainna ilaihi rajiun me ya sameshi? Amrah me ke damunshi?" Amrah tace cikin damuwa har yanzu doctors basu fito ba almost 3 hours kenan a sume aka sameshi a d'akinshi na chan dukku" hawaye ne ya fara gangarowa khairi me ya sameshi har haka bayan basu wuci awa shidda da magana dashi ba wayanta ta d'auko ta kunna fuskan hotonshi ne sanye da kayan daurin auren na d'azu yana gyara babbar riganshi aka d'auka fuskanshi cike da murmushi.

Kuka ne ya kwace mata tana ji dada na ta mishi adu'ar samun lafiya, Khairi tace "Dan Allah dada Ina son zuwa na dubashi" dada tace "Ashe baki da kunya? Kina Amaryan ko fah gidanshi

ba'a kaiki ba, bama haka ba ga en buki ba wadda ya tafi" kuka me sauti khairi ta sake tare da komawa ta kwanta tana nan kwance har su Amrah suka tafi kai nuriyyah din momma tace kar suje asibitin su raka yarsu ta kuma wakilta hajjiya ruqayyah tazo tayi mata fad'a dukda gidansu Marwan da gidansu duk abu d'aya ne yayisu amma seda hajiya ruqayyah tayi mata fad'a sossai kaman yadda momma zata mata kan aka tafi da ita se kuka take gidan duk an tafi kai nuriyyah yayinda waenda suka rakata In sun ajiyeta zasu raka maryam daga chan su dunguma raka zainab.

Bayan sun tafi ne hajiya ruqayyah ta shiga wurin dada, tana d'aura idonta akanta seda jiri ya so yarda ita wacece wannan haka me tsananin kama da innanta kukan da khairi keyi ne yaja hankalinta tayi sallama a sanyaye dada ta amsa hajiya ruqayyah de ta rud'e hakan yasa ta d'aga waya ta kira innanta tace "inna naga wani abun alajabi a gidan hajiya fatima" daga d'aya bangaren aka ce "ke kam ko yaushe zaki girma oho ruqayyah, wani irin abun alajabi ne da ze sa ki kirani a waya kina fad'amin" hajjiya ruqayyah tayi murmushi kan tace "naga me kama dake wallahi har muryanku iri d'aya" Da sauri Hajiyar dake zaune a wani tangamemen parlor ta mike tace "da gaske ruqayyah kar ki saka min ran ganin indo ko danginta In zo In samu ba haka bane" hajiya ruqayyah tace "nima wallahi ban tabbatarba amma gamu nan zuwa" ta fad'a tana kashe wayan.

Kallon khairi tayi tace "ummulkhairi tashi dan Allah ki bani Aron dadanki muje innanmu ta ganta wallahi suna tsananin kama" Khairi tace "ba komai Maami muje In raka ku" kallon dada tayi tace "dada itace hajiya ruqayyah da nake baki labari maami" godiya dada zata fara mata dukda maganganun da taji matar tayi ya matukar d'aga mata hankali da sauri tace "ba yanzu ba Dan Allah muje na san inna na chan tana zullumi" kama dada tayi da kanta suka fice khairi na binsu a baya har motan hajiya ruqayya driver yaja.

Wani unguwa da khairi bata ta'ba shiga ba suka shiga tare da horn a kofar wani katon gida, gateman dinne ya leko ganin motan gidan hajiya ruqayyah yasa ya koma ya bud'e suka shigo masha Allah gidan babba ne sossai gidan sama guda biyu suna facing juna se wani karamin part flat dake tsakiyarsu daga baya akwai wani flat din bayanshi wadda suna bangan kwanonshi, a parking lot driver yayi parking suka fito gidan shimfide da interlocks ga flowers ko ta Ina.

Karamin flat dinnan hajiya ruqayya ta nufa dasu tare da tura kofan babban parlorn da sallama, da mamaki khairi ke kallon farar bafullatanan dake zaune sanye da glass a idonta gefenta sanda ne me kyau da alamu shi ke taimaka mata wurin tafiya tana d'aura ido akan dada ta mike har gabanta hajiya ruqayyah takai dada tace "kin ganta inna baki ga kamanku ba?" Kuka inna ta fara tana rike hannun dada Haka kawai dada taji matar ta shiga ranta irin sossai din nan.

Musamman yadda ta rike hannunta take kuka dukda ba kallon matar take ba bayan tayi kukanta ma ishi kan ta zauna tana zaunar da dada gefenta khairi ma zama tayi inna tace "gayamini wacece ke? Me sunan mahaifinki da mahaifiyarki? Daga Ina kike haka kikayi kama da kanwata sossai?" Dada batayi musu ba ta bata labarinta inda ta fad'amata sunan mahaifinta bata san

sunan mahaifiyarta ba sede ta fad'a mata kauyen da aka aurota.

Cikin farin ciki inna tace "ke 'yar indo ce wallahi don Ali gamji mahaifinmu yaba aurenta tana da shekaru sha hud'u, kuma fulani me yawo ne sossai da shanukanshi, na d'auka har abada bazan ga jininta ba, Alhamdulillah Allah yaji kanta ya gafart mata" kallon hajiya ruqayyah tayi ta tambayeta "ke ruqayyah Ina kika samo su?" Nan hajiya ruqayya ta bata labarinsu inda momma ta bata, seda tayi hawaye ta kama khairi ta rungume murnan da khairi da dada suka shiga ba kad'an ba dukda dare yayi kusan goma hajiya ruqayyah ta kira momma ta fad'a mata Ashe su khairi en uwansu ne iyayensu mata uwarsu d'aya ubansu d'aya gashi yanzu ta kawo ta wurinta, dukda tashin hankalin da momma ke ciki hakan be hana ta nuna jin daadinta ba sossai tace a bata dada, ta taya ta murna khairi kam dama duk murnan da takeyi zuciyarta a chunkushe yake da rashin sanin halin da mijinta ke ciki, tana ji hajiya ruqayya ta tambayi ya jikinshi momma tace "hmmm gashinande har yanzu be farfad'o ba doctors din sun fita amma ba wadda yace mana komai" Adu'a hajiya ruqayya tayi mishi kan ta mikawa inna tayi mishi adu'a itama yayinda momma ta tayata murna don duk wadda ke tare da inna se ya san labarin indo.

Inda inna ta roka su khairi su kwana wurinta zuwa gobe se ta kawo mata khairi ta d'auki nabeel da nabeela da dada, dukda momma bata so haka ba taso ta zauna da su dada har mutuwa ya raba amma ya ta iya jini yafi gaban komai aka ce blood is ticker than water kuma ta san dadan ma zata fi son zama da en uwanta da "Toh inna" kawai momma ta amsa tare da musu seda safe.

Khairi kam hawaye ta dinga sharewa a fakaice ita kam tana son ganin mijinta wallahi inna dake ba masu aikinta umarnin abubuwan da zasu kawowa su khairi ce ta lura cikin masifa irin ta tsufa tace "eyeeeee kunga marar kunya, 'yar zamani yanzu akan wanchan sarkin had'e ran kike kuka? Mutum kullum fuska kaman an aiko mai sakon mutuwa ko kyauta aka bani shi bazan kar'ba ba sema In kai kasuwa amma shine kike 'bata hawayenki?" Shiru khairi tayi tana tura baki murmushi hajiya ruqayyah tayi kan tace "daughter rakani mota In tafi gida" mikewa khairi tayi ta raka ta.

A hanya hajiya ruqayya tace "ba kuka zaki dinga yi mishi ba ki mishi adu'a in shaa Allahu ze samu lafiya and I promise yhu gobe before eight zanzo mu tafi tare sannan karki damu da inna fah In tana miki irin maganganun d'azu a wasa takeyi kuma dama kullum In musharraf ya rako haidar wurinta se sunyi fad'a" murmushi khairi tayi tace "Toh Maami" kallon two storing buildings din dake gidan tayi tace "ga gidan uncles dinki guda biyu yayyuna kenan da safe duk zaki gansu" Kai khairi ta gyad'a Bayan sun isa mota tayiwa maamin seda safe kan ta koma.

Nan inna ta dinga hidima dasu ina za'a d'aga ina za'a saka, har seda dada ta hanata da kyar ta barsu ta je ta kwanta, suma kwanciya sukayi a katon d'akin da ta saukesu me kama da aljannan duniya don ba abunda babu a d'akin, bayan dada tayi bacci ta dinga kiran layin musharraf amma a kashe haka ta tasa hotunanshi na wayanta tana kallo da taga baze anfaneta ba kawai ta mike ta fara kai kukanta ga Allah har seda taji bacci ya kamata sossai kan ta kwanta bayan tayi adu'an bacci.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️8️⃣5️⃣▶️8️⃣6️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Washegari bayan sunyi sallahn asuba inna ta shigo suka bude shafin hirar indo da dada, ta bata labarin lokacin da aka aurar da indon ita bata sani ba tayi aure anan cikin gombe zuwa billiri kawai tayi ta samu an aurar da kanwarta tayi bakin ciki sossai gashi iyayensu su biyu suka haifa, a lokacin ta haifi 'ya'yanta duka uku Muddasir, Muzzammil, da ruqayyah, bayan auren indon da shekara biyu Allah ya kar'bi ran iyayensu sanadin gobara yanzu en uwa ne kawai a 'billiri 'ya'yan muddasir bakwai yayinda muzzammil ke da shida dukkanninsu mata bibbiyu suke da se 'ya'yan ruqayyah biyu.

Misalin karfe takwas part d'in inna ya cika da jikokinta a lokacin ta saka dada da khairi sunyi wanka da breakfast duk wadda ya shigo zatayimishi bayanin dada da khairi kuma se aka ci sa'an basu da wulakanci kwata kwata familyn da murna suke taran su en matan suka ja khairi zuwa cikin gida duk da yadda take suku suku sbd bata san halin da musharraf yake ciki ba.

Suna zaune a d'akin en matan da ke part d'in uncle muddasir da suke cewa dad shima sun gaisa da khairi a lokacin da suke shigowa be santa ba kuma yaran basu fad'a mishi wacece ba, hira sukeyi amma gabad'aya hankalinta baya tare dasu su shidda ne en matan duk kuma sa'annin ta ne hafsat da taci sunan inna, Asiya, fatima, firdausi, Asma'au se hauwa, hira sukeyi kaman ba 'yan kishiyoyi kuma ubbanninsu daban daban ba hakan ya tabbatarwa khairi tarbiya da had'in kan dake gidan ganin taki sakewa se kawai suka koma hiran su ya sa su ci gaba da hiransu su ya su akan waliman da zasuyi na kammala secondary, wani karamin yaro ne ya shigo da gudu yana cewa "Adda Asma'u wai kizo inji Anty Ruqayyah" kan Asma'u ta mike khairi ta mike hauwa tace "har mun gama hiran kenan?" Khairi tace "A'a In na dawo zamu ci gaba, fita zamu yi da Maami" Firdausi tace "Toh se kun dawo" sauran ma suka ce se ta dawo da asma'u suka fice zuwa part d'in inna tana kara yi mata bayanin yaran gidan amma jinta kawai khairi ke yi bata fahimta.

Suna shiga ta duka har kasa ta gaida Maami cikin fara'a ta amsa tana tambayarta ya bakunta murmushi kawai tayi tana kallon hafsan maamin da suka rungume juna da Asma'u tana saketa itama tayi hugging dinta tana cewa "welcome to the family sis" murmushi kawai khairi tayi tare da zama kusa da inna, Maami ta kalli khairi tace "kinga nace zanzo 8 gashi har 8 ya wuce, tashi muje na cewa hajiya fatima Ina zuwa" mikewa khairi tayi da sauri dama da hijab a jikinta inna tace "er kusun uwa daad'i miji".

Kai ta dukar tana cewa "dada mun tafi" dada tace "ki gaisheshi da jiki ki kuma gaida mommanku" bata amsa ba sbd masifar inna se ma ficewa da tayi Maami ta bi bayanta tana

cewa "se mun dawo" bayan fitansu Asma'u tace "yanzu inna khairi na da aure?" Inna tace "Eh mana ita kuma aka gayamiki kaman waenchan dalotayen yayyunkun nan ne da zasu ce se sun gama makarantar jami'a kan suyi aure, Toh da aurenta jiya da safe aka d'aura mata aure".

Asma'u tace "Kai inna tambaya fah d'aya na miki amma kin ban amsa uku, Toh me yasa ba'a kaita gidanta ba ta Kwana a gidan nan?" Hararanta inna tayi tace "ban sani ba" Hafsa tace "kyale innan nan muje zan fad'a miki" fita sukayi hafsa na mata bayanin abinda yasa ba'a kaita ba.

Da sallama hajiya ruqayyah ta tura d'akin asibitin khairi na biye da ita a baya momma ce kad'ai a d'akin tana zaune kan kujera shi kuma yana kwance sambal akan gado daga shi se dongon wando baki, fatanshi yayi fari sossai fuskanshi fayau idonshi a lumshe kaman me bacci amma sam ba baccin yake ba duniyar tunani ya fad'a me yayiwa ubangiji da ya tsinci kanshi a wannan rayuwa, da sauri kuma yayi istigfari ko ya yayi da idonshi hoton da aka turomishi yaki barin idonshi sam.

A jikinshi yaji zuwanta wurin me makon yaji sauki se yaji wani irin haushinta na mamaye zuciyarshi yana jin muryanta kuma a lokacin da take gaida dada se yaji kaman ya had'iyi zuciya ya mutu ya rasa me yasa sonta yaki ko da raguwa a zuciyarshi kaman yadda ya tsani surraya lokaci guda, wani kunyan momma taji tana ji dukda sabon dake tsakaninsu, bayan sun gama gaisawa ne hajiya ruqayyah tace "ya mai jikin dai har yanzu be farka ba?".

Momma tace "da sauki kuma tun tsakar dare ya farka amma wallahi ba yadda banyi ba ya gayamin me ya sameshi me ke damunshi yaki fad'a min komai bayan musharraf baya ta'ba boyemin komai" ta karasa da damuwa tuna irin damuwar da take hangowa a kwayar idonshi, hajiya ruqayyah tace "ki kwantar da hankalinki aminiya in shaa Allahu ze samu sauki kuma wtkl be son fad'amiki matsalarshi ne sbd kuna asibiti" momma tace "hmmm toh Allah yasa" ita kam khairi tsaye tayi tana mamakin me ya sameshi kuma me ke damunshi da har ya shigar dashi wannan hali.

Maganan momma ne ya dawo da ita daga tunaninta inda take cewa "daughter ki zauna dashi bari muje da hajiya ruqayyah gida sbd bakin da na tara" Khairi tace "toh momma" gyalenta ta yafa tana mikewa, hajiya ruqayyah ma ta mike a tare suka fita Bayan ta kalli fuskan musharraf tace "mun tafi" don ta san idonshi biyu ne kawai yasa ya amsa ta kasan makoshi, bayan fitansu khairi ta karasa bakin gadon ta zauna cikin kasa da murya tace "baby ya jiki?".

Shiru yayi kaman be ji ba ta kuma cewa "sannu hamma kayi breakfast?" Nan ma Shiru yayi a take hankalin khairi ya fara tashi bata daddara ba tace "Hamma musharraf" tsaki yaja yana juya kwanciyanshi tare da bata keya hawaye ne ya cika idonta se jin saukowansu tayi akan kuncinta komawa d'aya 'bangaren tayi tace "Hamma laifi nayi maka ne? Plz in wani abu na yi maka da ba daidai ba ka fad'amin In baka hakuri ba wai kayi fushi da ni ba" nan ma Shiru yayi d'an Shiru tayi tana tuna ko tayi mishi wani laifi da bata sani ba da sauri tace "ko don ban zo ba se yau?" Bata jira cewarshi ba ta kara da.

"Ka san mun sami en uwanmu? Ashe mahaifiyar maamin haidar Addan mahaifiyar dada ce" tsaki yayi tare da bud'e jajayen idanunshi yana kokarin mikewa yana taune lips hannu ta sa da niyyan taimaka mishi da sauri ya matsa yana cewa "don't yhu dare touch me" yayi maganan cikin danne hakwara da alamu controlling kanshi yake kokarin yi.

Baya ta matsa tana kallonshi, zama yayi tare da jingina bayanshi da pillow wuri d'aya ya kafawa ido yana ji a jikinshi kuka take ko be kalleta ba, wani abu yake ji ba daidai ba a zuciyarshi tuna irin wahalhalun da tasha ya fara daga farko har karshe to me ze jefata aikata zina da irin wannan rayuwar da tayi, ko de sbd ta taimaka musu da abinda zasu ci ko kuma samun wurin zama?.

Jin an turo kofan yasa shi kallon wurin se yaga haidar ne ya shigo, murmushi haidar ya sake ganin abokinshi zaune da alamu lafiya ya fara samuwa, yana zama yace "dude how far" yayi maganan yana mika mishi hannu kashewa sukayi amma fuskan musharraf ba ko d'igon fara'a yace "not too far friend" se a lokacin haidar yaga khairi cikin sake fuska yace "aa aa aa Amarya da kanta ce nan  ai ban lura dake ba" a fakaice ta share hwayen fuskanta tana murmushi tace "Ina kwana?".

Yace "lafiya kalau sister ya gajiyan buki?" Tace "Lafiya kalau, Ina Anty hanan" yace "tana gida se anjima tace zata shigo, welcome home dear Maami ta ban labari" murmushi kawai tayi, kallon musharraf yayi da ya kara had'e rai yace "ka kula min da kanwa na gayamaka da tun kafin bukin na sani ma da ban baka ba se kayi biyayya" Kau da maganan musharraf yayi da cewa "Ina wayata?" Hannu haidar yasa a aljihu ya d'auko mishi tare da mika mishi kar'ba yayi yana kunnawa don kashe yake.

Sam be da shakku akan haidar ya san be bud'e wayan bama balle yayi bincike har yaga abinda be son kowa ya sani kuma ya gani, hira haidar da khairi da ta koma ta zauna akan plastic chair suka ci gaba dayi dukda hankalinta dake a tashe amma bata son kowa ya sani tana ganin karamin sa'banine kuma zasu shirya bata so ace daga aure har sun fara samun matsala da shi har mutane su sani.

Tambayoyi haidar ya dinga mata akan rayuwansu na da tana bashi amsa, har hiran randa aka so mata fyad'e seda ya tambaya da kuma ranar da kare ya bita a Arabian estate, bashi labari tayi a tsanake abinda ya kaita anan yake ce mata "Ai ranan na kama mijinkin nan ya rakani gidan sister dina, au sister dinmu dani da ke 'yar uncle mudasir babba dake aure achan Adda fadeelah" Da mamaki tace "inda kuke zaunen shine kofan gidanta?" Yace "Eh kin shiga ne?" Tace "eh matar na da kirki sossai ba kad'an ba" ta bashi labarin yadda sukayi da ita yana murmushi yace "ai haka take da kirki wallahi ta jima da aure amma Allah be bata haihuwa ba har yau" Tace "Allah sarki Allah ya bata" yace "Ameen".

Su Amrah ne suka shigo gabad'ayansu harda nabeel da nabeela da gudu sukayi kanta suka rungumeta tana dariya Tace "chutu'be" suka had'a baki wurin cewa "Adda khairi good morning"

Tace "morning how are yhu? Ina pretty?" Nabeel yace "tana zuwa da Adda Miemie, Adda Ina kuka tafi ke da dada?" Khairi tace "wurin innan dada kakanku kenan" nabeela tace "dama dada nada mama?" Ta fad'a cikin waro ido Haidar ya lakaci hancinta yace "wa ye kika ta'ba ji ya fad'o daga sama" dariya sukayi kan suka gaishe shi ya amsa a lokacin Miemie sun shigo Amrah kuma na gaisawa da khairi wurinshi su nabeel suka koma suna tambayanshi me ke damun shi khairi ta zata suma baze amsa musu ba se kuwa ta ga akasin haka cikin sake fuska ya amsa su, haka da su Amrah da miemie ya amsa musu fuskan ba laifi.

Har cewa Amrah yayi ta sa mai abinci, da sauri khairi ta kalleshi amma ko 'bangarenta be kalla ba haka Amrah ta sa mishi breakfast yaci kaman baya so bayan ya gama wai ze yi wanka haidar ya taimaka mishi ya raka shi toilet din ya dawo, haka tana ji tana gani suka wuce ta gefenta kaman be santa ba, wayanta ta d'auka ta duba last chats d'insu zallan soyayya ne haka msg na karshe da ya turo mata shine na d'aurin aurensu Toh me ta mishi?.

Sossai ta tsinci kanta a matsanancin damuwa to ba wai ya santa bane a matsayin mace bare tace dama chan jikinta yake so ya kuma samu ze mata abinda ya ga dama, Ashe ya manta be d'auki kayan da su Amrah suka kawo mishi ba hakan yasa yayi magana daga chan akan haidar ya miko mai, haidar kuma se ya mikawa khairi yace "sister bashi" kar'ba tayi ta mike ta nufi cikin bayin knocking tayi se yace "come in" duk a zatonshi haidar ne, ita kuma batayi magana ba ta tura kofan ta shiga.

'Dago kan da zaiyi kenan se suka had'a ido d'an fara'an da ya saura a fuskanshi ya had'iye tare da had'e rai kaman an aiko mai da sakon mutuwa hawaye ne ya fara zuba a idonta daman kukan na kusa cikin kasa da murya tace "Don girman Allah hamma ka fad'a min laifin da na maka In baka hakuri wallahi ban san me nayi maka ba, fushinka na azabtar dani ka sabar min da kulawa da soyayyarka a kullum me yasa zaka gujeni yanzu?".

Kayanshi ya fisge ya fara sakawa kallon shi takeyi daga shi se towel a kwankwaso ginennen jikinshin nan ya fito sossai ba kaman a kaya ba kaman d'aura mishi akayi, ganin yana shirin cire towel din yasa tayi saurin juyawa se akan idonshi tsaki yaja a fili yace "kaman da gaske" yana sa buttons din farin riganshi da ya d'aura akan Ac Milan trouser black and red yace "I really hate yhu ummulkhair, yhu deceived me and my family and ki jira sakayya wallahi kin cuci zuciyata cuta mafi muni a duniya da ba wadda ya ta'ba yi min irinshi amma Ba komai yadda kika tsara haka za'a ci gaba da tafiya" murmushin takaici yayi kan ya furta "green snake under green grass" ya juya ya nufi fita amma jikinshi da ba karfi yasa yayi tagal tagal kaman ze fad'i da sauri ta tare shi dukda idan da faduwan zeyi sede su fad'i dukkansu don bata da wannan karfi na taranshi, da sauri ya sa hannu ya turata har ta buge da jikin gini kan ya ja tsaki ya fice a hankali.

kuka ta sake tana tana dafe goshinta da tafin hannunta ba wai kukan bugewa da tayi takeyi ba kuka take akan maganganun da ya gama fad'a mata me tayi da zafi haka innalillahi wainna ilaihi rajiun ta dinga maimaitawa tana kuka da kyar ta samu kukan ya tsaya ta wanke fuskanta ta fito kallo d'aya ya mata ya d'auke kai, haidar ne ya tambayi me ya sameta tace kwaro ne ya fad'a idonta, haka tayi yinin ranar sukuku a asibiti a gida kuwa har dada da inna sunje wurin momma

dasu Alhj mudan da Alhj muzammil godiya sossai sukayiwa momma inda tasa aka had'a kayan nabeel da nabeela da kuma na dada khairi kam nan zata ci gaba da zama har se mijinta yaji sauki su wuce Abuja.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION

(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️8️⃣7️⃣▶️8️⃣8️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Two weeks later

Rayuwa yaci gaba da tafiya wa khairi a birkice sbd bata san laifinta ba ake hukuntata hakan kuwa yafi komai mata ciwo musamman In ta tuna irin soyayyarsu me kashe zuciya da irin kulawar da yayi alkawarin nuna mata bayan aurensu amma gashi yanzu kwana goma sha biyu da samun Lafiyanshi.

Sunyi kwana biyu a gida tare da su momma kan ya shirya da niyyar komawa Abuja inda yace ze barta nan, nan fah momma da bata gane mishi ba kwata kwata a kwanankin tace be isa ba kaman yadda suka tsara da matarshi da little zasu tafi a sata a makaranta achan haka khairin ma results dinsu na fita ze nemar mata admission a chan.

A haka be so ba suka taho Abujan a maimakon jirgin da yayi niyyar bi ya fasa suka tafi a mota, tunda suka je a kwana goman da sukayi zatayi girki ta jera a dining amma ko kallon arean dining din baya yi, haka ze wuce sama dama d'akin kasa ya bata ya kuma ce kar ta kuskura ta hau mishi samanshi ko da bakin wasa.

Da little kad'ai yake d'an sakewa har ya ja ta saman wani lokacin har kwana takeyi amma khairi bata ta'ba hawa ba, yaron dake gyara mishi tun kan zuwanta shi ya ci gaba da gyara mishi abun na damunta ba kad'an kad'an ba amma ba yadda ta iya be bata fuskan tambayanshi laifinta ba bare ta kare kanta.

Kaman yau Bayan ta gama shirya little da sabon uniform d'inta na Hempstead da aka maida ta ta fara daga primary one, janta tayi zuwa kan dining tare da zuba mata irish and egg se tea da tayi musu ta fara ci ita kuma ta koma kitchen ta had'a mata lunchbox dinta, ta fito dashi ta ajiye a gefen jakanta dake d'aure saman dining se surutu take zuba mata amma da kyar take amsawa sbd yanzu magana ma na neman gagaranta, takun saukowanshi ta fara ji ko bata juyo ba kamshinshi da ya bule parlorn ya tabbatar mata da ya had'u yadda ya saba cikin suit dinshi na office.

A hankali ta juyo ta kalleshi aiko a shirye yake cikin 3 pieces suit d'inshi brown da farin shirt se brown necktie hannunshi rike da black brief case dinshi fuskan nan a matukar had'e kaman

kullum tun dawowarsu maroon lips dinshi a cikin bakinshi yana d'an tsotsa ya karasa dining din gaban 'yarshi ya tsuguna yayinda ko matan bata ishe shi kallo ba.

Little tace "good morning paapi" yana d'an sake fuska yace "morning sweetheart how was your night?" Tace "fantastic paapi, mom tace kullum In zanyi bacci se nayi alwala In kuma yi adu'a shed'an baze zo kusa da ni ba and she's right I'm always sleeping good with no dreams and shetan around me".

Satan kallon khairi yayi se yaga kanta kasa tana wasa da yatsun hannunta kallon seconds yayi mata ya fahimci raman da ya bayyana a jikinta fatanta da yayi wani irin kyau da yalki sbd gyaran da aka mata na buki se d'aukar ido yake lumshe ido yayi yana tuna laifinta ya gama yanke shawaran abinda ze yi kuma In shaa Allahu ze sanar da ita a yau ba se gobe ba, kallon little yayi yace "that's good but she's not your mom, your real mom is already gone".

Da sauri khairi ta kalleshi hawaye na cika idonta little tace "but paapi yhu told me that she's my mom and haka granny ta fad'amin that's why muke rayuwa gida d'aya a tare but meyasa yanzu zaka ce she's not?" Had'e rai yayi yace "na riga na fad'amiki am off to work" hanyar waje yayi khairi tabi bayanshi da sauri har seda suka fito kofan parlorn kan ta sha gabanshi dayake gidan ba daga kana fita bane zaka hango masu gadi, drivers da me bawa flowers ruwa kofan main parlorn a corner yake.

"Ina kwana" ta furta a sanyaye muryanta na cracking Shiru yayi yana kallon fuskanta yana mamakin irin son da yake wa yarinyar nan but she end up disappointing him ya rasa me yasa sonta ya ki barin zuciyarshi se ma tausayinta da ya fara ji a kwanan nan, ganin be amsa ta ba yasa tace "bakayi breakfast ba zaka fita?" Kaman ba ze yi magana ba amma ganin yadda tayi maganan a gajiye ga hawaye dake gangara daga fuskanta yasa shi cewa "am full" tare da ra'bawa gefenta ya fice daga gidan.

A wurin ta zauna tare da had'e kai da gwiwa hawaye na zuba a fuskanta sossai fin na farko, fitowar little tana kiran "Mommy, mommy, cutie" yasa khairi d'agowa ta share hawayen fuskanta tace "pretty har kin fito? Kin koshi kam" little tace "yes mommy" Khairi tace "Toh baby kije driver na jiranki banda rashin ji da tsokana plz always what?" Little tayi saurin cewa "listen to ur teachers" murmushi sukayi wa juna kan ta wuce tana cewa "bye bye mommy" Khairi tace "bye dear" da gudu tayi hanyar waje khairi kuma ta koma.

Shara tayi da moping na just kasa ta d'aura abincin rana don gama ayyukanta da wuri take jollof rice da yaji veggies tayi da salad ta zuba a wormers d'inta masu rike zafi sossai ta shirya su a dining area tare da rufe kan da wani farin abin saki kitchen ta koma ta gyara ta wanke abinda ta 'bata seda ta tabbatar komai tsab a gidan se kamshi dake tashi kan ta rufe kofan parlornta ta shige room dinsu da little tayi kwanciyarta sossai ta yabawa hajiya ruqayya da taimakon da tayi musu, taimako zata ce don lokacin da tayi mata kayan d'aki bata san su en uwa bane, kayan kasan nan gabad'aya itace tayi dukda one bedroom ta shirya saura two bed rooms din Ba komai ciki amma kujerunta na parlor da suka kasance Ash and black masu kyau ne sossai haka

kayan kitchen komai me ma'ana ta saya mata kuma sun kara mata kayan kitchen sossai ma kan dawowarsu suka kuma yi alkawarin shirya mata sauran rooms din kasan.

Wayanta ta d'auka tare da bud'e data family group da aka sata ta shiga taga se hira ake tsakanin juna dukda bata san wasu dayawa ba amma ta san en mata shidan nan da Hafsat din hajiya ruqayya da kuma haidar akwai Adda Fadeelah, Adda haneefa, Hamma Bashir, hamma faisal, Adda Marwa se hamma jamal, se yaron cikinsu wadda ze yi sa'a da su nabeel me suna Isma'il suna kiranshi Ameer.

Hira suka fara janta dashi ganinta online Ai ko ta biye musu suka dinga hira ta lura familyn akwai respect amma ba wani nuna isa da iko sbd yaran suna hira da yayyun kaman abokai har hotonta su Hamma Jamal suka ce se ta turo musu sun gani don su suna karatu ne a india, haka ta tashi ta gyara d'ankwalin atamphar jikinta ta yafa tare da d'aukan hoto ta tura musu aiko suka dinga santin kyaunta tana musu dariya.

Adda haneefa tace "Amma da kina da babban yaya ba abinda ze hanani makale mishi ya aureni sbd na san shima ze yi kyau" Hamma bashir yace "kinga kuwa twins?" Tace "su kuma su waye" hasiya tace "sibling d'inta nabeel da nabeela" Maryam ta turo hotonsu tace "kin gansu" wow wow Adda marwa tace kan suka fara muhawara akan wa ya fi kyau tsakanin khairi da twins.

Tuna d'an uwanta tayi se taji hawaye da yana nan da yanzu shima yana cikin wannan group suna shan dariya dukda su maryam d'inma kyawawa ne sossai kuma farare amma se wani santin kyaunsu suke dukda ta san bata fi su kyau ba, cewa tayi "nima ina da twin brother" kowa ya fara jefo mata tambaya Ina yake me yasa basu ganshi ba waye waye, basu labarin 'bacewarshi tayi nan kowa ya fara turo sad faces da sorry masu adu'ar Allah ya bayyana shi nayi, godiya tayi musu.

Adda Fadeelah ce tace "d'an Allah khairi kiyi mana voice note din labarinku muna son ji" dukda bata so ba amma ta san bazata iya cewa bazatayi ba nan de tayi musu voice note na about an hour, dukda ma tayi briefing kuma bata fad'i wasu abubuwan ba, kowa seda yayi voice matan kam ba wacce batayi hawaye ba  haka de suka ci gaba da hira suna tsinewa hauwa da mamanta daga baya kuma suka saki zancen suka koma hiran bukin Adda haneefa da Adda marwanatu da za'a yi nan da five months.

Abinda kenan ya debewa khairi kewa tana jin daadin kasancewarta da family d'inta, ta yaba sossai da hankalin Adda Fadeelah tunda taje gidanta ta gani tana son yin wani important magana da ita akan matsalanta da musharraf bata son yi da Amrah sbd kanwarshi ce kuma tana ganin itama batayi hankalin fahimtar abinda yake faruwa ba har ta bata shawara hakan yasa ta d'auki numbern Adda Fadeelah tayi saving tare da danna call.

Bayan ta d'aga tace "Khairi ya kike ya gidan ki?" Khairi tace "lafiya kalau Adda, Adda kin ganeni?" Fadeelah tace "wani irin ganewa khairi mun ta'ba had'uwa ko?" khairi ta tuna mata,

Take kuwa ta tunata nan ta dinga jimami da dana sanin kin bata aiki da tayi cikin dariya khairi tace "ba komai Adda haka Allah ya tsara kuma Ai ra'ayinki kika fad'amin am very sure har yanzu baki da mai aiki" Fadeelah tace "hakane".

"Adda wani magana nake son muyi dake akan matsala da muka samu da Hamma musharraf" Fadeelah tace "matsala da musharraf kuma? Toh Ina jinki khairi" nan khairi ta bata labarin komai ta karasa da fashewa da kuka, Shiru fadeela tayi na mintuna kan tace "kenan akwai matsala, amma Haka kawai musharraf baze yi miki haka ba sbd hankalinshi da hangen nesan shi why not in ya dawo aiki yau ki sameshi ki roke shi sossai fiye da yadda kikeyi da akan ya fad'a miki laifinki.

Ina kyautata zaton sharri aka yi miki wadda shi kuma ya kasa zama dake ya tambayeki gaskiya ne ko karya don ze ji tsoron amsan da zaki bashi" bayanai ta dinga mata akan yadda zatayi cikin damuwa khairi ke amsata har ta gama bata shawaran suka kashe waya tana mamakin me ta tarewa wani ko wata da zai so kin zaman lafiyanta a d'akin aurenta.

Bayan dawowar little tayi mata wanka tare da sa musu abinci suka ci tare sukayi sallahn kan suka zauna kallo a parlorn har karfe 3 kallon little dake bacci kan cinyanta tun awa d'aya daya wuce tayi tare da saukar da kanta a hankali ta d'aura mata akan trow pillow kitchen ta shiga ta fara harhad'a abubuwan da zatayi aiki dashi na abincin darenta, sossai ta dukufa aiki har seda taji ana kiran la'asar a masallacin dake cikin unguwansu kan ta fito Bayan ta sa zobon da ta gama cikin fridge.

Little ta tasar suka shige d'aki sukayi alwala sukayi sallahn kan khairi ta bata darduma da qur'aninta izu goma da kuma wasu kananan littatafai na usulul thalatha, da hakkul mubeen, fita tayi don ta tabbatar malaminta ya zo Ai ko de ta hangeshi daga bayan rumfar motoci tsaye karasawa tayi ya kar'bi katon sallayar ya shimfid'a musu suka zauna tare da fara d'aukar karatu.

A ciki kuma kitchen khairi ta koma ta ci gaba da aikinta kan magrib ta gama tuwonta na semo da miyan egusi da bitter-leaf  wadda yaji stock fish, ta shirya tsab a dining tare da dawowa kitchen ta fara tattare abinda ta 'bata tana gamawa ta shige d'aki tayi wanka tare da alawala don magrib da ya gabato aiko tana fitowa ana kira a daidai lokacin kuma little ta shigo sukayi sallah tare kan taje ta sa mata abinci ita kuma ta dawo daki tare da bud'e alqur'ani ta fara karantawa.

Little na cin abinci musharraf ya shigo rike da briefcase dinshi da alamu ya sha aiki don duk a gajiye ya shigo yana hana kanshi hutu ne sbd be son tunani ya mishi yawa, little dake cin abincinta a tsakiyar parlorn tana kallon cartoon tace "welcome paapi" yace "thanks dear, what are yhu eating?" Yace "your favorite, mommy cooked it bakaji daadinshi ba" murmushi kawai yayi yace "enjoy dear" kan ya nufi haurawa little ta sake cewa "paapi me yasa yanzu baka cin abinci a gida and in kaje Gombe kuma tare muke ci ko da wani lokaci?" Dafe goshinshi yayi tare da cewa "Ina ci mana little" tayi saurin cewa "ni de ban ta'ba gani ba, plz come and eat paapi yayi daad'i sossai ga best drink d'inka ma".

Ajiye briefcase dinshi akan kujera yayi tare da nufan dining ya tsakuri kad'an a plate ya ci be san sadda ya cinye ba ya kuma karawa tun ranar d'aurin aurensu rabon da ya ci abinci yaji yayi irin wannan koshi da yayi a yau hamdala yayi kan ya mike ya d'auki briefcase dinshi ya haura yana cewa little "let me freshen up" da Ohk ta amsa yayi haurawanshi.

Seda isha yayi khairi ta fito tayi mamaki sossai da little tace mata paapinta yaci abinci shi da yace he hates all what will come from her hands, girgiza kai kawai tayi kan ta jata d'aki sukayi isha bag pack din little ta d'auko ta sata a gaba tayi assignment d'inta kan tayi alwala tazo ta kwanta don tana bacci da wuri ita, seda khairi ta tabbatar ta kwanta kan ta mike ta shirya cikin nylon night gown fari me tsantsi sossai wadda ya kai kasan gwiwanta tayiwa kanta feshin Arabs performs d'inta kan ta zura hijabin sallahnta da ya ke sharan kasa ta fice fuskanta fayau Ba komai duk taku d'aya da zatayi na steps din da take bi bugawar zuciyanta karuwa yake.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️8️⃣8️⃣▶️8️⃣9️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Babban parlorn dake saman ta fara cin karo dashi had'adden parlorn da ya tafi da imaninta komai na ciki sky blue se ratsin fari fari a abubuwa dayawa wani katon wall sticker ne zagaye da parlorn da In baka sani ba zaka ce carpet ne aka manna tsabar had'uwanshi, bata tsaya kalle kalle ba ta bud'e d'akin farko dake parlorn babba ne sossai ba komai cikinshi se abubuwan gym dinshi dumbbell, treadmills da dai sauransu, janyo kofan tayi ta koma na karshe ta bud'e nan kuma ba komai se shimfid'add'an tiles fari da wani carb ward na littatafai kaman library sede litattafan basu dayawa har chan hakan yasa carb ward dinma ya zama daga jikin gini d'aya.

Jikin windown room din kuma study table ne me had'e da kujerunshi guda biyu se kofan toilet dake gefen kofa wurin ya mata kyau sossai musamman da ya kasance d'akin corner room ne, kallon white door din tsakiyan tayi kenan tabbas shine nashi zuciyarta dake ta tsalle ya kasa zama wuri d'aya ta dafe tsoro ne fal ranta amma ya ta iya hakan shine solution.

Seda tayi adu'o'inta kan ta tura kofan da sallama duhu dulum d'akin kaman ba wuta a gabad'aya gidan ko tafin hannunka baza ka iya gani ba sbd an kashe duk wani abu me supplying haske a d'akin, sake sallama tayi a hankali, jin ba'a amsa ba yasa ta juyawa don ficewa se taji an kunna wutan d'akin, a tsorace ta juyo se ta hangeshi zaune chan karshen gado a takure kaman ba gidanshi ba kallon seconds biyu yayi mata kan ya maida kanshi tsakanin cinyoyinshi.

A rud'e take kallonshi sbd hawayen da ta gani ke zuba a idonshi da kyar ta samu ta seta kanta kan ta karasa bakin gadon cikin natsuwa ta zauna a hankali tace "Hamma na zo mu yi maganar fahimta ne dakai, na gaji da irin wannan zama da mukeyi Ina rokon ka don alfarman annabi da alqur'ani ka fad'amin laifin da na aikata a gareka ko zan samu sa'idar azabtar danin da kakeyi".

Shiru yayi kaman baze ce komai ba kan ya d'ago kai yasa hannu ya share fuskanshi cikin

dashewar murya alamun ya jima yana kukan yace "me yasa zaki min haka ummulkhairi? Me yasa kika dasa min bishiyar soyayyarki a zuciyata wadda har root din ya mamaye ko Ina bayan kin san you are not pure? Me yasa baki gayamin komai akan hakan ba se kawai inji daga wani wuri kuma a ranar d'aurin aurenmu? Khair me na miki da zafi haka? Am really heartbroken am hurting down there" ya sa hannu a kirjinshi yana mata alama.

Hawaye ta fara yi me tayi ne haka da bata sani ba? Kukanshi ba karamin d'aga mata hankali yayi ba ita kanta ta san abun ba karami bane tunda har yasa jaruminta kuka amma bata da masaniya akan abinda yake cewa hakan yasa tace "I think am confused, Sam ban fahimci inda zantukan ka suka dosa ba" wayanshi ya jawo tare da kunna hasken har hannunshi na 'bari wurin hawan WhatsApp din da kyar ya kai kan numbern ya lumshe ido kan ya mika mata wayan.

Kar'ba tayi tare da kallon fuskan wayan Ai bata san sadda tayi wani irin mikewa ba tana ambaton "innalillahi wainna ilaihi rajiun" jikinta ne ya d'auki rawa har tana kasa tsayuwa a rud'e ta fara scrolling din fuskan wayan Ai bata san sadda tayi wani irin kara ba tare da sulalewa kasa ta fad'i sumammiya da gudu ya sauka zuwa kanta ya d'ago kanta zuwa kan kafanshi tare da sa hannunshi a hancinta ya zata mutanenta ne suka zo se yaga akasin haka don suma tayi chak ya d'agata ya d'aura kan gado tare da zare mata hijab din jikinta da sauri ya shig bayangida ya d'ibo ruwa yazo ya fara shafa mata a fuska zuwa wuyanta.

A hankali yakeyi yana yi yana karewa jikinta kallo, ajiyar zuciya me karfi ta sauke kan ta bud'e ido Shiru tayi na seconds kan ta tuna abinda ta gani Ai a rud'e ta rungumeshi tare da cusa kanta a cikin kirjinshi ta fashe da wani azababben kuka tana girgiza kai a jikinshi muryanta a rarrabe take cewa "wal........llahi ba.... ni ba..... ce, bani bace..... wallahi ban san sadda akayi hakan ba, kar ka ce min ka yarda ban sani ba amma ba ni bace zan iya mata rantsuwa da alqur'ani wani namiji be ta'ba ta'ba jikina ba bayan muharramaina se masu taimako na In jikina ya tashi amma wanchan ba ni bane, wallahi ba ni bace...." magana kawai takeyi cikin fitan hankali da tsantsar rudewa ga kuka da takeyi kaman ana zare ranta ta rasa a wani irin duniya take.

Hawaye ne ya gangaro mishi tausayinta na kashe mishi zuciya dukda be tabbatar da ba itan ce ba ganin tana kakkafewa da alamun zata sake suman ne yasa shi saurin d'agota tare da had'e bakinsu wuri d'aya a hankali ya fara bata wani irin hot kissing da ya fara goge mata duk wani abu dake adane a cikin kwakwalwanta, a hankali a hankali yake tafiyar da ita kaman ze yi kaman baze yi ba kaman kwai haka yake lalla'ba jikinta tun yana iya controlling kanshi har yaji ya kasa a lokaci d'aya ya birkice mata abinda ta san taji daga karshe shine kawai adu'ar saduwa da iyali daya karanto cikin dashewar murya.

Da gudu na fice don kar su lalatawa mamana da mommyna ni, a bakin kofa na makale se after like 15mins na lalla'ba na koma cikin d'akin.

Rungume da ita na hangoshi idanunshi na zubar da hawayen tsantsar sonta da tausayinta na shigarshi wani zazzafar kaunarta yaji yana huda jini da jikinshi har cikin 'bargonshi, farin cikin

babu wadda ya ta'ba sanin mishi mata na kara mamayeshi and kuma hakan ya kara tabbatar mishi ita d'in mallakinsa ce shi kad'ai, Toh amma waye ke son d'aura mata wannan sharrin? Waye yayi kokarin raba musu auren da suka gina cikin so da Amana har shiga cikin wannan ginin ya gagaresu?.

Da kyar ya samu hawayenshi ya tsaya a hankali ya mike yana kallon fuskanta a hankali take numfashi hawaye kuma na sauka a idanunta zuwa kan kunnuwanta rungumeta yayi a cikin kunnuwanta ya rad'a mata "am so sorry qalbee, am sorry na kasa tunkararki da maganan tun farko ne sbd tsoron irin amsar da zan samu daga gareki ki yafemin Dan Allah" mikewa yayi ya fad'a toilet d'inshi ya had'a mata ruwa me zafi a cikin jacuzzi dinshi bata ji dawowarshi ba se d'agata da taji yayi tare da zame blanket din, da sauri ta kuma shigewa jikinshi don ba komai jikinta ga kunya kaman ta nitse kasa ga takaici da damuwar tunanin wadda ya so 'bata mata aure, ga haushin musharraf da takeji na kin gayamata da wuri har seda ya wahalar mata da kanshi ya wahalar da ita.

Kara ta saki tana kankame shi jin zafin da ya ratsata yayinda ya ajiyeta cikin jacuzzin cike da tausayinta yace "sorry" nan ma bata tanka shi ba har yayi mata wankan da kanshi ya barta tayi wankan tsarki da kanta dukda yadda kunya ke cinta amma haka ta fuske tayi wankan a gabanshi ko kallonshi batayi ba, towel ya bata ta d'aura d'aga kafan da zatayi don takawa taji wani azababben zafi ya ratsa ta hakan yasata sakin ihu tare da dukawa ta fashe da kuka.

Murmushi ya sake marar sauti wallahi khairi raguwace shi ya tabbatar be yin abu biri biri ko da karfi karfi musamman ta wannan 'bangaren a natse ya bi da ita he's very sure bata ji ciwo ba sede ya san dole zata ji zafi ko kad'an ne sbd ba wadda ya ta'ba saninta kan shi, d'aukanta yayi ya fice da ita zuwa kan gado ya shimfid'e ta kan ya janyo riganta ya sanya mata gashinta daya sauko har kasan wuyanta ya sa towel din ya goge mata sossai kan ya koma toilet da towel din bayan ya ajiye ya fara had'a ruwan wankanshi.

A nan kuma bayan ya kyaleta har ta kwanta se kuma ta mike tare da janyo wayanshi da ta jefar daga kasan gadon ta kunna ta fara kallon hotunan, guda hud'u ne kuma duk ita kad'aice fuskanta ya fito namijin fuskanshi be fito ba, hoton farko zaune take a gaban dressing mirror daga ita se towel karami pink ta sheda towel d'inma nata ne iyakarshi cinyarta.

Gashinta zube a baje da alamu kuma a jike suke, wani ne da bata san ko waye ba tsaye daga bayanta ba'a kallon fuskanshi sbd ya binne cikin gashinta a tsakankanin wuyanta, hannunshi zagaye da cikinta ita kuma ta lumshe idanunta hannunta na d'aure akan nashi. Hoto na biyu kwance take akan kirjin wadda bata sani ba suna tsaye a tsakiyar shower ruwa na zuba akansu anan kam fuskanshi ya fito kad'an kurawa fuskan ido tayi hawaye na ta zarya a idanunta ita Allah ya gani bata ta'ba sanin me wannan fuskan ba amma gata kwance akan kirjin wani a cikin shower da alamu kuma jikinsu ba kaya don har tsakiyar bayanta ana gani.

Hoto na uku zaune take akan kafanshi tana facing dinshi tayi baya da kanta sossai daga ita se wani t-shirt iya cinya ya rike bayanta da hannu biyu tare da binne kanshi a tsakanin kirjinta,

hoton karshe suna kwance akan gado tana rigingine shi yana samanta bakinshi cikin nata yana kissing, hannu ta d'aura a bakinta tana sake siririn kuka, wayan taji an zame daga hannunta d'ago kai tayi se ta ganshi tsaye sanye da black three quarter jikinshi ba riga.

Dukar da kanta tayi tana me ci gaba da kukanta zama yayi tare da janyota cikin faffad'ar kirjinshi ya rungume yana shafa bayanta cikin kasa da murya yace "it's Ohk plz kukan ya isa haka it's hurting me" cikin kuka tace "ka duba Dan Allah it looks real wallahi bayan ni ban san sadda akayi ba, ban san yaushe akayi hakan ba" ci gaba da shafa bayanta yayi a hankali yace "na miki alkawari bazan ta'ba hutawa ba har se na gano wadda yayi miki wannan sharrin tabbas ba ke bace amma fuskanki ne hakan ya tabbatar min da editing ne, karki kara sawa kanki damuwa akan abun nan".

A hankali tace "plz komai ya faru irin haka ka fad'amin ba wai ka sani a cikin tunani da damuwa ba, hankalina ya tashi na kashe darare dayawa ido biyu sbd tashin hankalin da na shiga." Kara rungumeta yayi yace "I promise to be by your side forever and for always. I love you. Nothing can do us apart, nayi miki alkawarin bazan kara boye miki magana irin haka ko na dakika d'aya ba" Kai ta gyad'a mishi ya kara sata a jikinshi yana sauke ajiyar zuciya.

Bayan kaman seconds talatin yace "I am not the best husband in the world. But I promise you one thing, I will work hard every single second of my life to make you happy and make this relationship better each day. Please forgive me."  Cikin whisper tace "Apology Accepted" kara rungume ta yayi yace "thanks love, naji daad'i kwarai da yadda na sameki na gode da wannan kyautar mafi daraja a duniya Allah ya miki albarka" a hankali ta amsa da Ameen Shiru suka ci gaba da kwanciya har bacci ya d'auketa, mikewa yayi ya kwantar da ita tare da rufe mata jiki da blanket toilet ya koma yayi alwala tare da d'auro alwala ya fito ya fara nafilfilin godiya ga Allah har seda bacci ya kusa cin karfinshi kan ya zo ya kwanta tare da janyota jikinshi ya lullu'besu seda yayi pecking goshinta kan ya gyara ta da kyau tare da lumshe ido cikin salama bacci ya d'aukeshi.

Asubar fari ya farka ya shiga toilet yayi alwala ya fito se ya kasa tashinta fita yayi zuwa kasa ya wuce masallaci bayan an Idar da sallah ya zauna yayi musu adu'a sossai, kan ya taso zuwa gida d'akinta ya shiga ya tada little ya kaita bayi tayi alwala yazo ya d'aurata kan sallaya kan ya fita zuwa kitchen Kwai ya fasa ya soya har da attarugu ya d'an saka a ciki bayan ya gama ya sa wani a plate sauran yasa a wani karamin beautiful warmer ya d'aura akan wani mini silver tray me kyau, ruwan zafi ya d'aura ya had'a tea na daidai su uku ya zuba a flask karami ya d'aura a gefen trayn tare da sawa little a cup ya ajiye gefen plate din kwanta, bread ya d'auko ya d'aura akan trayn tare da wasu beautiful cups kanana guda biyu ya d'aga warmer din ya sa kananan plate guda biyu kan ya mayar ya d'aura coolern.

Trayn ya d'auka ya haura dashi zuwa d'akinshi janyo center table dake gefen gadon ya d'aura mata trayn tare da komawa jikin wardrobe dinshi ya d'auko joter da pen ya dawo ya zauna tare da yage paper d'aya yayi rubutu akai ya d'an d'aga flask ya ajiye rabin papern na nunawa yadda zata gani da kyau. Kan ya mike ya fice zuwa d'akinta ya samu little kwance tana bacci d'agata

yayi zuwa toilet yayi mata wanka nan ta ware ta fara mishi surutu yana amsata har suka gama shiryawa dayake yau yana cikin farin ciki fuskanshi a washe cike da fara'a da annuri, har kan dining ya kaita ya ajiye mata plate d'in Kwai da bread se tea d'inta, se lokacin tace "Ina mommy paapi?" Yace "mommy bata da lafiya tana bacci a room d'ina" fuska ta kwa'be zatayi kuka da sauri yace "karkiyi kuka little taji sauki bacci kawai takeyi" Kai ta gyad'a nan ya dinga mata wasa har ta sake bayan ta gama ya raka ta har mota ya ba driver empty lunch box d'inta da kud'i akan su biya restaurant ya sayata abinda take so na break d'inta.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️9️⃣0️⃣▶️9️⃣1️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Hasken rana da ya fito ne ya fara reflecting idonta hakan yasa ta dole bud'e idon a hankali ya sauka kan agogo dake jikin bangon d'akin da sauri ta mike zaune tana furta "ya subhanallah banyi sallah ba how comes yau na makara haka" nufan sauka daga gadon tayi se taga tray da warmer da flask akan stool dake ajiye inda zata sa kafa ta sauka, murmushi ta sake tuna abinda ya faru da irin soyayyar da musharraf ya nuna mata a daren jiya hannu ta saka ta zare papern da aka d'aura akan trayn rubutunshi dake kwance zarzar kaman computer ne yayi rubutun ta zubawa ido tana karantawa and she can't stop her self from blushing.

Ga abinda yace a paper din "Hey my darling wife
On this super awesome day
Just want to wish you good morning
With lots of kisses for the day
Good morning to you! Tauraruwar zuciyata" Ajiyewa tayi tana jin sonshi na kara samun mazauni a zuciyarta dira tayi a hankali take tafiya zuwa bayi alwala tayi ta fito, hijabin sallahnta da ta shigo dashi jiya ta d'auka ta zura tayi sallahnta ta d'an jima zaune tana istigfari kan ta mike ta cire khimar d'in.

Toilet ta koma ta d'auki sabon brush ta 'bare tare da sa macline tayi ta kuma wanke fuskanta kan ta fito zuwa kan gadon gyara zama tayi, tayi breakfast d'inta cikin kwanciyar hankali tana tunanin ashe musharraf ya iya shiga kitchen ita a ganinta ko kunna gas baze iya ba gashi har unique egg yayi mata fraying ga tea da ya had'a mata, bayan ta gama ta gyara d'akin tare da d'aukan tray d'in ta nufi kasa ba tare da ta sa hijab d'inta ba.

Tun daga saman steps ta hangoshi rike da mop yana moping fari kal d'in tiles dake shimfid'e a parlorn nasu na kasa, waro ido tayi tana saukowa da d'an sauri tace "hamma me kakeyin nan" d'ago ido yayi ya kalleta tare da sakin wani heart melting smile yace "qalbee am moping the floor bcs yhu can't do it today" kitchen ta nufa ta ajiye tray din kan ta dawo ta sa hannu ta kar'be tace "who said that?" Kashe mata ido d'aya yayi tare da d'age gira yace "really, so lafiyanki kalau?" Baki ta tura tana tsoma mop din a ruwan omo tace "good morning" yana kokarin kar'ba

yace "morning sunshine, ya jikinki baya miki wani ciwo ko?".

A dabarance tana kokarin kuma kwace mop d'in tace "yes baby" bata hankara ba taji ya d'agata chak zuwa kan kujera ita da mop d'in kan ya zare daga hannunta yace "just chill baby, will do all the house chores" remote ya d'auka ya kunna Tv ya kama mata zee world yace "oya yi kallonki I love yhu" murmushi kawai tayi tana maida kanta tvn da gaske baze barta tayi ba kenan.

Ganin ya shiga kitchen yasa ta guduwa d'akinta ta fad'a wanka tana cikin wanka taji yana kiran sunanta "qalbee, qalbee" watsa ruwa tayi don yaji tana bayi, yajin kuwa memakon ya tafi se ya bud'e bayin ya shige waro ido tayi tana neman d'aukan towel se tsantsi ya d'ibeta tayi baya zata fad'i saurin tareta yayi yana dafe gini don gujewa fad'uwar shima ruwan showern da ta kunna ya ci gaba da zuba a kansu gabad'aya.

Runtse ido tayi shi kuma ya saki murmushi cikin kasa da murya yace "dama me zaki gudu ki boye min? Kin manta ke mallakinace baki da abinda zaki boye min nima haka, mun riga da mun zama d'aya yanzu In har Ina cikin gidan nan duk abinda zakiyi tare zamuyishi, am I clear" murmushi tayi a kunyace tace "yes sir" dariya ya saki jin wai wani sir haka de suka ci gaba da hira kad'an kad'an suna wanka shi yayi mata inda ya nace se tayi mai a dai kunyace ta yi mishi bata karasa bama ta janye towel ta kwasa da gudu tana mishi gwalo, shima dariya ya saki yana cewa "zan kama ki ne qalbee ni zakiyiwa wayo" yana ta sake murmushi har yayi wankanshi ya fito d'aure da babban towel d'inta.

Gaban mirror ya sameta tana shafa mai bayan tayi drying kanta da hand drayer, wardrobe d'inta ya nufa kanshi tsaye ya ciro na biyo da babban akwatinta ya d'ibi kayanta ya cika tap dashi har sleeping wears, kananan kaya, atampha, jallabiyoyi, khimars da veils, tana mai ci gaba da shafa manta tace "Ina zaka kai kayan baby?" Yace "to my room don gaskiya ban son zirga zirgan nan kuma bani da ra'ayin raba room da mata ta shiyasa zan kai miki kayanki chan" Tace "ohk miko min medium size din trolleyn bari In zuba cosmetics" mika mata yayi ta zuba duk cosmetics d'inta Bayan sun gama ya bata wani d'an pingilin riga wai shi zata saka suje room dinsu na sama ta shirya shi bata da wani option se na sakawa iyakarshi cinyarta maroon ne rigan hannunshi na vest gashinta da ta kama a tsakiyar kan se lilo yakeyi fashion ear rings ta saka a kunnenta ta shafa powder da lips stick se kwalli a idonta ba karamin kyau tayi ba.

Se santin kyaunta yakeyi da kanshi ya ajiye mata flat shoe maroon me gashi a ciki sakawa tayi ya janyo babban akwatin ita kuma ta d'auko karamin suka nufi sama ba tare da ya shirya ba suka fara shirya kayan a cikin wardrobe dinshi sawunsu biyu daga sama zuwa kasa kan suka gama tattaro kayanta kab na little kad'ai suka rage.

Sunayi suna hiransu na masoya har suka gangaro kan sharrin da aka mata tana shafa mishi mai ya dube ta yace "kina tunanin waye ya aikata haka? Anty Rabi'ah" Kai tsaye khairi tace "I don't think so baby nafi zargin sufyan dukda ance zato zunubi" Shiru yayi na mintuna kan yace "tabbas shine kad'ai ze iya aikata hakan sbd d'aukar fansar abinda na mishi akanki amma yayi babban kuskure don me raba ni dashi se Allah" marairaicewa tayi tana rike hannunshi tace

"baby I have a request plz" Kai tsaye yace "go on qalbee fad'i ko ma menene In be fi karfina bazan ki miki ba" Tace "bana so kayi mishi komai ko ka tabbatar shine, ka kyale shi da halinshi ze girbi abinda ya shuka".

Wani kallo ya mata kan yace "this is impossible, ba ta yadda za'ayi In kyale sufyan wallahi, don ya cutar dani sossai ba kad'an ba ni kad'ai na san halin da na shiga you have no idea also" Shiru tayi ta ci gaba da shafa mishi man har ta gama bata kuma cewa komai ba fuskanta kuwa ba'a sake ba ba'a had'e ba, haka ta nufi wardrobe ta fiddo mishi army green three quarter da sky blue nylon armless shirt seda ta taimaka mishi ya saka ta juya ta nufi ficewa daga d'akin da sauri ya sa hannu ya janyota ta fad'o jikinshi cikin whisper yace "fushi kikayi?".

Tace "nop sbd me zanyi fushi, ni banyi fushi ba" yace "Toh Ina zaki?" Tace "I'm very sure bakayi breakfast ba kalli time gashi na tabbatar little ta kusa dawowa" mikewa yayi tare da ita a jikinshi yace "Ohk muje In tayaki, and kuma tunda bakya so in ma sufyan komai bazan yi ba In shaa Allahu" pecking kumatunshi tayi tace "thanks dear, yanzu muje mu d'aura abincin" kitchen suka shige a tare sukayi girkin rana inda suka girka Tuwo don ta lura yafi so hakan yasa tayi mishi Tuwon alabo(rogo) da miyan d'anyen kifi a dining suka jere suka kuma dawowa kitchen din suka tattare tare, tare da wanke abunda suka 'bata tanayi yana d'aurayewa yana kifawa har suka gama sukayi moping kitchen din duk sunayi suna shan love minti minti zeyi kissing lips d'inta yace "Ina sonki sossai" ko "I love yhu qalbee" a haka suka gama a daidai lokacin little ta shigo da gudu tayi musu oyoyo suka rungumeta a tare, bayan sunyi breaking hug din khairi tace "wanka ko cin abinci pretty?" Little tace "wanka mommy" nan fah musharraf yace shi be yadda ba yunwa yake ji ba yadda suka iya haka suka nufi dinning tayi serving d'insu sukayi bismillah suka fara ci se santi suke zuba mata inda little ta makalawa tuwon suna da tuwon chewing gum shi kuma musharraf yace sede a kira shi manne manne tsabar dankonshi se dariya khairi keyi musu.

TWO MONTHS LATER

Wani irin tsaftatacciyar soyayya wannan familyn suke shimfid'awa a tsakanin junansu kowa na so yaga ya burge d'an uwanshi dukkansu suna gudun 'bacin ran junansu yayinda komai na gidan In har yana nan to ya sabar musu yi a tare ko yaushe tana jikinshi don in yana nan be yadda da zama separate ba tun khairi na damuwa akan tarbiyar little kar ya ta'bo ya nuna mata Ba komai In shaa Allahu, result d'insu na waec da neco duk ya fito khairi ta basu kala don ta samu credits sossai bata da fail ko d'aya hakan yasa yana nema mata University of Abuja dake gwagwalada suka bata bayan tayi jamb ta cinye.

Haka a Gombe ma ya sa an samawa Amrah gombe state university don itama results d'inta sunyi kyau inda take karantan Geology (study of earth shape) yayinda khairi take Anatomy ( study of the structure of human body) don course din na burgeta, sun fara karatu last week inda suka zauna suka tsara time table na yadda zasu ci gaba da rayuwa cikin farin ciki despite ko wannensu na fita kuma yawanci yini sukeyi.

A tsare suka fidda komai nasu dama ya koya mata mota tun wata d'aya da ya wuce kuma ta iya sossai don har tana hawa kan hanya da nashi, a randa zata fara zuwa school a ranar ya bata kyautan mota sabuwa dal Accord maroon color sossai tayi farin ciki ta dinga zuba mishi godiya inda yace be yarda ba In tana so ya amshi godiyarta ta nuna mishi a gado, Ai ko a ranar ta bashi mamaki yayinda sonta da kaunarta suka ninku a zuciyarshi sbd seda ya zauna da ita ya san wacece ita.

Macece me yawan kulawa akan abinda take so da tarairayarshi bata da ganda ko ko na miskala zarratin ga ta da tsananin tsabta da son kamshi ga iya girki Allah ya bata, babban abinda yasa yake kara sonta kuwa yadda take son little ya yi imani ko ita ta tsuguna ta haifeta soyayyar da zata nuna mata kenan, yawancin Friday's zasu kashe awowi suna waya da su momma da kuma su dada inda suke kiranta a wayan inna suyi ta mata tsiya suna shan dariya kan ta mikawa dada tana musu wankin babban bargo, kuma baze hana In an kira next Friday ta fara d'agawa ba.

Sossai momma ke jin daad'in kwanciyar hankalinsu don ko bata gansu ba daga muryoyinsu ta san irin so da kauna da suke wa junansu bare yawanci khairi na turawa Amrah hotunansu a tare In ta matsa mata sede ta gansu a IG lokuta da dama kuma mutane suyi ta santin couples din har hakan ya karawa Amrah yawan followers.

In takaice muku readers a wata biyun nan ko ku aka ce muku ga khairi baza ku ganeta ba hutu ya nuna sossai a jikinta farinta ya kara haskawa tayi kumatu yayinda natsuwa da kwanciyar hankali tsantsa ya nuna a yanayinta ta zama kaman wata matar shugaban kasa komai cikin class take yinshi Haka musharraf ma ya d'an kara kiba yana girma ne amma kyaunshi kaman kara mishi akeyi, in kaji musharraf da khairi sunyi fad'a to akan 'yan matan dake rububinshi ne don ta bashi haushi wani lokacin In ya amsa call dinsu se ta koma gefe ta zauna ta fara mitar.

'Matsalan auren kyakyawa kenan da ma kauye na shiga na samu mummuna daidai ni na aura da ba'a nemi sawa mutum hawan jini ba' nan fah ta tsokono shi haka zasu yini suna fad'a a wasa wasa da tsokanan juna, saura wata uku buki a gidansu bukin marwa da haneefa wadda suka gama shirya abubuwan da zasuyi a group dinsu na WhatsApp sossai suka shaku da 'yan uwanta anan.

Yau da misalin karfe hud'u ta fito daga lectures kenan ta ji wayanta na kara tana fiddowa taga 'Zauj🔐💝' ne ke yawo a saman iphoneX d'inta da ya chanza mata d'agawa tayi tace "baby" daga 'bangarenshi yace "yes qalbee ya lectures?" Tace "Alhamdulillah ya office ko ka dawo gida?" Yace "nop motana ya samu matsala wallahi yaki tashi, ki biyo ki d'aukeni" murmushi tayi kan tace "ohkey on my way" kashewa yayi a daidai lokacin ta isa mota tayi mata key ta d'auki hanyar office d'insu.

Bayan ta d'aukoshi suka nufo hanyar gida suna d'an hiransu na masoya, da wani irin karfi ta taka Burki a tsakiyar titin inda wani mota yazo ya bugi nata dama gudu takeyi, a tsorace musharraf ya kalleta yace "are yhu alright khairi?" Inaaa bata ji shi hankalinta gabad'aya ya tafi

wani 'bangare guda da ta kurawa ido.

Toh readers me kuke gani ya firgita khairi haka?????

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION

(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️9️⃣2️⃣▶️9️⃣3️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

'Balle murfin motar tayi da sauri tayi d'ayan 'bangaren titin wani matashin saurayi dake tsaye a gaban wani mota dayake traffic ya tsaidasu, be ankara ba kawai se ji yayi an rungumeshi ta baya ko daga Ina, ko ya take, ko a wani hali take In har taga d'an uwanta ba ta gaba ba zata ganeshi.

Tana rungumeshi ta saki kuka da sauri musharraf ya dawo driver sit ya ja motan zuwa gefen hanya kan ya samu ya tsallaka zuwa bangaren da suke yana bawa mutanen da ta tara hakuri, har a lokacin taki sakeshi balle yaga waye se kiciniyar kwacewa yakeyi amma ta rike shi gam, seda musharraf yazo ya janye ta dukda haka taki sakin hannun d'an uwanta, wani babban mutum ne ya bud'e motar da d'an uwa ke tsaye a jiki ya fito dama traffic ne ya tsaidasu a natse yace "lafiya kuwa bayin Allah?" Abulkhairi da ya sawa khairi ido yana ta kallo ne ya juyo yace "Abba nima ban sani ba Haka kawai wannan tazo ta kamani tana kuka" mutumin ze yi magana kenan khairi data ke rike da hannun abulkhairi da d'ayan hannunta, musharraf ya rike d'ayan tace "Dan uwa!!!! Ni ce baka sani ba?" Se ta rushe da kuka.

Mutumin ya kalli musharraf da yayi wani iri sbd ganin yadda matarshi ke kuka yace "bawan Allah mu tsallaka se muyi magana don naga an kusa sake mu" tana rike da Abulkhairi dake ta mata wani irin kallo suka tsallaka mutumin yace "suna na Alhj Abdulrashid hameed ni babban d'an siyasa ne kuma d'an kasuwa, wannan d'ana ne sunanshi "Abdallah" dan Allah ko zaku iya min bayani yadda zan gane ku?".

Khairi tace "wallahi wannan sunanshi ba Abdallah ba, sunanshi Abulkhairi d'an uwa na ne, my twin brother that was lost decades ago, baka ga kaman mu ba?" Ajiyar zuciya mutumin ya sauke kan yace "Toh Alhamdulillah ga kama kam, maganan nan ba na kan titi bane in ba matsala ku bini gidana se muyi maganan cikin natsuwa" har musharraf yace "Toh Alhaji" Khairi tace "a'a baze yiwu ba sede ka bamu address zamu zo da dare sbd yarinyarmu ta taso school tuntuni gashi ba kowa a gidan" cike da wani irin so musharraf ke kallonta duk yadda ta matsu, duk yadda take marmarin ganin d'an uwanta amma sbd baza ta iya barin 'yarshi ita kad'ai ba ta hakura zasu koma gida se daga baya taje wajen d'an uwanta.

Ajiyar zuciya ya sauke kamin ya kalli Abdallah tabbas ba abinda ya banbanta shi da khairi sede kawai don ita mace ta fishi kyau, amma Toh ya akayi be ganeta ba? Kallon khairi yayi kallon

d'aya ya gane tashin hankalin da take ciki kawai bata son nunawa ne amma damuwa ya bayyana sossai a fuskanta, maida dubanshi yayi wurin Alhj Abdulrashid yace "ba komai Alhj ka bamu address din after isha prayer zamu zo In shaa Allah" Address din ya basu suka mishi sallama akan se ya gansu idon khairi na kan Abdallah suka wuce shima kur ya mata da ido yana kallo.

Musharraf ne yaja motan hannunshi na cikin nata ba wadda ya iya cewa kowa komai a cikinsu har suka isa gida suka samu little kuwa ta dawo har ta ci abinci ta chanza kaya tana baccinta, samansu suka haura sukayi wanka a tare suka chanza kaya duk ta kasa magana suka kuma gangarowa abincin da tayi tun kan ta fita lectures tuwon semo da miyan d'anyen ku'bewa ta saka musu da zafinshi jau kaman yanzu aka sauke sbd yanayin warmern da ta saka.

Sbd yana bata yana ci hakan yasa ta ci sossai amma ba wai don tana da apatite ba, suna gamawa ana kiran magrib ya mike yayi mata pec tare da cewa "se na dawo" Kai kawai ta gyad'a mishi ya fice ita kuma ta tada little dake kwance kan kujera tace "tashi pretty magrib yayi" tashi tayi tana kaikaya ido tace "yaushe kuka dawo mommy?" Murmushi khairi tayi tace "kina shan baccinki muka dawo, oya an shiga sallah a masallaci tashi kiyi sallah In kin idar ki tabbatar kinyi bitar karatunki Ohk?" Tace "Ohk mommy" ta mike ta shige d'akinta inda khairi ta haura sama.

Se bayan sallahn isha tukuna ya shigo gidan a parlor ya samu little na kallo da gudu taje ta mishi oyoyo don tun safe rabon da su had'u d'aga ta yayi sama ya sauke yace "Ina mommynki?" Tace "mommy na sama tunda ta shiga sallahn magrib bata fito ba" dayake ba kasafai take hawa musu saman ba ko irin baki haka khairi tayi iyakarsu kasa sam bata bari wani ko wata ya haura mata saman miji wadda hakan yasa little ma bata cika hawa ba don In har musharraf baya nan to suna kasa tare har se ya dawo take haurawa.

Sake hannun little yayi kan yace "Ohk yi kallonki bari In dubota" cikin parlorn ta koma shi kuma ya haura d'akinsu ya fara shiga be ganta ba ya tura toilet bata nan, study room/library dinshi ya duba nan ma bata nan, d'akin gym dinshi ya tura nan dinma bata nan kwankwaso ya kama yace "ikon Allah to Ina tayi? Qalbee! Qalbee!! Qalbee!!!" Shiru, kasa ya kara sauka ya tambayi little tace bata ga fitowarta ba kwata kwata.

Saman ya kara komawa ya sake duddubawa a tsakiyar d'akin gym dinshi ya tsaya yana tunanin Ina ta shiga, se ya ji sheshekan kuka kasa kunne yayi tabbas kuka ne kalle kalle ya fara se ya hangi hijab d'inta daga bayan wani gym machine da sauri ya nufi wurin ya duka a gabanta a sanyaye yace "qalbee" fad'awa tayi jikinshi ta kuma sa kuka a d'an rikice yace "menene? Me ya faru kike kuka haka?" Kukanta ta ci gaba da yi Ai ko se ya karasa rud'ewa ya dinga lallashinta da kyar ya samu tayi shiru inda ya tambayi me yasa take kuka haka.

A hankali tace "ban san me ya faru da d'an uwana ba, ban san me ya sameshi ba amma ko me ya sameshi ya kamata ya manta ni? His blood, I really can't believe wai d'an uwa ne ze ce be sanni ba" ta karasa a karye, girgiza kai musharraf yayi kan yace "haba baby yanzu dama don

wannan kike kuka? Ai munyi me wuyar tunda mun sameshi kika san ko wani abu ne ya faru dashi da yasa shi manta kowa nashi? Yanzu kinyi sallahn magrib?" Ta gyad'a kai ya kuma cewa "isha fah?" Ta girgiza kai yace "ji idonki fah bana son haka dan Allah, plz karki kara yin irin wannan kukan, se ya zama dole in ya zama dolen ma ki bari se na zo yadda bazan bar tsad'addun hawayenki su zubo a kasa ba, tashi muje kiyi sallah ki shirya mu wuce gidan Alhj Abdulrashid d'in" mikewa tayi yana rike da hannunta har d'aki a gabanshi tayi sallah kan ta d'auko wani Arabian gown ta saka ta yafa gyalen shi kuma ya saka bakin jallabiya suka fito In ka gansu kaman ka sace tsabar kyaun da sukayi.

Har d'akin little tare suka shiga ta saka mata doguwar riga itama suka rike hannunta zuwa mota, da kanshi yayi driving har zuwa wuse zone 3 inda anan ne gidan Alhajin yake, daidai number din house da ya basu a cikin card d'inshi suka tsaya tare da yin horn, me gadin ne ya taso da gudu zuwa inda suke sanye da uniform d'inshi na masu gadi se wasu police dake zaune kofan gidan da alama securities ne, "sannu yalla'bai Kaine wadda kukayi zaku gana da Alhaji bayan isha?" Kai musharraf ya gyad'a mishi ba tare da yayi magana ba, mutumin yace "yace in kazo ka sameshi a annur hospital amenity room 20" nan ma kai musharraf ya gyad'a kan ya karkace ya zaro kud'i ya mikawa mai gadin se godiya yake zubawa har suka wuce.

Da sallama suka shiga room din wasu 'yan mata biyu da zasuyi sa'a da khairi suka fara karo da suna tsaye daga bakin gadon d'aya dake d'akin, d'ayan gadon kuma empty se Alhj Abdulrashid dake zaune akan wani plastic chair, kan gadon kuma Abulkhairi ne kwance yana kallon 'yan matan da alamu wani labari suke mishi don se murmushi yake zubawa, Alhj na ganinsu khairi ya mike har kasa gabad'ayansu suka duka suka gaisheshi ya amsa fuska a sake, 'yan matan da suka rud'e da ganin musharraf suma suka gaidasu suka amsa Kallon khairi d'ayan tayi tace.

"Laaa Abba kaga carbon copy na Abdallah" murmushi Abban yayi kan yace "Nasreen twin sister d'inshi ce" d'ayan tace "wow masha Allah ashe Abdallah ya samu 'yan uwanshi?" Nan Abban ya ba wacce ya kira Afreen labarin yadda suka had'u dasu khairi, khairi kam hankalinta na kan Abulkhairi da shima kallonta yakeyi, runtse ido yayi da karfi jin kanshi na Sara mishi a take rayuwanshi na baya ya fara dawo mishi daki daki har rana yi ta yau yadda ya rike kan yana jujjuyawa yasa khairi cewa "he need a doctor" a rud'e ai ko kaman doctorn na kusa se gashi ya shigo da wata nurse a bayanshi da sauri suka karasa bakin gadon suna cewa su khairi su basu wuri plz.

Fita sukayi suka tsatsaya daga bakin kofan kowa da abinda yake sakawa a ranshi, bayan kaman 30mins Doctor din ya fito ya mikawa Alhj hannu yana cewa "Alhamdulillah patient d'inka ya warke don gabad'aya memory d'inshi ya dawo congratulations" ihu 'yan matan suka sake cikin jin daad'i yayinda khairi ke Allah wadai da d'abi'ar su Alhaj ne kad'ai ke ta godiya ga Allah.

Komawa d'akin sukayi khairice karshen shigowa aiko yana d'aga ido ya fad'a cikin nata hawaye ne ya fara gangara a idonshi cikin rawan murya yace "'yar uwa!!" Da gudu taje ta fad'a mishi ta fashe da kuka runtse ido musharraf yayi kukanta na yau ya ishe shi haka da ta san yadda yake ji da batayi ba kwata kwata, seda suka yi me isarsu kan suka saki juna little dake rike da

hannun musharraf ta sake taje ta kama khairi tace "mom why are yhu crying? Akwai wadda ya dakeki ne?" Kai khairi ta girgiza tace "kukan murna ne pretty na samu d'an uwana see my twin brother" kallonshi tayi tana murmushi tace "hi mommy's twin brother" dariya su Afreen suka saka inda Abul yace "hello twin sister's pretty" dariya suka kuma sawa har khairi empty gado dake d'akin Alhj ya nunawa su khairi suka zauna yayinda Afreen da Nasreen suka zauna a gefen Abul kallonsu Alhj yayi yace.

"Na san kun matsu ku san yadda akayi Abdallah ko ince Abulkhairi sunan da naji kin kirashi dashi ya fad'o hannuna, akwai wani rana wattani dayawa da suka wuce na fito Adamawa zan tafi kano motarmu ta samu matsala kan mu iso gombe dayake mota na bi kuma daga ni se driver na hakan yasa ya nema mana mechanic inda muka jima sossai motar be gyaru ba, da kyar de motar ta tashi a lokacin Yamma likis.

Umarni na ba driver dina akan mu ci gaba da tafiya har muka shigo cikin gombe yayi insisting mu kwana gombe ni kuma naki nace sede mu ci gaba da tafiya, ba yadda ya iya sbd nine sama dashi ba shine sama dani ba a cikin Gombe mukayi magrib da isha kan muka ci gaba da tafiya mun bar gombe Abadan har mun fara nitsawa cikin kauyukan bauchi se muka ga mutum ya fad'o mana from nowhere hakan yasa driver yayi losing control har muka kadeshi inda ya fita hayyacinshi sossai, ba tare da wani tunani ba muka d'auke shi to nearest town inda aka bashi taimakon gaggawa bamu tsaya ba muka ci gaba da tafiya a daren a kano muka kwana inda na kaishi asibiti mu kuma muka kwana a wani hotel.

Kwananmu uku a kano kan ya farfad'o inda ya farfad'o da bacewar kwakwalwa sossai na shiga cikin tashin hankali and I blamed myself hakan yasa guiltiness ya kasa sakeni har se yau, d'aukanshi nayi muka dawo nan Abuja da zama na sa mishi suna Abdallah, kaman yadda kuka sani sunana Alhj Abdulrashid hameed bani da mata ta rasu a wurin haihuwan nasreen inda Afreen ce babba" cike da gamsuwa suka ta mishi godiya.

Inda khairi ta kalli Abul tace "d'an uwa ya akayi daga kaje kasuwa ka sayo mana abun anfani aka tsince ka a hanyar Bauchi?" Runtse ido yayi yana tuna abinda ya faru a hankali ya fara cewa "bayan na fito daga gida na fara takawa a hankali don neman abin hawa ban samu da wuri ba se da nayi nisa da gida se ga wani katuwar jeep baka ta tsaya a gabana ci gaba da tafiya nayi se wani ya fito daga cike ya tare ni inda yace "bawan Allah dan Allah tambaya nake" Kai tsaye nace mishi "Allah yasa na sani tambayana yayi a cikin unguwanmu ko na San wane kaza ni na manta sunan mutumin da ya kira nace ban sanshi ba sbd ni bako ne, ya kuma tambayar ina zanje nace kasuwa yace muje su rage min hanya fir na ki shi kuma ya kafe har yayi nasara ya sakani shiga motan ba don na so ba.

Muna shiga naga manyan maza akallah hud'u na gaban ne yace "aikinka yayi kyau weezy wannan ze yi" kan nayi wani yunkuri sun shafamin wani farin powder, ban tsinci kaina a ko Ina ba se wani katoton d'aki me cike da kayan alatu inda ina farkawa wani babban mutum Alhaji ya shigo ya fara min daad'in baki da nunamin ze bani duk abinda nake so a duniya In har zan amince mishi.

A take na gane manufarshi inda na kafe da yarda na kam baze samu hakan ba, har barazanar kisa da bindiga ya min naki amincewa se adu'a da nake tayi a zuciyana yana fita daga d'akin na bishi a baya inda na maqale Ina karewa babban parlorn kallo waya naga yanayi yana cewa matsalan Ai boka yace se da amincewar yaro za'ayi gashi wannan yaki amincewa.

Banji abinda aka ce mishi a d'ayan bangaren ba se naji yana cewa "Ai yaron na gayamaka kyakyawa ne na karshe ni raina ya biya ko ta karfi zanyi mishi In yaso In nemo na tsafi kuma" dariya ya dingayi bana de jin me ake fad'amishi ban bar adu'ar da nakeyi ba sam don kubuta daga hannunshi d'akin da nake naga ya nufo da sauri na 'buya a Bayan labule ya wuce ba tare da ya bud'e ba ya sa key ya murza yana dariya ya fice a sad'ad'e na dinga bin bayanshi har zuwa wajen katon gidan dake ciki daji, ban tsaya ba na dinga bin jikin gini zuwa bayan gidan na samu da kyar na haye ginin sbd tsawonshi Ina samun fitowa na ranci na kare ba ni na tsaya ba se akan titi gaban wani mota kan In ankara naji motar ta kad'e ni, Toh kunji abinda ya faru".

Kuka khairi ta dingayi yayinda musharraf ke jin zafin kukan nata har ranshi kaman wani punishment takeyi mishi hakan yasa ya had'e rai sossai kaman be ta'ba dariya ba, Abul ne ya kalleshi ya kuma kallon little tukuna ya kalli khairi yace "'yar uwa ya bayan rabuwa kuma? Ina Dada da twins? Ya kukayi rayuwa bayan 'bacewata?" Khairi tana share fuskanta tace "labari ne me tsawo" kallon musharraf tayi ta tabbatar ta 'bata mishi rai da kukan tan nan hakan yasa tace "yanzu dare yayi kuma naga nurse ta kawo takardar sallama kana bada labarin nan, kuje gida muma gida zamu tafi gobe in Allah ya kaimu zamuzo zakaji duk yadda akayi" kai Abul ya gyad'a sallama sukayi musu kan suka fice musharraf na sa'be da little da tayi bacci a kafad'a basu jima da fita ba su Abul dinma suka fito suka wuce gida.

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️9️⃣4️⃣▶️9️⃣5️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Har suka shigo gida uffan be ce mata ba kuma be sake fuska ba hakan yasa suna shiga d'aki tayi narai narai da fuska tare da kwanciya a gadon bayanshi ta zagaye cikinshi da hannunta duk biyu cikin taushin murya tace "am so sorry dear, plz Kayi hakuri bazan kara ba" lumshe ido yayi yana tunanin anya son yarinyar nan baze yi ajalinshi ba? Juyota yayi ya rike tafin hannunta yace "ni zan rokeki qalbee baki san yadda hawayenki suke da tsada da daraja ba? Zubar dasu kaman wani babban asara ne a gareni plz ki dauri ki dena irin wannan kukan it really hurt here wallahi" ya karasa yana nuna setin zuciyarshi.

Dukar da kai tayi tabbas maganganunshi sun shigeta kuma da yardar Allah bazata sake kuka a gabanshi ba tunda yana damunshi, tsintar muryarshi tayi yana cewa "baza kiyiwa assiddiq d'inki wannan alfarmar ba?" Dayake haka In ta bushi iska take kiranshi kuma sunan na mishi daad'i sossai kasancewar ba wadda ke kiranshi ko da Abubakar d'inshi ne bayan 'yan office d'insu.

Zagaye hannunta tayi ta wuyarshi ta kara tsai tayi brushing lips d'insu kan tace "In shaa Allahu bazan kara kuka haka ba baby" murmushi yayi yana cewa "Ohk baby amma fah kin tada wani fitinar" kashe mishi ido tayi tana jefanshi da wani irin murmushi da shi kad'ai ya san ma'anarshi

bata hankara ba se ji kawai tayi ya rabata da kasa zuwa gado, a hankali na fita na ja musu kofa.

Washegari kuwa suka koma gidan Alhj Abdulrashid inda anan ya roki sanin su wanene su, ba tare da wani damuwa ba Abul ya zayyane mishi labarinsu wadda seda sukayi hawaye musamman Afreen da Nasreen da suka kasance masu raunin zuciya, irin kallon da musharraf ke wullo mata ne ya hanata kuka a wannan karon da ta tuna labarinta for the first time in history, bayan Abul ya gama ta basu labarin bayan barin Abul gidan har kawo yau, jinjina kai Abul yakeyi cike da farin ciki wai yau 'yar uwarshi ce tayi aure a garin Abuja tana jin daad'inta cike da soyayyar mijinta gashi tayi wani irin mugun kyau ta kara haske.

Nan musharraf ya roki alfarmar Abul yayi zamanshi dasu Abba In sun tashi komawa Gombe se su tafi gabad'aya suyiwa dada surprise, tambaya Abul yayi "yaushe ne tafiyankun hamma?" Musharraf yace "nan da three months" dukda Abul be so ba sbd kewan dadanshi da kannenshi da yakeji amma ba yadda ya iya musamman da yaji Abba na cewa "hakan shine daidai sbd ko ni zan samu nayi scheduling duk wani aiki nawa" haka suka tsayar kan kowannensu ya wuce abinda ze yi Afreen da Nasreen duk Nile university suke karatu amma different courses.

Bayan wata uku

Khairi ta samu nasarar kare exams d'in first semester cikin nasara don Allah yayita me kwakwalwa hakan yasa exams d'in be yi mata wahala ba, ta 'bangare d'aya kuma soyayyarsu da musharraf se kara gaba yake yi basu ta'ba ji sun gunduri juna ba, dukda zaman yau da kullum ana samun sa'bani amma daga d'aya ya hau d'aya ze sauka se wadda ya hau d'in ya sauko da kanshi tukun su fahimci juna, haka zumuncinsu da su Abba ya kara tsanani In ka gansu kaman wasu family yawanci 'yan matan suna gidan khairi hakan yasa Abul ma nan yake tarewa In Abba ya samu sarari da kanshi yake zuwa ya tattara su amma baze hana a washegari khairi ta gansu ba, little ma ta kare term d'inta itama ta saba sossai dasu Anty Nasreen d'inta, dukda khairi ta lura da take taken Afreen na son musharraf hakan be sa ta chanza mata ko a fuska ba don ta yarda da kanta ta tabbatar ita kad'ai ce a birnin zuciyar mijinta dukda shi musharraf d'in ba kowa ke ganin fuska a wurinshi ba halin shin nan na nan yadda yake treating su Amrah haka yake yiwa su Nasreen.

A washegari zasu bar Abuja to gombe Abba yayi musu komai na flight da zasu bi dukkansu har 'ya'yanshi don yana so da kanshi ya damka Abul a hannun mahaifiyarshi gashi kuma yana son yaron har ranshi, zaune suke akan gado shi yana daga bakin gadon kafafunshi na zube a kasa system ne akan desk dake gabanshi yana dannawa gefen system d'in hot coffee ne yana sipping daga shi se wani gutun three quarter milk in kuka ga yadda ya kara wani irin haske da murjewa se kunyi mamaki.

Khairi na kwance daga bayanshi daga ita se a wani 'bingilelen riga nylon pink me hannun vest gashinta a sake bata saka mishi ribbon ba ko de tace ta saka musharraf ya cire fuskanta d'auke da kwalliya sossai wadda har seda nayi mamaki (a su khairi an waye😜) kunnenta sanye da fashion pink video call takeyi da Amrah da miemie se surutu suke zubawa ba ma su san

musharraf na gefenta ba se tsokananta suke.

Amrah tace "irin wannan kyaun haka khairi ko hammanmu ya miki ajiya ne" hararar ta tayi tace "wallahi ki kiyayi bakinki na gaya miki ba wani ajiya" suka saka dariya Miemie tace "seriously Khairi kinga wani irin fresh da kikayi sa'banin Adda nuri da ciki ke wahalar da ita ba kaman farkon aurenta ba itama baki ga yadda ta zama ba amma yanzu se kashi bata iya cin komai" Khairi ta waro ido tare da yin fuskan tausayi tace.

"Dama haka cikin yake? Da gaske mutum baya iya cin komai?" Amrah na dariya tace "matsoraciya khairi ke damuwanki kar babynmu ya hanaki d'urin da kika saba ko" harara ta wurga mata "ban son tsiya dama chan ci ne dani?" Miemie tayi saurin cewa "a'a kede yanzu me albishir d'in?" Ta san karamin aikin khairin ne ta kashe wayanta kan ta fad'a musu albishir da ta kirasu dominshi, murmushi ta saki tace "muna hanya gobe idan Allah ya kaimu" wani irin ihu suka saka cikin jin daad'i maida idonsu da zasuyi kan wayan suka had'a da musharraf Ai da gudu suka watse suka bar fuskan wayan na kallon gini, murmushi ya saki yayinda khairi ke dariya harda rike ciki.

Kallonta yake tayi yana mamakin mutanen da suke cewa In ka auri mutum sonshi raguwa yakeyi a zuciyarka, shi kam be gani ba sema sonta da kaman kara mishi a keyi a kullu yaumin sossai ya shagala da kallonta har be san sadda ta gama dariyar ba se iska me kamshin strawberry da ta hura mishi a fuskanshi hakan ya sashi lumshe idon ya kuma ware a kanta a hankali yace "Ina sonki ummu Abdurrahman".

Juya ido tayi alamun tunani kan tace "waye ummu abdurrahman kuma?" Yace "ke mana duk kika haifi d'a namiji Abdurrahman Sudays zanyi naming d'inshi don Ina son sunan" shagwa'be fuska tayi tace "zan iya kuwa baby? Baka ji su Amrah na cewa Adda nuri na wahala ba?" Yace "I didn't believe them me yasa muna waya da nuriyyah bata ta'ba sanar da ni ba? And more over Ai kowa da yadda pregnancy dinshi ke zuwa so plz ki manta da maganansu" shafa cikinta yayi yace yana karya wuya "ni kam Ina mamaki duk irin jarumta na dinnan ace har yanzu banyi ajiya anan ba?".

Baki ta turo tare da ture hannunshi wayanta ta d'auko ta kira momma ta sanar dasu zuwansu, haka ma dada nan kam ya kar'ba suka gaisa da dadan da kuma twins, nan fah ta shiga group din family d'insu ta sanar da shigowarta gombe a goben don saura kwana uku a fara events d'in bikin su marwa duk ankon da za'ayi sun turo mata sample ta nema a nan abujan telan su Afreen ya kashesu da styles d'inshi masu tsananin kyau aka goge mata sune ma kasan akwatin tafiyansu.

Bayan ta gama wayoyinta ne ta dubi musharraf dake kwance rigingine ya zuba mata idanu tace "baby lafiya kuwa irin wannan kallon?" Yace "wallahi kyau kika min bana ta'ba gajiya da kallonki hasken idaniyata Ina sonki har ban san adadi ba, a tsakankanin da kika shigo rayuwata ban ta'ba zaton zan fad'a irin wannan komar son ba ko da ance zan fad'a to tabbas me rabani da wadda ya fad'a d'in se Allah.

Amma gashi yau Abubakar Assidiq (musharraf) ya zurma ciki yayi Nisan da baya jin kiran, idonshi yayi rufewar da inba tauraruwarshi ummulkhair ba baya ganin ko wacce mace a matsayin mace se ma maza 'yan uwanshi da ya maishe su" fuskanta ta matso setin nashi tana d'an hawa jikinshi tace "ummulkhair ma na tsananin son mijinta, hasken rayuwanta, me cetonta har yau Ina jinjina tsayuwa da kayi ka ceceni a lokacin da wasu suka so keta min haddi na tabbatar da kai ka so hakan ne sbd kaine me driving a lokacin kuma kai ka fara fitowa kan haidar, sannan ba'a mamaki da ikon Allah baby, Allah shi ke sawa bawanshi son wadda ya so a lokacin da ya so, zaka sha mamaki In na ce maka tun daga randa na fara d'aura idona a kanka a arabian estate na fad'a tarkon sonka me tsanani da azaba so me hana bacci..." katseta yayi ta hanyar maidata kasanshi yayi mata runpa da broad bare chest d'inshi.

Yana kallon tsakiyar idonta yace "ya isa haka qalbee In ba so kike zuciyata ta fashe da kalamanki ba, dukda kin riga fara sona amma kuma na fi sonki yanzu akan son da kike min, kece numfashi na, In har bakya tare dani to tabbas na dena numfashi kece hasken idaniya na a duk sadda kika barni to bana iya gani sbd kin tafi da hasken dake haska min hanya ta cikin idanu na, kece fitilar zuciyata a duk sadda kika dusashe toh fah zuciyata bazata kara wani anfani ba sbd ba jigonta kinyi kane kane a cikinta, bana iya kwararren minti guda ba tare da kwalkwalwana, zuciyana da kuma numfashina sun ambaci sunanki ba, wallahi ban san iya son da nake miki ba, Ina miki....." bakinta ta rufe da nashi duk tsikar jikinta na tashi kalamanshi na narkar mata da zuciya.

Amsa yayi ya fara aika mata da wasu irin darrusa da ita kad'ai ce me iya fahimta har tayi hadda ta kuma rubuta gwajin aji da jarabawa a kanshi ba tare da ta kuskure ko abu guda ba, ita kad'aice me fitowa da flying colors a wannan class na malamintan, zamewa nayi waje kan waennan malama da d'aliban su rutsani, sossai suka nunawa juna irin son da sukeyiwa juna bayan sunyi wanka ta saka mishi akwati biyu a gaba tana mika mishi kaya yana shiryawa nata ya fi girma komai ta d'auko ta miko.

Dariya da mamaki suka kamashi yana dariya yace "qalbee Ina zaki da waennan kayan? Ba de planning barina kikeyi ba don wannan yafi karfin sati biyu sede shekara biyu" turo baki gaba tayi tace "baby me abun dariya anan? Duk fah zanyi anfani dasu" yana ci gaba da murmushi ya girgixa kai ashe da gaske ne da aka ce duk inda mace take bata rabo da tarukucen kaya yanzu dan Allah ina zata kai duk waennan kayan, be kara cewa komai ba se dariyan da yakeyi jefi jefi yana kallon akwatintan, Ai kuwa ta turo bakin nan kaman ze ta'ba gini hakan kuwa kara bashi dariya yake.

"Kina da kyau" ya fad'a In a whisper kallonshi tayi ya d'aga mata gira tare da kashe ido, murgud'a mishi bakin tayi tare da ficewa daga d'akin yana murmushi ya ja musu zips d'in akwatunan tare da d'agawa ya jingina da jikin wardrobe jallabiya ya sanyo sbd su nasreen da suke nan ya sauko kasa d'akin da suke sauka ya kalla dayake dad da Abban gombe sun turomata da kayayyakin d'akin, kokonto yake na inda ta shiga daga karshe d'akin little ya bud'e se kuwa suka had'a ido tana tsaye tana shirya mata kayanta cikin akwati yayinda little ke zaune

bakin gado tana zuba mata surutu.

Ciki ya karasa ya biyewa little sukayi ta surutu har sukayi nasarar sata dariya harda rike ciki cikin farin ciki da kaunar juna suka fito khairi na cewa "yau na bar baba A'i da aiki" me aikin da hajiya ruqayyah ta turo musu mijinta ya rasu kuma bata ta'ba haihuwa ba gashi ta manyanta don zatayi sa'a da momma hakan yasa suke girmamata kaman ba me aiki ba, bayan su musharraf sun zauna ta kawo musu natural lemo da take harhad'awa ta sa a fridge a gabansu ta ajiye da cup ta wuce kitchen don duba baaba A'i.

A daren su nasreen suka tafi don samun su had'a kayan da zasu tafi dashi washegari karfe goma cip suka had'u a airport ba wani 'bata lokaci suka sauka a gombe motoci biyu suka zo taryansu daga gidan momma Inda ba 'bata lokaci suka isa har parlor momma tayi musu iso Bayan gaisuwa da sannu da hanya ta gabatar musu da abinci dayake 'yan boko ne ba wani fulako suka zauna suka kwashi gara.

Momma kam farin ciki kaman ya kasheta don ganin yadda tilon d'anta ya koma gashi kulawar da khairi ke bashi a gida haka take bashi a gaban kowaye don shi ya koyarmata da hakan Bayan sun gama ci suka koma parlor inda khairi tace "momma banga su Amrah ba" bata rufe baki ba suka shigo parlorn ihu suka saka tare da nufarta suka rungume suna jin daad'in ganinta tsaki musharraf yaja yana girgiza kai bayan gama oyoyo d'insu musharraf ya dubi momma.

"In zaki lura da wanchan zaki ga irin kaman da sukeyi da qalbee ko momma?" Ta kalli Abul tace "kwarai kuwa" yace "toh shine twin brother d'inta" nan ya basu labarin yadda ya tsinci kanshi a hannun muggan mutane da yadda ya tsira momma salati ta dingayi tana mamakin halin mutanen duniya maganan musharraf ne ya katse mata mamakinta "yanzu na tara familyn Alhj Abba Umar suna jirana da surprise da nace zan musu" mikewa momma tayi tace "Toh ku tashi mu tafi" mikewa sukayi suka fito, ababban parlorn inna suka tarda mutanen gidan gabad'aya zaune, sallaman Abul ne yasa dada mikewa da karfi.

*Aslm kwana biyu kun jini shiru banji daad'i bane na lalla'ba na yi muku ba don na warke ba se don kar nayi ta ajiyeku jira zanyi briefing in shaa Allah 2-3 pages left*

#vote

#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

IGIYAR RAYUWA😭

🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Page➡️9️⃣6️⃣▶️9️⃣7️⃣
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️

Da sassarfa ya karasa ya fad'a jikinta yana jin kewan mahaifiyarshi na dawo mishi sabo hawayen tausayin kansu ya ci gaba da sulala daga idanunshi, mutuwar tsaye dada tayi na mintuna abunda bata ta'ba mafarki ba, bata ta'ba sa rai ba, ko a kiyasce bata ta'ba kiyasta ganinshi yanzu ba sede ba'a mamaki da ikon Allah, Allah aka ce yafi gaban komai yau gashi bata mutu ba Allah ya had'a ta da d'anta da ta fidda ran ganinshi kuka ta fashe dashi tana tuna rayuwansu na baya.

Khairi da tayi narai narai da ido alamun itama kukan zatayi suka had'a idanu da musharraf harara ya sakar mata hakan yasa ta mayar da hawayen nata don dole inna ce ta katse shirun parlorn da cewa "Kai Habu menene wai ka wani tara mutane ba tare da wani jawabi ba

kwatsam wani katon saurayi yazo ya fad'a jikin safiya yana ta kuka kaman wadda akayiwa mutuwa" murmushi musharraf yayi yace "Abulkhair kukan ya isa haka plz saketa ka samu wuri ka zauna, inna yanzu zamu miki bayani" sake dada yayi ta zauna shima ya zauna a gefenta tare da riko hannunta se a lokacin yaji kunyan abunda yayin ya kamashi ganin mutane dayawa a parlorn don duk familyn an had'u sbd bukin da suke dashi.

Cikin natsuwa Alhj Abdulrashid yayi musu bayanin kanshi da yadda ya samu Abul inda yana ajiye aya Abul ya d'auka ya musu bayanin bayan fitanshi gida da abunda ya faru dashi inna kuwa ta dinga zagin waenchan mutane yayinda Abba ya sha Adu'a dada ma sossai ta mishi godiya murmushi kawai yayi nan 'yan matan sukayi waje haka hajjiya ruqayya, dada da momma sukayi d'akin dadan inna ma ta tafi d'akinta yayinda haidar da su Jamal suka ja musharraf zuwa part d'in samarin gidan.

Drinks aka kawo wa iyaye mazan inda shafin hira ya bud'e anan Alhj Abdulrashid ya amayar da abunda ke ranshi don d'an boko ne tsantsa be iya rufa rufa ba, sunyi murna sossai inda suka ce zasu tuntu'bi dada, a bangaren musharraf kuwa suna de zaune da su jamal se hiransu sukeyi amma shi kam be sa musu baki ba sam sede abun dariya yayi murmushi, haka 'yan matan da suka kasance su goma sha d'aya chas a zaune a parlorn mommy suna shan hira amare da Adda fadeelah suna site d'in umma little ita kad'ai zaune a parlor tana kallo sbd su nabeel suna makaranta haka Ameer ma, a gaba suka saka khairi da su Amrah suna rokonsu su dawo gidan nan da zama har a gama buki, murmushi kawai khairi takeyi tana ayyana yadda zata iya rabuwa da musharraf na sati guda ta san shima ba yadda ze yi ba sun riga da sunyi shakuwar da ko kwana d'aya da kyar zasuyi In ba sa tare da juna.

Amrah ce ta dubi su Asiya tace "tab ku gama 'bata nyau bakinku kuyi shiru don wannan Juliet d'in baza ta iya rabuwa da romeo d'inta ko na awanni biyar ba bare kwana bakwai" harara khairi ta sakarwa Amrah yayinda 'yan matan suka kwashe da dariya tana murmushi tace "seriously baby baze yarda nayi kwanakin nan ba tare da shi ba amma ku gwada tambayarshi wala alla ya yarda".

Hafsat tace "kaji 'yar air kema kin san ba yarda zeyi ba shine zaki turamu ya dizga mu" Asma'u tace "bare ma yadda yake wani ciccin magani yake 'bata ran nan Ina muka ga fuskan tambaya" Afreen tace "bari zan gwada tambayarshi" murmushi kawai khairi tayi tana girgiza kai kan wayanta ta maida hankali ganin yana haske sakon musharraf ta gani inda ya turo "You are everything I think about. Yes, I am mad. I am madly in love with you." Murmushi me kyau ta saki tana girgiza kai ta fara replying.

"My very existence revolves around you. I am nothing without you my sweetheart. And I love yhu too baby" ajiyar zuciya ya sauke yana sake murmushi me sauti haidar yace "hmmm wannan irin unique dariya haka na tabbatar kanwarmu ce sila so pay for it" harara musharraf ya sakar mishi suka kwashe da dariya musharraf yace "Ai let me tell yhu something da baka sani ba no amount in this world that can buy this happiness neither gold nor diamonds, kai gaskiya ya kamata wadda be yi aure ba yayi aure don wollah duk wadda be da aure be san abunda ake

kira happiness, natsuwa da enjoyment ba" waro ido su jamal sukayi don sun san da su yake tunda haidar na da aure.

In disbelief bashir yace "Lallai ma musharraf dama ka iya zolaya?" Faisal kam se dariya yake jamal yace "kwantar da hankalinka muma mun kusa angwancewa muji abinda kukeji" musharraf yace "yhu are not serious da kun shirya da munji a kasa" haidar yace "Ai ko gashi har sun fara zama tuzurai" dariya musharraf ya sake yana kallon faisal da ya fusata kaman ze naushi haidar kan shima ya fara 'bula shi nan fah suka fara tsokanansu suna musu dariya tun suna jin haushi har suka komar da abun wasa.

Se yamma lis su musharraf suka shirya tafiya zasu wuce da su nasreen yayinda Abba ze kama hotel ba yadda su daddy basuyi da shi ya kwana anan ba yaki Abul kam nan suka barshi 'yan matan gabad'ayansu suka rako su parking lot su nabeel na ta shagwa'ban zasu bi su sbd little da suka gani amma dada ta ki sun dawo suka samu hammansu ya dawo inda daad'i kaman ya kashesu ganinshi.

Kasa kasa hafsa tace "Afreen tambayar mana shi mana" kallon shi Afreen tayi zuciyarta na tsinkewa gaskiya baza ta iya ba yadda ya had'e rai kaman be ta'ba dariya ba yasa tsoron tunkararshi ya shigeta kaman ya san zasu so hakan dama seda ya raya a ranshi khairi zata so tambayarshi kwanaki anan abunda baze yarda dashi ba kenan.

Har suka ja motarsu suka fice daga gidan fuskan nan nashi ba a sake ba, a d'akin nuri momma ta sauke afreen da nasreen yayinda little ta sauka d'akinta, khairi kuma part d'in mijinta ta yada zango, kullum sede suje gidan buki su yini su dawo, ranar d'aurin aure da safe khairi suna zaune daga parlorn hajiya suna jin d'aurin auren da ake daga nan sbd a kofan gidan ake yi, kaman daga sama khairi taji d'aurin auren da akayi daga karshe inda maroka suka fara sanarwan 'an d'aura auren safiyya Ali gamji da mijinta Alhj Abdulrashid hameed' khairi is beyond shock abunda bata ta'ba zata ba bata ta'ba kawo hakan a ranta ba, sossai ranta ya sosu taji ba daad'i.

Bawai don auren da dadan tayi ba se don rashin fad'amusu Ai ya kamata ta fad'a musu amma suji abu daga sama haka sam ba daad'i bata gama tunaninta ba taji nabeela na cewa "Adda Khairi dada d'o nyaune"(dada na kira) kallon su nasreen dake ta murna tayi kan ta mike ta nufi sauka daga saman zuwa part d'in inna, "salamu alikum" ta furta a sadda ta sa kanta a d'akin na dada.

Dada da Abulkhairi ne suka amsa ta karasa ta zauna a sanyaye tace "dada gani" Shiru dada tayi na mintuna sama da biyar kan tace "na san ban kyauta ba, na san bazakuji daad'in auren da nayi ba tare da shawaranku ba, nima ban san da gaske zanyi auren ba seda aka fara zartar da d'aurin auren su Marwanatu, tun randa kuka zo gidan nan da dare inna ta kirani take fad'amin abunda Abdulrashid yazo dashi inda take sanar dani yace tun kan zuwanshi tun be ganni ba be san ya nake ba ya kudiri aure na, sbd labarina ya matukar bashi tausayi.

A lokacin na nunawa inna ban yarda ba, ba yadda batayi ba naki, su Hamma muddasir ma sun yi sun yi naki, inda suka bashi hakuri amma shi kullum se ya zo yayi magiya ban fad'a muku bane sbd ban da niyyan auren amma maganganun inna na yau sun karya min zuciya har na aminta da auren a kurarren lokacin da ban samu nayi shawara da ku ba, kuyi hakuri ni karan kaina ban ta'ba zaton auren wani namiji ba bayan mahaifinku ya soni son da ban ta'ba ganin irinshi ba ya zauna dani tun daga farkon zaman mu har karshe ba tare da ido ba amma be ta'ba nuna gajiyawarshi gareni ba bare yayi maganan auro wata, na soshi kaman numfashi na kuma har gobe Ina sonshi, ban so yin wani aure ba sbd Ina son zama shugaban matanshi na gidan aljannah amma Allah be yi ba, Allah yaji kanka Umar ya kai haske makwancinka, ban ta'ba kai kaina kasa da sunan sallah ban nemar mishi gafara ba, ban fata auren da nayin nan ya katse wanna........"

Kuka ne ya sarke ta dama tunda ta fara maganan hawaye ke tsiyaya a idonta, su Abul da khairi ma kuka suka sake suna jin mutuwan ya dawo musu sabo ta'bon na nan ashe be da ranan warkewa a cikin zukatansu, kuka suka dinga yi kaman yanzu ne akayi musu mutuwan inna ce ta shigo da sallama baki sake take Kallonsu d'aya bayan d'aya kan tace "wani irin shashanci ne wannan safiya? Me kukeyin nan? Yanzu fisabilillahi god'e god'e dake ki zauna kisa yara a gaba kina kuka sunayi auren dole aka yi miki?".

Girgiza kai dada tayi tana share hawaye hararan su khairi tayi tace "ko su waennan pakarun ne suka ce miki basa son auren naki?" Nan ma girgiza kai dada tayi tace "mahaifinsu muka tuna" inna tace cikin takaici "ji min shashanci yanzu don kun tuna umaru se ku ta mishi kuka? Ba adua ya kamata ku dinga mishi ba? Baku san kukan nan kara mishi nauyi kuke ba aduarku kawai yake bukata? Mtseww ku ci gaba In kun ga dama" ta juya ta fice.

Abul yace "Dada Allah sanya alkahiri na tayaki farin ciki sossai don Abba ba mutumin banza bane mutum ne me sanin darajar d'an Adam, yana da karamci sossai da mutunci duk yadda zan kwatanta miki shi baza ki fahimta ba se kin zauna dashi" Shiru kawai dada tayi, khairi tace "Allah sanya alkahiri" tare da mikewa ta fice, dada tace "Abulkhairi kaman 'yar uwarka bata so auren nan ba" shima ya lura da hakan sede ya ta iya aikin gama ya gama tunda an riga da an d'aura hakan yasa yacewa dada "zata so ne with time in shaa Allah".

Direct motan momma da keyn ke hannunta ta shiga ta ja ta fice daga gidan, yana tsaye yaga wucewarta dama doguwar riga sea green ce jikinta kirar kasar Oman me stones dayawa a hannu da jikin rigan gyalen ne a d'aure a kanta ko warwarewa batayi ba bare ta yafa Allah ya sa ma rigan me kaman bubu ne daga wuya har gwiwan hannunta duk a rufe suke, yanayin driving da yaga takeyi ya tabbatar mishi akwai abunda yake damunta dama jikinshi ya riga ya gama bashi, motanshi ya shiga da yake a jikinshi yake jingine bayanta yabi.

Tana parking a haraban gidan ta bud'e kofa ta fita zuwa part dinsu a kan gado ta fad'a tana lumshe ido hawaye na gangara mata Allah sarki Abbanta, bata ji shigowarshi ba se ji tayi an dafa goshinta tare da sa tattausan hannu aka share mata hawaye kamshin turarenshi ne ya sanar da ita waye tun kan ta bud'e ido a hankali ta bud'e ta zubo mishi idanuntan da suka

chanza launi.

Kallo d'aya ya mata ya san ba yanzu ta fara kukan ba cikin damuwa yace "qalbee auren dadan ne bakya so?" Se ta sa mishi kuka da sauri ya zauna da kyau tare da jawota jikinshi ya rungume yana shafa bayanta a hankali ya fara rad'a mata wasu kalamai masu kashe jiki da shiga zuciya cikin hausa da turanci kai har fulatanci inda yayi mata nasiha sossai akan kin auren dadan da takeyi ya nuna mata shine mutuncinta sossai bayananshi suka gamsar da ita tayi lakwas a jikinshi Ai ko batayi niyyan hakura ba dole tayi don waye ita da zata iya fuskewa wannan lallashi.

Basu koma gidan ba suka yini soyewa abinsu se dare suka shirya zuwa dinner kawai, sun yi kyau kuwa sossai kaman ka sacesu ka gudu, suna like da juna suka shiga event center din inda suka tafi da imanin mutane dayawa tunda suka zauna be barta ta tashi ba sema wani tsare gida da ya karayi fuskanshi na nuna tsantsar kishin shi akan matanshi don gani yake kowa kallon young beautiful wife dinshi yakeyi don tayi masifar kyau fiye da amaren.

Bayan kwana uku Abba ya d'auki dada, nabeel, nabeelah, Abul, nasreen da Afreen suka wuce Abuja don ya ce shi ze rikesu bisa amana kaman shi ya haifesu don ya san dada baza ta ta'ba iya muzantar da yaranshi ba so me yasa baze iya rike nata ba, har suka tafi khairi bata nunawa dada ta sauka ba don har yau In ta tuna da wai dada tayi wani aure se taji wani irin kishin Abbansu nasreen ya kamata, bata ta'ba bari sun had'u dashi ba tun bayan auren.

Sati d'aya mekyau suka kara tare da su dada kan suka fara shirin tafiya sunje sun yini a dukku suka gaishesu suka dawo cike da abun arziki don yanzu dadda ta sauka akan kin auren ta riki khairi kaman sauran surukanta, tare suka je gidan nuriyyah aiko khairi ta kara tsorata da ciki don ganin yadda nurin ta koma bata iya cin komai duk abunda ya shiga se ya fita musharraf ma ya tausaya mata, marwan ke sanar dasu Doctor yace In cikin yayi wata hud'u zata dena su dena tada hankalinsu.

Cike da tausayinsu suka dawo sunje gidajen uncles dinshi gabad'aya amma hajiya Aisha mahaifiyar marwan ce kawai ta yi mata tarba ta mutunci amma banda hajiya zulai, haka Anty rabi ma wulakanci kawai ta mata bata damu ba sam ko a kwalan riganta mijinta na zuwa ta nanukeshi suka wuce, sossai su Amrah suka ji haushin tafiyansu don zasuyi kewansu sossai musharraf yayi musu alkawarin zuwa Abuja next hutunsu suka tafi suka barsu da kewa.

#vote

#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo 6763

'Yar mutan Adamawa

Second To The last page

Page➡️9️⃣8️⃣▶️9️⃣9️⃣
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Bayan kwana biyu da dawowarsu suka je gidan Abba a parlor suka samu familyn gabad'aya zaune ana hira gidan gabad'aya an sake renovating har furnitures din an chanza kuma Abban ne da kanshi yayi yaki sam su Alhj mudassir suyi, da gudu su nasreen suka zo suka rungume khairi suna murnan ganinta bayan sunyi breaking hug din suka je zasu rungumi little da gudu tayi kan cinyar dada tana tura baki.

Dariya suka saka don sun san fushi tayi da suka fara rungume mommynta, sukayi kanta a cewarsu se sun rungume tan, da gudu ta fara zagaya parlorn suna binta, d'an karamin tsaki musharraf ya saki da su Amrah ne ba abinda ze hanashi make yarinya, khairi tace kasa kasa "sorry mu karasa" karasawa sukayi Abba na musu Sannu da zuwa haka dada ma har kasa suka duka suka gaisheshi ya amsa da fara'a haka dada ma, bayan sun gama gaisuwan ne suka mike suka zauna saman cushions.

hira suka fara khairi de se kallon dada takeyi tana mamaki dada ta dawo wata hajiya tashi d'aya ko leshin jikinta ma abin kallo ne se ta fito a marar shekarunta anan ne ma take ji wai next week zasu tafi Spain akwai abinda ze kai Abban ze tafi da ita a gwada mata aikin ido, sossai khairi ta nuna jin daad'inta tayi ta wa Abba godiya yana dariya yace "me na godiya ummulkhair bayan matata nayiwa" murmushi tayi tana dukar da kai, sallama musharraf ya musu ya fice akan se da dare ze dawo ya d'aukesu, har wurin mota khairi ta raka shi suna 'yar hiransu na masoya.

A d'akin Nasreen ta yada zango inda nan ta samu Afreen suka shiga hira suna tuna abubuwan da aka yi tayi lokacin bukin su marwa, kan ta shiga seda ta leka little a d'akin nabeela ta gansu suna wasa da kayyayakin wasan nabeelan d'akin kawai abin kallo ne an shiryashi gwanin sha'awa.

Bata ga Abul ba seda suka zo cin abinci daga gani da alamu yanzu ya tashi daga bacci "eyeee jin daad'i se yanzu ka tashi?" Murmushi yayi yace "to 'yar uwa me mutum ze yi yanzu bayan baccin ba karatu ba komai gashi Abba ya hanani d'inki" murmushi tayi kan tayi magana Abba yace "Eh ba wani d'inkin da zakayi da raina da lafiya na ga kud'i, zaman rashin karatun ma na this year ne kawai next year zakayi waec da neco In had'aka da 'yan uwanka a Nile" murmushi kawai Abul ke ta bugawa cikin jin daad'i wai yau shine ze je Nile university hmm Allah kenan, se kuma tunanin Abbanshi ya fad'o mishi adu'a kawai ya mishi ya ci gaba da cin abincinshi.

Bayan sun gama cin abinci d'akin dada khairi ta shiga ta fad'a gadonta se bacci dayake fashin sallah take se la'asar lis ta farka ta shiga ta wanko fuskanta da bakinta a bakin gado taga dada zaune bayan fitowanta tana murmushi tace "dada kinyi ta shigowa Ina bacci ko?" Dada tace "Ai ko de wannan baccin naki kaman ba na lafiyannan ba har yanzu yana nan khairi? A gidanki wa ke miki aiki?" Tura baki tayi tace "na dena fa dada, yanzu dinma don baya nan ne amma ai matsalan hamma dayawa yake In yana tare dani" dada tace "hmm to an ji me miji, ba de haka kike sake baki kiyi ta surutun miji da kawaye ba kam?" Bubbuga kafa ta fara "haba haba dada se kace wata sakarya, wannan ma fah don kene" hmming dada tayi inda suke ci gaba da hiransu na tsakanin 'ya da uwa inda har dada ta tambayeta jikinta baya tashi ko, tace tunda suka tashi ranar kamu da dare basu sake tashi ba.

Dada Tace "ranar kamunku?" Khairi ta amsa da Eh inda ta bata labarin duk abinda ya faru yadda taji a bakin su Amrah girgiza kai kawai dada tayi tace "Allah ya kyauta" anan ne ma khairi ta fad'a mata sharrin da aka mata wadda seda tayi hawaye da ta tuna, da farko dada taji tsoro sossai amma da taji sunyi resolving issue din se kawai tayi adu'ar kariya a garesu.

Se bayan isha musharraf yazo ya d'aukesu anan dada ta sa aka ma surkinta special girki suka tafi da shi bayan Abba ya bata kud'i da farko kin kar'ba tayi seda taga ranshi ya 'baci ya nuna mata kaman su nasreen take yanzu a wurinshi da ba don ma tayi aure ba da tare ze had'asu ya zama Abban triplet dariya kowa yayi aka raka su har mota suka tafi.

Ranar tafiyan su dada har airport suka rakasu su nasreen harda shagwa'ba suke mata akan zasuyi missing d'inta se ka rantse itace ta haifesu haka suna ji suna gani suka tafi, dama Khairi tayi niyyan d'aukan su nabeel kan su dawo Abba yace be yarda ba kar a raba mishi kan 'ya'ya dada ba bata goyi bayan hakan ba hakan yasa ta hakura, a airport din duk suka rabu kowa ya kama hanyar gidanshi.

BAYAN WATA SHIDDA

Rayuwa ta ci gaba da tafiya cikin hukunci na Allah yau da gobe asarar mai rai, wani lokacin ayi farin ciki yayin da wani lokacin akasin hakan, inda wani lokacin ayi fad'a wani lokacin a shirya, haka rayuwa ta ci gaba da gurguzawa su khairi tana karatunta cikin mai da hankali hakan yasa take samun cin nasarar duk wani abinda tasa a gaba a school d'in inda tayi suna a department d'insu ta kasance 5pointer.

Kowa ji da ita yake musamman lecturers d'insu, a 'bangaren musharraf ma Alhamdulillah aikinshi yake cikin yarda da amana zuwa yanzu ko warin taba ma baya son ji bare a kai ga sawa a bakinshi da sunan sha Amma har yanzu d'an bakin da yayi mixing da asalin red lips d'inshi na nan, murjewa da kyau kam ya ninka na da sbd kulawar da yake samu daga qalbeenshi hakan ke sa su fad'a akan 'yan matan dake binshi.

Little na nan tana karatunta yayinda Abba ya sa su nabeel makarantansu class d'insu d'aya inda suka kasance kaman wasu triplet gasu ba laifi Allah ya basu ilimi, Abul de har yanzu ba abinda yakeyi daga bacci se kallo a sabuwar system d'inshi da Abba ya aiko mishi don har yanzu basu dawo ba, kuma yaki fad'a musu ko aikin idon dada anyi nasara ko ba'a yi ba.

Tafe take cikin sauri sbd makara da tayi ta san zuwa yanzu babynta ya dawo be cika rigata dawowa ba itama ta fi so ta ringa rigashin sbd shirya wasu abubuwan kan ya dawo amma yau gashi exams ya d'an Chaza mata kai bata fito da wuri ba har lokaci ya wuce sossai ga go slow da ta gamu da shi a hanya.

A hanzarce tayi horn gateman ya bud'e mata da mamaki take kallon tsakar gidan ganin ba motanshi a parking space time ta kalla tuni ya kamata ace ya tashi daga office da mamaki ta sauka ta rufe motanta ta shige cikin gidan a parlor ta samu little da gudu tazo tayi mata oyoyo rungume ta tayi tana cewa "sannu pretty yau ba karatun yamma ke kad'ai a gidan" murmushi little tayi tace "kin kira malam d'in kinji ya jikinshi mommy?" Khairi tace "wallahi ban samu kiranshi ba kinga bari nayi wanka na ci abinci se na kirashi" little tace "Ohk mommy se kin fito zan baki labarin abunda duk ya faru a school" khairi na murmushi ta haura sama har tayi wanka

ta shirya cikin riga armless wadda ko cibinta be kai ba yellow da jeans blue ta sauko musharraf be dawo ba.

Abun ya matukar d'aure mata Kai ta kira kusan sau biyar kan ta gama Shiri wayanshi switch off, zama tayi tana jin hiran little ba tare da tana fahimta ba ko abinci bata yi niyyan ci ba, haka suka zauna har magrib kowa ya mike sukaje sukayi sallah a d'aki ta zauna tayi karatunta har lokacin isha tayi adu'o'inta tare da kiran layin shi ya shiga ba'a d'aga ba, sallah tayi ta idar tare da saukowa ta leka d'akin little taga tana sallah ta dawo parlor ta zauna kenan taji an turo kofa.

Da sauri ta mike ganin shine tace "sannu da dawowa" tare da karasawa tayi hugging d'inshi shima rungumeta yayi se yaga tayi saurin janyewa yace "sorry baki ganni ba, ba kuma ki jini ba wallahi munje wani office dinner ne da ma'aikatanmu a gidan wani friend dinmu and my phone was slipped from my hand ya dena yi kwata kwata, se Ina dawowan nan na biya na sayi wata".

Ba tare da ta yarda ba tace "Ohk" tare da kar'ban brief case d'inshi ta haura sama ta barshi da 'yarshi tana welcoming d'inshi, da ido ya bi bayanta se yaga kamar bata yarda da abinda yace ba haka ya haura de bayan ya had'a little da chocolates da ya saya mata a hanya, a bakin toilet ya ganta tana share hannunta da karamin towel ba tare da ta kalleshi ba tace "ruwa na toilet" a d'an dame yace "wai qalbee me ya faru ne? Look am sorry for not informing yhu shima kuma with reason am sorry plz".

Murmushi kawai ta mishi ya shige bayin ba tare da ya yarda ta aminta dashi ba, yana shiga ta ga wayanshi da ya ajiye a kan dressing mirror yayi haske, haka kawai ta ji tana son gani ta mike taje ta danna fuskan "I'm very sure zuwa yanzu ka isa gida, can I call yhu plz baby? am missing you" jiri ne taji yana neman kada ita ta sauri ta dafa jikin mirror ta zauna tana jin wani tension na building cikin kanta da kirjinta tashin hankali kenan shi yasa ya jima? Dalilin kenan da ta ji yana kamshin turaren da ba nashi ba?.

Kuka ta saka sossai, wani irin bala'e'en kishi ne ke cinta bata ta'ba zaton tana da kishi haka ba se yau tashin hankali mijinta ya fara dare a waje sbd wata? Ta kai five minutes tana kuka kan taji motsin fitowanshi da sauri ta mike ta kwanta akan gado tare da juya ma kofan toilet baya tana ci gaba da hawaye, kallon bayanta yayi na mintuna kan ya sauke ajiyar zuciya ba haka ta saba mishi ba ya kamata tazo ta tare shi ta shafa mishi mai ta taimaka mishi ya sa kaya amma tana kwance.

Shafa mai yayi ya sa kayan baccinshi cotton trouser da riganshi me igiyar d'aurewa kawai daga tsakiya gabad'aya gaban kirjinshi a bud'e yake  kara feshe turarе yayi.

gadon ya hau tare da juyota a take hankalinshi yayi matukar tashi ganin hawaye na gangara a idonta a rud'e yace "qalbee me ya faru? Me yasa ki kuka?" Se kuwa ta fashe mishi da kuka me sauti rungume ta yayi a kirjinshi yana shafa mata baya har tayi ta koshi idonshi a runtse Allah kad'ai ya san me yake ji, ganin kukan yaki lafawa ne yasa shi d'agota tare da had'e bakinsu special lallashi ya dinga mata har seda ya ga kukan ya d'auke chak dukda kokarin tura shi da

take yaki sakinta sam.

Yana saketa ta mike da sauri tayi bayi ta dinga tofar da nyau ranshi ya fara 'baci da wannan sabon d'abi'a nata shine ze yi kissing d'inta ta tofar da nyau? Kwanciya yayi ya rufe ido da nufin fita harkanta tunda haka ta za'ba, yana ji ta dawo ta kwanta a chan karshen gadon haka suka kwanta ta jima sossai tana juye juye shima yana kwance Shiru be tanka mata ba dukda ba bacci ya yi ba, yana ji ta mike da fita da alamu duba little taje yi, Ai ko hakan ne seda ta tattabatar ta kwanta kan ta hauro ta chanza zuwa kayan bacci ta koma ta kwanta Shiru.

Har misalin shabiyu da rabi ba wadda ya iya bacci a cikinsu don basu saba irin wannan fad'an ba tunda suka shirya basu ta'ba 'batawa sun kwana ba'a jikin juna ba, ganin kaman yayi bacci yasa ta mike ta zauna ta had'a kai da gwiwa tana me ci gaba da kukanta sossai yayi kokarin share ta amma sam ya kasa hakan yasa shima mikewa yayi ya zauna cikin taushin murya yace "ummulkhair" d'ago kai tayi dukda baya kallon fuskanta sbd kashe wuta da tayi tun kan ta kwanta amma ya tabbatar kuka take yi.

"Gayamin plz me na miki da zafi haka? Ko kina tunanin zan fara miki karya ne a zamantakewar mu abunda ban ta'ba miki ba?" Shiru tayi tana shesheka kaman baza tayi magana ba kuma se tace "yhu never lied to me but I didn't believe what you said earlier, kana smelling different perfume ba naka ba, naji hakan ne a sanda nayi hugging d'inki shigowarka and".

Se ta mike ta je gaban mirror ta d'uko sabuwar wayan nan ko samun ya duba da kyau be yi ba, ta kunna hasken har yanzu sakon na nan ta kawo mishi ta kunna mishi fuskan wayan kar'ba yayi ya karanta da sauri ya mike tsugunne akan gadon tare da sa hannu ya kunna hasken d'akin yadda ze kalleta da kyau yace "I swear to God ban san wacece wannan ba, kin san ba yadda zanyi in miki rantsuwa akan karya ko to wallahi ban santa ba sannan kuma turaren da kika jin nan.

Nuruddeen ne ya saya yace inji kamshin naki shine ya fesa min a kirji ban bari ya karasa ba na ture hannunshi wallahi ba abinda kike zato bane haba ummulkhair kin 'bata min rai banyi zina Ina saurayi ba banyi bayan abunda surrayyah ta min ba, banyi bayan fitowana prison ba se yanzu da nake tare da masoyiyata, abin alfahari na, uwar 'ya'ya na?" Shiru tayi kanta kasa yace "In baki yarda ba lemme call him tunda ba mata yake dashi ba" wayan ya bud'e ya fara dannawa da sauri ta rike hannunshi In low tune tace "am sorry".

Rungume ta yayi suka sauke ajiyar zuciya a tare cikin kunnenta yace "kar ki kara plz bana so, bana son zargi ya dinga shiga tsakanin mu sbd yana 'bata aure, kin kuwa san yadda na tsani zina to tun daga randa na kalli mahaifina akan......" da sauri ta had'e bakinsu bata so sam taji zancen sbd duk waenda sukayin suna tare da mahallicinsu bata so sam ya dinga aibanta mahaifinshi bata yarda In har a gabanta ne.

Seda suka farantawa juna sukayi wanka kan suka dawo suka kwanta a manne da juna kaman zasu had'iye juna, washegari da safe aka sanar da su haihuwan nurriyyah inda ta samu d'a

namiji aiko khairi tace zasu zo tunda ranar Monday zata gama last papper d'inta na first semester level 200, sati uku ne hutun Bayan sun gama wayan ne taga kiran dada.

'Dagawa tayi suka gaisa take tambayarta Abba tace ya fita da turanci da mamaki khairi tace "dada kaman turanci naji kinyi?" Dada tayi saurin cewa "nop hausa ne, na san Monday zaki gama paper in ba matsala ki roki mijinki zamu tafi taraba Abbanku ya matsa akan na komawa mahaifina watakil yanzu gaskiya tayi halinta" Khairi tace "Toh zan gwada tambayarshi Allah ya sa ya amince, da su nasreen?" Tace "a'a kin san tsarin makarantanku ba d'aya ba zamu dawo Wednesday mubi jirgin Adamawa se mu karasa jalingo a mota".

Khairi tace "sede tafiyanmu inaga zeyi daban daban sbd nuriyyah ta haihu yau da safe zamu tafi gomben watakil Tuesday" dada tace "masha Allah, Allah ya raya ya d'ayyaba, me ta samu?" Khairi tace "namiji" dada tace "d'ayyib zan kira hajiya fatima In mata barka, zan kira me jegon ma, muma wucewa be kama mu ba zamu shigo gomben kafin suna in shaa Allahu se mu wuce gabad'aya tare" sallama sukayi.

Musharraf dake tsaye a gefenta yana had'a tea duk wayan da sukayin a kunnenshi sbd a speaker wayan yake yace "gaskiya ya kamata ku waiwayi gida haka shekaru dayawa se muje tare zan d'auki leave na two weeks kinga hutun su little ma three weeks ne tafiyan yazo a daidai" Kai ta gyad'a duk fargabanta maganan mahaifin dada ne na ze tsine mata duk randa ya kuma ganinta kofan gidanshi da kuma tuna irin rantsuwar da mahaifinta yayi kan fitowarsu Allah sarki Allah ya ji kanka Abba, ko ya rayuwan su hauwa? Ta'be baki tayi suka ci gaba da abunda sukeyi.

Sunday suka had'e kayansu tsab trolley uku kowa da nashi Monday tayi last paper d'inta tuesday suka kama hanyar gombe a mota sukayi tafiyan wannan karon duk khairi ta galabaita ko don bata saba tafiya me nisa irin haka a mota bane se Allah, sun samu tarba sossai daga wurin momma gidan a cike da 'yan barka da shike tun kan nuriyyahn ta haihu ta dawo gidan da zama sbd matsalolin da cikin yayi ta bata.

Khairi kam kaman ta had'iye yaron, suna zaune da musharraf suna ta kallon yaron gwanin sha'awa da sauri taga ya mike ya fita chan kuma ya dawo ranshi ba daad'i kwata kwata don fuskan nan a had'e yana zama Anty rabi da Hajiya zulai tare da Afreen da kuma sufyan suka shigo, uncle Ahmad da uncle nasir biye da su, duk zama sukayi khairi ta zame kasa ta gaida su Haka musharraf amma shi Uncle's din shi kad'ai ya gaisar ya koma yayi zamanshi tare da gaidasu Anty rabi a haka, ta'be baki tayi ba tare da ta amsa ba ta mike ta zo ta kar'bi yaron, tare da satan kallon su Uncle Ahmad dake gaisawa da su momma tace tana kallon hajiya zulai "kinga gara na kar'beshi kar ta hallakashi sbd bakin ciki abinka da juya" hajiya zulai tace "Ai ko de kinga irin abinda ake gayawa su Alhj suka ki ji gashi ko wacce da akayi aurensu tare na shirin juyewa yau ko gobe amma banda ita da ko alamun abun arzikin babu ace mutum be sonka tsakani da Allah dukiyarka yake bukata aki yarda, banza juya" tassssss suka ji saukar mari, a razane kowa ya waigo zuwa inda suke. To fah

Alhamdulillah thanks for the prayer 🙏

#vote
#share
#comment

'Yar mutan Adamawa

🎗🎗🎗🎗🎗

IGIYAR RAYUWA😭

🎗🎗🎗🎗🎗

💫ANNUR WRITERS ASSOCIATION
(Home of peace, honor, charity and super writers)

Story and written by: fateemah Muhammad Gurin

Wattpad:- Gureenjo6763

'Yar mutan Adamawa

Las Las

Page➡️1️⃣0️⃣0️⃣▶️🔚🔚🔚
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

Gabad'aya parlorn mikewa sukayi ganin yadda yake 'bari kamar mazari dama ranshi a 'bace yake ga maganganun hajiya zulai da Anty Rabi'ah yau ba don matar uncle Ahmad bace, ba don yana ganin girman uncle Ahmad fiye da sauran uncles dinshi ba, ba don ba tarbiyar momma ba kenan da ba abinda ze hanashi yiwa matar dukan mutuwa, shiyasa ya sauke hannunshin akan d'anta da dama shine silar 'bacin ranshi tun farko, uncle nasir ne yace "musharraf wai lafiyanka kuwa?" Momma tace "me ya maka haka?" Hararan da sufyan ke mishi ne yake kara tunzura shi hakan yasa shi had'ashi da gini ya shakeshi da sauri khairi ta dafa hannunshi ganin yadda hajiya zulai ke ihun ze kashe mata d'a.

Momma ta karaso ta d'aga hannu da niyyar sauke mishi mari da hanzari khairi ta shiga marin ya sauka a fuskanta har seda ta zube a kasa tsabar karfin marin, ido ta runtse yanzu da haka marin ze sauka a fuskanshi inaa ta san komai musharraf yayi akwai dalili tana kyautata zaton ba Haka kawai ze hau dukan shi ba, da azama musharraf ya sake Sufyan yana d'agota kallon cikin idanunshi da yayi ja tayi ta runtse ido se hawaye da kirjinshi ya had'ata yana kallon momma da ta tsaya kaman mutum mutumi haka su uncle nasir ma karfin halin khairi suke jinjinawa.

A hankali ya fara magana cikin rawar murya ya bada labarin abunda aka turamishi ran aurenshi wadda yayi sanadiyar kwanciyanshi asibiti ya kara da irin zaman da yayi da khairi kan ya zo ya gane karya ne da alqawarin da ya mata ya d'aura da "na shafe wata shidda chur Ina neman me wannan numbern, har experts a harkan tracking fiye da mutum hud'u na biya amma ba'ayi nasara ba se yau a d'azu d'aya ya kira ni ya bani full details na wadda ya had'a hoton kuma sunje sun sameshi da police inda ya amsa fault d'inshi ya kuma bada details na waenda suka sa shi, and that turns out that sufyan ne ya biyashi don aikata hakan and wanchan munafukan ya nuna Afreen ita ta zo har cikin gidan nan ta d'ad'auki qalbee hotuna daban daban" yana shafa bayan khairi yace "am sorry qalbee na kasa cika alkawarinki sbd munanan kalaman da iyayensu suke jefanki dashi" kallon su Hajiya zulai yayi yace "and yhu this is my first and last warning Wallahi wallahi mata ta kara zagarmin mata se nayi mata abunda bata ta'ba tsamanni ba, ku kuka hallici juyan? Ko ku kuka h......" "musharraf" momma ta kira shi In a whisper.

Shiru yayi tare da jan hannun matarshi suka fice daga parlorn, basu karasa fita ba suka ji saukar mari har kusan kala hud'u, uncle nasir ne yake saukewa sufyan duk sanyinshi seda ranshi ya 'baci yau haka ya rufe Afreen da duka wasu irin yara ne su, seda uncle Ahmad ya gama dawowa daga suman tsayen da yayi kan ya kalli Hajiya zulai yace "ki tafi gidanku se na neme ki" waro ido sufyan yayi tare da zubewa a wurin yace "kayi hakuri dad wallahi bazan kara

ba, karka hukunta mom akan abinda ba ita ta aikata ba na tuba" harararanshi uncle Ahmad yayi kan ya juya ya fice momma de bata ce komai ba amma kallo d'aya ka mata zaka san ranta a 'bace yake haka su Amrah da mai jego ma se harara suke sakewa su afreen din, wato uncle Ahmad ya san hukunta mahaifiyar sufyan ne kad'ai ze sa shi ladabta yayi nadamar gaskiya sanin yadda yake kaunar mahaifiyar tashi, ita kuwa cikin kuka da ihu ta fice daga gidan, hajiya rabi'ah ta rufa mata baya Afreen kuwa Uncle nasir yace da ita ze tafi zata ci me unguwan garinsu a gidanshi cikin sacewar gwiwa sufyan ya mike ya fice, nan momma ta kira bappa ta fad'a mishi duk abunda ya faru ta kuma tabbatar mata da hakan, inda bappa yayi alkawarin sa taheer yaje har gidanta ya ci mata mutunci kuma shima ze kirata haka diddinsu ma, hakuri ya dinga bata har taji kunya.

Bayan ta kashe suka zauna tattaunawan da su Amrah, a bakin gado ya ajiyeta shima ya zauna hannunshi na kan yatsun momma da suka fito a kumatunta cikin kasa da murya da tsantar damuwa yace "am so sorry qalbee, me yasa kika shiga? Dan Allah karki sake da na gani da ban bari ba am sorry" murmushi khairi tayi tana kifa kanta akan kirjinshi tace "mind not hayatee, bazan iya ganin wani abu ya ta'ba min lafiyanka ba da rai na da lafiyata In bari" zagaye hannunshi yayi zuwa cikinta yace "Ina sonki" murmushi me sauti tayi tace "same here hayatee".

Anan suka shantake, kwana uku da zuwansu su dada suka sauko Gombe ana washegari suna kenan, tun washegarin barinsu Abujan suka diro, musharraf da khairi ne suka je taransu mota biyu sukayi amma gidan inna zasu sauka shi kuma Abba a hotel ze kwana tunda kwana biyu kawai zasuyi, a natse matafiyan suka fara fitowa Arrivals janye da akwatunansu khairi kam kaikaya ido tayi tana tunanin idon ya fara deceiving d'inta amma abu guda kaman na farko ta gani dafa musharraf tayi tace "kana ganin abunda nake gani kuwa?" Murmushi yayi yace "surprise ni na hana a fad'amiki daidai idonki ke gani".

Da gudu khairi ta karasa wurin dada da take shirye cikin atampha super wax da yaji kud'i d'inkin riga da zani ta d'aura d'ankwalinta me kyau ta yane kanta da orange kashka babba idonta sanye da medicated glass fari hannunta riqe da designer hand bag kai ko agogonta abun kallo ne, sossai tayi kyau da gudu khairi ta fad'a jikinta dada ta murmushi ta d'agota "me haka khairiyyah? Look everybody here is eying you se kace ba matar aure ba" kuka khairi ta saka tana kallon idon dada tace "yanzu dada kina kallo na?" Dada tace "kwarai kuwa Godiya ta tabbata ga Allah yau gashi Ina ganin jarumar 'yata" sake rungumeta khairi tayi tana shesheka Abul yace "oh Abba kaga d'aughter d'inka kaman wata baby se afkin shagwa'ba" Abba yace "kyale min daughter tayi son ranta kaima Ai same reaction ka nuna sadda kaga maman naku" gwalo khairi ta mishi tana cewa "sannu da zuwa Abba" yana murmushi ya amsa a lokacin musharraf ya karaso ya duka har kasa ya gaidasu suka amsa a sake kan suka dunguma mota khairi de duk motsin dada a kan idonta tana mamakin ikon Allah da ta gaji da jin yadda dadan ke jefa turanci d'ai d'ai a cikin magana tace "dada dan Allah makaranta kika shiga?" Dariya Abba yayi yace "Eh tayi school na 5months" Khairi de se daad'i takeji har suka isa gidan inna, kowa ya shigo mata sannu da zuwa se yayi mamakin ganinta inna kaman zata maida ta ciki don murna amma be hana In dadan ta jefa turanci cikin magananta innan ta tsigale boko ba.

Washegari dada a gidan momma suka yini da su hajiya ruqayyah suna shan hira sossai momma tayi farin cikin ganin chanjin da ta samu sossai, gidan ya cika da 'yan suna yaro yaci sunan Abbansu musharraf mahmoud zasu na kiranshi irfan sossai kuwa su musharraf sukaji daad'in sunan inda kayanshi da na khairi kawai abun kallo ne bare a zo na momma se na sauran dangi yaro ya sha gata, Hajiya Rabi'ah da Hajiya zulai ko lekowa basuyi ba.

Washegari da safe da misalin karfe shidda su dada suka zo suka d'auki su khairi dayake mota biyu zasuyi tafiyar da ita dukda Abba ya so jirgi amma ba'a cika samun jirgi zuwa jalingo ba se kawai suka hakura zasu bi mota da de su bi jirgin zuwa yola su kuma bi mota zuwa jalingo, manyan prado ne guda biyu da suka ji kud'i fari da baki d'aya Abul, khairi, musharraf da little bakin kenan, farin kuma dada, Abba nabeel da nabeela dayake tsoffin drivers da suka san kan hanya suka samu nan da nan suka fara cin taya.

Awa shidda me kyau ya kawo su jalingo dukda sun tsaya a hanya yafi sau abunda yafi don khairi ta galabaita sossai tayi ta amai duk hankalin musharraf a tashe gashi ta kasa cin komai suna isa Abba ya cewa drivern su ya kaisu unguwa da za'a samu hotels masu kyau su samu su huta kan su nemi asibitin da za'a Kai khairi don taji jiki, magami ya kaisu suka za'bi hotel suka shiga suka biya kud'in inda har drivers d'in suka kama musu d'aki d'aya su biyu, ganin yadda khairi take lafe a jikin mijinta ko tsayuwa ta kasa yasa Abba kama musu d'aki su biyu su ma, shi shi kad'ai, Abul da nabeel suma su kad'ai, se little, nabeela da dada.

Wanka ya taimaka mata tayi duk shima ya zama wani iri kaman shine marar lafiyan ordern abinci ya bayar seda ya tambayeta me zata ci tace pepper soup d'in kayan ciki da black tea me zafi sossai haka aka kawo mata da kanshi yayi ta bata amma abun takaici tana gama ci ta kwararar, har hawayen tausayinta musharraf yayi da kyar ya samu bacci ya d'auketa yayi wanka ya shirya shima yazo ya kwanta don basu da bashin sallah, se la'asar khairi ta tashin wadda tashintan ya jawo tashinshi wanka suka sakeyi sbd zafin da akeyi suka yi sallah kan ya taimaka mata ta shirya tana ya complain ciwon kai, fita sukayi a waya ya sanar da Abba zasu asibiti driver d'aya ya d'aukesu se FMC jalingo khairi de se kallon jalingo takeyi cike da kewa, da suka zo daidai junction d'in asibitin kuwa se taji kuka na zuwa mata hango police division inda aka tsare Abbanta da kyar ta had'iye kukan.

Babu wani 'bata lokaci suka samu ganin Doctor wacce macece gwaji tayiwa khairin cikin abunda be fi awa ba tayi musu congrats da samun juna biyun khairi sossai sukayi murna khairi harda kwalla tuno abunda aka gama gaya mata satin nan, da farin ciki suka dawo musharraf kam ya kasa shiru seda ya gayawa su dada suka dinga ma cikin da uwan Adu'a a kunyace ta gudu nasu d'akin.

Kulawa sossai musharraf ya ci gaba da bata ninkin a kan na da bini bini me ta ke so, me zata ci sede tayi murmushi, washegari misalin karfe tara sukayi wanka suka fito se unguwan sarki suna shigowa memory din rayuwansu na kara taryo kanshi shekara goma sha bakwai a unguwan nan abunda yake musu zafi yadda mutanen cikinta suka kasa gasgata abinda zasu iya da

wadda baza su iya ba, a kofan gidan su ummu sulaimi suka parker gidan an gyara shi gwanin kyau ya dawo na zamani ba kaman na da me kyauren buhu ba yanzu harda karamin get brown, gidansu ta kai idonta ga mamakin ta yana nan yadda suka tafi suka bari se bala'e'iyar kura da zaka hango daga inda kake duk yana ya cika ko Ina zanan kuma ya ru'be.

Sauka sukayi dada da khairi suka isa kofan gidan baban sukayi knocking wata mata ce ta zo ta bud'e musu da alamu 'yar aiki ce don riganta daban zaninta daban se d'ankwali daban murmushi tayi musu kan tace "bismillahnku ku shigo" shiga sukayi ta isar da su har madaidaicin parlorn gidan umma dake zaune rike da wata yarinya 'yar shekara d'aya da kad'an ne ta mike da mamaki tace "wa nake gani haka? Kaman khairi da dada???" Murmushi suka mata alamun tabbatarwa da sauri ta ajiye yarinyar tazo ta rungume dada tare da fashewa da kuka se tatta'bata take tana kallonta da kyau, ihun kiran "sulaimi" da takeyi yasa khairi maida hankali don ganin ta inda zata fito, aiko se gata sanye da leshi green riga da skirt ta kafa d'auri da mamaki ta tsaya Kallon khairi kan ta karaso da gudu suka rungume juna bayan gama farin cikin ganin juna dada tace "da mutane fah muke suna waje" umma tace "su shigo mana sulaimi kuje ku shigo da su" fita sukayi ba jimawa suka dawo da su Abba Bayan sun zazzauna nabeel da nabeel kam suna makale da sulaimi ganin umma yasa su sakinta suka je suka rungumeta waya ta d'aga ta kira Baba tace "yayi maza ya dawo suna da manyan baki" Ai ko ba jimawa sukaji tsayuwan machine a kofan gidan se gashi ya shigo ya mikawa su Abba hannu suka gaisa seda ya je kan Abul tukuna ya gane su waye suka zo farin ciki sossai ya bayyana a fuskanshi yana hangen irin motocin da ya gani a kofar gidan da alamu da shi suka zo.

Introducing su Abba dada tayi musu inda aka kara gaisawa Baba ya d'aura da "Ai dayake Allah ba azzalumin bawansa ba, baku jima da tafiya ba gaskiya tayi halinta, wata biyu da barinku garin nan wasu marasa imani kartai suka shiga har gidan su maman hauwa suka ma hauwan muguwar fyad'e se anan ne suka san me asalin fyad'en don yanzu maganan da nake mukun nan gabanta ya ru'be ance HIV da cancer take dashi ita kuma uwar an wayi gari aka ganta a shanye kafanta da hannunta kaman na jarirai tsabar shanyewa komai na jikinta a karkace wasu sunce garsa ne ya buge ta don ko magana da kyau bata iyawa, da bakinsu suka dinga tona asirin kansu".

Abba yace "Allah kenan" Abul yace "baba gidanmu kuma ba waenda suka shiga ne se naga kaman har kwad'on da muka bari ne a jiki" Baba yace "hmmm gida kam ya gagari kowa zama duk waenda suka shiga basa kwana d'aya suke guduwa suce wai aljannu ne a gidan ba abinda ba'a mishi ba amma an kasa zama" kallon gidan su baban kawai khairi keyi kaman baza tayi magana ba se kuma tace "umma babyn waye hannunki kyakyawa haka?" Umma Tace "'yar sulaimi ce sunanta ummulkhair, tafiyan ku da wata d'aya Allah ya fitar mata da miji tayi aure na rufin asiri tana zaune a millennium suit" yadda unman tayi pronouncing seda ya sa su dariya sulaimi ce ta gyara har suka iya fahimta sossai khairi taji daad'in takwaran da aka mata, inda umma ta ci gaba tana hararan Sulaimin "yanzu ma yini ta zo mana shine kuka same mu nan, kinga gidan nan duk mijinta yayi wahalan gyare mana, ya saya wa babanku babur ya chanza mishi Sana'a Alhamdulillah kawai".

Sun d'an jima suna hira don har abinci su khairi da sulaimi sukayi  aka ci aka koshi, dukda khairi bata jin daad'i sossai ga tashin zuciya ko abincin bata iya ta ci na kirki ba, kan sukayi haraman tafiya don a yau d'in suke son shiga Baaba gaasa, kan su tafi dada tace "kuzo muje mu duba jikin su maman hauwa" baki gaba khairi ta ke tafiya ita bata ga dalilin shiga musu ba amma ba yadda ta iya haka ta karasa suka shiga musharraf na mata gwalo a fakaice hakan yasa ta murmushi tare da jefa mishi hararan wasa.

Suna ganinsu se kuma tausayinsu ya kamasu ganin yadda suka koma abun tausayi rayuwa ta musu d'aurin kazan kuku duk sun fice hayyacinsu gafara suka dinga rokansu duk suka amsa da sun yafe, khairi ce ta fara fitowa musharraf ya bi bayanta a jikin mota suka tsaya yana kallonta yace "ya akayi kikayi saurin yafemusu qalbee?" Murmushi tayi kan tace "na yafe musu ne sbd sune silar had'uwata da hasken rayuwata, muradin raina, taurarona, rayuwana gabad'aya da numfashina" juya ido yayi yana murmushin shi me kashe 'yan mata yace "tab amma wannan tauraro sa'a ne dashi duk wannan matsayi shi kad'ai?" Itama tana murmushi tace "Ai ya fi haka hayatee ya zarta duk inda kake tsammani I love him to the moon and back, i will love him to the square of infinity, I will definitely be nothing without him cos he's my oxygen" wani irin murmushi musharraf ke yi da duk wadda ya gani ze san irin shaukin da yake ciki, dafe saitin zuciyanshi yayi yace "ashhh waennan kalaman sun soke ni dayawa baby, ki bari haka kar na fad'i na rasa me tallafe ni" far tayi da ido kan tace "aka gayamaka zan iya bari ka fad'i har kasa ne? Inaaa bazan iya barin kwaina zuwa kasa ba don na san in ya fad'i rayuwata tazo karshe" kad'a harshenshi yayi kan yace "Ina sonki dayawa" ganin su dada sun fito yasa ta fasa bashi amsa.

Sama sama suka shiga sauran makwabtan kan suka tafi da alqawarin in sun dawo yini guda zatayi a gidan sulaimi su sha hiran bayan rabuwa, duk abinda sukayin nan bata ga idi ba runfar sun ma babu a wurin kuma bata tambaya ba, kallon hanya kawai sukeyi suna hira kasa kasa suna ganin yadda hanyar duk ta lalace In ba mota me kyau irin nasu ba jiggatan da mutum ze yi Allah ne kad'ai ya sani, fulanin da ke kiwo da masu tallan nono da suke wucewa jefi jefi ba karamin burge musharraf suke ba be ta'ba ganin irin hakan dayawa ba don na gombe basu cika yawa haka ba kuma al'adunsu da shigensu daban daban kasancewar fulatancin ma kowa da irin nashi.

Dada ce ta dinga kwatance har kofan gidansu sauka tayi tana kallon yadda gidan yayi mugun lalacewa da fargaba fal ranta ta shiga cikin gidan, da sallama kallo d'aya ta mishi ta san ba mace ganin yadda duk gidan tarkace ne up site down, da sauri ta karasa d'akin babanta jin ana tari daga ciki, kwance yake kashir'ban kaman macecce kallo d'aya ya mata ya fashe da kuka yana mika mata hannu da gudu ta karasa ta rike bata damu da kazantar da yake ciki ba, ta d'agoshi ya zauna yana zama ya fara rokan yafiyanta akan hukunci da ya yanke akanta ba tare da bincike ba, bakinshi ta rufe tana hawaye tace "Ina umma?" Yace "ta rigamu gidan gaskiya bayan ciwon da tayi fama da shi na shekaru uku ba ta iya ko mikewa zaune, ta ban labarin duk halin da ta saka ki a ciki ki yafemin dan Allah safiyya" mikewa tayi ta d'ibi ruwa a rijiya ta mishi wanka tsab bata ko damu da su Abba dake zaune a mota ba seda ta kimtsa shi ta fito suka shiga tare ta nuna wa Abba shi a matsayin mijinta na yanzu a hankali ta bashi labarin rayuwanta gabad'aya inda ta tambayeshi yayyunta yana kuka yace "anyi wani cikowa da ya

hallaka su gabad'aya cikin dare nima lokacin bana nan na tafi kiwo shine sanadiyar kwanciya na, har 'yan gidan su umar gabad'aya ba wadda ya tsira" Abba ne ya nuna be ga anfanin zaman su ba su d'aukeshi su tafi dashi Inda musharraf ya bada goyon baya da kyar ya yarda suka d'aukeshi suka tafi basu yada zango ba se cikin jalingo kwana kawai sukayi washegari suka wuce yola sukayi komai na jirgi don tafiya da Abba dayake national ne kuma Abba ya san mutane cikin kankanin lokaci aka gama komai suka wuce Abuja se ta waya suka sallami su sulaimi akan zasu sake zuwa In shaa Allahu tunda zumunci ya kullu.

Suna isa Abuja Suka wuce da baba asibiti, khairi kam seda aka mata Karin ruwa sbd stress da yayi mata yawa ta huta sossai kan aka sallameta baba ma an bashi kulawa sossai cinkin lokaci kankani ya warware ashe ba warwarewan lafiya bane na kiran Allah ne kullum se ya roki yafiyan dada kan wata ranar juma'a ya cika wadda hakan yasa 'yan gombe kusan duk suka zo mata ta'aziyya tayi kuka sossai na rashin mahaifinta gashi yanzu ko 'yan uwa bata da.

Bayan shekaru goma

"Lastly Dr. Ummulkhair Umar Farouq" tafi wurin ya d'auka raf raf raf a hankali ta mike sanye da wani arniyar leshi da yaji kud'i blue d'inkin doguwar riga ta d'aura rigan grad dinta a kai maroon color akan kafaffen d'ankwalinta ta d'aura hulan mayafinta zagaye da wuyanta wow da kyar na gane khairi ce ba don an kira sunanta ba se na karyata, tayi wani irin cika ta kara fari sossai, murmushin da takeyi ya fito da hakirin makkanta cikin jerin fararen hakwaranta, wuwulla ido tayi tayi da kyar ta hango hayateen ta wadda shine gatanta da komai nata shi ya tsaya mata wurin cika burinta na karatu me tsananin zurfi har ya kai ga yau ta kamalla phd d'inta.

Hannunshi d'aya ya d'aga mata murmushi kwance a fuskanshi yayi wani irin kyau ya kara girma ya ajiye gemu me tsananin kyau yadda yayi style dinshi ma kawai abun kallo ne, wata kyakyawar yarinya 'yar shekara d'aya da wata takwas ce rike a d'aya hannunshi se zizzillewa take yana rike ta, murmushi tayi tana girgiza kai rigiman Arwa se ita.

Cikin karramawa bayan dogon yabon da aka yi mata aka bata kwalinta a hannu wadda ya sata zub da hawaye, komawa wurin zamanta tayi tana share hawayen fuskanta, bayan an gama taro suka fito se dube dube take ta inda zata hango family d'inta chan kuwa ta hangi Little na zuwa wadda yanzu ta koma Adda zarah don taki yarda da Little kuma In ba babanta ba rike da hannun wasu kyawawan yara biyu waenda zasuyi shekara goma goma se wata 'yar shekara biyar bayansu tana tafiya bakin nan a zum'bure da alamu laifi aka mata.

Juya kai tayi se taga dada, momma, Amrah da tayi aure da yaranta uku, se miemie ita kuma yaranta hud'u se Abul da yanzu ake shirin yi mishi aure wadda ya zama doctor Abulkhairi umar faruq gwararren likitan kashi, se Afreen itama babynta d'aya da Nasreen me fama da tsohon ciki, dada ta kara haihuwan yara maza biyu Abdulhaleem da Abdulrahim ba 'yan biyu bane. duk a tsaye wuri d'aya hannun da taji cikin nata da wannan fitinannen turaren nashi ya sanar da ita

waye ne murmushi tayi tana kallonshi sadda se ji sukayi ana zuba musu ruwan pics, zarah tace "Kai mommy and paapi kunga yadda kukayi kyau ga little arwa se murmushi take zubawa".

Hararanta khairi tayi ta kuma harari yaranta na fari da suka kasance 'yan biyu suka kuma ci sunan Abbanta da Abban su musharraf ake kiransu 'mussadiq' da 'mu'allim' tace "waye ya ta'bamin 'ya?" Musu suka fara wannan na ba ruwana wanchan na ba ruwana babyn me suna Nihal wacce taci sunan dada tace "mommy ya mussadiq ne ya mareni don na kira sunanki da karfi ana event" kallonshi tayi da sauri yace "am sorry mommy" girgiza kai tayi ya san bata hakura ba wuyan su koma gida ne kawai.

Suna 'yar hira suka karasa wurin su momma se mamakin zarah da ta koma buduruwa 'yar sixteen nake wacce ke dab da fara jarabawar gama secondary da su nabeel amma yanzu basa nan suna jalingo wurin umman su sulaimi, sossai su Abba suka taya ta murna inda suna komawa gida taga surprise walima daga mijinta inda su Anty farha suka zo kusan gabad'ayansu yanzu ta haihu har uku ma, su Asma'u duk anyi aure da 'ya'ya taji daad'in ganinsu sossai inda aka ci aka sha a ranar suka juya kowacce ta koma inda take aure dukda rabinsu anan Abuja suke dama khairi na lecturing a Base university kuma anan ta yi phd d'inta anan kuma aka kara mata matsayi ta ci gaba da kayanta cikin farin ciki da jin daad'in rayuwa, sufyan ya jima da nadama inda ya roki yafiyarsu suka kuma yafe mishi ya kuma auri Afreen 'ya'yansu uku, Hajiya zulai da hajiya Rabi'ah duk sunyi nadaman abunda suka dinga yiwa khairi sbd yadda take kyautata musu.

Inda dadda da Mamaji da kuma bappa duk suka riga gidan gaskiya har inna amma duk mutuwan lokaci daban daban diddi ce kad'ai ta saura a dole ta dawo cikin gombe tare da momma a sabuwar gidanta da musharraf ya sauya mata tunda ba yadda basuyi ba ta sake aure taki kuma ba komai ya haddasa hakan ba se rashin samun jin daad'inta a auren na farko wadda take gani duk haka ne, shiyasa ta za'bi zama da yaranta har sukayi aure abunsu.

hajiya ummulkhair da Alhaji musharraf soyayyarsu na nan se ma abunda yayi gaba don sun yarda da kalman nan na true love never fade, tsohon gidan su khairi ta gina gidan marayu a wurin da niyyar ladan ya kaiwa mahaifinsu inda dada da Abul sukayi rijiyoyi da massallatai duk da niyyar ladan ya kai mishi don har gobe suna jin sonshi suna kuma alhinin mutuwanshi.

Alhamdulillah! Alhamdulillah!! Alhamdulillah!!!

Anan na kawo karshen littafin nan na IGIYAR RAYUWA abunda mukayi kuskure Allah ya yafe mana abunda muka rubuta daidai kuwa Allah ya bamu ladanshi.

Godiya me yawa a gareku:

ANNUR WRITERS ASSOCIATION.

Mu Karu da juna group: ba karya na ji daad'in kasancewa da ku sossai kuma har abada Ina alfarahi da ku na gode kwarai Allah ya bar kauna.

Ban manta da ku ba readers d'ina na queen bee, waenda suka karanta suka kuma nuna sun karanta suka kuma yi comment na gode kwarai da kaunarku.

Sauran masu karantawa without vote, comment or showing Appreciation Allah ya shirya.

Adama Aliyu duk da a karshe kika zo amma na ji daad'in comments dinki sossai 'yar garinmu Allah ya bar kauna.

My Oda half Haneefa Muhammad Gurin godiya dubu ba don ke ba da se kuyi sati uku baku samu update ba, yadda kika matsamin akan typing🙄☹️hmmm shaa I love yhu.

My blood Aisha Muhammad Gurin me karatun sirri Allah kar ya tona asiri🤭😜

Maman khalil🥰
Maman heedaya❤️
Ummu rijaaal🥰
Maman meenat❤️
Zainab Ads🥰
Hauwa Adam(jiddo)❤️
Aisha lawal shahud🥰
Salmerhalee🥰
Saadah sanusi🥰
Salmer🥰
Nagartacollection🥰
Ummu muzammil🥰
Khadija Ads❤️
Ummu Ameer🥰
Hassana S Fagge🥰
Sadiya muhammad🥰
Khadija(queen)🥰
Sadiya tijjani❤️
Maijidda❤️

Waii da ma waenda ban ambata ba duk ina yinku kuma ina sonku Allah ya bar kauna.

Lastly my wattpadians kar ku ce na manta da ku kuna raina na gode kwarai Allah ya bar kauna, big heart for yhu guys❤️❤️❤️❤️

'Yar mutan Adamawa na muku fatan alkhairi.